# Zaɓaɓɓun Littattaffai

Na

Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

*Sihili Na*

**2**

**© Iqra'a Publishing House**

An tsare dukkan haƙƙoƙin wannan littafi. Kada a samar da wani sashi na wannan littafi ta hanyar na'urori ko kuma ta kowace irin hanya daban ba tare da izinin Maɗaba'ar Iqra'a ba.

**NATIONAL LIBRARY OF NIGERIA CATALOGUING-IN-PUBLICATION DATA**

SELECTED writings of Sheikh Othman Bn Fodiyo, volume 2.

1. Muslims – Intellectual life (Hausa) 2. Fodiyo, Sheikh Othman. I. Faru, Mande [compiler]. II. Title.

BP 163.S464 F653 vol.2 2013 297.07

ISBN: 978-978-52418-4-6 (Cased) AACR2

**IQRA'AH PUBLISHING HOUSE** — طبعة دار اقرأ للطباعة والنشر

**Samaru**, Gusau. — **عنوان** : سامرو، غوسو.

**Tel**: +234(0)8026010020 — **هاتف**: +٢٣٤(٠)٨٠٢٦٠١٠٠٢٠

+234(0)7063282525 — +٢٣٤(٠)٧٠٦٣٢٨٢٥٢٥

**Email**: iqragroup99@gmail.com — البريد الإلكتروني

**Website**: www.fodiyobooks.com — الموقع الإلكتروني

**TABBATARWA**

Mu da sunayenmu ke rubuce a ƙasa, mun karanta waɗannan littattafai mun tace su, mun gamsu da fassarar da aka yi. Hakanan kuma mun amince da Maɗaba'ar **Iqra'a** ta buga su domin amfanin Musulunci da jama'ar Musulmi.

1. Dr Sa'adiya Omar,
   Cibiyar Nazarin Hausa, UDUS.
2. Dr. Hamza A. Ainu,
   Cibiyar Nazarin Hausa, UDUS.
3. Malam Ahmad Abdullahi Sokoto,
   Cibiyar Nazarin Hausa, UDUS.
4. Farfesa Sulaiman Musa,
   Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci.
5. Farfesa Atiku Ahmad Dunfawa,
   Dept. of Nig. Languages, UDUS.
6. Dr. Haruna Bagudu,
   Jami'ar Usmanu Ɗan Fodiyo
7. Mallam Bello Hassan,
   C.I.S. Jami'ar Usmanu Ɗan Fodiyo.
8. Mal. Mustafa Aliyu,
   School of Matriculation, UDUS.
9. Mal. Mustafa Muhammad,
   Dept. of Arabic, UDUS.
10. Mal. Aliyu Muhammad,
    C.O.E. Shehu Shagari, Sokoto.

# ABUBUWAN DAKE CIKI

Bayanin Tushen Walittaka .................................................................... 1
Littafin Ishiriniyar Shehu Dan Fodiyo .................................................... 29
Faɗaƙar Da Al-Umma Game Da Kusantar Tashin Kiyama ......................... 37
Hanyar Aljannah ........................................................................................ 99
Faɗakar Da Rafkanannu........................................................................ 145
Kora Masu Gaskiya ................................................................................ 153
Daliyah Ta Yabon Manzon Allah ........................................................ 171
Gargaɗi Ga Alamomin Fitowar Mahadi ................................................ 179
Amsa Tatacciya A Kan Tambaya Tabbatacciya ....................................... 189
Bayani A Kan Bidi'o'in Shaiɗan............................................................ 217
Tushen Adalci Ga Shugabanni Da Masu Falala ....................................... 241
Haskakawa 'Yan'uwa Muhimman Abubuwa .......................................... 263
Gargaɗi Ga 'Yan'uwa Game Da Da'awar Mahdi Mai Bayyana A Karshen Zamani.......................................................................................... 301
Wasiaƙar Mutanen Hausa ...................................................................... 323
Madogarar Masu Ibada da Masu Sana'a ................................................ 331

# أصــول الــولايــة وشــروطــهـا

# BAYANIN TUSHEN WALITTAKA

Na


Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Imam Musa Tanimu

**Edita**

Dr. Hamza A. Ainu

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ....................................................................5
FASALI NA FARKO: Rukunan Istiƙama Wajen Bin Allah Azza Wajalla. ..........6
FASALI NA BIYU: Manyan Ɗabi'un Istiƙama..........................................7
FASALI NA UKKU: Hanyar Sufaye Da Abin Da Aka Gina Ta A Kai..........8
FASALI NA HUƊU: Madogarar Sufaye da Tushensa...............................10
FASALI NA BIYAR: Asali Biyar..........................................................11
FASALI NA SHIDDA: Asalin Mu'amala................................................12
FASALI NA BAKWAI: Maganin Ciwon Zuciya Da Shi...............................13
FASALI NA TAKWAS: Asalin Bala'i....................................................13
FASALI NA TARA: Yadda Mutum Zai Gane Aibin Kansa..........................14
FASALI NA GOMA: Karyata Wanda Ya Yi Da'awar Wani Hali Tare da Allah.................................................................................15
FASALI NA GOMA SHA ƊAYA: Shehi Mai Tarbiyya ...........................15
FASALI NA GOMA SHA BIYU: Asalin Suluki Da Tarbiyya Da Shehuntaka. .......................................................................................16
FASALI NA GOMA SHA UKKU: Sharuɗɗan Niyyar Manufar Muridi da Abin da Zai Kare Shi Da Katangarsa......................................................18
FASALI NA GOMA SHA HUƊU : Hanyar da Muridi Zai Bi Ya Tarbiyyantar da Kansa Wajen Jirkita Ɗabi'u Munana Kuma Zuciya Tana Karɓar Wannan Jirkitawa (Riyala)........................................................................20
FASALI NA GOMA SHA BIYAR: Hanyar da Muridi Zai Bi Wajen Sabar Wa Kansa Da Yunwa ........................................................................22
FASALI NA GOMA SHA SHIDDA: Ladabtar da Muridi Don Kada Ya Faɗa Wa Yaudarar Shaiɗan da Kaidinsa (Dabararsa) Don Kada Ya Sami Fatahi (Buɗi). Amma Ya Bar Sharaɗin Fatahi...................................................24
FASALI NA GOMA SHA BAKWAI: Ladabin Muridi Tare da Shehu Da 'Yan'uwa Da Zikirin Sufaye Waɗanda Suke Amfani da Shi A Manufofinsu.25
FASALI NA GOMA SHA TAKWAS: Haƙiƙanin Karama da Kusantar Allah Ta'ala da Saduwa Zuwa Gare Shi. .........................................................26

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Suna Allah Mai Rahma Mai Jin-Kai

Allah Ya yi salati ga shugabammu, Annabi Muhammadu da iyalansa da Sahabbansa da aminci mai yawa.

Bawa mabuƙacin rahamar Ubangiji, Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usman, Bafillace Bamalike mai aƙidar Ash'ari yana cewa: Godiyata ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai: Mafificin salati da aminci su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu da iyalansa da sahabansa baki ɗaya. Yardar Allah ta tabbata ga shugabanni da tabi'ai da malamai masu aiki da iliminsu da shugabannin nan guda huɗu masu ƙoƙari da masu koyi da su har zuwa ranar tashin ƙiyama.

Wannan littafi yana bayani a kan tushen walittaka da sharaɗin walittaka. Ina cewa muwafaƙa na ga Allah. Ka sani ya kai ɗan'uwana, asalin walittaka da sharaɗinta, an gina su ne a kan bin ko riƙo da Alƙur'ani da Hadisi da barin bin ra'ayi da barin bidi'a da girmama alfarmar Shehunnai da yin aiki ba tare da kallon halitta ba wato kawar da riya.

A cigaba da yin wuridi ba tare da yankewa. Abul-Kasimul Junaid (Allah Ya yarda da shi) ya ce: "Dukkan hanyoyi zuwa ga Allah, tushe suke sai hanyar bin Manzon Allah (saw) Sahalu ibni Abdullahi (rta) ya ce: Ku yi riƙo da a kan abubuwa shida su ne: Riƙon Alƙur'ani da bin sunnar Manzon Allah (saw) da cin halas, da kamewa daga cuta da nisantar laifi da ba da haƙƙoƙi. Abu Hamzatul Bagadadi (rta) ya ce: Wanda ya san hanyar gaskiya, za ta yi masa sauƙin bi.

Ya ce: "Ba a samun bin hanyar Allah sai ta wajen bin masoyin Allah (saw) da bin zancensa da aikinsa da halayensa."

Abul-Abbas ɗan Aɗa'i (rta) ya ce wanda ya lazimta wa kansa bin hanyoyin sunna, Allah Zai haskaka zuciyarsa da hasken ma'arifa (wato sanin Allah). Babu wani muƙami wanda za a samu wajen Allah Mai daraja kamar bin masoyin Allah, Annabi (saw) wajen bin umurnin Manzo (saw) da aikinsa da maganarsa da ɗabi'unsa. An tambayi (Imam) Shabliy (rta) kan mene ne Tasawuffu? Sai ya ce shi ne koyi da Annabi (saw). Malamai sun yi magana da yawa kan wannan fanni kamar yadda aka ciro daga gare su. Allah dai Ya yi mana muwafaƙa.

## FASALI NA FARKO:

**Rukunan Istiƙama Wajen Bin Allah Azza Wajalla**

Su guda biyar ne kamar yadda Ɗan Abdus Sadiq ya faɗa a cikin littafin **Hidayatul-Abidi.**

**Na Farko:** Ka bauta wa Allah a matsayin kai bawanSa ne.

**Na Biyu:** Ka sani cewa kai ɗin nan ana sarrafa ka ne kuma a aikatar da kai ne don waninka, ba kai ne mai yin komi ba.

**Na Uku:** Ka kuma sani kuɗin da ke a hannunka, shi ne wanda aka yi shi don amfaninka.

**Na Huɗu:** Ka kuma sani duk abin da ka ci a cikinka ko ka ciyar da waninka. Wannan abu, mallaka ne daga wurinka.

**Na Biyar:** Duk ni'imar da ka gani daga Allah ne, kuma falalarSa ce. Idan kuma ka ga azaba, to, kaffara ce ta laifinka.

Waɗannan su ne jimillar rukunan Istiƙama (daidaituwa). Duk wanda ya kiyaye su, ya yi aiki da su, to, ya shiga hanyar walittaka.

## FASALI NA BIYU:

### Manyan Ɗabi'un Istiƙama

Sun kuma guda Goma sha biyar ne, kamar yadda Ɗan Abdus-Sadiq ya faɗa a cikin littafin **Hidayatul-Abidi.** Haka shi ma Gazali ya tsara su a cikin **Minhaj.** Ya yi bayanin su ƙwarai har ba sa buƙatar wani daɗi.

**Na Farko:** Ilimi shi ne gwargwadon abin da zai wajaba a kanmu na sanin asalin addini da fiƙihu da tasawwufi.

**Na Biyu:** Tuba daga dukkan zunubi wanda ke tsakaninka da Ubangijinka ko kuma tsakaninka da sauran halittu.

**Na Uku:** Zuhudu ga (gudun-duniya) kayayyakin duniya sai dai gwargwadon lalura.

**Na Huɗu:** Janye jiki daga yawan cuɗanya da jama'a sai dai a lokacin salla ko lokacin karatu ko kuma lokacin amfani na addini.

**Na Biyar**: Yaƙi da shaiɗan ta hanyar neman tsari da dafa'i.

**Na Shida:** Mujahada (ƙoƙari) ga zuciya da sanya mata linzamin tsoron Allah.

**Na Bakwai:** Tawakkali ga Allah a cikin al'amarin arziki.

**Na Takwas**: Miƙa lamari zuwa ga Allah lokacin haɗuwa.

**Na Tara:** Yarda da hukuncin Allah

**Na Goma:** Haƙuri idan masiba ta samu.

**Na sha Ɗaya:** Lazimtar tsoron Azabar Allah a kowane lokaci.

**Na sha Biyu:** Lazimtar fatar rahamar Allah a kowane lokaci.

**Na sha Uku:** Kawar da jin-kai wajen tunawa da sanin dukkan baiwa daga Allah take.

**Na sha Huɗu:** Kawar da aikin riya.

**Na sha Biyar:** Lazimtar godiya bisa ni'imar da Allah Mai girma da Ɗaukaka Ya yi mana.

## FASALI NA UKKU:

### Hanyar Sufaye Da Abin Da Aka Gina Ta A Kai

Ahmadu Zaruƙ ya ce a cikin littafinsa mai suna **Umdatul-Muridis-Sadiƙi** ka sani shi, fiƙihu, da Tasawwuffi, 'yan'uwan juna ne wajen nuni ga dokokin Allah (swt). Saboda ma'anar sufanci ita ce gaskiyar fuskantar Allah (swt). Fiƙihu da Usulu, sharuɗɗa ne na sufanci. Kuma abin da aka sani ne cewa, fiƙihu da sufanci, abokan tafiya ne watau tare suke. Allah Ya ce:

﴿وَلَا يَرۡضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلۡكُفۡرَ﴾ الزمر: ٧

***"Ba Zai yardar wa bayinSa su aikata kafirci ba." Alƙur'ani 39:7***

Saboda haka ana buƙatar lazimtar imani.

A wani wurin kuma Ya ce:

﴿وَإِن تَشۡكُرُواْ يَرۡضَهُ لَكُمۡ﴾ الزمر: ٧

***"Idan suka gode wa Allah, Zai yardar muku." Alƙur'ani 39:7***

Ka ga nan kuma ya nuna lizamtar ka yi aikin Musulunci. Saboda haka Sufanci ba ya amfani idan babu fikihu saboda da fiƙihu ne ake gane dokokin Allah na zahiri. Shi kuma fiƙihu ba ya cikin sai da sufanci saboda gaskiyar lamari ita ce yin aiki. Aiki kuma ba ya samuwa sai da gaskiyar fuskantar Allah (swt). Su kuma guda biyun ba sa samuwa sai da su.

Sai dai hangen masanin fiƙihu ya taƙaita a kan abin da zai kawar da laifi kaɗai. Shi kuwa sufi, kallonsa shi ne ta ya ya asali zai gyaru watau imani da bin sunnah. Shi kallon sufi wajen jinginarsa, shi ne yadda za a sami kamala a wajen aiki saboda haka zai nemi tabbacin aiki ta wajen asalinsa, ta wajen kyutata imani har a zama mai addini a bayyane.

Idan an lura ta wajen fiƙihu, ana buƙatar riƙo ta hanya maɗaukakiya kodayaushe. Kuma wannan yana da hukunci na daban watau shi ne ya zama a kodayaushe cikin riƙo wajen bin hanya mafi kyau kuma mafi cika. Kamar yadda Allah (swt) Yake cewa:

﴿ٱلَّذِينَ يَسۡتَمِعُونَ ٱلۡقَوۡلَ فَيَتَّبِعُونَ أَحۡسَنَهُۥٓ﴾ الزمر: ١٨

***"Su ne waɗannan idan sun ji magana sai su bi mafi kyau." Alƙur'ani 39:18***

Saboda haka mazhabarsu (Sufaye) ita ce koyi da hanyar Salaf wajen tsarkake Allah da kore kamanta Allah da siffar da ba ta dace da Allah ba, ba tare da zuwa ga kaifiyya ba, ko wani tawili. Mazhabarsu ita ce mazhabar **Ahalil-Fiƙihu** tsantsa sai dai su, suna ɗauka game da mazhaba abin da ya yi muwafaƙa da hadisi ne kawai domin su haɗa tsakanin hasken biyayya da hasken shiriya kuma su riƙe mazhaba guda ɗaya kaɗai. Kuma ba tare da suna musun wata fatawa mashahuriyya ba sai dai idan akwai wata lalura.

Mazhabarsu wajen bin hanyar falala ta yi daidai da mazhabar Ahalul – Hadisi, ba sa aiki da wani hadisi maudu'i (abin jefarwa) kamar yin sallar mako-mako da makamantansu, duk da malamin nan Abu-Talib ya tabbatar da su a cikin littafi **Manasik.** Shi ma Gazali ya bi shi a wannan ra'ayi. Sun kaɗaita a cikin mazhabarsu wajen bin Adab (ladubba) ta hanyar haɗa kansu da Ubangijinsu ta kowace fuska da ta yi musu sauƙi ko abin mubahi (halal) ne bayyananne ko ruhusa (sauƙi) ko kuma aikin wani al'amari da aka yi saɓani a kansa.

Ta wannan dalilin ne, za ka gan su suna magana cikin abin da ake yi musu inkari (musu) amma mutanen da ba su san manufarsu ba, suna nema daga gare su da su yi aiki da irin hanyarsu ta wajen ibada wajen Ihtiyaɗi (kiyayewa) ko kuma Isari (zaɓin wani) abin da ya fi inganci, Sheikh Junaidu (ra) ya yi nuni zuwa ga irin wannan abin inda yake cewa: Duk abin da zai haɗa bawa da soyayyar Allah, to, wannan abu yana da kyau. Haka nan shi ma Gushaili daga Abiz-Ziƙaƙi (ra) inda ya ce: Shehunnai sun ce: "Duk abin da zai haɗa zuciya da soyayyar Allah babu laifi idan mutum ya aikata shi."

## FASALI NA HUƊU:

**Madogarar Sufaye da Tushensa**

Gazali ya ce: Ginshiƙin tushen sufanci, abubuwa biyu ne;

**Na Farko**: Barin duk abin da zai shagaltar da kai ga barin hanyar Allah.

**Na Biyu:** Lazimta wa kai yawan zikirin Allah a kodayaushe.

Amma tushensa: Abubuwa guda biyar ne kamar yadda Ahmad Azzuraƙ ya faɗa:

**Na Ɗaya:** Jin tsoron Allah a ɓoye da a bayyane. Abin da ake ce wa tsoron Allah, daidaituwa a kan aikata wajibai da kiyaye wa daga ayyukan da suke haramun ne.

**Na Biyu:** Bin sunnar Manzon Allah (saw) wajen magana da aiki. Abin da ake nufi da bin sunnah, shi ne kiyaye sunnah Kyawun ɗabi'a, shi ne yin mu'amala da kowane mutum ta hanyar da zai ji daɗi in dai abin bai saɓawa shari'a ba.

**Na Uku:** Kawar da kai ga halitta wajen fuskantar su, ku juya masu baya. Ma'anar kawar da kai ga halitta ita ce yin haƙuri da tawakkali.

**Na Huɗu:** Yarda da Allah cikin abin da Ya hukunta na arzikin mutum ko kaɗan ko mai yawa. Abin da ake nufi da yarda da Allah, shi ne Kana'a (rashin zucci) da fawwala lamari ga Allah.

**Na Biyar:** Komawa da lamari zuwa ga Allah a ɓoye da bayyane. Abin da ake nufi da komawa zuwa ga Allah, ita ce yawan godiya a ɓoye da bayyane da fakuwa zuwa gare Shi lokacin bala'i.

## FASALI NA BIYAR :

### Asali Biyar

**Na Ɗaya:** Su ma guda biyar (5) ne kamar yadda Ahmadu Zaruƙ ya ce:

**Na Farko:** Himma maɗaukakiya, ita ce mutum ya zaɓa wa kansa babban lamari ban da ƙasƙantartun al'amura. Ya zaɓi Allah game da al'amuran ibadarsa, ba neman duniya ko kashafi ko karama ba.

**Na Biyu:** Kiyaye alfarmar Allah da alfarmar Shehu da alfarmar halitta. Abin da ake nufi da kiyaye alfarmar Allah, shi ne sadar da umurninSa da nisantar abin da Ya hana. Abin da ake nufi da kiyaye alfarmar Shehu, shi ne girmama sha'aninsa. Abin da ake nufi da kiyaye alfarmar halitta, shi ne tausaya masu.

**Na Uku:** Hidima mai kyau, ita ce muwafaƙa da bin sunna a wajen ayyuka na ibada.

**Na Huɗu:** Zartar da himma saboda mutum yana da maƙiya guda biyu: Zuciya da shaiɗan. Duk lokacin da mutum ya tashi zai yi aikin ibada sai su kama shi  da faɗa saboda haka sai ya zartar da himmarsa sai ya ƙyale su, ya ci gaba.

**Na Biyar:** Girmama ni'imar Allah kuma ta wajen girmama ni'imar ne Allah Yake ƙara yawan ni'ima. Duk wanda himmarsa ta zama maɗaukakiya, darajarsa za ta ɗaukaka, zai gane haka gaskiya ce. Duk wanda ya kiyaye alfarmar Allah da alfarmar shehu da alfarmar halitta, shi ma za a kiyaye alfarmarsa. Duk wanda ya kyautata hidimarsa, karamarsa za ta tabbata wadda himmarsa ta tabbata, shiriyarsa ta dawwama. Wanda ya girmama ni'imar Allah, Allah Zai daɗa masa yawan ni'imar.

## FASALI NA SHIDDA:

### Asalin Mu'amala

Su ma guda biyar (5) ne waɗanda Ahmadu Zaruƙ ya faɗa:

**Na Ɗaya:** Neman ilimi don tsayar da al'amura na addini.

**Na Biyu:** Haɗa kai da Shehunnai da 'yan'uwa don samun basira saboda haɗa kai da salihai yana daga cikin tabbatar da aiki na kirki. Misali, wanda ya yi aboki da mai yin salla sai shi ma ya riƙa yin sallar. Wanda ya yi aboki da mai yin azumi shi ma sai ka ga ya zama mai yin azumin da dai makamantansu.

**Na Uku:** Kada a riƙa yi wa kai sauƙi domin kiyaye ayyukan ibada.

**Na Huɗu:** Kiyaye lokutta da yawan yin wuridi saboda ya samu halara wurin Allah.

**Na Biyar:** Tuhumar zuciya saboda fita daga soyayyarta da kuɓuta daga kure da neman ilimi duk da shi ma yana da aibi, shi ne haɗa kai da ƙananan yara masu kyawun siffa. Shi kuma aibin haɗa kai da Shehunnai da 'yan'uwa shi ne faɗawa cikin ruɗi da fululi. Amma aibin barin sawwaƙa wa kai shi ne ji wa kai tausayi amma aibin kiyaye lokutta da wurudi shi ne yawan kallon aiki na mustahabbai. Amma aibin tuhumar kai shi ne natsuwa da halayenta ko istiƙama.

## FASALI NA BAKWAI:

## Maganin Ciwon Zuciya Da Shi

Su ma guda biyar ne kamar yadda Ahmadu Zaruƙ ya ce:

**Na Ɗaya:** Rage wa ciki nauyin abinci..

**Na Biyu:** Fakuwa zuwa ga Allah cikin abin da suke zuwa masa na damuwar zuci lokacin saukar damuwa.

Asalin shamaki guda huɗu ne. Son zuciya da bin shaiɗan da son duniya da son rayuwa. Shamakin son zuciya da bin shaiɗan sun fi kowane ƙarf. Shi, shamakin bin mutane, yana gushewa idan kai nesa da su. Shamakin son duniya yana gushewa idan ka yi mata zuhudu. Shamakin son zuciya ya fi shamakin shaiɗan kuma yana gushewa da ka yi zikiri ko ka yi tilawa amma son zuciya ba ya gushewa da wani abu sai dai ka koma zuwa ga Allah.

**Na Uku:** Ya haɗa kai da wanda zai haɗa shi zuwa aikin Allah ko bin umurnin Allah.

**Na Huɗu:** Ya haɗa kai da mutumin da zai nuna masa Allah ko zai nuna maka dokokin Allah.

**Na Biyar:** Dawwama cikin istigifari ko salati ga Manzon Allah (saw). Yawan istigfari da Manzon Allah (saw) yake yi kullum saba'in (70) zuwa ɗari (100). Mafi yawan salatin da ake buƙata ga mutum a kullum shi ne dubu (1000) matsakaici kuwa shi ne ɗari biyar (500); mafi ƙanƙanta kuwa ɗari (100).

## FASALI NA TAKWAS:

## Asalin Bala'i

Guda uku ne kamar yadda Ibni Sadiƙ ya faɗa a cikin littafin **Hidayatu**.

**Na Farko:** Yarda da aibin da zuciyarka alhali tana da laifi.

**Na Biyu:** Rashin tsoron Allah a gaibi (fakaice).

**Na Uku:** Zama cikin saɓon Allah.

## FASALI NA TARA:

**A Bayanin Yadda Mutum Zai Gane Aibin Kansa**

Abubuwan guda huɗu (4) ne kamar yadda Imamu Al- Gazali ya faɗa a cikin littafin **Ihya'u**.

**Na Farko:** Ya zama gaban Shehu wanda ya san aibin zuciya, mai hangen aibi na ɓoye, ya ba da kansa zuwa gare shi; ya bi umurninsa wajen yaƙi da kansa. Wannan shi ne sha'anin muridi ta haka ne Shehunsa ko malaminsa zai sanar da shi aibin kansa kuma zai sanar da shi hanyar maganinsu.

**Na Biyu**: Ya nemi aboki mai gaskiya, kuma mai kula da addini, ya mayar da shi abin kallon shi a gabansa don ya riƙa duba halayen abokinsa da aikace-aikacensa. Idan abokinsa ya ga wasu halayensa munana ko aikace-aikacensa ko aibinsa na bayyane ko na ɓoye sai ya faɗakar da shi don ya daina.

**Na Uku:** Ya gane aibin kansa ta harshen maƙiyansa saboda idon maƙiyi, shi kullum yana ganin muninka ne. Wani lokaci, mutum yana amfana da maganar maƙiyinsa mai tsananin gaba fiye da maganar masoyinsa mai yi masa almundahana (rufa-rufa) mai yabo gareshi. Yana yabon shi kullum, yana ɓoye masa aibinsa. Kodayake ɗabi'ar mutum tana ƙaryata maƙiyi ne tana ɗaukar shi mai yin hassada ne kawai, sai dai shi, mai hankali, yana amfani ne da maganar maƙiyinsa ne saboda munanan ayyuka. Kullum ana jin su ne a harshen maƙiya.

**Na Huɗu:** Ya riƙa cuɗanya da mutane. Duk abin da ya gani, to, ya binciki kansa shi ma yana aikata shi ne. Idan yana aikata shi, to, ya bari saboda mutum mumini madubin mumini ne. Idan ya ga aibi a idon wani, to, shi ma yana da shi ne saboda ɗabi'un mutane sun yi kama da juna wurin son zuciya. Idan aboki yana da wata siffa mummuna, to, shi ma abokin yana da ita, ko ma fiye da ita wajen girman laifin ko kuma mai kama da ita saboda haka ya riƙa duba zuciyarsa, ya tsarkake ta daga duk abin da yake zargin waninsa. Saboda haka ina ba ka shawara ka bi wannan hanyar koyarwa. Da dai mutane za su bar munanan ɗabi'u na wajen abokansu da an huta da malami mai ladabtarwa.

## FASALI NA GOMA:

**Karyata Wanda Ya Yi Da'awar Wani Hali Tare da Allah**

Duk wanda ya yi da'awar wani hali tare da Allah sannan abubuwa guda biyar suka bayyana a gare shi , wannan maƙaryaci ne ko da kuwa wanda aka san, cewa mai imani ne. Allah Ya kare mu daga wannan

**Na Farko:** Mai ƙyale gaɓoɓinsa su yi ta saɓon Allah.

**Na Biyu:** Mai nuni da jin-kai wajen yi wa Allah biyayya (ɗa'a).

**Na Uku:** Tsammanin samun wani abu wajen abokin halitta.

**Na Huɗu:** Cin mutuncin bayin Allah.

**Na Biyar:** Rashin girmama 'yan'uwa Musulmai ta hanyar da Allah Ya umurta.

Duk mai aikata waɗannan abubuwan biyar da ƙyar zai cika da imani.

## FASALI NA SHA DAYA:

**Shehi Mai Tarbiyya**

Su ma guda biyar ne kamar yadda Ahmadu Zaruƙ ya faɗa:

**Na Farko:** Ingantaccen ilimin shi ne wanda aka samo daga Alƙur'ani da Hadisi.

**Na Biyu:** Ingantaccen zauƙi (basira).

**Na Uku:** Himma maɗaukakiya.

**Na Huɗu:** Hali yardajje. Wanda ya yi muwafaƙa da Alƙur'ani da hadisi gwargwadon yadda Shehunnai suke a kai.

**Na Biyar:** Yana da basira mai kaifi wanda take iya hangen abubuwa na ɓoye da bayyane da ita (wannan basira mai kaifi).

## FASALI NA SHA BIYU:

### Asalin Suluki Da Tarbiyya Da Shehuntaka

Ka sani mutanen farko na malamai ba su da wata ƙa'ida ta jeranta Shehuntaka ko wani istilahi (hanya) game da suluki (bi) wanda aka saba da shi amma abubuwan da suka sani su ne abokantaka da haɗuwa da malamai.

Idan almajiri ya haɗu da malami sai ya samu fa'ida ta ganin halayen malam kawai saboda duk wanda ya sakankance da hali sai wannan hali ya sauka mashi balle halayen da aka gada. Saboda haka ne Gazali ɗan Arifi (ra) ya ce: "Ta yaya mutum zai tsira alhali bai haɗa kai da wanda ya tsira ba?" Sahabai (ra) sun amfana da ganin Manzon Allah (saw) kaɗai, haɗa kai ya'ishe su samun mabuɗi na Manzon Allah (saw) da samun ilimin gaba da gaba daga Manzon Allah (saw).

A wannan lokaci kuwa ya jiɓinci Shehunsa sai ya amfana da falalar Shehu, ya gode kyautatawar da ya yi masa kuma sai ya amfana. Wannan abu ya samu tushe daga zancen Allah inda Ya ce:

﴿وَٱتَّبِعۡ سَبِيلَ مَنۡ أَنَابَ إِلَيَّۚ﴾ لقمان: ١٥

***"Ka bi hanyar wanda ya koma zuwa gare Ni." Alƙur'ani 31:15***

Amma da zamani ya yi tsawo; zuciyoyi suka gurɓata sai malamai suka yi isɗilahi (suka fito da hanya) wajen jeranta tarbiyya da jeranta Shehuntaka kamar yadda aka san shi a wannan lokacin. Su ma sun kafa hujja da ayar da aka faɗa:

﴿وَٱتَّبِعۡ سَبِيلَ مَنۡ أَنَابَ إِلَيَّۚ﴾ لقمان: ١٥

***"Ka bi hanyar waɗanda suka koma zuwa gare Ni." Alƙur'ani 31:15***

Saboda shi, Manzon Allah (saw), yana tarbiyyantar da Sahabbansa, yakan ba kowa abin da ya dace da shi. Misali, ya yi wa wani Wasicci da cewa: "Kada ka yi fushi."

Ya ce wa wani kuma:

(قل ربي الله ثم استقم)،

***"Ka ce Allah Ne Ubangijina sai ka tsayu daidai."***

Ya ce wa wani;

(لا يزال لسانك رطبا بذكر الله)

*"Kada harshenka ya gushe yana ɗanyantaka da zikirin Allah."*

Ya kwaɗaitar da wasu jama'a da yawan zikiri, wasu da neman ilimi. Misali, ya ce wa Abdullahi ɗan Amar:

(صم وأفطر)

*"Ka yi azumi kuma kana hutawa."*

Amma ya tabbatar wa Hamza ɗan Umar Aslimi da ya jeranta azumi da dai makamantan wannan ta hanyar tarbiyya saboda haka ka fahimci haka. Daga nan malamai suka samo hanya saboda fahimtar ilimi da fahimtar haƙiƙanin lamari saboda haka ba su ƙyale ɗaukar alƙawari ba daga wajen lizimtar wa kai ɗabi'un tsoron Allah, suna kafa hujja da hadisin da aka ruwaito daga Ubaidatu bin Samiti (ra) wanda Manzon Allah (saw) ya ce masa:

(بايعوني على أن لا تشركوا بالله شيئا)

*"Ka yi mani mubaya'a a kan ba za ka haɗa Allah da komi ba."*

Manzon Allah (saw) yana maimaita bai'a a wurare daban-daban kamar yadda ya auku tare da Salmata ɗan Akwa'i da waninsa kamar yadda aka sani cikin hadisai na yaƙoƙi. Haka halin Manzon Allah (saw) yake yana kiran su zuwa ga wannan bai'a. Duk da imaninsu da kuɓutarsu daga kafirci, manufarsa ita ce ya ƙarfafe su. Allah Ne kaɗai Masani. Mutum ba ya shiga matsayin istiƙama shi ne ɗaukar zuciya zuwa ga ɗabi'un Alƙur'ani da mafi kyawo, ba tare da daɗi ko tawaya ba saboda mutum yana jahiltar abin da ya cancance shi.

Sai malamai su lazimta masa abin da zai kawo masa kashafi wajen ƙoƙarin da kuma abin da zai sadar da shi zuwa gare shi kamar jin yunwa da rashin barci da kawaici da halwa don su lazimtar sa abubuwan da zai bayyana halinsa domin sada abin da ke wajensu.

Sai muridi ya zama wajen malaminsa kamar gawa wajen mai wanke ta kamar yadda aka sani wurin sharaɗin muridi tare da Shehinsa sai dai ba su lizimta wa kowa wannan hali sai sun ga yana cikin ahalin (wanda ya cancanta) abin, yana kuma da hali na kamala.

## FASALI NA SHA UKKU:

**Sharuɗɗan Niyyar Manufar Muridi da Abin da Zai Kare Shi Da Katangarsa**

Gazali ya faɗa a cikin littafin **Ihya'u**, ya kamata muridi ya sani cewa, akwai sharuɗɗa da ba makawa sai an gabatar da su a farkon lokacin niyya. Kuma dole ya sani cewa, akwai madogara wadda dole ya yi riƙo da ita kuma ya sani akwai katanga, dole ya yi kariya da ita don ya aminta daga 'yan-fashin lahira.

Amma sharaɗin da ba makawa ya gabatar da shi wajen niyya, shi ne kawar da hijabi tsakaninsa da Allah. Hijaban da suke tsakanin bawa da Allah guda huɗu ne:

**Na Farko:** Kuɗi.

**Na Biyu:** Son girma.

**Na Uku:** Taƙalidi (biyayya a maƙauce).

**Na Huɗu:** Saɓon Allah.

Shi, hijabin son kuɗi, an ɗauke shi da sanin sharrin kuɗi da kuma cire son kuɗi daga zuciyarsa. Ya zama abin da zai ragu sai buƙatun yau da kullum. Shi kuma shamakin son girma an ɗauke shi da nisanta kai wajen da ake girmama shi, ya rika yin tawali'u kodayaushe; ya riƙa son ɓuya daga idon jama'a da guje wa abin da zai kawo bayyanar suna ko ɗaukakar suna da aikata abin da zuciyar jama'a ke ƙyama.

Shi kuma shamakin takalidi, ana ɗauke shi da rashin zarɓaɓi wajen riƙon magana, Shehun ne a fannin tauhidi ta yadda da ma'anar ***"La'ilaha'illallah Muhammadu Rasulillah***" yarda ta gaskiya, ya kwaɗaitar da kansa wajen sanin haƙiƙanin gaskiyar lamarin ta wajen kawar da duk abin bauta in ba Allah Azzawajallah ba. Mafi girman abin bautar bawa, shi ne son zuciyarsa saboda haka ya yi nesa da wannan. Idan ya'aikata haka zai gane haƙiƙanin lamari wajen ma'anar kulli imanin da ya yi amma kada ya yi zaton zai sami haka ta wurin jayayya.

Idan yana da zarɓaɓi wajen riƙo da maganar Shehu, idan ya yi haka kuwa sai zuciyarsa ta kasa buɗewa ta hangi wata magana daban. Wannan abu sai ya zama dabaibayi, ya zama masa kuma hijabi. Amma hijabin saɓon Allah ba abin da ke ɗauke shi sai tuba da fita daga zalunci da kuma niyya mai ƙarfi

cewa ba za a koma wa laifin ba da cikakkiyar nadama kan abin da ya wuce da mayar da zalunci da neman yardar wanda aka yi husuma da shi.

Amma madogarar muridi bayan sharuɗɗan da muka faɗa ita ce, Shehinsa ya yi riƙo da umurninsa kamar yadda makaho yake riƙe da mai gani a gefen teku. Idan muridi ya gabatar da waɗannan sharuɗɗa guda huɗu kamar wanda ya yi wanka ya yi alwala ya cancanci ya yi salla kenan. Saboda haka yana buƙatar limamin da zai yi koyi da shi. Haka nan muridi shi ma yana buƙatar Shehi ko malami da zai koyar da shi. Wannan dole ne domin ya shiryar da shi hanyar ƙwarai.

Saboda hanyar addini ta cika wuyar ganewa amma ita kuma hanyoyin shaiɗan ga su nan da yawa a bayyane saboda haka muridi ya fawwala lamarinsa gaba ɗaya zuwa ga Shehi. Kada ya riƙa saɓa masa a komin ƙanƙantar abu. Ya sani zai amfana ko da Shehinsa ya yi kure fiye da tunanin cewa, shi zai amfana idan ya dace. Amma katangun muridi waɗanda za su kare shi daga 'yan-fashin hanyoyi guda huɗu ne:

**Na Farko:** Nisantar mutane, sai dai lokacin salla kaɗai ko lokacin karatu ko kuma lokaci na amfanin addini.

**Na Biyu:** Kawaici, kada ya cika magana sai gwargwadon lalura.

**Na Uku:** Zama da yunwa, kada ya ci said a yunwa.

**Na Huɗu:** Rashin barci, kada ya yi barci sai gwargwadon lalura.

Waɗannan abubuwa gudu huɗu su ne katangar muridi daga 'yan fashin addini. Saboda manufar muridi ita ce gyara zuciyarsa don ya yi mushahada (ya samu saduwa) da Ubangijinsa kuma ya iya haɗuwa da Shi lafiya lau.

## FASALI NA SHA HUƊU:

**Hanyar da Muridi Zai Bi Ya Tarbiyyantar da Kansa Wajen Jirkita Ɗabi'u Munana Kuma Zuciya Tana Karɓar Wannan Jirkitawa (Riyala)**

Gazali ya ce a cikin littafin **Ihya'u** hanyar riyala (horawa) ita ce shiga hanyar da take kishiya ga abin da zuciya take so ko kuma abin da ta karkata

Ya kamata da Shehi mai tarbiya ya duba mene ne ciwon muridi a halin da yake ciki yanzu sai ya gina riyala a kansa. Idan muridi jahili ne da dokokin shari'a tun farko sai ya koya masa tsarki da salla da ayyukan ibada na bayyane. In ko muridin ya shagaltu da dukiyar haram ne ko yana aikata saɓon Allah sai tun farko sai ya umurce shi da barin su.

Idan muridi ya yi ado da ibada ta bayyane, ya tsarkake zuciyarsa daga saɓo saboda haka sai ya duba gaɓoɓin na boye don ya duba kyan ɗabi'arsa da kuma mene ne ciwon zuciyarsa. Idan malam ya gane cewa wannan muridi yana son tsafta ta jiki da ta tufafi, ya ga zuciyarsa ta karkata zuwa gare ta. Kuma yana murna da su kuma ya karkata zuwa gare ta, sai ya tashi ya riƙa aikin ɗebo ruwa da wanke wajen ƙazanta.

Haka nan idan ya lazimta masa yin azumin nafila a kai-a kai ko kuma ya ƙaranta masa cin abinci sannan ya tilasta masa dafa abinci mai daɗi; ya hana shi ci, ya ba wani har zuciyarsa ta saba da haƙuri da rashin haɗama. Haka nan idan ya gane muridin yana sha'awar aure, ga shi bai da halin yin auren sai ya umurce shi da yawan yin azumi. Idan sha'awarsa ba ta natsu ba, duk da haka sai ya umurce shi da buɗe baki da ruwa kaɗai ban da abinci mai nauyi, wani lokaci abinci mai nauyi amma ban da ruwa. Ya hana shi cin nama kwata-kwata da miya mai romo har zuciyarsa ta ƙasƙanta sha'awarsa ta karye babu magani mafi amfani ga muridi kamar yunwa.

Idan ya ga muridi yana da yawan fushi sai ya lazimtar masa juriya da ƙarancin magana. Wannan misali da na bayar zai maka amfani wurin hanyar maganin ciwon zuciya kwata-kwata ba manufarmu mu yi bayani filla-filla ba, domin bayani filla-filla zai zama dogon abu sai dai manufarmu faɗakarwa a kan hanya wadda mai shiga zai shiga ta kishiyar da zuciya ba ta so ko kuma ta karkata zuwa gare shi. Wannan bayyanin yana cikin kalma ɗaya inda Allah (swt) Ya ce:

﴿وَأَمَّا مَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفْسَ عَنِ ٱلْهَوَىٰ ﴿٤٠﴾ فَإِنَّ ٱلْجَنَّةَ هِىَ ٱلْمَأْوَىٰ﴾ النازعات: ٤٠ – ٤١

***"Amma wanda ya ji tsoron tsayawa a gaban Ubangijinsa, ya hana zuciya daga son abin da take so, to, Aljanna ita ce makomarsa."***
***Alƙur'ani 79:40-41***

# FASALI NA SHA BIYAR:

## Hanyar da Muridi Zai Bi Wajen Sabar Wa Kansa Da Yunwa

Gazali ya faɗa a cikin littafin **Ihya'u**, ka sani cewa muridi game da abin da zai ci ko ya ba cikinsa akwai martabobi guda huɗu:

**Martaba ta Farko:** Kada ya ci komai sai halas. Ka ga sauran martabobi uku waɗanda suke keɓance cin abinci su ne ƙaddara yawan abinci ko yawo da ƙaddara lokaci wajen jinkiri ko gaggautawa da ayyana jinsin abinci. Amma wajen ƙaranta cin abinci: Hanyar ita ce bi a hankali, wanda ya saba cin abinci da yawa sai rana ɗaya kwatsam ya koma zuwa ga ci kaɗan. Jikinsa ba zai iya ɗauka ba sai ya faɗa wa wahala mai tsanani. Ya kamata ya ɗauka a hankali, hanyar da zai bi ita ce ya ɗan rage abin da ya saba ci da kaɗan. In yana ma buƙata ya auna ko kuma ya yi amfani da hankali kullum ya rage loma ɗaya a kan abin da ya ci jiya.

Wannan yana da darajoji guda huɗu:

**Na Farko**:Yin ƙoƙari ta mayar da kansa gwargwadon yadda zai 'ji' da ɗan wani abu a cikinsa kaɗan wanda cikinsa ba zai buƙaci ƙasa da haka ba. Wannan ita ce daraja mafi ɗaukaka.

**Na Biyu**: Ya mayar da kansa a kwana da yini ga sulusin (⅓) cikinsa.

**Na Uku**: Ya mayar da kansa abin da zai ci sulusainin (⅔) cikinsa.

**Na Huɗu**: Ya mayar da kansa ya ɗan ƙara a kan sulusainin kaɗan, wato (⅔+).

A nan sai a samu hanya ta biyar ita ce babu wata ƙimantawa sai dai wajeje mai wahalar gaske shi ne ya ci abinci in dai yana jin yunwa ta gaskiya kuma ya daina cin abincin yana sha'awarsa da gaske. Duk wanda waina ɗaya ko biyu ba za ta ishe shi ba. Ya yi maganar horar da kansa da yunwa bai yiwuwa saboda haka sha'awarsa sai ta zama ta ƙarya ce.

Ita, yunwa, ta gaskiya tana da alamomi. Yana iya cin gurasa ba ruwa ko wani irin burodi ya zamo duk lokaci da aka ga mutum yana neman kalar biredi ko mahaɗi, to, ba yunwa yake ji ba.

Alama ta gaba a ce mutum yana jin yunwa ita ce zai zubar da yawu koda ƙudaje ba za su bi ba. Ya nuna babu komai na maiƙo a cikinsa. Kodayake sanin wannan shi ma yana da wahala. Abin da ya fi dace wa muridi shi ne ya ci gwargwadon yadda ba zai yi rauni wajen ibada ba. Idan ya kai

haka sai barin abinci ko da yana da buƙatarsa amma lokacin cin abinci da kimanta lokacin jinkirta shi, shi ma yana da darajoji guda uku:

**Daraja ta Farko:** Ita ce ta sama ita ce ya ɗarme cikinsa na kwana uku ko sama da haka. Akwai daga cikin muridai wanda ya mayar da riyalar kansa wajen jin yunwa. Wajen ɗarme ciki ba wajen kimantawa ba har akwai waɗanda suke ɗame cikinsu a kwana talatin zuwa arba'in. Akwai malamai masu yawa waɗanda suke yin haka. A cikinsu akwai Salim bin Abdullahi da AbdurRahman bin Ibrahimutaimi da Sulaiman da Khauwas.

**Daraja ta Biyu:** Ya ɗarme cikinsa kwana biyu zuwa uku.

**Daraja ta Uku:** Ita ce mafi ƙasa ita ce taƙaita cin abinci sau ɗaya a kwana da yini amma cin abincin game da wanda ya shafi muridi shi ne kada ya ci abinci mai tsada ko mai nauyi, al'adar hana shan miya mai romo da rashin cin abinci na sha'awa kodayaushe wanda bai da ikon hana kansa na sha'awa, ya kamata kada ya rabkana ya manta da kansa ta yadda zai kutsa cikin sha'awa.

Ya kamata idan ya ci ya ƙoshi kada ya kwanta ya yi barci sai ya haɗa ragganci biyu. Ya saba da rashin ibada kuma ga bushewar zuciya amma maimakon ya kwanta sai ya yi salla ko ya yi zikirin Allah. Wannan ya fi nuna alamar godiya. Mafi ƙanƙanta ya yi salla koda raka'a huɗu ko kuma ya yi tasbihi ɗari. Malam Sufyanu Sauri ya zama idan ya ƙoshi da daddare ba ya barcin dare.

Ka sani abin da ake nema ga muridi game da riyalar kansa wajen jin yunwa shi ne tsaka-tsaki kamar yadda hadisi ya ce:

(خير الأمور أوسطها)

***"Mafificin alheri ga al'amura na tsakiya ne."***

Amma fa duk hadisan da suka zo game da falalar yunwa ba ana nufin matsawa kai ne ba, a'a ba shi ake nufi ba. Shi malami, ya san abin da yake nufi na tsakiya. Abin da ya fi kyawun shi ne ka ci yadda cikinka ba zai yi nauyi ba. Kuma raɗaɗin yunwa ba zai dame ka ba, saboda manufar cin abinci ita ce tabbatar rayuwa. Amma idan aka ci abincin har ciki ya yi nauyi sai ya hana yin ibada.

Haka nan shi ma raɗaɗin yunwa yana tayar da hankali amma a farkon lamari. Idan zuciyar mutum ba ta bin doka, ga ta da sha'awar cin abinci kuma ta karkata zuwa ga zarɓaɓi, zama a tsakiya bai yi mata amfani dole a kai

matuƙa wajen wahalar da ita da jin yunwa kamar yadda ake horar da dabba wajen yunwa da dukar ta a farkon lamari har ta daidaita.

Idan ta daidaita sai a dawo da ita tsakiya sai a bar azabtar da ita.

Ka sani wanda ya bar bin sha'awar abinci, al'amura guda biyu na aibi manya suna iya samun su waɗanda sun fi cin abincin muni.

**Na Farko**: Ya kasa barin cin wani abinci amma bai so a gane shi in shi kaɗai ne sai ya ci da yawa in yana tare da jama'a sai ya ci kaɗan.

**Na Biyu**: Ya iya karya kansa wajen cin abinci amma yana son jama'a su san haka kuma ya shahara wajen kamewa daga barin sha'awar cin abinci. Duk wanda ya bar sha'awar cin abinci sannan ya faɗa cikin sha'awar riya kamar mutumin da ya ga kunama sai ya gudu ya faɗa kan macijiya saboda sha'awar riya ta fi cutarwa daga sha'awar abinci.

## FASALI NA SHA SHIDDA:

### Ladabtar da Muridi Don Kada Ya Faɗa Wa Yaudarar Shaiɗan da Kaidinsa (Dabararsa) Don Kada Ya Sami Fatahi (Buɗi). Amma Ya Bar Sharaɗin Fatahi

Ya kai wannan muridi, kar ka ɗauki jahilci, ka bar ilimi kar ka zama cikin wanda yake bin hanya kawai. Ka tabbatar da ka riƙe sunnar Manzon Allah (saw). Kar ka ƙetare zuwa bidi'a; ka bi malamai masu maganar gaskiya, kar ka bi maɓarnata; kada ka shagaltu da neman fuskantar jama'a zuwa gare ka da bayyana da'awa ta ƙarya maimakon ta gaskiya da ƙyale abokantaka da 'yan-duniya. Ka tsaya da asali kar ka zama cikin waɗanda suka ruɗu da ba da labarin mutanen ƙwarai. Kai kuma ba ka aiki irin nasu sai ya zama ka fita daga asalin hanya.

## FASALI NA SHA BAKWAI:

### Ladabin Muridi Tare da Shehu Da 'Yan'uwa Da Zikirin Sufaye Waɗanda Suke Amfani da Shi A Manufofinsu

Amma ladabin muridi tare da Shehunsa da 'yan'uwa guda biyar ne, kamar yadda Ahmad Zaruƙ ya faɗa:

**Na Farko:** Bin umarni koda a ganinsa abin ya saɓa wa saninsa.

**Na Biyu:** Nisantar hani koda yana ganin mutuwarsa a cikinsa.

**Na Uku:** Kiyaye alfarmar malaminsa yana nan ko ba ya nan; yana raye ko ya mutu.

**Na Huɗu:** Tsayar da haƙƙoƙin malaminsa gwargwadon iko ba tare da taƙaitawa ba.

**Na Biyar:** Kawar da fahimtarsa ko wani muƙaminsa sai in ya yi muwafaƙa da na Shehunsa.

Waɗannan ladubba guda biyar da su ne zai yi mu'amala da 'yan'uwa idan bai sami Shehu murshidi ba. Idan ko ya sami Shehu kuma ya kasa cika abubuwa biyar ga Shehu, to, ya cika su ga 'yan'uwa.

Amma Azkarun wanda sufaye suke amfani da shi a manufofinsu suna da yawa ba a iya ƙididige su. Akwai waɗanda suka ɗauki zikirin Kalmar Allah kawai, waɗanda zikirinsu shi ne **La'ilaha Illallahu Muhammadur Rasulillah**. Akwai wanda zikirinsa: **Subhanallahi walhamdu Lillalahi wallahu akbar**. Akwai wanda zikirinsa, salatin Annabi (saw) ne kuma shi ne mafi amfanin zikirorin wajen ƙarfafa zuciya ta zama kamar ruwan sanyi bayan ta yi kasala. Malamai masu yawa fiye da mutum ɗaya sun ce shi, salatin Manzon Allah (saw), yana sadar da bawa zuwa ga Ubangijinsa yakan tsaya matsayin Shehu mai tarbiyya idan aka rasa Shehu saboda albarkar Manzon Allah (saw).

## FASALI NA SHA TAKWAS:

**Haƙiƙanin Karama da Kusantar Allah Ta'ala da Saduwa Zuwa Gare Shi**

Amma abin da ake nufi da karama kamar yadda Malam Ɗan Aɗɗa'i Iskandariya ya ce a cikin littafin **Alhukhum**, da yawa Allah Yakan azurta wani bawa da karama amma bai kamala ba a wajen istiƙama. Sai mai sharhin maganar ya ce karama ta haƙiƙa ita ce wusuli zuwa istiƙama, wusuli zuwa cikarsa yana da ma'anoni biyu: Ingancin imani da Allah (swt) da bin abin da Manzon Allah (saw) ya zo da shi a ɓoye da bayyane. Abin da yake wajibi ga bawa shi ne kwaɗayin waɗannan abubuwa biyu. Amma idan mun duba karama ta fuskar keta al'ada ba wani abin kula ba ne wajen kusantar Allah, shi ne bawa ya yi shuhudi da kusantar Allah (swt) zuwa gare shi.

Ibni Aɗɗa'ilah ya ce a cikin littafin **Alhukhum,** kusantarka zuwa gare Shi zai nuna kusantar Shi zuwa gare ka. Mai sharhin wannan magana sai ya ce kusanta na haƙiƙa shi ne, kusantar Allah zuwa gareka kuma. Bawa amfanin da yake samu a wannan shi ne ya yi mushahadan kusantar Allah zuwa gare shi. Fa'idar da ake samu ta wannan mushahada kuwa ita ce muraƙaba (kula) da jin kwarjini da ladabtuwa cikin halarar da ake amma kai (bawa) ba abin da ya dace maka sai siffar bauta da ya ce ganin wannan daga kanka. Yadda ibn Kubbada ya ce wusuli zuwa ga Allah (swt) wanda malaman ɗariku suke nuni zuwa gare shi shi ne saduwa zuwa ga ilimi na haƙiƙa game da Allah (swt). Ni (Shaihu Usmanu) sai na ce ba ana nufi da ilimi na haƙiƙa ba, cewa: Bawa zai sadu zuwa ga ilimi na Allah ta ilimin zauƙi wanda ya wadatu daga hujjoji daga abin halitta.

Wannan shi ne matuƙar shigar masu shiga zuwa ga Allah, Shi Ne matuƙar tafiyar masu tafiya. A nan ne kuma muka zo ƙarshen abin da muka yi nufin wallafawa na littafin da ake kira Asalin Walittaka da sharaɗinta. Wannan littafi ya cika da taimakon Allah (swt) ne, Ya Allah Wanda kyautarSa ba ta ta'addi a kan kadararShi kuma ba Ya juyar da shi Ya siffanta zatinSa da cewa:

Ka ce musu "Allah Shi ne ɗaya, Allah Ne abin nufi da buƙata. Bai haihu ba, ba a haife shi ba, babu kuma abin da ya yi kama da Shi cikin halitta."

Ka aikata mana daga wajenKa abin da ya cance Ka, Kada ka aikata mana abin da ya cancance mu domin Kai ne Ka cancaci aji tsoron Ka. Kai Ne Ka cancanci a nemi gafararKa. Salatin Allah da aminci su tabbata a kan

mafificin abin halittar Allah baki ɗaya. Allah Ya isar mana kuma madalla da ya zama wakilin mu ba dabararmu ba, ba ƙarfinmu ba sai na Allah Maɗaukaki.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai mafificin salati da cikakken aminci ya tabbata ga shugabanmu, Annabi Muhammadu da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya. Allah Ta'ala Ya yarda da manyan shugabanni na tabi'ai da malamai masu aiki da iliminsu da shugabanni nan guda huɗu (Maliki da Shafi'i da Abu Hanifa da Ahmad bn Hanbal) masu ijtihadi da masu koyi da su zuwa ranar tashin ƙiyama. Ya Allah Ka yi gafara ga muminai, maza da muminai, mata da rayayyu daga cikinsu, matansu da mazansu. Ya Allah Ka yi rahama ga al'ummar Annabi Muhammad (saw) rahama gamammiya. Amin.

# عشرينية ابن فودى

# Littafin Ishiriniyar Shehu Dan Fodiyo

Na

Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**<u>Mai Fassara</u>**

Muntaƙa Muhammad Bilbis

**<u>Edita</u>**

Ahmed Abdullahi Sokoto (A.A. Sokoto)

## GABATARWAR MAWALLAFI

**Da Suna Allah Mai Rahma Mai Jin-Kai**

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Shugabammu, Muhammad da Alayensa da Sahabansa. Bawan Allah mai tsananin neman rahamar Ubanginsa, Usmanu Ɗan Muhammad, wanda aka fi sani da Ɗan Fodiyo, Allah Ya lulluɓe shi da rahamarSa, amin.

1. Ya wanda ke da bigire a ƙololon sama,
   Ya wanda shamakan jalala suke sunkuya gare shi,
   Ya wanda fuskarsa ta fi rana haske,
   Na zo da kurakurai kai ne mafaka,
   Tallafe ni a kwance ni daga waɗannan abubuwa domin don haka aka yi ka.

2. Da izzarka ake rubuta sunanka a Attaura,
   Da baiwarka kowa ke walwala a duniya,
   Da haskenka kowa ke tafiya a haskenka,
   Da sonka ne kuma bayi zaɓaɓɓu ke jaba,
   Saboda laifina ne nake gudu zuwa gare ka.

3. Tsarki ya tabbata ga Wanda Ya aiko ka domin rahama,
   Ka samu daraja da matsayi a gare Shi,
   Ya zaɓɓabe ka ɗauki amana daga gare Shi,
   Haske ya haskaka lokacin da ka tafiyar da duhu,
   Ka karanta littafin da yake a cikinsa akwai miskin hujjoji.

4. Yabo ya tabbata ga wanda bai saɓa alƙawari,
   Ina neman ninkin lada na ranar da za a tashe ni,
   Bayana ya yi nauyi, da shi ne nake riƙo,
   Ku amince da wanda ake magana a kansa,
   Ku zabura ku miƙe ku nufi Manzo, ku nemi (ceto).

5. Kyakkyawa majidaɗi, wanda ya yi ado da kyau,
   Mai gwaggwaɓar baiwa, ba a rufe ƙofarsa,
   Mai yawan baiwa, alheri ne hanyarsa,
   Mai goshi da haske ke ɓuɓɓuga daga ciki,
   Ya zama dole ne a gare mu, mu yi tafiya muna kutsawa zuwa gare shi.

6. Masoyi wanda haskensa ke haska Madina,
   Mai godiya mai girma mai shimfiɗa hannu mai nasiha,

Mai haƙuri da kowa ke yabon sa,
Mai kiyayewa wanda ke nasiha ga talikai,
Mai tausayawa ga maƙwabta safe da yammaci.

7. Maji daɗi, masoyi shugaban da ba a masa tsawa,
Cikamakon addini mai goge shari'o'i,
Mai bayani tsakanin talikai ranar busa ƙaho,
Ranar da za a tara na duniya da na lahira,
Mai faɗin farfajiya ga shi yaro, amma mai siffar dattawa.

8. Mutane baki ɗaya sun san Ahamad shi ne shugaba,
Jagoran talikai wanda ba misalinsa,
Magani a gare ni idan cuta ta auka mini, Ahamad,
Bara na kira shi a duhun dare, Muhammad (saw),
Na ruɗe zuciya tana ƙuna ta soyayya.

9. Wutar soyayya ta ruru ina jin daɗin ta,
Na ɗimauce, zuciyata na karkatsewa saboda rabuwa,
Na tsorata da takubban da ake wasawa,
Zunubaina suna sharuwa da wanda ke ceto na,
Gare shi ake fakewa ranar Kiyama.

10. Manzo amintaccen Allah mai godiya gare Shi,
Mai jinƙai mai haƙuri, mai raya Masallatai,
Mai tausayi, mai yawan godiya, mai gaggawa ga gyara,
Maɗaukaki, mai inganci, ƙarshen annabta,
Mayalwacin baiwa, mai ciyar da mutane, mai tsarki.

11. Mai ƙanshi, mai hikima, mu'ujiza ga al'umma,
Shugaba, mai ceton mutane, marabauci da girma,
Zamanin Manzon Allah ya samu sa'ada,
Linzamin ɗaukaka a hannunsa yake, gagara-gasa,
Ya tsarkaka, sai ayyukansa da ɗabi'unsa suka tsarkaka.

12. Tafarkin tsirar talikai, mai adalci,
Mai sakin fuska mai aikata alheri, mai sakin hannu,
Likitan talikai, mai shiryarwa, mai fushi a kan kafirci,
Mai maɗaukakiyar daraja, duk wani mai gaba da shi zai faɗi,
Mai iya magana, wanda ba shi da makamanci.

13. Bayyananne, ɗan Abdallah, mai fushi da shirka,
Yana da inuwar takobi dukkan maƙiya na ƙarƙashinta,
Mai taimakon talikai, daga gare Shi ake samun waraka,

Ni mai yawan zunubai ne, yaya Manzo zai dube ni?
Zatona da shi, in dai wa'azi bai min amfani ba.

14. Mai girma, mai ɗaukaka, mai riƙo da shiriya,
Mai rainon al'umma, ya mallaki duk wani kyau,
Mai yawan keɓantuwa, ba wanda zai riski matsayinsa,
Mai girma, duk wanda ya ƙi shi halakakke ne,
Mai yawan baiwa, mai aiwatar da maslaha ne.

15. Yana da fifiko a kan dukkan Manzanni,
Waɗanan dalilai ne a wurin masu lura,
Shi ne ya tafi al'arshin Allah ba wanda ya sani,
Da haskensa ne taurarin shaiɗanu suka ɓace,
Yana wasila daga wurin Ubangijin talikai.

16. Matabbaci mai baiwa a wurin Allah,
Abin bi masanin sirrin haƙiƙa,
Mai taimako, amintacce, jagoran mutane, mai jinƙai,
Da Jibrilu suka tafi, mutane na barci,
Mala'ikun Allah suna yi masa sallama.

17. Manzo, mai baiwa, mai bayyana hanyoyi,
Mai ceto abin so, mai aikata addini cikin yarda,
Mai yawan nasiha, mai kunya, shugaban mutane, mai sauƙi,
Mai baiwa, darajarsa ta bayyana ga mutane,
Shi za mu kewaye ranar da lamura za su yi wuya.

18. Mai yawan haƙuri, da fitinar duniya ya samu keɓantaccen kusanci, Mai yawan gaskiya, mai fasaha, mai kamalar mutane, mai ikhilasi, Tsarkakakken mutane, halinsa ba ya raguwa, Mai yafewa mai kyauta, ba za ku iya lissafo halinsa ba, Mai haske, mai turmuza hancin maƙiya.

19. Mai ƙunshe da alheri, ba ya rowa, Mai bugu da takobin Ubangiji, mai gabatar da alheri, Mai yawan dariya, amma ba ya wasa, Mai haske, saboda haka maganganunsa ba sa warware juna, Ina mai ƙishin begensa, bege kuma nasa ciwo.

20. Mai yawan tausayi, mai jinƙai, mai jalala, maɗaukaki,
Daga cikin Al'ajubansa shi ne ɓuɓɓugar ruwa,
Mai girman matsayi, mai ceton al'umma,

Mai daraja, dukkan matakai nasa ne,
Mai girma, mai haske daga wurin Ubangiji.

21. Mai wadataccen addini daga Allah wanda aka rina shi da jalala,
Mai agajin talikai, mai kaiwa ga aljanna,
Mai gwaggwaɓar baiwa, maras abin zargi,
Girgijen da ruwan sama ke koyi da shi,
Abin halattawa ganimar kafirai.

22. Kada ka manta ni, kai ake faɗa wa baƙin cikin talikai,
Babu wani Manzo face bayanka yake bi,
Alƙawarinka cikawa ne, ba ka saɓawa,
Kai ne mai ceto ranar tsayuwa,
Dukkan fanni na ɗaukaka kai ake ninninka wa.

23. Makusanci, manisanci, ba a halicci misalinsa ba,
Mai ƙarfi, ga sauƙin hali da tausayi,
Maganganunsa da almiski ake lulluɓewa,
Fadi gaskiya, ka ce ƙofarsa ba a rufewa,
Da shi ne mai ƙanƙanin aiki ko mai saɓo yake rataya.

24. Ɗan majidaɗin Ubangiji, wannan mai tsarkin,
Tafarkin tsira ba rikitarwa,
Mai nason baiwa, gare shi alheri yake da maɗaura,
Mai rige-rige ga alheri, rayuwa na begen sa,
Roƙona daga masoyina shi ne yaye baƙin ciki.

25. Mai kama da majidaɗin Ubangiji, daga nan ne asalinsa,
Mai ceton talikai, sonmu a gare shi yake,
Mai warkar da marasa lafiya, begen sa ya cika ciki,
Mai tausayinmu, ƙunar son sa ya cika ciki,
Mai kyakkyawan bayani, bai taɓa yin alfasha ba.

26. Mai bayyananniyar shiriya, ba wanda ya yi kamarsa,
Shi ne zaɓaɓɓe, kuɓutacce daga kowane aibi,
Farin wata, muna da matsayi tsakanin talikai,
Da shi ne Madina ta yi daɗi, kai tafi komai daɗi,
Shi ke wannan bigire mai ƙanshi.

27. Wasilarmu ita ce wadda ke zaune a turɓayar Ɗaiba,
Makaɗaicin matsayi, ba mu da wani ban da shi,
Abin so, mai yawan ƙauna, zuciyar so ta ƙonu da shi,

Mai alfarma da shi zuciyar soyayya ke ƙonuwa,
Mai hasken fuska, duhu ya yi haske da shi.

28. Manzo Ahmad na da alkhairai, da shi Talikai ke walwala,
Saboda girmansa kowa ke kama ƙafa da shi,
Da isra'insa ne kowa ya samu baiwa,
Don girmama shi tutocinsa ke keta sama,
Don ɗaukaka shi ne ake ba shi shafa'ar (ceton) a farko.

29. Shi ke gusar da Shaiɗan kafin ya yi makirci,
Nuni yake da hanyar Ubangiji domin shi mai kira ne,
Yana baiwa da kyauta, bai zamo mai jafa'i ba,
Ya tsaya a matsayin da ba wanda ya taɓa tsayawa,
Da shi ne duniya da lahira suka cika ga mai arziƙi.

Mun kammala da godiyar Allah da taimakonSa. Tsira da aminci su tabbata ga Manzon (saw), Amin.

# تنبيه الأمة

## على قرب هجوم أشراط الساعة

# FAƊAKAR DA AL-UMMA GAME DA KUSANTAR TASHIN KIYAMA

Na

**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

**Mai Fassara**

**Imam Musa Tanimu**

**Edita**

**Ahmed Abdullahi Sokoto (A.A. Sokoto)**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ........................................................................ 41
FASALI NA FARKO : Yawan Kwanakin Duniya .................................... 43
FASALI NA BIYU : Rashin Tabbas na Ranar Tashin Kiyama da Lokacin Sharaɗinta ........................................................................ 47
FASALI NA UKU : Alamomin Tashin Kiyama ....................................... 53
FASALI NA HUƊU : Fitowar Mahadi (rta) ............................................. 67
FASALI NA BIYAR : Fitar Dujal (la) ..................................................... 72
FASALI NA SHIDA : Dawowar Annabi Isah (as) .................................... 79
FASALI NA BAKWAI : Yajuju da Majuju ............................................. 85
FASALI NA TAKWAS : Ɗauke Alƙur'ani .............................................. 88
FASALI NA TARA : Fitar Dabba ........................................................... 90
FASALI  NA GOMA : Fitowar Rana Daga Mafaɗarta .............................. 93

## GABATARWAR MAWALLAFI

Na fara da sunnan Allah Mai rahma Mai jinƙai Allah Ya yi salati ga shugabammu, Muhammadu da Iyalansa da Sahabbansa da aminci mai yawa.

Bawa mai buƙatar rahamar Allah mai suna Usmanu ɗan Muhammadu, wanda aka fi sani da Ɗan-Fodiyo: Allah Ya yi masa rahama yana cewa:

"Mun gode wa Allah da Ya gabatar da sharuɗan tashin Kiyama kafin aukuwar ta. An yi haka ne, domin a faɗakar da jama'a da su daina barci kafin aukuwar tashin ƙiyama."

Salati da aminci su tabbata ga Muhammad cikamakon Annabta da Manzanci, wanda ya kasance aiko shi yana daga cikin farkon sharuɗan tashin ƙiyama. Salati ya tabbata ga Iyalansa da Sahabbansa, da jama'ar Da'awa da Jama'ar ijaba.

Bayan haka, wannan littafi mai suna ***Tanbihul-Ummati*** watau 'Faɗakar Da Al'umma A kan kusanta Sharuɗan Tashin Kiyama,' koda-yake wasu daga cikin alamun tashin ƙiyama, sun riga sun bayyana, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya bayar da labari.

Manufarmu a nan ita ce mu faɗakar da jama'a kan kusantar waɗannan alamomi, domin mu himmatar da su a kan kiyaye kawunansu da yawan tuba ga Allah, kafin a tsare tsakanin su da tuba, a kan abin da suka yi sakaci, domin su yi wa kawunansu ƙiyamu laili, su jefar da tsananin son bin duniya.

Su yi wa kansu tattali game da tashin ƙiyama kamar yadda aka yi alƙawarin zuwan tashin ƙiyama. Saboda alamun da suka zo, suna nuni ne da cewa duniya ta zo ƙarshe.

A wannan littafi na rubuta fasali guda goma ne daidai.

1. **Fasalin Farko**: Bayanin a kan ambaton maganar da ta zo game da yawan kwanakin duniya.
2. **Fasali na Biyu**: Ambaton rashin ayyana lokacin tashin ƙiyama da lokacin sharuɗanta.
3. **Fasali na Uku**: Ambaton abin da zai auku bayan waɗannan sharuɗan.
4. **Fasali na Huɗu**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da bayyanar Mahadi (rta).

5. **Fasali na Biyar**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da bayyanar Dujal (la).
6. **Fasali na Shida**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da bayyanar Annabi Isah (as).
7. **Fasali na Bakwai**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da bayyanar Yajuju da Majuju.
8. **Fasali na Takwas**: Ambaton Hadisan da suka yi bayani game da ɗaukewar Alƙur'ani
9. **Fasali na Tara**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da bayyanar dabba.
10. **Fasali na Goma**: Ambaton Hadisan da suka yi magana game da fitowar rana daga mafaɗarta.

## FASALI NA FARKO

### Yawan Kwanakin Duniya

Za mu gabatar da abubuwa guda uku a wannan fasali.

**Na Farko:** Bayani a kan cewa yawan zamanin duniya shekaru ne dubu bakwai (7000) kaɗai.

**Na Biyu:** Bayanin cewa Manzon Allah (saw) an aiko shi ne a shekarar dubu shida (6000) ta ƙarshe.

**Na Uku:** Kamar yadda Malam AbdulrRahman Suyuɗi ya ce: "Wannan al'umma, watau al'ummar Manzon Allah (saw) ba za ta wuce shekara dubu ɗaya da ɗari biyar ba (1500)"

Sai ni (Shehu Usmanu) na ce: "Dukkan muwafaka na ga Allah" Amma bayanin cewa duniya zamaninta shekaru ne dubu bakwai (7000), an sami ruwayar Hadisi daga Hakimu da Tirmizi sun ruwaito a cikin littafi mai suna **Nawadirul-Usuli** daga Abu-Huraira (rta) Manzon Allah (saw) ya ce a cikin Hadisin da yake magana game da 'yan-wutar Jahannama:

(وأطولهم مكثا فيها يعني في جهنم من يمكث فيها مثل الدنيا منذ يوم خلقت إلى يوم فنيت وذلك سبعة آلاف سنة).

***"Cewa wanda zai fi daɗewa a cikin Wutar Jahannama shi ne wanda zai zauna a cikinta, ya yi zama na lokacin zamanin duniya, daga halittar duniya zuwa ƙarshen duniya, watau shekara dubu bakwai (7000)."***

Bini Askir ya ruwaito, cewa Anas bini Malik (rta) ya ce: Manzon Allah (saw) ya ce:

كتب الله له عمر الدنيا سبعة آلاف سنة صيام نهاره وقيام ليله). (من قضى حاجة المسلم في الله

***"Duk wanda ya biya wa wani ɗan'uwa Muslim buƙatarsa saboda Allah, Allah Zai rubuta masa lada kamar mutumin da ya yi Azumi, ya yi ƙiyamul laili, yawan zaman duniya, watau shekara dubu bakwai (7000)."***

Bini Adiyyu ya ruwaito daga Anas (rta) ya ce Manzon Allah (saw) ya ce:

(عمر الدنيا سبعة أيام من أيام الآخرة).

***"Yawan zamanin duniya daidai yake da kwana bakwai, amma irin kwanakin lahira."***

Kuma Alƙur'ani ya ce:

﴿وَإِنَّ يَوْمًا عِندَ رَبِّكَ كَأَلْفِ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ﴾ الحج: ٤٧

***"Kwana ɗaya a lahira daidai yake da shekaru dubu ɗaya irin na duniya, waɗanda kuke ƙidayawa."*** **Alƙur'ani 22:47**

Bini Abu Hatim ya ruwaito a cikin Tafsiri daga Abdullahi bini Abbas (rta), "Tsawon zamanin duniya daidai yake da mako ɗaya na lahira, watau shekara dubu bakwai".

Kuma shekaru dubu shida sun riga sun wuce daga cikin dubu bakwan. Bini Abu Duniya ya ruwaito a cikin wani littafi mai suna **Kitabu Zammil Amal** daga Sa'idu bini Jubair ya ce: "Duniya kamar mako ɗaya ne daga makonnin lahira".

Abdullahi bini Humaidi ya ruwaito a cikin Tafsirinsa daga wani mutum Banasare ko Bayahude da ya musulunta ya ce: "Allah Ta'ala ya halicci sama da ƙasa, cikin kwana shida" Allah Ya ce:

﴿وَإِنَّ يَوْمًا عِندَ رَبِّكَ كَأَلْفِ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ﴾ الحج: ٤٧

***"Kwana ɗaya na lahira daidai yake da shekara dubu ɗaya na duniya."*** **Alƙur'ani 22:47**

Sai aka sanya zamanin duniya kwana shida irin na lahira, sai aka sa wata sa'a a cikin kwana na bakwai, a halin yanzu, kwanaki shida watau shekara dubu shida sun wuce saura kwana ɗaya watau shekara dubu ɗaya". Bini Is'haƙ ya ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas (rta) cewa: "Yahudawa suna wata magana wai kwanakin duniya, shekaru dubu bakwai ne, saboda haka, za a yi masu azaba ta kwana bakwai ne, duk shekara ɗaya kwana ɗaya. Saboda haka, bayan kwana bakwai an gama yi masu azaba." Sai Allah Ya saukar da Aya domin a ƙaryata su. Ayar ita ce:

﴿وَقَالُوا لَن تَمَسَّنَا النَّارُ إِلَّا أَيَّامًا مَّعْدُودَةً﴾البقرة: ٨٠

***"Suna cewa wuta ba za ta ƙona su ba, sai cikin yawan kwanaki kaɗan har zuwa...."*** **Alƙur'ani 2:80**

﴿هُمْ فِيهَا خَالِدُونَ﴾ البقرة: ٣٩

***"Za su dawwama a cikin wuta."*** **Alƙur'ani 2:39**

Bini Jarir ya fitar da wata magana da shi da Abu-Hatim, Abdullahi bini Humaid ya ruwaito daga Usman bini Za'idu cewa wani Bawan Allah mai himma wajen ibada, sai aka ce masa, "Ba ka yi wa kanka sauƙi ba." Sai ya ce; "Ina tambayar ku, nawa ne kwanakin duniya?" Sai suka ce masa shekara dubu bakwai Sai ya ƙara tambayar su ya ce: "Nawa ne tsawon tashin ƙiyama?"

Suka ce masa shekara dubu hamsin. Sai ya ce "Ina hasara ga mutumin da ya yi aiki na kwana bakwai, domin ya sami tsira daga wannan lokaci na shekara dubu hamsin."

Amma game da bayanin cewa Manzon Allah (saw) an aiko shi a shekaru dubu shida na ƙarshe, AbdurRahaman Suyuɗi ya ce a cikin littafi mai suna **Al- Kashafu An Mujawazati Hazihil Ummatil Alfu** cewa, Hadisan da ke magana, kan cewa Manzon Allah (saw) an aiko shi a ƙarshen shekaru na dubu shida sun nuna haka.

Yana daga cikin Hadisin da ya yi nuni da haka, wani Hadisi marfu'i, wanda Dhahak Ɗan Umar ya ruwaito da Juhniyi, ya ce, "Na yi wani mafarki sai na faɗawa Manzon Allah (saw), a cikin abin da na gani, sai na yi mafarki na gan ka ya Rasulul-Allah (saw) a kan wani minbari, a kan mataki na bakwai, kuma kai ne na ƙarshen bakwai, ɗin." Sai Manzon Allah (saw) ya fassara mafarkin da cewa:

(أما المنبر الذي رأيت فيه سبع درجات وأنا في أعلاها درجة فالدنيا سبعة آلاف سنة، وأنا في آخرها ألفا)."

***"Wannan mimbarin wanda ka gani yana da mataki bakwai, ka kuma ganni a can na ƙarshen mataki. Ma'anarsa ita ce, duniya za ta yi shekaru dubu bakwai ne kawai, ni kuma ina na ƙarshen dubun na bakwai ne."***

Baihaƙi ne ya fitar da shi a cikin littafi mai suna **Dala'ilu**; Suhaili ya zo da shi a cikin littafi mai suna **Raudha**. Sai Suhaili ya ce An ruwaito Hadisi mauƙufi daga Abdullahi bini Abbas (rta) ta hanya mai inganci. Ya ce: "Duniya kwana bakwai ne za ta yi, amma kowane kwana ɗaya yana daidai da shekara dubu."

An kuma aiko Manzon Allah (saw) a bakwai na ƙarshe ne. Abu Ja'afar Ɗabari ya inganta wannan, ya kuma ƙarfafa shi da wasu Hadisai.

Sai AbdurRahaman Suyuɗi ya ce kalimar cewa "Ni ne aka aiko a ƙarshen dubu bakwai." Ma'anar maganar shi ne mafi girman Addini a cikin bakwai na ƙarshe, domin maganar ta yi daidai da maganar cewa an aiko shi ne a ƙarshen dubu na shida. Da a ce an aiko Manzon Allah (saw) a cikin bakwan

farko ne da alamun tashin ƙiyama sun bayyana kamar Dujal da Isa da Fitar rana daga mafaɗarta da tuntuni sun bayyana kafin wannan lokaci tun shekaru ɗari (100), domin ya zama tashin ƙiyama zai auku a cikin dubun ƙarshen ke nan.

Amma ba a sami wata magana mai kama da haka ba, da ta nuna cewa ke nan abin da ya rage bayan shekara dubu ya fi shekara ɗari uku ke nan.

Sai ni (Shehu Usmanu) na ce yana daga cikin hujja mai ƙarfi cewa Manzon Allah (saw) an aiko shi ne a ƙarshen. Malam Wahab ya faɗa, wadda maganar za ta zo nan kusa, watau inda ya ce: "Duniya ta yi kamar shekara dubu biyar da ɗari shida (5600)."

Amma bayanin cewa wannan al'umma ba za ta wuce shekara dubu ɗaya da ɗari biyar (1500) ba.

AbdurRahaman ya faɗa a cikin littafi mai suna **Al-Kashfu,** abin da Hadisai suka yi nuni shi ne, wannan al'umma za su ƙetare shekara dubu ɗaya. Kuma ba za su iya ɗora ɗari biyar (500) a kan dubu ɗaya ba.

Abin da ya sa haka, Hadisai sun zo ta hanyoyi masu yawa cewa, yawan zamanin duniya shi ne dubu bakwai (7000), shi kuma Manzon Allah (saw) an aiko shi ne a ƙarshen dubu shida. An faɗa a cikin littafi mai suna a sama yanzu cewa, na gani a wani littafi mai suna **Al-Fitanu** na Imam Ahmad bini Hanbali ya ce; Ismail ya yi mana Hadisi daga AbdusSamad cewa ya ji Wahab yana cewa Duniya ta fi shekaru dubu biyar da ɗari shida (5600), na kuma san dukkan Sarakuna da Annabawansu.

Sai AbdurRahman Suyuɗi ya ce: "Wannan yana nuni da cewa, wannan al'umma za ta wuce shekara dubu da misalin shekara ɗari huɗu, amma Allah kaɗai ne Ya san daidai."

## FASALI NA BIYU

### <u>Rashin Tabbas na Ranar Tashin Kiyama da Lokacin Sharaɗinta</u>

A wannan fasali ma za mu kawo al'amura guda uku.

**Na Farko:** Lokacin tashin ƙiyama babu wanda ya san shi. Haka sanin sharuɗanta sai Allah kaɗai.

**Na Biyu:** Bayanin ɓacin maganar ayyana lokacin tashin Kiyama da sharuɗanta.

**Na Uku:** Bayani a kan cewa duk abin da Manzon Allah (saw) ya faɗa dole ne ya auku, saboda labarinsa gaskiya ne. Domin kada a jingina masa ƙarya. Ina faɗar cewa dukkan muwafaƙa tana ga Allah Shi kaɗai.

Amma bayani game da lokacin tashin ƙiyama da sharuɗanta, wannan babu wanda yake da yaƙini da shi sai Allah. An sami magana a wani Hadisi na Mala'ika Jibrilu (as) lokacin da Manzon Allah (saw) ya ce wa Jibrilu:

(ما المسؤول عنها بأعلم من السائل)

***"Wanda ake tambaya game da lokacin tashin ƙiyama, bai fi mai tambaya sanin lokacinsa ba."***

Muslim ya fitar da wannan Hadisi.

Haka nan Sha'abiyu ya ruwaito Hadisi: Jibrilu (as) ya gamu da Annabi Isah (as), sai Annabi Isah (as) ya tambayi Jibrilu: "Yaushe ne tashin ƙiyama?" Sai Jibrilu (as) ya kaɗa fukafukansa ya ce: "Wanda ake tambaya bai kai wanda ke tambaya sanin lokacinta ba." Wannan ilimi na sanin lokacin tashin ƙiyama ya fi ƙarfin sama da ƙasa. Tashin ƙiyama ba za ta zo ba, sai bagatatan.

Da za ka ce lokacin da aka tambayi Manzon Allah (saw) game da tashin ƙiyama, sai ya ce:

(ماالمسؤول عنها بأعلم من السائل)

***"Wanda ake tambaya bai fi mai tambayar sanin lokacin tashin ƙiyama ba."***

Wannan magana tana nuni ke nan bai san lokacin aukuwarta ba. Idan kuma, ka ɗauko maganar nan da ke cewa, Manzon Allah (saw) ya ce:

(بُعثت أنا والساعة كهاتين)

***"An aiko ni da lokacin tashin Kiyama, kamar haka, ya haɗa yatsunsa guda biyu."***

Wannan magana ta nuna kenan Manzon Allah (saw) ya san lokacin tashin ƙiyama. To, ta yaya za a haɗa wannan magana? Amsar wannan magana, ita ce kamar haka: A cikin Alƙur'ani aya ta nuna cewa:

﴿ قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ رَبِّي ﴾ الأعراف: ١٨٧

***"Ka Faɗa masu sanin tashin ƙiyama, Allah ne kaɗai Ya sani."***
**Alƙur'ani 7:187**

Saboda haka, Manzon Allah (saw) bai sani ba, balle waninsa.

Amma Hadisin da yake cewa:

(بعثت أنا والساعة كهاتين)

***"An aiko ni da tashin ƙiyama kamar haka, ya haɗa yatsu guda biyu."***

Ma'anarsa, ita ce Annabi (saw) shi ne Annabin ƙarshe, daga shi sai tashin ƙiyama. Ba wani Annabi: Tashin ƙiyama ne kawai, ke biye da shi, kamar yadda yatsa ɗan-Ali ke biye da yatsu na tsakiya, babu wata yatsa a tsakaninsu.

Wannan magana ba dole tana nunin cewa Manzon Allah (saw) ya san lokacin tashin ƙiyama ba ne, amma lokacinta ya kusa saboda sharuɗanta suna ta bayyana, ɗaya bayan ɗaya.

Allah Ta'ala Ya ambaci sharuɗanta inda Ya ce:

﴿ فَقَدْ جَاءَ أَشْرَاطُهَا ﴾ محمد: ١٨

***"Sharuɗan (Tashin Kiyama) sun zo."*** **Alƙur'ani 47:18**

Ma'anar wannan ya kusanto saboda kusancinsa ne, Malamai suka ce, ba a ruwaito wani Hadisi ko sharuɗanta, waɗanda suke nuna lokacin tashin ƙiyama tabbatacce ba.

Amma, rashin ingancin maganar shi ne abin da aka ruwaito, game da ayyana waɗannan sharuɗa, Kurɗabi ya ce, a cikin littafi mai suna **Attazkiratu Fil- Ulumi** "Gargaɗin da Manzon Allah (saw) ya yi game da ɓacin zamani da jirkitar addini da ɗaukewar amana, wanda ya fi gaban a faɗe su da Hadisai na ƙarya game da tashin ƙiyama."

Katada ya ruwaito daga Anas bini Malik (rta), daga Manzon Allah (saw);

(إن في سنة مائتين يكون كذا وفي عشر ومائتين يكون كذا وكذا وفي العشرين كذا وفي الثلاثين كذا وفي الخمسين كذا قال وفي الستين والمائتين تعكف الشمس ساعة فيموت نصف الإنس والجنّ)

***"A cikin shekara ta ɗari biyu (200), wani abu zai auku, a cikin shekaru na ashirin ko talatin ko Hamsin, abu kaza da kaza zai auku, a cikin shekara ta ɗari biyu da sittin (260), rana za ta yi kusufi na kamar awa ɗaya, sai rabin mutanen duniya da Aljannu su rasu."***

Shin wannan abu ya auku? Kuma wannan lokacin ya riga ya wuce. Kuma wannan abin ya kamata ya game ko'ina ne? Kodayake, wasu abubuwan da aka faɗa sun auku, a wasu ƙasashe na duniya, kamar yadda kusufin rana ko na wata yana iya aukuwa a wani sashen duniya, amma bai auku a wani sashin ba.

Kuma yana nuna rashin ingancin Hadisin, saboda shekaru ɗari biyu (200) sun wuce daga rasuwar Manzon Allah (saw) Kuma a zamanin Manzon Allah (saw), ba a fara rubuta tarihin shekaru da kwanan wata ba, sai zamanin halifancin Umaru. To, ta yaya za a ce da shekara kaza, zuwa shekara kaza, abu kaza zai auku? Bayan ba tarihin watanni da kwanaki.

Yana daga cikin Hadisai marasa inganci, wanda Abu Sa'idu Al-khudiri ya ruwaito daga Manzon Allah (saw) yana cewa:

(إذا كانت سنة تسع وتسعين وخمس مائة يخرج المهدي في أمتي على خلاف من الناس يملأ الأرض عدلا كما ملأت ظلما يرضى عنه ساكن السماء وساكن الأرض ويفتح الله كنوز الأرض وينزل من السماء قطرها ويخرج من الأرض ثمرها ويزرع الزارع صاعا فيصيب مائة صاع ويذهب القلاء والقحط والجوع من الناس...)

***"Idan aka kai shekaru ɗari biyar da tis'in da tara (599) Mahadi zai bayyana a cikin jama'a, Zai cika ƙasa da adalci; kamar yadda ta cika da zalunci, halittar da ke sama da ƙasa, za su yarda da shi. Allah Zai buɗe taskar ƙasa, a sami ruwa daga sama, ƙasa ta fitar da amfaninta, har ya kai da za a shuka tiya ɗaya, ana iya samun tiya ɗari. Yunwa da fari da wahala su tafi su bar jama'a..."***

Har dai zuwa ƙarken Hadisin.

Sai Kurɗabi ya ce, "Duk abin da aka faɗa ga Hadisin da ya gabata, kamar Hadisin Huzaifa da waninsa, bai inganta ba, saboda an ayyana tarihin shekaru da watanni."

Kuma shekarar da aka ambata watau (599) ta riga ta zo, ta wuce, kuma wani abu mai kama da haka bai auku ba. Sannan ya ci gaba da cewa abin da ya kamata a faɗa game da wannan babi shi ne: "Cewa abin da Manzon Allah (saw) ya faɗa na fitinu. Waɗannan kuma sun auku. Amma ayyana lokacin aukuwarsu yana buƙatar ƙaƙƙarfar hujja."

Kamar lokacin tashin Kiyama ne ba wanda ya san watan ko shekarar da zai auku. Sai dai an san ranar Juma'a ce, amma wace Juma'a ce? Ba wanda ya sani sai Allah Shi kaɗai Wanda Bai da abokin tarayya. Haka nan, sharuɗan tashin ƙiyama su ma ba wanda ya san lokacin zuwansu sai Allah. A nan ne zancen Kurɗabi da ke cikin littafin **Attazkirah** ya ƙare.

Ya yi wata magana kuma a wani wuri a dai cikin wannan littafi, Abul-Hassan Ahmadu bini Ja'afar ya ce: A cikin littafi mai suna **Al-Malahimu** wato abubuwan da suka auku, ko kuma za su auku wanda aka ɗauko daga cikin littafin **Daniyal**. Akwai na ƙarya wanda abin da ke ciki na maganar yana warware juna; kuma zindiƙawa suna amfani da shi, wajen ƙaryata Manzon Allah (saw). Kamar maganar da suke cewa:

(إن في سنة ثلاث مائة يظهر الدجال من يهودية أصبهان).

***"A shekara ta Ɗari Uku (300), Dujal zai bayyana a garin Asbahan."***

Wannan abin kunya ne da aka ɗauko cikin Isra'ilanci kuma daga wajen Daniyal ne yake.

A cikin littafi mai suna **I'itisam** cewa Abdullah bini Abbas (rta) ya ce: "Yaya za ku riƙa tambayar Banu-Isra'ila game da wani abu, bayan littafin da aka saukar wa Annabinku (saw) ya ce mana sun canja littattafansu. Sun rabuta ra'ayinsu da hannunsu. Littafi na ƙarya kuma suka ce daga wajen Allah yake domin neman duniya?" "Saboda haka ilimi ya zo maku kan cewa kar ku tambaye su wani abu na harkar addininku." Ɗan Dihyat (rta) ya ce: "Ta ya ya mutum zai yarda da maganar mutanen da suka yaudari Allah, suka ƙaryata Shi, suka yi maSa kafirci, suka yi girman kai, suka yi fajirci za a yarda da maganarsu?" Watau Yahudu da Nasara.

Sai na ce (Shehu Usmanu) rashin ingancin maganarsa, lokacin tashin ƙiyama ya yi daidai da abin da ke cikin littafi mai suna **Al-Fitaru** wallafar Nu'aim bini Hammad inda ya ce: "Abu Yusuf Al-Mukdasiyyu ya yi mana Hadisi shi ne mutumin garin Kufa, ya ji Hadisin daga Muhammad ɗan Hannafiyya yana cewa: "Mahadi zai bayyana a shekara ta dubu ɗaya da ɗari biyu (1200) bayan hijira."

Akwai kuma wani Hadisin wanda Nu'aim ya fitar daga Ja'afar yana cewa: "Zai bayyana a shekarar dubu ɗaya da ɗari biyu (1200)". Haka nan, Abu-katili yana cewa: "Akwai ijima'i cewa, Mahadi zai bayyana a shekarar dubu ɗaya da ɗari biyu da hudu (1204) bayan hijira."

Kuma dukkan waɗannan shekaru sun auku, amma har yanzu Mahadi bai bayyana ba. Saboda haka, wannan ya nuna ke nan, sanya lokaci abin da bai inganta ba ne.

Kodayake ni (Shehu Usmanu) na yi wannan hasashe na rashin ingancin sanya lokaci, kodayake ban ga wani Malami da yake musun sanya lokaci ga tashin ƙiyama ba. Kodayake AbdurRahman Suyuɗi ya zo da shi a cikin littafi mai suna- **Urful Wardi Fi Akhabaril Mahdi** da littafin **Kashfu** inda ya ke cewa na gani a cikin littafin **Al-Fitanu** wallafar Nu'aim bini Hammad inda ya ce: "Dukkan shekarun da aka faɗa sun wuce, amma Imam Mahadi bai bayyana ba. Amma AbdurRahman Suyuɗi da Nu'aim, ana iya yi masu hanzari, saboda bai auku a shekarun da suke raye ba, domin sun rasu kafin lokacin. Saboda haka, idan sun yi hukunci da ingancin Hadisin, ba laifi ba ne, saboda kamar gaibu na zamaninsu ne."

Amma ni (Shehu Usmanu) an haife ni ne, na san waɗannan zamuna. Kuma na ga ni kuma na samu Mahadi bai bayyana ba a waɗannan shekarun da aka faɗa, saboda haka ne nake magana da rashin ingancin wannan magana. Kuma labari ya gabata cewa, malamai ba su ruwaito wani Hadisi daga Manzon Allah (saw), wanda ya ayyana wani lokacin tashin ƙiyama, ko lokacin bayyanar wani sharaɗi ba. Saboda haka duk abin da aka ruwaito, ko aka rubuta ko aka ce in ji daga bakin jama'a na ayyana lokacin tashin ƙiyama, ko lokacin aukuwar alamominta ba gaskiya ba ne. Ba shi da wani asali, daga Manzon Allah (saw). Haka nan kuma, abin da masana Hisabi suka yi magana, saboda ayoyi guda biyu.

**Na Farko:**

﴿فَقَدْ جَآءَ أَشْرَاطُهَا﴾محمد: ١٨

***"Sharuɗan tashin ƙiyama sun zo."*** **Alƙur'ani 47:18**

**Na Biyu:**

﴿أَتَىٰٓ أَمْرُ ٱللَّهِ فَلَا تَسْتَعْجِلُوهُ﴾النحل: ١

***"Al'amarin Allah ya zo, ba sai kun nemi zuwansa da gaggawa ba."***
**Alƙur'ani 16:1**

Da makamatansu, ba a bin jingina ba ne. Saboda ba su da asali daga Manzon Allah (saw). Kuma abin da ya bayar da labarin aukuwarsa, ba makawa zai auku, saboda haka labarinsa bai saɓa wa juna ba.

Saboda faɗin gaskiya wajibi ne game da haƙƙin Manzannin Allah. Daga nan, mun sani duk abin da Annabi ya faɗa gaskiya ne, zai kuma auku. Idan lokacin da aka ruwaito Hadisin, an sanya ma abin lokaci, to, sai lokacin ya zo, amma abin bai auku ba. To, mun sani ke nan labarin ko Hadisin bai da asali. Saboda an ruwaito daga Manzon Allah (saw), cewa:

(سيكذب علي)،

***"Za a riƙa yi mani ƙarya."***

Kamar yadda malamai suka faɗa (rta). A cikin muƙaddimar littafin Sahihu Muslim yana cewa:

(يكون في آخر الزمان دجالون كذابون يأتونكم من الأحاديث بما لم تسمعوا أنتم ولاآباؤكم، وإياكم وإياهم لايضلونكم ولايفتنونكم).

***"A ƙarshen zamani, za a sami Dujal maƙaryata, za su zo maku da Hadisin da ba ku sani ba, haka nan iyayenku, kashedinku da su, kada su fitine ku ko su ɓatar da ku."***

AbdurRahaman Suyuɗi ya ce a cikin sharhin littafin mai suna **Alkawakib** yana daga cikin Hadisin da ake tabbatarsa da rashin ingancinsa idan aka fahinci cewa akwai ɓarna a cikinsa, kuma bai iya karɓar tawili ba, sai a yi watsi da shi, saboda isma na Manzon Allah (saw) daga faɗin ɓarna.

# FASALI NA UKKU

## Alamomin Tashin Kiyama

Za mu kawo abubuwa guda biyar a wannan Fasali na Uku.

**Na Farko:** Bayanin bayyanar munanan ɗabi'u waɗanda ake ƙidaya su cikin alamun tashin ƙiyama kamar yadda Hadisan Manzon Allah suka bayyana.

**Na Biyu:** Bayanin aukuwar girgizar ƙasa ta alamun tashin ƙiyama kamar yadda ya zo a cikin Hadisai

**Na Uku:** Bayanin aukuwar kusufi, wanda aka ƙidaya shi cikin alamun tashin ƙiyama, kamar yadda suke a cikin Hadisai.

**Na Huɗu**: Bayanin fitar wuta daga ƙasar Hijaz, yana daga cikin abin da aka ƙidaya cikin alamun tashin ƙiyama, kamar yadda yake a cikin Hadisai.

**Na Biyar:** Bayanin aukuwar fitinu, kamar yadda aka ƙidaya su cikin alamun tashin ƙiyama kuma kamar yadda Hadisai suka faɗa.

**a) Munanan Ɗabi'u**

Amma bayanin munanan ɗabi'u waɗanda ake ƙidaya su cikin alamomin tashin ƙiyama, kamar yadda Hadisai suka zo da su, wajen magana a kansu bayan sun tabbata, kamar matsa wa kai ne, marar amfani, kamar yadda Kurɗabi ya faɗa a cikin littafin **Attazkira**. Kuma ya ce kodayake ya zama dole a faɗe ta, domin jama'a su sami tabbas, kuma su san gaskiyar mu'ujizar Manzon Allah (saw) da kuma gaskiyar abin da ya faɗa.

An ruwaito a Sahihul Bukhari cewa: "Yana daga cikin alamomin tashin ƙiyama a sami ƙarancin ilimin addini jahilcin kan harkar addini ya yi yawa da yawan zinace-zinace da yawan mata fiye da maza, har ya zama namiji ɗaya yana daidai da mata hamsin (1:50)."

Ka ga irin waɗannan abubuwa, suna aukuwa a ƙasashen duniya, kamar yadda suka zo a cikin Hadisai, kuma yadda Kurɗabi ya faɗa a **Attazkira**.

Ya yi wata magana game da yawan mata a kan maza. Wannan abu ya auku a ƙasar Andulus (Spain). Abu Nu'aim ya faɗa a Hadisin Makahul daga Huzaifatul Yamani inda ya ce; "Manzon Allah (saw) ya ce: "Tashin ƙiyama yana da alama" sai aka tambaye shi mene ne alamar? Sai ya ce fasiƙai su shugabanci masallatai. Mutanen banza sun fi mutanen kirki yawa da ƙarfi (na kuɗi)." Waɗannan abubuwa mutane sun gan su ƙuru-ƙuru.

Yana daga cikin munanan ɗabi'u bayar da shugabanci ga mutumin da bai cancanta ba da manyan gine-gine. Kamar yadda Bukhari ya ruwaito daga Abu-Huraira (rta) ya ce: "Wata rana muna tare da Manzon Allah (saw), yana mana wa'azi, sai wani Baƙo ya zo ya ce yaushe ne tashin ƙiyama? Sai Manzon Allah (saw) ya ci gaba da maganarsa, sai wasu suka ce ya ji abin da ya ce, ba ya son abin da ya faɗa ne. Wasu kuma suka ce a'a bai ji ba, sai da ya gama jawabinsa. Manzon Allah (saw) ya ce:

(أين السائل عن الساعة؟)

***"Ina mai tambayar yaushe ne tashin ƙiyama? Idan aka tozartar da amana, to, ku saurari tashin ƙiyama."***

Sai ya ce:

(إذا ضيعت الأمانة فانتظر الساعة).

***"Yaya ne tozartar da amana, ya Manzon Allah?"***

Sai ya ce:

(إذا أسند الأمر إلى غير أهله فانتظر الساعة).

***"Idan aka ɗauki shugabanci aka bai wa wanda bai cancanta ba, to, ku saurari tashin ƙiyama."***

Hadisi ya zo daga Bukhari daga Abu Huraira: Manzon Allah (saw) ya ce:

(إن الساعة لاتقوم حتى يتطاول الناس في البنيان).

***"Ba a tashin ƙiyama sai mutane sun tsawaita manyan gine-gine."***

Waɗannan Hadisai guda biyu na Bukhari sun bayyana ƙuru-ƙuru. Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** Malamammu (rta) sun ce abin da Manzon Allah (saw) ya ce ya bayyana, ana bayar da shugabanci ga mutanen da ba su cancanta ba. Mutanen banza (mashaya da mazinata) sun zama su ne shugabanni a gari, sun kwashe dukiyar jama'a sai gine-gine suke yi, kamar yadda dai yake a wannan lokacin nan namu.

Bayyanar Dujal yana daga cikin alamun Tashin Kiyama. Kurɗabi ya ce a cikin littafin **Attazkira** Hadisin Huzaifa ya faɗi yawan Dujal da za su zo, inda ya ce Manzon Allah (saw) ya ce:

(يكون من أمتي دجالون كذابون سبعة وعشرون، منهم أربع نسوة وأنا خاتم النبيين لانبي بعدي).

***"Za a sami Dujal cikin al'umma ta, na ƙarya, guda ashirin da bakwai (27), akwai mata guda huɗu daga cikinsu, ku sani ni ne cikamakon Annabawa, babu Annabi bayana."***

Abu Nu'aim ya fitar da shi. Alƙali 'Iyal ya ce; "Waɗannan sun bayyana, da ma a ce za mu ƙidaya waɗanda suka yi da'awar Annabta a zamanin Manzon Allah (saw) zuwa yanzu suka shahara, kuma jama'a suka bi su a kan halinsu na ɓata wannan adadi zai samu". Duk wanda ya yi nazari a cikin littafin tarihi zai san wannan.

Yana daga cikin alamun tashin ƙiyama gabatar da Ajamawa ga shugabanci a kan Larabawa a garin Musulunci, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya ce:

(ويل للعرب من شر قد اقترب).

***"Ina tausaya wa Larabawa, saboda aukuwar wani sharri a gare su da yake kusa da su."***

Bini Arafat ya ce abin da ake nufi shi ne baƙin cikin da zai same su.

Manzon Allah (saw) ya ba da labari cewa:

(ويل للعرب من شر قد اقترب)،

***"Na tausaya wa Larabawa bisa abin da zai same su."***

Na abin da zai zo bayansa da abin da Larabawa za su aukawa na bala'i da yaƙe-yaƙe.

Wannan ya auku, lokacin da aka ƙwace masu mulki da Daula da Dukiya, suka koma ga Turkawa (Turkey) da Ajamawa, suka watsu a daji, bayan sun zamo shugabannin duniya, saboda albarkar Manzon Allah (saw) da abin da suka samu na kayayyakin duniya da Musulunci saboda wasunsu sun yi butulci, suka yi ta kashe mutanensu da ƙwace masu dukiya, sai Allah ya ƙwace mulkinsu: Ya ba wasunsu-Turkey da Farisawa.

Yana daga cikin ɗabi'un da aka ambato daga Zarnab bin Burtamala, wanda Annabi Isah (as) ya yi ma wasici. Abubakar Haɗibu ya faɗa, mai suna Ahmad Bini Aliyyu daga AbdurRahamn bini Ibrahim Rasiyyi ya ce; Malik bin Anas ya ce daga Nafi'u daga Abdullahi bini Umar ya ce Umaru bini Khattab, ya rubuta wa Sa'ad bini Abu Waƙƙas (rta) lokacin sa, Sa'ad na Jagoran rundunar sojan Musulmi a ƙasar Iraƙi, daidai Kadisiyya, cewa ya aika da Falalatu bini Mu'awiya Al'ansari, ya jagoranci runduna zuwa garin Khalwani na ƙasar Iraƙi, domin su kai hari a cikin garuruwansu.

Sai Sa'adu ya tura Falalatu da sojoji ɗari uku (300), har suka isa garin Khalwani, suka kai hari a garuruwansu, Allah ya ba su nasara, suka sami ganima ta dukiya da bayi, suka dawo. A hanya lokacin La'asar, lokacin rana ta kusa faɗuwa, sai Falalatu ya ajiye ganima a gefen wani dutse, sai ya yi kiran sallah. Lokacin da Falalatu ya ce; Allahu Akbar, Allah Akbar, sai ya ji an amsa masa daga wajen dutsen da ya aje ganima kamar haka: "Kalima ce ka faɗa ta girmama Allah."

Lokacin da Falalatu ya ce; Ash - hadu an - la'ilaha illalah - sai aka amsa masa da cewa kamar haka: "Kalima ce mai tsarki. Ka faɗa ya Falalatu."

Lokacin da ya ce Ash-hadu Anna Muhammadar Rasulullahi, sai Falalatu ya ji an amsa masa da cewa; "Wannan shi ne mai gargaɗin da Annabi Isah (as) ya yi mana albishir da shi, kuma a cikin al'ummarsa ne tashin alƙiyama zai auku." Sai Falalatu ya ce; Hayya alal-salat, sai aka amsa masa da cewa. "Al-Jannah ta yi daɗi ga wanda ya je wajen sallah, ya yi muwazaba a kanta." Sai falalatu ya ce; Hayya alal-Falah, sai ya ji an amsa masa da cewa: "Duk wanda ya amsa wa Manzon Allah (saw) ya tsira, kuma shi ne mai wanzuwa ga al'ummar Manzon Allah (saw)."

Lokacin da Falalatu ya ce; Allahu Akbar.... Sai aka amsa masa da cewa; "Ka tsarkake Allah gaba ɗaya, ya Falalatu, saboda haka ka haramta jikinka daga shiga wuta." Lokacin da ya gama kiran sallah, sai muka miƙe muka ce; "Wane ne ke amsa mana? Allah ya ji-ƙanka! Mala'ika ne? Ko ko mazaunin dutse ne na Aljani, ko ko wani bawan Allah ne? Kamar yadda muka ji sautinka na nuna mana surarka; saboda masu wannan buƙata jama'ar, Allah ne; Jama'ar Manzon Allah ne jama'ar Umar (rta) ne."

Mai ruwaya sai ya ce: "Sai dutse ya tsage, sai ga kan mai maganar nan gashin kansa da na gemunsa sun yi fari fat, yana sanye da tsumma na fata sai ya gaishe su da kalimar; "**Assalamu alaikum wa rahamatul-lahi wa barkatuhu.**" Sai su ma suka amsa masa da cewa; "**Wa'alaikas-salam wa rahamatullahi wa barkatuhu**, ko kai wane ne, Allah Ya gafarta Malam?"

Sai ya ce "Ni ne Zarnab bini Bartamala, wasiyyar Bawan Allah na kirki ɗan Maryam (as). Ya Umurce ni da in zauna a kan wannan dutse, ya yi mani addu'a da tsawon rayuwa har zuwa lokacin da zai sauko daga sama, ya kashe al'adu, ya karya gumaka, ya kawar da kansa game da abin da Nasara ke haɗa shi da shi. Tun da saduwa da Manzon Allah (saw) ta kucce mani, to, isar mani da gaisuwata ga Umar (rta).

Ku faɗa wa shi, Umar, ya shirya ya dage, domin tashin ƙiyama ya kusa, ku faɗa wa shi, Umaru, abin da na faɗa maku. Idan wannan abu ya

bayyana a cikin al'ummar Manzon Allah (saw), ku nemi mafita, ku nemi mafita. Ɗabi'un kuwa su ne kamar haka. Idan maza suka biya buƙata da maza 'yan'uwansu a halitta; idan mata suka biya buƙata da mata; idan aka shiga taƙama da dangin da ba naka ba; idan aka shiga taƙama da iyayen gidan da ba naka ba, idan manya ba sa tausayin ƙananansu; idan kuma ƙananansu ba sa girmama manyansu; idan kuma aka bar umurni da kyawawan ayyuka, ba a ayyuka da shi; idan aka aikata munanan ayyuka, ba a yin hani a kan munanan ayyukan ba.

Kuma Malamai suka mayar da iliminsu na neman kuɗi; ga yawan rashin ruwan sama (fari); idan kuma yara suka zama damuwa ga iyayensu; sai manyan manara na masallatai; suka ƙawata littafi (Alƙur'ani ), suka yi manyan gine-gine; suka bi son sha'awa; suka sayar da addini suka karɓi duniya; suka mayar da zubar da jini abu mai sauƙi; kuma suka yanke zumunci. Kotu ta zama sai mai kuɗi shi ke da nasara; suka mayar da cin riba a gare su mai sauƙi; suka mayar da girma ga masu kuɗi ne kawai; idan mutum ya fita daga gida, bai gai da kowa sai mai kuɗi; kuma mata suka shiga hawan abin hawa mai tsada." Bayan ya gama wannan jawabi sai muka neme shi muka rasa.

Sai Falalatu ya rubuta duk bayanin ga Sa'adu bin Abu Waƙƙas. Shi kuma Sa'adu ya rubuta wa Umar bini Khattabi (rta). Sai Umar ya rubuta wa Sa'ad, ya ce, "Ya Sa'adu, na haɗa ka da Allah, ka tafi wajensa da wanda ke tare da kai, na Muhajirun da Ansar, ku je ku same shi a dutsen. Idan kun same shi, ku ce masa, Umar na gaishe shi. Kuma ku faɗa masa cewa almajiran Annabi Isah (as) sun sauka a wannan dutse a ƙasar Iraƙi."

Mai ruwayar Hadisin sai ya ce sai Sa'ad bini Abu-Waƙƙas ya fita tare da Muhajirun da Ansar kamar su Dubu Huɗu (4000), har sai da suka kai wajen dutsen; suka yi kwana arba'in. Kowace sallah sai sun yi kiran sallah, amma bai amsa masu ba. Mun sani a halin yanzu duk ɗabi'un da Zarnab ya faɗa sun zo a wannan zamani.

Ya zo a ruwayar Huzaifa bini Yamani (rta) Abu Nu'aim ya ruwaito daga Hadisin Huzaifa bini Yamani (rta), inda ya ce, Manzon Allah (saw) ya ce:

(من علامات اقتراب الساعة إثنان وسبعون خصلة إذا رأيتم الناس أماتوا الصلاة وأضاعوا الأمانة وأكلوا الربوا واستحلوا الكذب واستخفوا بالدماء واشتغلوا بالبناء وباعوا الدين بالدنيا وتقطعت الأرحام ويكون الحكم ضعفا والكذب صدقا والحرير لباسا وظهر الجور وكثر الطلاق وموت الفجأة وأتمن الخائن وصدق الكاذب وكذب الصادق وكثر القذف وكان المطر قيظا والولد غيظا وفاض الأيام فيضا وغاض الكرام غيضا وكان الأمراء فجرة والوزراء كذبة والأمناء خونة والفقراء ظلمة والقراء فسقة إذ لبسوا مسرق الضأن وقلوبهم أنتن من الجيفة وأَمَرُّ من الصَّبِرِ يغشهم الله

**فتنة يتهاوكون فيها كما تهاوك اليهود الظلمة ويظهر الصفراء** (يعني الدنانير) **وتطلب البيضاء** (نعني الفضة) **وتكثر الخطايا وتبقل الأمراء وحُلِّيت المصاحف وصوت المساجد وطولت المنار وأرخيت الستور وشربت الخمور وعطلت الحدود وولدت الأمة ربتها وترى الحفاة العراة قد صاروا ملوكا وشاركت المرأة زوجها في التجارة وتشبه الرجال بالنساء والنساء بالرجال وحلف بالله وشهد المرء من غير أن يستشهد وسُلم للمعرفة وتفقه لغير الدين وطلبت الدنيا بعمل الآخرة واتخذ المغنم دولا والأمانة مغنما والزكاة مغرما وكان زعيم القوم أرزلهم وعق الرجل أباه وجفا أمه وبر صديقه وأطاع زوجته وعلت أصوات الفسقة في المساجد واتخذ القينات والمعازف وشرب الخمور في الطرق واتخذ الظلم فخرا وبيع الحكم وكثرت الشره واتخذ القرآن مزامير وجلود السباع صفاقا والمساجد طرقا ولعن آخر هذه الأمة أولها فليرتقبوا عند ذلك ريحا حمراء وخسفا ومسخا).**

***"Yana daga cikin alamun kusantar alƙiyama, idan abubuwa guda saba'in da biyu suka bayyana. Idan kuka ga mutane sun ƙyale yin sallah; sun tozartar da amana; suka ci riba; suka halasta ƙarya, zubar da jini ya zama mai sauƙi ga Jama'a; suka shagaltu da gine-gine; suka sayar da addini; suka sayi duniya,;suka yanke zumunta; ba hukunci ko hukuma mai iko; aka ɗauki ƙarya ta zama gaskiya; aka ɗauki sanya kayayyakin ado na alhariri; zalunci ya yi ƙarfi a bayan ƙasa; mutuwar aure ta yawaita; da yawan mutuwar farat ɗaya; da yawan ha'inci; da gasgata maƙaryata da ƙaryata masu gaskiya da yawan ƙazafi da ƙarancin ruwan sama da taɓarɓarewar tarbiyyar yara da yawan gudun kwanaki da ƙarancin mutane masu kyauta da zamowar shugabanni azzalumai, mashawartansu maƙaryata, ga yawan cin amana, talakawa kuma na goyon bayan zulunci; Malamai kuma ga ƙin gaskiya; masu hali kuma ga kece raini da kayayyakin ƙawa; zuciyarsu tana wari kamar mushe; zuciyarsu tafi guna (maɗaci) ɗaci; suna cikin fitinu koyaushe, kamar yadda Yahudawa suke. Sauran sun haɗa da: tsananin neman tara duniya, ga yawan aikata laifi; ga zaluncin shugaba, ga ƙawata littafi, ga yawan hayaniya a masallatai, ga yawan gina manyan manara na Masallatai, ga ɓuyar shugabanni sai na kusa da su kaɗai, ga yawan shan giya, ga yawan jefar da hukuncin Allah; Baiwa ta zama ta haifi shugabanta da zamowar talakawa masu tafiya ba takalmi, huntayen mutane su zama su ne sarakuna, mata su yi gogayya da mazansu a kasuwanni ko a ofisoshi, maza su yi kama da mata wajen tufafi, mata su yi kama da maza wajen tufafi, ga yawan rantsuwa a kan ƙarya da bayar da shaida a kan ƙarya da shagaltuwa da ilimin da ba na addini ba da yawan bin ko son duniya da aikin da ya kamata ya yi ya kasance na lahira ne da cinye ganima da cin amana da hana zakka da shugabantar da ƙasƙantacce da rashin biyayya ga iyaye da bin ra'ayin aboki ra'ayin da bai da kyau da bin ra'ayin da bai da kyau na matarsa da shugabantar da fasiƙai harakar masallaci da yawan tara kayayyakin ado da kayayyakin ƙidaya da yawan shan giya a kan hanya wato a bayyane, ga yawan taƙama da zalunci, ga hukunci na zalunci, ga yawan haɗama da canja***

***sautin Alƙur'ani ya zama kamar na kiɗa da yawan ado, har da sanya fatu na Zaki, a mayar da Masallatai kamar hanya da kasancewar al'umma ta ƙarshe tana zagin al'umma ta farko; Duk lokacin da aka ga waɗannan abubuwa sun auku, to sai a saurari iska jawur kamar wuta da yawan kusufi da shafe halitta."***

Waɗannan ɗabi'u da aka faɗa a wannan Hadisi: Dukkansu sun auku. Kurɗabi ya ce a cikin littafin nan mai suna **Attazkira** dukkansu sun bayyana sai dai kalimar nan da ta ce fatar zaki Al-Jauhar ya ce, kalimar Assifak yana nufin fata mai taushi wadda take ƙasan gashi.

**b) Girgizar Kasa**

Amma game da yawan girgizar ƙasa, wadda tana daga cikin alamun tashin ƙiyama, kamar yadda Hadisai suka faɗa, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya ce lokacin da yake bayani game da sharuɗan tashin Kiyama cewa, girgizar ƙasa za ta yi yawa, kamar yadda Bukhari ya ruwaito daga Abu-Huraira (rta). Haka nan ma Abul-Farhi bini Al-Jauzi ya ce, wannan irin girgizar ƙasa ta auku a ƙasashen Ajamawa da yawa. Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**. Wannan girgizar ƙasa mai tsanani mun gan ta a ƙasar Andulus (Spain) Bini Jauzi ya ɗauko wani labarin girgizar ƙasa a Misra, a zamanin Sarki Almuɗi'u Lillah, har sai da manyan garuruwa suka ɓace; mutane suka koma cikin Hamada suka zauna. Irin wannan mummunar girgizar ƙasa da mutum kamar dubu ɗari (100,000) suka rasu, ya auku a garin Tabriz, har sai da mutane dole suka koma ga Allah.

**c) Kusufi**

Amma game da aukuwar kusufi wanda aka lissafa daga cikin alamun tashin ƙiyama, kamar yadda ya zo a cikin Hadisai, kamar yadda aka faɗa a Hadisin Huzaifa (rta) inda ya ce;

(إن الساعة لاتكون حتى ترى عشرة آيات: خسف بالمشرق، وخسف بالمغرب، وخسف بجزيرة العرب، والدخان، والدجال، ودابة الأرض، ويأجوج ومأجوج، وطلوع الشمس من مغربها، والنار تخرج من قعرعدن ترحل الناس).

***"Tashin ƙiyama ba zai auku ba, sai ka ga abubuwa guda goma: kusufi a Jazirar Larabawa da HayaƘI da Dujal da Dabba a bayan ƙasa mai Magana da Yajuju da Majuju, bayyanar rana daga mafaɗarta, bayyanar wuta, daga cikin garin Addan tana bin mutane."***

Muslim ya fitar da wannan.

Wannan kusufi da aka faɗa cikin Hadisin nan, ya auku, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya faɗa.

Abul-Faraji bini Jauzi ya ce: Ya auku a ƙasar Ajamawan Iraƙi Kusufi mai tsanani har ya yi sanadin rasuwar mutane masu yawa. Kurɗabi ya ce; "Haƙiƙa, mun sami labari daga shehunnammu, an yi wani kusufi a ƙasar Andulus (Spain) a garin da ake kira Kaɗaraɗanda, inda wani dutse ya faɗo wa garin, ya nutsar da shi.

Ya kuma ce a wani gari da ake kira Tursat cikin Jihar Barkat, girgiza ta shafe ta inda dukkan garin ya nutse, sai 'yan kaɗan ne suka iya kuɓuta. Haka nan Abdul-Wahab Sha'arani ya ce a cikin littafi mai suna **Al-minanu**, an samu ruwaya daga bini Jauzi cewa, Allah Ya shafe ƙasar Al-Rayi tare da wasu alƙaryu, kamar ɗari da hamsin (150), duk garin ya zama wata ƙasar ta kekkece, hayaƙi ya fito tare da abin da ke cikin ƙasa har da ƙasusuwan matattu.

Abdul Wahab Sha'arani ya ce; "A zamanin Sarki Abul-Futuha (Allah ya shafe masa) wasu tsibirai guda bakwai da ke gefen Teku, wajen sashen **Akaka,** bayan sama ta zubar da ruwan jini kwana bakwai. Kuma labari yana zuwa mana yau da kullum a garin Rumawa da Iraƙi. Sai ya ce: "Na ji Sayyadi Aliyuul Khawasi (rta) yana cewa, wannan shafe gari abu ne mai yiwuwa a kowane lokaci, a kowane gari ba mai musun haka sai jahili, saboda ya ruɗu da ni'imar Allah (swt).

### d) Fitar Wuta Daga Kasar Hijaz

Amma game da bayanin wuta da za ta fito daga ƙasar Hijaz, wadda aka ƙidaya ta daga sharuɗan ko alamun tashin ƙiyama, kamar yadda ya zo a cikin Hadisi.

An ruwaito daga Bukhari da Muslim: Abu-Huraira (rta) ya ce:

(لاتقوم الساعة حتى تخرج النار من أرض الحجاز).

***"Tashin ƙiyama ba zai auku ba, sai an ga wuta ta fito daga ƙasar Hijaz."***

Ita wannan wuta ta bayyana kamar yadda Manzon Allah (saw) ya faɗa. Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** inda Manzon Allah (saw) ya ce:

(حتى تخرج نار من أرض الحجاز).

***"Sai wuta ta fito daga ƙasar Hijaz."***

Haƙiƙa, wuta babba ta fito. Lokacin da ta bayyana, an yi girgizar ƙasa mai tsanani, ta auku ranar Laraba bayan sallar Isha'i a watan Jumadal Akhir a shekarar ɗari shida da hamsin da huɗu (654), ta kai har hantsin ranar Juma'a ta wannan mako sannan ta mutu.

Haka nan wuta ta bayyana a garin Kurudat wajen Tau'im gefen Harra. In ka gan ta, ka ce wani babban gari ne. Duk inda ta bi, ko da dutse ne sai ta narkar da shi. Tana daga cikin abubuwan da suka bayyana, wani rafi mai ruwan ganye, yana nuni kamar tsawa, wutar ta kai har birnin Madina. Amma a gefen birnin Madina, akwai wata kumfar ruwan. Saboda albarkar Manzon Allah (saw). Wannan kumfa yana tare da iska mai sanyi cikinsa. za a bi wannan wuta har wajen Yaman sai ta ƙona shi. Sai Kurɗabi ya ce, wasu abokammu sun faɗa mani cewa, sun ga wani gajimari a sararin samaniya daga Madina, zai kai faɗin tafiyar kwana goma sha biyar.

**e) Aukuwar Fitintinu**

Yana daga cikin fitinun da aka faɗa na alamun tashin ƙiyama, kamar yadda Hadisi ya faɗa, ita ma ta bayyana kamar yadda muka gani. Huzaifa ya ruwaito ya ce; "Manzon Allah (saw) ya tsaya cikimmu ya yi mana bayanin duk abin da zai auku na fitinu har tashin ƙiyama, wanda ya haddace ya haddace, wanda ya manta ya manta. Abokaina sun faɗa mani idan sun tuna mani, nan da nan nikan tuna, kamar yadda mutum yake tuna fuskar mutum, idan ya tuna da shi, ko ya gan shi". A ckin ruwayar Abi-Dauda: "An ce wallahi Manzon Allah bai bar kome ba na labarin jagororin fitina, har zuwa ƙarshen duniya, ya faɗi sunansa da sunnan babansa da sunan ƙabilarsa."

An ba mu labari cewa tun lokacin da aka kashe halifa Usmanu, aka buɗe wutar fitina. Tirmizi ya ruwaito daga Abdullahi bini Salam, lokacin da ya faɗa wa mutanen da suka kewaye gidan Usmanu halifa na uku, domin su kashe shi: "Ina roƙon ku da Allah, kada ku kashe wannan mutum, wallahi idan kuka kashe shi sai Mala'iku sun yi nesa da maƙwabtaka da ku, sai a kunna wutar fitina har tashin ƙiyama."

Yana daga cikin fitinun, yaƙin Jamal da yaƙin Saffain da kashe Hussaini a Karbala, kamar yadda Hadisai suka zo da su ba sai mun faɗe su ba. Yana daga cikin irin wannan fitina yaƙin da Turkawa suka yi wa Musulmi, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya ce ta ruwayar Imam Ahmad bini Hanbal a cikin Musnadinsa: daga Abdullahi bini Buraida daga babansa, ya ce muna zaune tare da Manzon Allah (saw) sai na ji shi yana cewa:

(إن أمتي يسوقها قوم عراض الوجوه صغار الأعين كأن وجوههم الجحف ثلاث مرات حتى يلحقوهم بجزيرة العرب. وأما السياقة الأولى فينجوا من هرب منهم. وأما السياقة الثانية فيهلك بعض وينجوا بعض، وأما السياقة الثانية فيهلك بعض وينجو بعض وأما السياقة الثالثة فيصطلمون).

***"Al'ummata wasu mutane za su yaƙe su, har sau uku. Siffar mutanen ita ce: Masu faɗin fuska da ƙananan idanu, masu kwarmi, har sai sun kai su Jaziratul***

***Arabi. Amma lokacin korar farko, za su tsira, amma a kora ta biyu, da yawansu za su halaka, wasu su tsira, amma a karo ta uku, za su gudu."***

Sai suka tambaye shi, su wane ne ya Annabin Allah? Sai ya ce:

(هم الترك)

***"Su ne Turkawa (Turkey)."***

Sai kuma ya ce:

(أما والذي نفسي بيده ليربطن خيولهم إلى سواري مساجد المسلمين).

***"Wallahi za su ɗaure Dawakansu a gefen masallatan Musulmi."***

Sai Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** Hadisin yana nunin bayyanarsu da kuma yaƙin Musulmi da za su yi. Haƙiƙa, wannan abu ya auku, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya faɗa. A wannan lokaci al'umma za su fito masu da yawa, Allah kaɗai Ya san adadinsu, ga su da ƙarfin sojoji, babu wata runduna ta Musulmi da za ta iya yaƙar ta, sai dai Allah. Idan ka gan su, ka yi zaton Yajuju da Majuju ne.

Kurɗabi ya ce shugaba Alhafizu bini Dihya (rta) ya ce wannan abu ya auku a shekarar Hijira ɗari shida da sha bakwai (617), a watan Jimada ula, Turkawa suka fito da babbar runduna suka fasa birane masu yawa; suka halasta kashe mata da yara, har yaƙin ya kai cikin Iraƙi. A fita ta biyu, suka kashe mutane masu yawan gaske, suka ɗaure Dawakansu a gefen masallatan Muslimi, kamar yadda aka faɗa a Hadisin, Manzon Allah (saw). Babu shakka Turkawa su ne mutanen da aka ba da tsoro da su a cikin Hadisi da Nasara.

Sai Kurɗabi ya ce "Mun gode wa Allah, domin dukkan fitowa guda uku ta Turkawa sun riga sun yi. Da farko dai, sun auka wa ƙasar Iraƙi, ta biyu, ƙasar Iraƙi suka sake aukawa; a fita ta uku sun kai har Bagadaza da garuruwan da ke kewaye da ita. Suka kashe mutane masu yawa da Sarakuna da Malamai da sauran mutanen kirki da bayin Allah na ƙwarai, har sai da suka mallaki dukkan Iraƙi da Sham (Syria) a ckin lokaci ƙanƙani.

Sai da Sarkin Misra, mai suna Muzaffar mai laƙabi da Faɗas, ya haɗa rundunar da ke tare da shi ta Misra da sauran maƙwabta. Lokacin da ma mutane sun fusata. Saboda haka suka auka masu da gaske. Sun haɗu a wurin da ake kira Aina-Jaluta. Allah Ya ba su nasara, kamar yadda Allah Ya ba Ɗaluta ya kashe masu sojoji masu yawa da dai sauran mabiya, daga nan suka janye daga Sham (Syria). Birnin Sham ya koma yadda yake da Musuluncinsa da jama'arsa. Sauran Turkawan suka haye kogin Furat, suna masu rashin

nasara; suka faɗa wa ƙasƙancin da ba su taɓa zato ba, suka juya ba nasara, ga ƙasƙanci, ga wulaƙanci.

Duk mai son ya san labarin da ya auku na fitinu da waɗanda suka auku da waɗanda ba su auku ba, ya duba littafin **Al-Fitar** na Abu-Shehu, da littafin **Al-Fitar** na Nu'aim bini Hammad, ɗaya daga cikin mahaddata, ɗaya kuma daga cikin malaman Bukhari. Wannan zamani, lokacin faɗace-faɗace ne, domin bayyanar Mahadi ta kusa. Abu Dauda ya ruwaito daga Mu'azu bini Jabal (rta), Manzon Allah (saw) ya ce:

(عمران بيت المقدس خراب يثرب وخراب يثرب خروج الملحمة وخروج الملحمة فتح قسطنطينية وفتح قسطنطينية خروج الدجال).

***"Rayuwar Baitul Muƙaddis ita ce rushewar Madina, rushewar Madina ita ce bayyanar faɗace-faɗace, bayyanar faɗace-faɗace, shi ne cin nasara a garin Kusɗanɗaniyya, shi kuma cin Kusɗanɗaniyya, shi ne fitar Dujal."***

Alƙali Iyal ya faɗi cewa alamun sun bayyana, kamar yadda ya rubuta a cikin littafin **Ashafa**.

Sai na ce yadda fitinu suka yi tawaturi, da faɗace-faɗace manya da mutuwar sunna da rayar da bidi'a da barin umurni da abu mai kyau da hani a kan munana, yana daga cikin magabatan zuwan Mahadi, kamar yadda aka rubuta a cikin littafin **Al- Malahim** na Manawiyi. Mene ne ma ake buƙata wajen sifanta sharrin wannan zamani, alhali gani ya kori ji a wannan zamanin da muke tsoron zuwansa. Kamar yadda Ka'abu da bini Mas'ud suka faɗa:

"Zamani ne da ake jefar da gaskiya baki ɗaya. Amma mugunta da zalunci, ba a jefar da su. Idan wannan hali na zamani ya ci gaba da haka, ba a sami canji ba, to, don mutum ya rasu, ba za a yi masa kuka ba, domin ya huta ne. Haka nan kuma ba za a yi murna da abin da aka haifa ba don ya zo a zamanin fitina."

Sai (Shehu Usmanu) ya ce: "Duk mutumin da ya ga abin da mutane suka nace a kansa a wannan zamani abubuwan munkirai da bidi'o'i, sai ka gane cewa al'amarin tashin ƙiyama ya kusa."

Abdul Wahab Sha'arani ya ce a cikin **Al-Minan**, "Wani tsuntsu ya kai girman Giwa, ya hau kan wani tsauni, ya yi kururuwa da murya mai fasaha. Ya ce: 'Lokaci ya kusa.' Ya yi haka tsawon kwana uku, sannan ya shiga Teku ya ɓace."

Sai Shehu Usmanu ya ce: "Ba abin da ya yi saura a yanzu, sai bayyanar faɗace-faɗace waɗanda daga su sai rugujewar duniya, wadda farkonta faɗar

Iskanɗariyya (Egypt).” AbdurRahaman Suyuɗi ya ce a littafi mai suna **Al-Kashfu** Dailami ya ruwaito daga Abu Zarri, ya ce ya ji Manzon Allah (saw) yana cewa:

(إنه سيكون بمصر رجل من قريش أخنس يلى سلطانا ثم يغلب عليه أوينزع منه فيفر هاربا إلى الروم فيأتي بهم إلى الأسكندرية فيقاتل أهل الإسلام بها).

***“Za a yi Sarki a Misra Bakuraishe, mai gajeren hanci, zai bi bayan wani Sarki sai ya rinjaye shi, ko kuma a kwace masa iko, sai ya gudu zuwa Rum. Sai ya sami gudummuwa daga can sai ya dawo Iskanɗariyya, ya yaki Muslimi na garin Iskanɗariyya.”***

Wannan shi ne farkon faɗan da za a yi. “Ɗan Askar ya fitar a littafinsa na tarihi, Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira.** Ɗan Wahab ya faɗa cewa, Abdullahi bini Umar da bini Assi (rta) lokacin da aka ce masa mutane sun tsorata a garin Iskanɗariyya, nan da nan ya sa aka ɗauki makamai da Dawakai. Sai wani mutum ya zo masa ya ce me ya kawo wannan tsoron? Sai ya ce Jiragen ruwa ne aka hango su, sun fito wajen Kuburus? Sai ya ce; “Ku kawar mani da Dokina.” Sai aka ce “Yallaɓai, ai mutane sun riga sun yi hawa na Dawaki don yaki.” Sai ya ce; “Wannan ba shi ne yakin da zai zo Iskanɗariyya ba. Shi, yakin da zai zo, zai fito daga yamma ne daga wajen Tarabulus (Libya). Za su zo da runduna dubu, sannan dubu ɗari har sau tara.”

Wa'ilu ya fitar a littafi mai suna **Al-Inabatu**. Daga Hadisin Rushdu bini Sa'adu daga Akilu daga Ruhriyi daga Ka'abu ya ce, “Ni na samu a cikin littafin da aka saukar daga wajen Allah ga Annabi Musa bini Imrana; cewa a garin Iskanɗariyya, akwai shuhada'u waɗanda za su yi shahada a rafin garin, sun fi shahidan baya masu zuwa. Allah Yana alfahari da su, kamar na shuhada'un Badar.”

Abu Nu'aim ya faɗa daga Abu Maran Alhawafi da Abu Haruna Abalriyi sun ji magana daga Nufal-Bakali yana cewa ita, duniya, an yi ta kamar tsuntsuwa idan aka yanke fukafukanta, sai ta ruguje. Garin Misra da Basra, fukafukan duniya ne. Idan aka tsinke su, sai duniya ta kare. Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**, Aliyyu (rta) ya ruwaito daga Manzon Allah (saw) ya ce:

(قال الله تعالى: ((إني إذا أردت أن أخرب الدنيا بدأت ببيتي فأخربه ثم أخرب الدنيا على أثره)).

***“Allah Ya ce idan Ya so Ya rusa duniya Zai fara da ɗakinSa, watau Masallacin Ka'aba, ‘sai In rusa shi, sai in rusa duniya nan take.”***

Huzaifa bini Yaman (rta) ya ruwaito daga Manzon Allah (saw) ya ce:

(يبدأ الخراب في أطراف الأرض حتى تخرب مصر، ومصر آمنة من الخراب حتى تخرب البصرة، وخراب البصرة من العراق، وخراب المصر من جفاف النيل، وخراب مكة من الحبشة، وخراب المدينة من الجوع، وخراب اليمن من الجراد، وخراب الأيلة من الحصار، وخراب الفارس من الصعاليك، وخراب الترك من الديلم، وخراب الديلم من الأرمن، وخراب الأرمن من الجزر، وخراب الجزر من الترك، وخراب الترك من الصواعق، وخراب السِّندِ من الهند، وخراب الهند من الصين، وخراب الصين من الرمل، وخراب الحبشة من الرجفة، وخراب الزوراء من السفياني، وخراب الروكاء من الخسف، وخراب العراق من القحط).

***"Za a fara rushe duniya ta gefenta ne, har a iso Misra. Amma Misra tana cikin amana, sai an fasa Basra, ita kuma Basra daga Iraƙi ce. Ita kuma Misra, ƙonewar kogin Nil za ta jawo mata rushewa. Rushewar Makka daga Habasha, Madina kuwa rushewarta da yunwa da fara ne za su rushe ta Yaman. Birnin Ailata kuwa tserewa za a yi masu. Farisawa kuma daga tawayen talaka ne. Turkawa kuma daga ƙabilar da ake kira Deilan na garin Arman. Ita kuma Arman daga ƙabilar Jazar, su kuma Jazar daga Turkawa, su kuma Turkawa, bala'in tsawa. Rushewar garin Sinda daga Indiya, Indiya kuma daga China, ita kuma China daga Ramala. Ita kuma Habasha daga Safayani, Zauka'a daga Kisfewa. Ita kuma Iraki daga fari na rashin ruwan sama."***

Sai Shehu Usmanu ya ce, "Duk wani gari sai an rusa shi kafin tashin ƙiyama". Allah Ta'ala Ya ce:

﴿وَإِن مِّن قَرۡيَةٍ إِلَّا نَحۡنُ مُهۡلِكُوهَا قَبۡلَ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَوۡ مُعَذِّبُوهَا عَذَابٗا شَدِيدٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا﴾

الإسراء: ٥٨

***"Kowace alƙarya sai Mun halakar da ita, kafin tashin ƙiyama, ko kuma Mu yi mata azaba mai zamani."*** **Alƙur'ani 17:58**

Haka yake a rubuce a cikin littafi. Imam Al-Bagawi ya ce a cikin tafsirin ayar ma'anar za a rushe ta, a halakar da ita, watau mutanen garin ko kuma a yi mata azaba mai tsanani, idan suka kafirta, ko kuma suka saɓa.

An yi wata magana kuma, Maƙatilu da waninsa ya ce za a halakar da ita wajen muminai, ko kuma za a azabtar da ita, idan kafirai ne da na'u'in azaba.

Bailawi ya ce a cikin tafsirinsa, za a halakar da su da mutuwa da tumɓuke su, ko kuma a azabtar da su azaba mai tsanani da kisa da nau'o'in bala'i. Shehu Sunusi ya ce a farkon sharhin **Wusɗa** ba ɓoyayyen abu ne ba cewa, duniya a yanzu tana cikin magagin mutuwa, kuma tana sanar da lokacin

tafiya ya yi da kusantar rushewar duniya, saboda bayyanar manyan sharaɗi da tsoro masu girma.

Sai Shehu Usmanu ya ce: "Wannan magana saboda zamani ne na mutuwar Sunna da rayar da bidi'a, abin zargi da barin umurni da abu mai kyau da hani da aikin munkari, suna daga cikin muƙaddima ta fitar Mahadi kamar yadda suke cikin littafin **Al- Mulahim** na **Al-Manawi** kamar yadda aka faɗa a baya" Dukkan muwafaka tana ga Allah.

## FASALI NA HUƊU

### Fitowar Mahadi (rta)

A wannan Fasali zan bayyana abu guda biyar:

**Na Farko:** Bayanin wasu malamai da suka ce, ai Mahadi ya riga ya wuce, kuma shi ne Umar bini Abdul'Aziz ko kuma waninsa ne.

**Na Biyu:** Bayanin cewa abin da ya fi daidai, cewa dai Mahadi bai zo ba tuna, sai Dujal ya bayyana tukuna.

**Na Uku:** Bayanin cewa Mahadi yana daga cikin 'ya'yan Fatima 'yar Manzon Allah (saw), ba daga zuriyar Abbas ba baffan Manzon Allah (saw).

**Na Huɗu:** Bayanin zancen Hassan Al-Iraƙi yana cewa shi, Mahadi, yana raye kodayake ban ga haka a cikin Hadisi ba.

**Na Biyar:** Game da alamar fitarsa da kuma in da zai fito. Dukkan muwafaƙa tana ga Allah.

### I- Bayanin Malamai Kan Wucewar Mahadi, Ko Kuma Shi Ne Abdul'Aziz

Amma game da bayanin wasu malamai da suke cewa lokacin Mahadi ya riga ya wuce, domin shi ne Umar bini Abdul'Aziz, ko kuma waninsa. Ahmad Azzaruk ya ce a cikin littafi mai suna **Umdatu** mafi yawan malamai suna cewa; Mahadi ya riga ya wuce, kuma shi ne Umar bini Abdul'Aziz, ko kuma waninsa. A kan saɓanin cikin haka sai ya ce; "Gaskiyar magana ita ce wannan lamari abu ne a rufe."

### II- Dataccen Bayani Kan Cewa Mahadi Bai Zo Ba, Sai Dujal Ya Bayyana

Amma game da bayanin cewa shi dai Mahadi bai zo ba tukuna, har sai lokacin fitar Dujal, Sayyadi Hassan Alyusiyi bini Mas'udu ya ce a wani majalisinsa lokacin da Du'a'u bini Taumarata ya yi da'awar cewa, shi ne Mahadi, ya ce malamai sun yi masa musu, a kan haka da mabiyansa. Suka ɗauke su a matsayin ɓatattu, kuma wannan magana ba shakka a kanta, ga duk wanda ya yarda da cewa, Mahadi zai zo ne a ƙarshen zamani.

Ya ce Suyuɗi ya wallafa littafi mai suna **Al-Urful- Waridi**, ya yi dogon bayani a cikinsa wanda ya zama gamsasshe, cewa Mahadi bai zo ba tukuna, amma zai zo a ƙarshen zamani ne, lokacin bayyanar Dujal da lokacin saukar Annabi Isah (as), ba kuma ɗan Taumarata ba ne, ko masu kama da shi, daga cikin mutanen da suke da'awar cewa su ne Mahadi a wannan zamani. Sai

Shehu Usman ya ce; Na gode wa Allah domin na gani da idona, littattafan da suka yi bayani, cewa Mahadi bai zo ba har sai Dujal ya fito tukuna kamar yadda Hassan Alyusiyi (rta) ya ce: a wajen majalisinsa.

### III- Mahadi Yana Daga Cikin 'Ya'yan Fatima Ɗiyar Manzon Allah (saw)

Amma bayanin cewa Mahadi yana cikin 'ya'yan Fatima (as) ne. Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** da kuma wasu Hadisai daga wajen Annabi (saw), wanda ya nuna zuwan Mahadi daga zuriyarsa, kuma daga 'ya'yan Fatima, kuma wannan magana haka take. Kuma ya ce Abul-Hassan Muhammad bini Hussaini bini Ibrahim bini Asim Assinja Ziyi ya ce: "Labari ya tabbata, kuma ya yawaita daga Manzon Allah (saw) cewa, Mahadi zai zo ne daga iyalan gidansa". Darul-kuɗni ya ruwaito a cikin littafin **Al-Afarad**. Haka nan bini Asakir a tarihinsa daga Usman bini Affan (rta) ya ce, "Ya ji Manzon Allah (saw) yana cewa:

(المهدي من ولد العباس عمي

***"Mahadi daga cikin 'ya'yan baffana ne Abbas."***

Sai Darul-Kuɗni ya ce wannan Hadisi garibi ne. Muhammad bini Walid maula bini Hashim shi kaɗai ne ya ruwaito wannan Hadisi. Sai (Shehu Usmanu) ya ce Darul-kuɗni ya faɗakar da wannan ne, domin a gane cewa Hadisan da aka ruwaito game da Mahadi yana nuni ne, inda zai fito daga iyalansa ne (saw), ta wajen Fatima (as), ba daga 'ya'yan Abbas baffansa (saw) ba. Bini Majah ya ruwaito Hadisi daga Anas (rta) inda yake cewa:

(لامهدي إلا عيسى ابن مريم عليه السلام).

***"Babu wani Mahadi sai Isah ɗan Maryam."***

Sai Kurɗabi ya ce, a cikin **Attazkira.** Isnadin wannan Hadisi mai rauni ne. Tun da yake an sami Hadisai daga Manzon Allah (saw), waɗanda suke nuna cewa Mahadi yana cikin iyalan Manzon Allah (saw) ne, kuma cikin 'ya'yan Fatima. Ingancin wannan magana ya fi na sauran Hadisan, saboda haka da su ne za a yi hukunci.

Ya ce; yana iya zamowa, kalimar-wala Mahadi illa Isah-ai Mahadi cikakke ma'asumi sai Isah (as). Ya ce ta haka ne ake iya haɗa Hadisan guda biyu, domin a kawar da su kan Kalimar. Bini Asakir ya ce wannan Hadisi a zahiri ya saɓa wa Hadisan da suka zo wajen tabbatar da Mahadi ban da Isah ɗan Maryam (as). Wajen Malam Tawadi'i cewa babu suka a maganar, ba mamaki abin da ake nufi da maganar shi ne cewa, Annabi Isah (as), shi ma yana daga cikin Mahadi, ya nuna akwai wasu Mahadi ban da Isah (as).

## IV- Bayanin Hassan Al-Iraƙi Cewa Mahadi Yana Raye

Amma bayanin cewa zancen Hassan Al-Iraƙi ya sanar cewa Mahadi yana nan a raye tun wasu shekaru masu yawa. Ni dai ban ga wannan magana a cikin Hadisin Annabi (saw) ba. Shehu AbdurRahaman Sha'arani ya ce a **Lawaƙihu** a cikin tarihin Hassan Iraƙiyi (rta), Allah Ya amfane mu da albarkarSa. Akwai daga cikinsu, Shehu Arfun billahi Sayyadi Hassan Iraƙiyi ya ce "Na ji wajensa tare da Shehu Abul Abbas Harishiyi ya ce "Zan ba ka labarina tun ina ƙarami kamar muna tare". Sai na amsa "Ina so." Ina ƙarami a garin Damaskas, ina yin sana'a, sai ranar Juma'a muka taru wajen wasa da shaye-shaye. Sai Allah ya fitar da ni, na ce a zuciyata, ba domin wannan aka halitta ni ba. Sai na bar su a cikin halinsu na wauta, na gudu na tafi, suka biyo ni, amma ba su same ni ba, har sai da na kai Masallacin bani Umayya.

"Sai na ga wani mutum a zaune a kan kujera yana magana, game da Mahadi (as), sai na yi sha'awar mu haɗu da shi. Daga nan sai na shiga wani hali, duk lokacin da na yi sujuda, sai na roƙi Allah, Ya haɗa ni da shi. Wata rana ina zaune bayan sallar magariba ina yin Nafila, sai ga wani mutum a bayana, ya taɓa mani kafaɗa, sai ya ce: "Allah Ya amsa addu'arka, kai yaro mene ne matsalarka? Domin ni ne Mahadi."

Sai na ce; "Ina son in bi ka zuwa gidanka sai ya yarda, sai muka isa gidansa na roƙi ya ba ni wani ɗaki ni kaɗai, na zauna a nan kwana bakwai (7), sai ya laƙana mani wani wuridi. Ya kuma umurce ni da in riƙa yin sa kullum. Kuma ya ce in yi azumi, amma ina fashin kwana ɗaiɗai da sallah raka'a ɗari biyar (500) a dukkan dare. Ni kuma saurayi ne kyakkyawa, yakan ce mani in riƙa zama a bayansa. Haka kuma nake yi."

Rawaninsa ya zamo na Ajamawa ne. Ya sanya alkyabba ta gashin tozon Raƙumi. Lokacin da kwanaki bakwai suka ƙare, sai ya fita ya yi ban-bakwana da ni, ya kuma ce mani ya Hassan: "Ban taɓa haɗuwa da wani kamar yadda muka haɗu da kai ba. Saboda haka ka lazimci wannan wuridin, har sai ka kai muhallin gajiyawa, saboda kana da tsawon rayuwa." Nan ne ƙarshen maganar Mahadi (as). Sai mai ruwayar ya ce a yau da nake maku magana shekaru na ɗari da ashirin da bakwai (127).

"Bayan Mahadi mun rabu da shi sai na tafi ƙasar Indiya da Sinda da China. Daga nan kuma na dawo garin Ajamawa, sai garin Rumawa da ƙasashen yamma, daga nan sai na dawo garin Misira bayan na yi yawo na shekaru hamsin" in ji Hassan.

Wannan labari tabbatacce ne kamar yadda AbdulWahab Sha'arani ya rubuta a littafinsa mai suna **Lawaƙi'u**. Ya ce kuma a cikin alamar "Yana daga cikin baiwar da Allah Ya yi mani, nakan gane mai da'awa ta gaskiya, haka nan kuma mai da'awa ta ƙarya da wata alamar da Allah Ya yi mani ta ilhama. Har ya zamo mani Jiki."

Wata rana wani saurayi sharifi ya zo wajen mai siririn jiki ya yi naɗi, ya yi huni sai ya yi mani magana da wasu ilumummuka, ba wanda ya san su sai Mahadi (as). Sai ya ce mani ai shi ne Mahadi, kuma lokacin bayyanarsa ya kusa. Sai ban damu da abin da ya faɗa ba. Sai ya ce mani ba za ka gasgata ni a kan wannan labari ba? Duk da yake saurayi ne mai kwarjini mai kyan kawaici. Sai na ce masa, "Sautinka bai kama da na sharifi Mahadi ba, shi ko Mahadi, sharifi, ne" sai ya buɗe hunin da ya yi sai ya ce, "Ka yi gaskiya, amma a nan yamma jama'a da yawa sun ruɗu da abin da na gaya masu suka gasgata ni, har suna cewa Mahadi ya bayyana."

Sai na ce masa: "Me ya kai ka yin wannan abu?" Sai ya ce "Domin kada mutane su manta da maganar Mahadi, saboda ya kusa bayyana. Kuma abin da nake nufi cewa ni, Mahadi, ne, shi ne Allah Ya shiryar da ni ga Musulunci". AbdulWahabi Sha'arani ya ce, "Ni kam na gode wa Allah, domin Ya haɗa ni da Shehu Hassan Iraƙi, ya kuma faɗa mani cewa ya haɗu da Imam Mahadi, lokacin da yake roƙon Allah Ya haɗa shi da Imam Mahadi, a nuna wannan sai da ya kai shi shekara ɗaya cur. Ya ce mani fuskarsa ta yi kama da ta kakansa, Manzon Allah (saw) sai dai fuskar kakansa ta fi kyau ƙwarai.

Ya ce sai na tambaye shi shekararsa. Sai ya ce, "Yau shekara ɗari shida (600) da wani abu, amma daga ran da nake ba ku labarin shekara ɗari ɗaya ke nan." Haka dai ya ba ni labari. To, haƙiƙa, ilimi yana ga Allah, don ni ban gan shi ba balle in ce na gan shi. Sai Shehu Usmanu ya ce. maganar Hassan Iraƙiyi yana nuni da cewa Mahadi yana raye a halin yanzu. Saboda ya tambaye shi shekarunsa, sai ya ce shekara ɗari shida (600) da wani abu. Amma ni ba ni da tabbas a kan cewa yana nan a raye a wani Hadisi.

Duk Malamin da ya ce Mahadi na nan a raye, to, da wannan labari yake dogara. Ba kuma na rubuta maganar Hassan Iraƙi da nufin shi ne madogarata ba, saboda muna dogara ne da abin da shari'a ta zo da shi, ba kuma ina musun maganar ba ne, saboda ba ni da wata hujja a shari'a na cewa Mahadi ba shi a raye. Ba mamaki shi, Hassan Iraƙi, waliyyi ne na Allah, kuma maganarsu tana da wani sirrin da ake kiyayewa, ba a buɗe wa kowa. Allah kaɗai Masani. Mai labarin bayan ya yi hikayar nan sai ya ce, "Haka aka faɗa mani, Allah ne Ya san haƙiƙanin lamarin, tun da ban haɗu da shi ba, balle in san shi da kaina."

## V- Fitar Mahadi Da Kuma Inda Zai Fito

Amma bayanin alamar fitarsa da kuma inda zai fito, haƙiƙa, Darul kuɗini ya ba ni labari a cikin sunnoninsa daga Muhammad bini Aliyu (rta) ya ce: "Bayyanar Mahadi yana da ayoyi guda biyu, ba a kuma same su ba tun da Allah Ya hallici sama da ƙasa. Na farko, mashaƙon wata a farkon Ramalan, sai kusufin rana a tsakiyar Ramalan. Ba a kuma yi ba, har yanzu tun halittar sama da ƙasa.

Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**, "Abu Dauda ya ruwaito daga Ummu Salma (rta) matan Manzon Allah (saw) daga Manzon Allah (saw) ya ce:

**(يكون إختلاف عند موت خليفة فيخرج رجل من أهل المدينة هاربا إلى مكة فيأتيه ناس من أهل مكة فيخرجونه وهو كاره، فيبايعونه بين الركن والمقام).**

***"Za a samu saɓanin lokacin rasuwar wani halifa, sai wani mutumin Madina ya fito da gudu zuwa Makka, sai mutanen Makka su kore shi, a tilas sai kuma su yi masa mubayi'a tsakanin Rukuni da Maƙamu Ibrahim."***

Sai ya ce bayan dogon bayani, wannan mubayi'a ba a yi ta ba, a da can kuma kamar ba zai zama haka ba, saboda an ruwaito Hadisi daga Abdullah bini Masa'udu da waninsa na sahabbai cewa, a ƙarshen zamani wani zai fito daga yamma mai nisa, har zuwa ƙarshen Hadisin.

Jama'a za su zo ta kowane sashe da kowane gari, su yi ta yi masa mubaya'a a garin Makka. Shi kuma yana tsakanin Rukuni da Maƙama Ibrahim amma shi ba ya son mubayi'ar ta biyu, bayan an riga an yi ta farko, bayan mutune sun yi masa mubayi'a a yamma.

AbdurRahaman Suyuɗi ya ce a ƙarshen littafinsa mai suna **'Al-Urful Wardi'**- Kurɗabi ya zo da shi a littafinsa **Attazkira**, cewa, "Mahadi zai fito ne daga yamma mai nisa, a cikin wata ƙissa mai tsawo", duk da dai labarin bai da asali. Dukkan muwafaƙa ta Allah ce.

## FASALI NA BIYAR

### Fitar Dujal (la)

A nan za mu zo da abubuwa guda biyar shi ma:

**Na Farko:** Alamun fitarsa.

**Na Biyu:** Bayani wajen fitarsa.

**Na Uku:** Bayanin hujjar da aka bayar cewa, Dujal shi ne Ɗan Siyada da hujjar waɗanda suka ce waninsa.

**Na Huɗu:** Bayanin zai shiga ko'ina a duniya, sai dai Makka da Madina.

**Na Biyar:** Bayanin abin da zai fitar da mutum daga fitinarsa.

### 1- Alamun Fitar Dujal

Dukkan muwafaƙa ta Allah ce.

Amma bayani game da fitar Dujal: Ɗabarani ya ruwaito daga Asma'u 'yar Yazid cewa Manzon Allah (saw) ya yi bayanin Dujal a gabanta. Ya ce:

(إن قبل خروجه ثلاثة أعوام: تمسك السماء في العام الأول ثلث قطرها والأرض ثلث نباتها، والعام الثاني تمسك ثلثي قطرها والأرض ثلثى نباتها، والعام الثالث تمسك السماء قطرها والأرض نباتها، لايبقى ذات ضرس ولاذات ظلف إلا مات). وفي بعض الروايات بعد قوله: (في السنة الثالثة يمسك الله المطر وجميع النبات، فما تنزل من السماء قطرة ولاينبت من الأرض خضرة ولانبات حتى تكون الأرض كالنحاس والسماء كالزجاج فيبقى الناس يموتون جوعا وجهدا وتكثر الفتن والهرج. فعند ذلك يخرج الملعون الدجال من ناحية أصبهان. ومن علامة خروجه فتح القسطنطينية).

***"Idan sauran shekara uku Dujal ya fito, ruwan sama zai ragu da sulusi, watau ɗaya cikin uku (1/3), ita ma ƙasa za ta fitar da sulusin amfaninta ne. A shekara ta biyu, ruwan sama zai ragu da sulsani (2/3), ƙasa ita ma ta rage da sulsani (2/3). A shekara ta uku, sai sama ta riƙe ruwanta, ƙasa ta riƙe amfaninta. Duk wata dabba mai haƙori (haure) ko mai ƙumba (akaifa) sai ta mutu." A wani sashen ruwayar bayan zancensa, A shekara ta uku, Allah Zai ɗauke ruwan sama da amfanin da zai fito a bayan ƙasa, ko ɗigon ruwa ba zai sauko ba. Haka nan ko ciyawa guda ɗaya ba za ta fito a ƙasa ba, har ƙasa ta zama kamar ƙarfe (dalma), sama kuma ta zama kamar kayan ƙarau (glass). Sai mutane su***

***yi ta mutuwa, saboda yunwa da wahala da yawan fitina da yaƙe-yaƙe. A wannan lokacin ne sai Dujal (la) ya fito daga wajen Asbihan."***

Yana daga cikin alamun fitarsa cin nasarar buɗe garin Kusɗanɗaniyya. Kurɗabi ya ce a littafin **Attazkira.** "Labari ya tabbata cewa tsakanin fitar Dujal da buɗe garin Kusɗandaniyya wata bakwai ne." An kuma ce an ruwaito idan ƙarshen zamani ya zo, wata mace za ta fito daga cikin Teku kyakkyawa da ba kamarta, sai ta gayyaci mutane zuwa wajenta. Yana daga cikin bala'in da za ta kawo na rusa garuruwan duniya. Duk wanda ya bi ra'ayinta ya kafirta. Daga nan ne sai Dujal ya yi tsawa sau uku. Dukkan mutane na gabas da na yamma za su ji wannan tsawar.

## 2- Wajen da Dujal Zai Fito

Amma garin da zai fito, Tirmizi ya ruwaito daga Abubakar Siddiƙ (rta) ya ce: Manzon Allah (saw) ya ce:

(الدجال يخرج من أرض بالمشرق يقال لها خراسان يتبعه أفواج كأن وجوههم المجان).

***"Dujal (la) zai fito a gabashin duniya, ana kiran garin Khurasan, Jama'a za su bi shi; fuskarsu kamar garkuwa."***

Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**, "An samu daga Tirmizi cewa zai fito daga Khurasan. A wata ruwaya wajen Isbihan, a garin da ake kira Yahudiyatu. Amma a da Hadisin Bini Majah da Muslim sun ce zai fito ne tsakanin Sham (Syria) da Iraƙi. Amma yadda za a iya haɗa Hadisan shi ne farkon fitarsu ita ce Isbihan sai hijaz, tsakanin Iraƙi da Sham (Syria), Allah kaɗai ne Masani.

## 3- Bayani Kan Hujjar Masu Cewa Dujal Shi Ne Ɗan Siyada

Amma bayani kan hujjar masu cewa Dujal (la) shi ne Bini Siyada ta ruwayar da Muslim ya ruwaito daga Muhammad bini Munkadir ya ce, "Na ga Jabir bini Abdullahi (rta) yana rantsuwa da Allah cewa bini Siyada, Dujal ne." Sai na ce masa, "Ka yi rantsuwa da Allah a kan wannan abu? Sai ya ce na ga Umar yana rantsuwa a haka a gaban Manzon Allah (saw) bai hana shi ba." Haka Abu Dauda ya ruwaito a cikin sunnoninsa.

Nafi'u ya ce, Ɗan Umar (rta) ya ce: "Wallahi ba na shakka Bini Siyada shi ne Dujal." Abu Dauda ya fitar da shi. Nafi'u kuma ya ce: "Ɗan Umar ya gamu da Bini Siyada a cikin Madina, sai ya faɗa masa maganar da ta ɓata masa rai, ya yi ta nuna fushi har ya cika wajen da fushi. Sai Ɗan Umar ya je wajen Hafsat ta ce masa, Allah ya gafarta maka me ya kai ka wajen Bini Siyada, Ba ka san cewa Manzon Allah (saw) ya ce:

(إنما يخرج الدجال من غضبة يغضبها)؟

*"Dujal zai fita daga wurin fushi da wani zai yi."*

Imam Muslim ya fitar da shi a cikin sahihinsa. Yusuf Ɗan Umar ya ambata a littafi mai suna **Kitabul Futuhati**, cewa Abu Sairat lokacin da ya sauka garin Susu, rundunar Musulmi suka kewaye garin, sai malaman Yahudu da na Nasara suka zo wajen suka ce masu "Ya ku Larabawa, Malamammu sun faɗa mana ba masu cin garin Susu sai Dujal, ko kuma mutanen da ke tare da Dujal. Idan ba tare da Dujal kuke ba, kada ku wahalar da kanku da wannan tsarewa." Sai Bini Siyada ya yi fushi lokacin da ya ji wannan maganar, sai ya tafi ƙofar ganuwa. Ya tokare ta da ƙafa, ya ce buɗe, sai ta ɓalle, sarƙoƙi suka tsuntsunke, maɗauranta suka yanke, sai ƙofa ta buɗe. Musulmi suka shiga garin.

Abu Sa'idul Khudiri (rta) ya ce "Mun fita za mu je Hajji, ko Umara, muna tare da Bini Siyada sai ya ce; "Sai muka sauka a wani wuri sauran jama'a, kuma suka sauka a wani wuri dabam." Sai ya rage daga ni (Abu-Sa'idu) sai shi (Bini Siyada). Sai na shiga cikin damuwa mai tsanani. Saboda abin da ake jingina masa, sai ya ɗauko kayayyakinsa ya haɗa da kayayyakina, sai na ce masa, ka ga garin akwai zafi da ka ajiye naka a ƙarƙashin waccan itaciya sai ya kwashe kayayyakinsa ya kai can ɗin. Sai ya je wajen Awaki ya zo mana da nono a gora ya ce ga shi ka sha ya Abu-Sa'idu.

"Na ce garin na da zafi, saboda haka ba zan iya sha ba. Ni kuwa ina ƙyamar in karɓi kyautarsa ce. Sai ya gane abin da nake nufi, sai ya ce mani ya Abu Sa'idu kai dai masanin Hadisin Manzon Allah (saw) ne. A cikin Lansar, idan abu ya ɓuya kai ake tambaya, saboda saninka da Hadisin Manzon Allah (saw). Ashe Manzon Allah (saw) da yake maganar Dujal bai ce shi Dujal kafiri ne ba? Ni ko Musulmin ne, ashe ba a ce shi, Dujal, ba zai haifu ba, ni ko na bar ɗana a Madina. Manzon Allah (saw) ya ce, "Shi, Dujal, ba zai shiga Madina da Makka ba, ni ko na fito Madina ne zani garin Makka."

A wata ruwayar za ni aikin hajji sai Abu Sa'idu ya ce, "Har na kusa in karɓi hamzarinsa sai shi, Bini Siyada, ya ce mani "Wallahi na san garin da aka haifi shi, (Dujal), na san inda yake a yanzu," sai na ce masa "Tir da kai da sauran kwanaki." A wata ruwayar sai na ce masa a ce kai ne wannan mutum (Dujal) yaya za ka ji? Sai ya ce "Ai da za a yi mani tayin zama Dujal, ba zan yi musu ba."

Amma hujjar masu cewa Dujal ba shi ne Bini Siyada ba, a cikin Hadisin da aka ruwaito daga Tanimud Dari da Hadisin Bini Majah wanda ya ruwaito daga Fatima 'yar Kaisu (rta). Ta ce "Wata rana Manzon Allah (saw) ya yi sallah sai ya hau kan mimbari, irin hawan da bai yin irinsa, sai ran juma'a kaɗai, sai mutane suka nuna damuwa sosai, lokacin wasu na zaune, wasu a tsaye, sai ya yi nuni da mu zauna. "Wallahi, ba na miƙe ba ne don in ba ku

labarin abin da zai tauye maka fatan da kuke da shiga lahira, ko ya tauye maku yawan tsoronku ba sai dai zan faɗa maku labari mai daɗi ba, saboda murna har na kasa barcin rana (ƙailula), idanu sun yi sanyi. Shi ne na so in ba ku, domin kuma ku ji wannan labari mai daɗi wanda Annabi (saw) ya ji sai ya ce:

Tanimud Dari ya zo ya faɗa mani, suna tafiya cikin Teku sai iska mai ƙarfi ya ja mu zuwa wata Jazira, a tudun tsibiri cikin wanda ba su san shi ba, sai suka fito daga cikin jirgin rowan, sai suka ga wani abu mai ban tsoro, ga shi ɓaki ga shi mai gashi da yawa, sai suka ce mene ne wannan? Sai ya amsa da cewa shi ɗan leƙen asiri ne (Jasusu). Sai suka ce ba mu labari, sai ya ce a'a ba zan ce komi ba, ba kuma zan tambaye ku kome ba, sai dai ku je ga wani ɗaki can wanda kuke hange, akwai wani mutum a ciki zai ba ku labari.

Suna shiga ɗakin sai ga wani tsohon mutum a ɗaure, ya sha ɗauri da alamun yana cikin baƙin ciki, yana kuma kai kukansa ga jama'a. Sai ya ce masu "Daga ina kuka fito?" Suka ce daga ƙasar Sham (Syria), sai ya ce; "Yaya labarin Larabawa?" Suka ce; "Ai mu ma Larabawa ne, me ka ke so ka sani?" Sai ya ce; "Yaya labarin mutumin nan da ya fito?" Sai suka ce, "ya zo mana da alhairi. Allah Ya ba shi nasara, Ya umurce su da bautar Allah ɗaya ƙarƙashin Annabi (saw), addini ɗaya." Sai ya ce; "Yaya labarin kogin Zagarata." Suka ce "sai alhairi, akwai ruwa na shuka, na sha da na shayar da dabbobi." Ya ce "Yaya dabinon Uman da Bisan?" Suka ce "Lafiya, ana samun amfanin gonar duk shekara." Sai ya ce "Yaya Kogin Buhaira da Tibrit?" Suka ce: "Akwai ruwa mai yawa ga amfanin gona. Sai ya yi kururuwa sau uku, ya ce: "Da za a sake ni da na je ko ina ban da garin Madina. Wannan ban da iko a kanta." Sai Annabi (saw) ya ce:

(إلى هذا انتهى فرحي هذه طيبة، والذي نفسي بيده مافيها طريق ضيق ولاواسع ولاسهل ولاجبل إلا وعليه ملك شاهر سيفه إلى يوم القيامة).

***"Kun ji dalilin murnata, saboda ba zai shiga Madina ba. Na rantse da Allah wanda numfashina na gare Shi, duk wata hanya ta shiga Madina, ko babbar hanya, ko ƙaramar hanya, sai ka sami Mala'ika yana tsaye da takobi na kashe masu tayar da fitina, har tashin Kiyama."***

Kurɗabi ya faɗa a **Attazkira** cewa wannan Hadisi sahihi ne. Muslim ya fitar da shi da Tirmizi da Abu Dauda da waninsa (rta). A ruwayar Tirmizi ya ce "Sai Tsohon nan ya ce masu ni ne Dujal. Kuma an kusa a yi mani izini da fitowa. Idan na fito zan je ko'ina a faɗin duniya a cikin kwana arba'in 40, ban da Makka da Madina, su kan an hana ni shigar su."

Shehu Imamul-Hafiz Abubakar Baihakiyyu (rta) ya ce, "Bayan ya yi magana a kan Hadisin Bini Siyada, duk wani malamin da yake kafa hujja da cewa Bini Siyada ba shi ne Dujal ba. To, da wannan Hadisin na Tanimud dari suke kafa hujjarsu, kuma isnadin Hadisin ya fi inganci. Saboda siffarsa ta yi daidai da siffar Dujal. Kuma shi, Dujal, ba Bini Siyada ba ne; kamar yadda ya zo a labarin cewa ya yi kama da Abdu-uzza bini Kusayyi, amma Bini Siyada, shi dai wani fitina ne, kamar yadda aka fitini mutanen Musa (as).

Sai dai Allah Azza wajalla ya kare al'ummar Annabi (saw), Ya kiyaye su daga sharrinsa, kodayake Manzon Allah (saw), Ya yi, shi ma lokacin da Umar ya yi magana, wataƙila yana jiran ya samu tabbas ne daga wajen Allah Ta'ala cewa ba Bini Siyada ba ne, amma ai ka gani a labarin Tanimud Dari ya yi jawabi, amma dukkan ilimi ya tabbata ga Allah Shi kaɗai.

Abu Suleiman Hattabi ya ce, "Ruwayoyi sun saɓa game da lamarin Bini Siyada. Wannan abu ya faru ne bayan ya girma. Akwai wata ruwayar cewa ya tuba daga baya, kuma ya rasu ne a Madina, kuma da aka zo yi masa salla jama'a, an buɗe shi, don kowa ya gan shi, su tabbatar da cewa shi ne." Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** Saɓanin wannan shi ne sahihiyar Magana, domin Jabir da Umar har rantsuwa suka yi cewa Bini Siyada shi ne Dujal.

An ruwaito daga Abu-zarri (rta) ya ce Bini Siyada shi ne Dujal. Ɗan Umar shi ma ya ruwaito haka. Jabir ya ce "Ba mu gan shi ba, ranar yaƙin Harrat da aka yi a Madina. Kodayake akwai wata ruwayar da ta saɓa da wannan, mai cewa ya mutu a Madina ne Allah kaɗai Masani. A cikin littafin Abu Dauda game da labarin Jassatu na Hadisin Abu Salmata bini AbdurRahman Sahalu bini Jabir ya ce, "Dujal dai shi ne Bini Siyada". Sai na ce, to, ko da ya mutu? Na ce ko da ya zama Musulmi, na ce ko da ya shiga Madina? Na ce ko da ya shiga Madina.

Amma wasu malamai sun kafa hujjar cewa, Bini Siyada ba shi ba ne Dujal ta Hadisin Jassasa. Amma ingantacciyar magana ita ce, shi ne Dujal watau Bini Siyada. Ba mamaki ba ne, domin an same shi ne a Hijaz a wannan lokacin, ya zamo cikin sahabbai. A wani lokacin har suka daina ganin sa a lokacin da aka yi yaƙin Harra. Da kuma maganar da ya faɗa wa Abu-Sa'idul Khudri cewa, "Wallahi, ni na san Dujal, na san inda aka haife shi, a wannan lokacin na san kuma inda yake yanzu." Ya zama kamar nassi ke nan, cewa a lokacin sa, Muslim, ne. Kuma har ya haihu, kuma ya shiga garin Madina amma ba zai dawo ba. Kuma zai kafirta idan ya fita, kuma ba zai haihu fa, ba kuma zai dawo garin Madina ba. Kurɗabi ya ce a **Attazkira** bai haihu ba, amma zai haihu a ƙarshen zamani. Sai ya ce; amma magana ta farko ta fi muhimmuci, cewa Bini Siyada shi ne Dujal.

## 4- Dujal Zai Shiga Ko'ina Ban da Makka da Madina

Amma game da bayanin Dujal zai zagaya duniya dukkanta, sai dai ba zai shiga garin Makka da Madina ba, an ruwaito Hadisi daga Bukhari da Muslim daga wajen Anas bini Malik (rta) ya ce, Manzon Allah (saw) ya ce:

(ليس من بلد إلا سيطئه الدجال إلا مكة والمدينة).

***"Babu wani gari a duniya sai Dujal ya shiga a cikinsa ban da garin Makka da Madina."***

A ckin Musnad na Ahmad daga Hadisin Jabir ya ce:- "Dujal zai fito a lokacin addini ya yi rauni, ga ƙarancin ilimin addini, yana da kwana arba'in zai yawata a cikin duniya. Kwana ɗaya cikin daidai da wata, wani kwanan daidai da mako ɗaya, sauran kwanakin kuma babu bambamci da kwanakin da aka saba. Yana da wani Jaki na hawa tsakanin kunnen Jakin ya kai kamar zira'i arba'in, sai ya ce wa mutane, "Ni ne Ubangijinku". Amma yana da ido ɗaya ne, amma Allah ba ido ɗaya Yake da shi ba. An rubuta tsakanin idonsa KAFIRI NE. Duk wani mumini zai gani, ko ya iya karatu ko bai iya ba. Zai je kowace mashayar ruwa (Kogi) ban da Madina ko Makka. Allah Ya (haramta masa shigar su). Akwai Mala'iku a ƙofar shiga. Shi, Dujal, yana tare da dutsen waina (burodi).

Ga kuma mutane suna fama da yunwa, bai ba kowa sai wanda ya bi shi. Yana tare da ruwan sha na ƙorama guda biyu, ni na san su, yana kiran ɗaya Aljanna ɗaya kuma wuta. Duk wanda ya zaɓi Aljanna, to, ita ce wutar. Duk wanda ya zaɓi wutar, to, ita ce Aljannar. Ya ce za a haɗa shi da Shaiɗanu guda biyu, suna magana da mutane; yana tare da fitina mai girma, saboda zai umurci sama da ta yi ruwa, nan da nan sai ruwan sama a ganin idon mutane. Ya kashe rai, kuma ya rayar da shi a ganin mutane, har ya tambayi mutane wa ke yin haka in ba Allah ba?

Sai mutane su ruga da gudu wajen dutsen. Dukkan a Sham (Syria). Sai ya je ya tsare su mai tsanani, su faɗa wa wahala. Sai Annabi Isah (as) ya sauka da sammako ya ce masu; "Ya Jama'a me ya hana ku, ku je ku yaƙi wannan mummunan mutum" sai su fito, sai su ga Annabi Isah (as). Sai a kira sallah, sai su ce masa ya yi masu limanci, sai ya ce a'a. Limaminku ya yi maku.

Idan suka gama sallah sai su fita zuwa wajen Dujal da ganin Annabi Isah sai Dujal ya narke, kamar yadda gishiri ke narkewa cikin ruwa. Sai Annabi Isah (as) ya kashe shi da kuma Yahudawa masu ba shi (Dujal), goyon baya, har ta kai itace, ko dutse zai ce ga wani Bayahude a bayana, ba zai bar

shi (Dujal) da wanda ya bi ra'ayinsa ba. A cikin Sahihul Bukhari, an zo da Hadisai masu kama da wannan. Ma'ana a cikin Hadisin Asma'u bintu Yazid Balansariyya yana cewa, "Abincin mumini a wannan lokaci tasbihi."

(طعام المؤنين يومئذ التسبيح). وفي صحيح مسلم: (يجزؤهم مايجزء أهل السماء من التسبيح والتقديس).

***"A cikin Muslim zai isa mumini abin da yake isar Mala'iku da ke sama na tasbihi da Taƙdisi."***

## 5- Abin da Zai Fitar da Mutum Daga Fitinar Dujal

Amma game da bayanin wanda zai tsira daga fitinar Dujal. Abin da Muslim ya ruwaito daga Abu Darda'u: Manzon Allah (saw) ya ce:

(من حفظ عشر آيات من أول سورة الكهف عصم من الدجال).

***"Wanda ya haddace aya goma na farkon suratul Kahfi, za a kare shi daga sharrin Dujal."***

A wata ruwayar: Ayoyi goma na ƙarshe. A ruwayar Abu Amamatul Bahil ya ce:

(وإن من فتنته أن معه جنة ونار فناره جنة وجنته نار فمن ابتلي بناره فاليستغث بالله واليقرأ فواتح الكهف فتكون عليه بردا وسلاما كما كانت النار على إبراهيم).

***"Yana daga cikin fitina Dujal yana da wuta da Aljanna. Wuta ita ce Aljanna, Aljanna ita ce wuta. Wanda aka fitine shi da wutarsa, ya karanta farkon surar Kahafi, sai wutar ta zamo mai sauyi mai lafiya, kamar yadda ta zamo ga Annabi Ibarahim (as)."***

Dukkan muwafaƙa tana ga Allah Ta'ala.

## FASALI NA SHIDA

### Dawowar Annabi Isah (as)

Za mu zo da abubuwa guda biyar a nan ma:

**Na Farko**: Bayanin hikimar saukar Annabi Isah (as).

**Na Biyu:** Bayanin idan ya dawo zai tabbatar da wannan shari'a ce ba zai zo da sabuwa ce ba.

**Na Uku:** Bayanin dukkan sauran addinai za su ɓace, sai addinin Islam kaɗai.

**Na Huɗu**: Bayanin yadda za a haɗa Hadisin zaman Isa (as) na shekaru arba'in ko shekaru bakwai.

**Na Biyar:** Bayanin wajen saukar shi da inda za a yi masa Kabari.

### 1- Hikimar Saukowar Annabi Isah (as)

Amma bayanin hukuncin saukarsa: Kurɗabi ya ce a **Attazkira** "Da za ka yi tambaya ka ce mene ne hikimar saukarsa a wani lokaci? Amsa ta fuska uku ce. Ta ɗaya: Yana iya ɗaukar cewa saboda Yahudawa suna da niyyar kashe shi, ko son kashe shi. Al'amarinsu ya bayyana kamar yadda Allah Ya faɗa a cikin littafinSa, saboda su har kullum sun ce sun kashe shi, kuma sun jingina shi da sihiri da makamantar haka. Amma Allah Ya kuɓutar da shi.

Allah kuma Ya sa wa Yahudu ƙasƙanci, ba su da sauran daraja, tun lokacin da Allah Ya ɗaukaka Muslunci, ya bayyana tutarSa, ba su da sauran wani iko a wata ƙasa ta kansu, ba su da sauran ƙarfi, ba iko, ba za su gushe ba a cikin wannan halin, har sai gaba da tashin Kiyama.

Sai Dujal ya bayyana, shi ne mafi sihirin masu yin sihiri, sai Yahuduwa su bi shi, su zama a wannan lokacin su ne rundunarsa, domin su azabtar da Musulmi. Shi ya sa Allah Ya sanar da mu cewa Yahudu sun kashe Isa (as), domin su gan shi da sauran munafukai da masu saɓawa, kuma Allah Ya taimake shi a kan shugabanninsu da masu da'awar rububiyya.

Annabi Isah (as) zai kashe Dujal, kuma ya ci nasara a kansa da kuma su, Yahudawa, da ƙarfin Allah da na sauran muminai. A ranar ba su da maɓoya da Bayahude zai ɓuya a jikin itace, ko dutse, sai itacen ko dutsen ya yi kira da cewa ya Ruhun Allah ga wani Bayahude a nan har sai an kama shi,

an kashe, ko kuma ya musulunta, har sai ya zama a bayan ƙasa babu wani kafiri.

**Ta Biyu:** Yakan ɗauki cewar ajalin Isah (as) ya kusa, shi ya sa zai sauko ba domin kashe Dujal ba. Saboda bai kamata ga wani abin halitta ya rasu a sama ba, sai dai dole a ƙasa kamar yadda Allah Ya tsara a ayar:

﴿ مِنۡهَا خَلَقۡنَٰكُمۡ وَفِيهَا نُعِيدُكُمۡ وَمِنۡهَا نُخۡرِجُكُمۡ تَارَةً أُخۡرَىٰ ﴾ طه: ٥٥

***"Mun halicce ku daga ƙasa, a cikinta za Mu mayar da ku, daga ita kuma za Mu mayar da ku a wani lokaci, don wanda suka yarda da shi su gan shi."***
**Alƙur'ani 20:55**

Su kuma ji maganarsa, sai Allah Ya ƙaddara masa mutuwa. Kuma muminai su jiɓinci yi masa wanka da salla da biznewa, a inda aka rufe Annabawa, nan ita ce ƙasar Kudus, inda dangin Maryam suke. Za a tashe shi idan aka zo tashin Annabawa. Saboda haka wannan shi ne sababin saukarsa, sai dai wannan lokaci ya yi daidai da zuwan Dujal zai zo ƙofar Masallaci, kamar yadda ya zo a cikin Hadisi, "Idan ya yi muwafaƙa da zuwan Isah (as) da zuwan Dujal, kuma a lokacin fitinar Dujal ta yi tsanani, domin ya yi da'awar Rububiyya.

Kuma ba wani muminin da zai iya yaƙar Dujal, sai ya zama shi, Isah (as) ne kaɗai yake da ikon haka, kuma aka ƙaddara mutuwar Dujal a hannunsa, saboda zaɓin da Allah Ya yi wa Annabi Isah na ba shi littafi da manzanci. Kuma Ya sanya shi da mahaifiyarsa su zama wata ayar Allah, ta wannan fuskar ya zama ya sauko ba domin ya kashe Dujal kaɗai ba. Allah ne kaɗai Masani.

**Hanya ta Uku:** Allah Ya nuna wa Annabi Isah (as) falalar al'ummar Manzon Allah (saw) a Linjila. Inda Ya ce, kuma maganar Allah gaskiya ce:

﴿ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِۚ وَمَثَلُهُمۡ فِي ٱلۡإِنجِيلِ ﴾ الفتح: ٢٩

***"Wannan shi ne misalinsu cikin Attaura misalinsu cikin Linjila kuwa..."***
**Alƙur'ani 48:29**

Saboda haka sai ya roƙi Allah da Ya haɗa shi da al'ummar Manzon Allah (saw), sai Allah Ya amsa addu'arsa, sai Ya ɗauke shi zuwa sama, domin a saukar da shi a ƙarshen zamani, domin ya jaddada abin da ya tsufa na al'amarin addinin Islam. Addinin Manzon Allah (saw), sai kuma ya yi muwafaƙa da bayyanar Dujal, sai ya kashe shi. Kuma bai zamo abin mamaki ba, yaƙin da zai da Dujal. Saboda bayyanar da ya yi cikin jama'a da kuma

tayar da fitinu ga al'umma. Ka ga yaƙi ya zama dole ke nan, kamar yadda sauran farillai suka wajaba. Saboda haka shi ne zai jagoranci a yaƙe shi, kuma ya nuna bayayyarsa ga Manzon Allah (saw).

**<u>2- Dawowar Annabi Isah (as) Don Tabbatar da Shari'a da Shari'a Ba Sabuwa Ba</u>**

Amma game da bayanin cewa in har Annabi Isah (as) ya sauka, zai yi aiki da wannan shari'a ce. Kuma zai jaddada ta, Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**; "Mutane sun yarda cewa, idan Annabi Isah (as) ya dawo za a cire masa wajabcin isar da manzanci, domin kada a sami wani Manzo mai umurni da hani bayan Manzon Allah (saw) Saboda ayar da take kiran Manzon Allah (saw) da hatimin nabi'in da inda shi ma ya ce:

﴿وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ﴾ الأحزاب: ٤٠

***"Babu wani Annabi bayana."*** **Alƙur'ani 33:40**

Saboda haka ba za a ce Isah (as) zai zo da wata shari'a sabuwa, daban da ta Manzon Allah (saw) ba. Idan ya zo zai bi shari'ar Manzon Allah (saw). Kamar yadda Manzon Allah (saw) yake faɗa:

(لعمري لوكان موسى حيا ماوسعه إلا اتباعي)،

***"Wallahi da Musa yana nan da rai, bai da iko sai dai ya bi ni."***

Saboda haka idan Isah (as) ya dawo zai bi addinin Islam ya kuma Jaddada shi; domin shi ne na ƙarshen Annabawa, sai ya zama malami mai adalci a lokacin da babu wani shugaba na Musulmi ko Liman, ko Alƙali, ko Mufti. Saboda Allah Ya ɗauke ilimi; mutane ba su da sauran ilimin addini, sai Annabi Isah (as) ya sauko a lokacin Allah Ya sanar da shi dukkan ilimi na addini na shari'ar Manzon Allah (saw), wanda zai yi wa mutane hukunci da shi. Sai dukkan muminai su haɗu a wurinsa, ya zama yana yi masu hukunci. Saboda shi kaɗai ne ya dace da wannan abu domin tozarta da hukunci bai kamata ba.

**<u>3- Batun Ɓacewar Sauran Addinai Sai Na Musulunci Kaɗai</u>**

Amma bayanin cewa dukkan addinai za su halaka, sai addinin Islam, an ruwaito a Sahihul Bukhari;

(لينزل ابن مريم حكما عدلا فليكسرن الصليب وليقتلن الخنزير وليضعن الجزية).

***"Ɗan Maryam zai sauka, a mai hukucin adalci, ya karya gumaka, ya kashe alhanzir ya yafe Jiziya."***

A wata ruwayar ta Dayalisi na cewa:

(أنه يكسر الصليب ويقتل الخنزير ويفيض المال حتى يهلك الله في زمانه المسيح الدجال الأعور الكذاب وتقع الأمانة في الأرض حتى يرعى الأسد مع الإبل، والنمر مع البقر، والذئب مع الغنم، وتلعب الصبيان مع الحيات فلايضر بعضهم بعضا).

***"Zai karya gunki (cross), ya kashe alade, dukiya ta wadata har zuwan mai ido ɗayan nan ɓatacce, maƙaryaci watau Dujal, wanda Annabi Isah zai halaka shi. Amana ta dawo har Zaki ya yi kiwo cikin garken Raƙuma, Daminsa cikin garken Shanu, Kura cikin garken Awaki, yara su yi wasa da Macizai lafiya lau."***

## 4- Bayanin Haɗa Hadisai Masu Nuna Shekaru Arba'in Ko Bakwai da Annabi Isah (as) Zai Yi Idan Ya Dawo

Amma bayanin haɗa ruwayoyin guda biyu, na shekara arba'in da na shekara bakwai, AbdurRahaman Suyuɗi ya ce a littafi **Itmamul Diraya** sharhin **Anniƙaya** da sharhin **Al-Kaukab**: A tsarinsa na Jami'ul Jawami'u da cikon tafsirin sa kamar yadda muka Ambato a ɗazu da waninsa.

(ويبقى عيسى عليه السلام في الأرض أربعين سنة ثم يموت ويصلي عليه المسلمون ويدفنونه).

***"Annabi Isah zai zauna a bayan ƙasa shekaru arba'in, sannan ya rasu, Musulmi su yi masa sallah, su rufe shi."***

A wata ruwayar:

(يمكث سبع سنين)،

***"Zai zauna shekara bakwai."***

Shi ne ya fi dacewa.

Abin da ake nufi da shekara arba'in a manyan farko, ma'anarsa yawan zamansa a duniya, kafin a ɗauke shi da bayan ya dawo, lokacin da aka ɗauke shi yana da shekaru talatin da uku. An faɗi wannan magana a ruwayar Muslim cewa zai zauna shekara bakwai. A Hadisin Abu Dauda Dayalisi, shekaru arba'in, sannan ya rasu a yi masa sallah ma'anarsa zaman da zai yi a bayan an dawo da shi.

Na ce haka AbdurRahaman Suyuɗi ke haɗa Hadisin guda biyu a mafi yawan rubutunsa na ta'lifi, kamar **Itmajud Dirayat** sharhin **Anniƙaya**, sharhin **Kaukab**, na **Jami'ul Jawami'i** da **Takmilati**. Kamar yadda muka faɗa a nan sama kaɗan da littafin **Ajawaba** da **I'ilamu** na saukar Isah (as) kodayake Malam Mahammad bini Abdul Baƙiy Zarƙani, ya yi wa Suyuɗi musu a cikin sharhin Hadisan da cewa Isah (as) zai zauna a bayan ƙasa shekara bakwai ne. Ya yi jifa da na shekara arba'in, ta hanyar tawili da muka faɗa a sama.

Sai ya ce Suyuɗi ya ba ni mamaki duk da yawan iliminsa da yawan bincikensa, amma duk da haka sai da ya haɗa Hadisan ya ƙyale ruwaya bayyananniya, ta zaman da Isah (as) zai yi na shekaru arba'in. Ya ce kodayake na ga wata magana ta Suyuɗi inda ya yi wa Abu Dauda sharhi mai suna **Mirkatus-Sa'ud** sai na ga inda Suyuɗi ya janye ra'ayinsa.

Haka nan kuma Imam Suyuɗi ya janye daga ra'ayin haɗa Hadisan a cikin littafi mai suna **Nawahidul-Abakar**. Annabi Isah (as) zai sauko daga sama, lokacin da Dujal ya fito zai zauna a bayan ƙasa na shekaru arba'in, sannan ya rasu, Musulmi su yi masa sallah, su kuma bizne shi.

Hafiz Amadud-din bini Katsir ya yi shakkar tabbatar a Sahihul Muslim daga Abdullahi bini Umar, cewa zai zauna a bayan ƙasa shekara bakwai. Sai ya ce, "Sai dai idan an ɗauke shi yana da shekaru talatin da uku ne". A mashahuriyar magana. Allah kaɗai ne Masani. Sannan Jalalud din Suyuɗi ya ce, "Na daɗe da wannan ra'ayi, sai da na gani a littafin Baihaƙi Al-Ba'asu Wamushur sai ya ce a Hadisin Annabi Isah (as) zai zauna a bayan ƙasa shekaru arba'in, a Hadisin Abdullahi Ɗan Umar a ƙissar Dujal: "Za a aiko Isah (as) ya neme shi, ya halakar da shi, sai mutane su zauna shekara bakwai babu adawa tsakaninsu."

Baihaƙi ya ce yana yiwuwa a ɗauki Hadisin da cewa sannan daga baya ya zauna, bai nuna yawan shekarun Isah (as) ba, saboda haka babu saɓani da na farko. Hanyar duba ta biyu: Kalimar "summa" tana da wata tawili, saboda Kalimar jinkiri ce.

**Hanya ta Uku:** Inda ya ce sannan daga bayansa sai mutane su zauna. Ana iya ɗaukar lamirin zuwa ga Isah, don shi ne na kusa da aka ambata.

**Hanya ta Huɗu:** Hadisi guda ɗaya ne ya zo da waccan kalima, mai iya ɗaukar tawili, amma Hadisan da suka zo da Kalmar shekaru arba'in sun yi yawa, sun kuma zo ta hanyoyi masu yawa. Wannan shi ne ingantanccen Hadisin Ɗabaraniyi daga Abu Huraira Manzon Allah (saw) ya ce:

(ينزل عيسى فيمكث في الناس أربعين سنة).

***"Annabi Isah (as) zai sauko ya zauna a cikin mutane shekaru arba'in."***

Akwai daga cikinsu abin da Ahmad ya fitar a cikin Zuhudu daga Abu-Huraira (rta) ya ce, "Kasa shekaru arba'in, duk rafin da aka umurta da ya zubo ruwan zuma sai ya zubo." Akwai Hadisin Ahmad a musnadinsa daga Aisha marfu'i a Hadisin Dujal sai

(فينزل عيسى ابن مريم فيقتله ثم يمكث عيسى في الأرض أربعين سنة إماما عادلا وحكما مقسطا).

***"Isah (as) zai sauko ya kashe Dujal, ya kuma zauna a bayan ƙasa shekaru arba'in yana shugaba, adili mai hukunci, a adalci ya zo."***

Kuma a Hadisin Bini Mas'ud wajen Ɗabari, waɗannan Hadisai masu yawa ne bayyanannu, sun fi Hadisi mai iya ɗaukar tawili, maganar da muka ɗauko cikin **Mizƙatus Su'al** ya zo ƙarshe.

**5- Wurin Da Annabi Isah (As) Da Yi Masa Kabari**

Amma game da bayanin wurin da zai sauka da wajen ƙabarinsa, ya gabata a Hadisai. Abu Dauda Dayalisi, cewa mutane suna gudun Dujal har zuwa dutsen Dukkan a Sham (Syria), ya zo masu ya tsare su. Suna nan sai Annabi Isah (as) ya zo masu lokacin asuba sai ya ce, "Ya ku mutane me ya hana ku, ku fita, ku yaƙi wannan maƙaryacin, mai munanan hali?" Sai su fito sai su ga Annabi Isah (as).

Amma bayanin wajen ƙabarinsa, a nan malamai suna da bambancin ra'ayi. Wasu suka ce a Kudus haka, Hailami ya faɗa. Wasu suka ce a Madina tare da Manzon Allah (saw), kamar yadda ya zo cikin Hadisi. Kurɗabi ya ce a **Attazkira**: "Za a rufe shi, Isah (as), a gefen Manzon Allah (saw) a ɗakinSa, kuma an ce za a rufe shi ne a Kudus, inda aka rufe Annabawa (saw).

# FASALI NA BAKWAI

## Yajuju da Majuju

A nan ma za mu zo da abubuwa guda biyar ne:

**Na Farko:** Bayanin dangantakarsu.

**Na Biyu:** Wajen da za su toshe.

**Na Uku:** Bayanin lokacin fitowarsu.

**Na Huɗu:** Bayanin ɓarnar da za su yi a bayan ƙasa idan sun fito.

**Na Biyar:** Bayanin yadda Allah Zai halakar da su.

## 1- Dangantar Yajuju da Majuju

Amma game da dangantakarsu, haƙiƙa, Kurɗabi ya ce a **Attazkira** Dahhaku ya ce: "asalinsu Turkawa ne." Makatil ya ce, "Su 'ya'yan Yafsu ne 'ya'yan Nuhu (as), wannan magana, An ruwaito daga Amr bini **Al-Ass** (rta). Ya ce; Yajuju da Majuju, 'ya'yan Nuhu (as) ne. Muhalli ya ya ce a cikin tafsirinsa, inda Allah Ya ce:

﴿ وَجَعَلْنَا ذُرِّيَّتَهُۥ هُمُ ٱلْبَاقِينَ ﴾ الصافات: ٧٧

*"Muka sanya zuri'arsa su ne masu wanzuwa."* **Alƙur'ani 37:77**

Mutane dukkansu daga zuri'ar Annabi Nuhu ne, yana da 'ya'ya uku; Samu, shi ne kakan Larabawa, sai Hamu, kakan Baƙar fata sai Yafisu, kakan Turkawa da Hazaraj da Yajuju da Majuju da makamantansu.

## 2- Inda Yajuju da Majuju Za Su Toshe

Amma inda zai toshe, Ahufiyi ya yi bayani a tafsirinsa, a wani yanki ne na ƙasar Turkawa, wajen mafitar rana, kamar yadda ya zo a **Attazkira** na Kurɗabi. Muhalliyi ya ce a cikin tafsirinsa inda aya ta ce;

﴿ ثُمَّ أَتْبَعَ سَبَبًا ۝٩٢ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيْنَ ٱلسَّدَّيْنِ ﴾ الكهف: ٩٢ – ٩٣

*"Sannan ya bi sababi har ya isa tsakanin ƙafa biyu."* **Alƙur'ani 18:92-93**

Su ne duwatsu guda biyu a yankin garin Turkawa, inda Askandariyya ta toshe tsakaninsu.

## 3- Lokacin Fitar Yajuju da Majuju

Amma lokacin fitarsu: Bini Hajari Shehul Islam ya yi bayani a cikin sharhin Bukhari, cewa lokacin fitar Yajuju da Majuju. A zamanin Annabi Isah (as) ne kamar yadda yake a cikin sharhin **Kaukab** na AbdurRahaman Suyuɗi.

Muslim ya fitar da Ɗan Majah da Abubakar bini Shaibatu da Lafizina bini Majah daga Abdullahi ɗan Mas'ud (rta) ya ce: “Lokacin da aka yi Isra'i da Manzon Allah (saw) ya gamu da Annabi Ibrahim da Isah da Musa (as) suka yi magana na kamar sa'a ɗaya. Aka fara da Annabi Ibarahim (as). Suka tambaye shi amma bai da masaniya a kanta. Sai aka tambayi Musa (as), bai da masaniya a kanta, sai aka juya da magana ga Annabi Isah (as), “An yi mani alƙawarin lokacinta, amma ba a faɗa mani ba, ba wanda ya san lokacinta sai Allah.” Sai aka yi maganar Dujal, sai ya ce zai sauka in kashe shi sai mutane su koma garinsu, sai su haɗu da Yajuju da Majuju ta kowane tudu za su hau.

Abul-Hassan Muhammad bini Abaidullahil Kasa'iyi ya ce a littafin **Kisasul Anbiya** (as). Wahab bini Munbahhu da Ka'abul Ahabar (rta) sun ce: Bayan Annabi Isah Ɗan Maryam ya kashe Dujal zai auri wata mace Balarabiya, ya yi kwanakin da Allah Ya so sannan Yajuju da Majuju su bayyana, su cika ko’ina da kowane tudu.

## 4- Ɓarnar Yajuju da Majuju A Doron Kasa In Sun Fito

Amma bayanin abin da za su aikata na ɓarna a bayan ƙasa idan sun fito, Bini Majah ya fitar daga Abu Sa'idul Khudri (rta) cewa Manzon Allah (saw) ya ce;

(تفتح يأجوج ومأجوج فيخرجون كما قال الله تعالى: ﴿ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٍ يَنسِلُونَ ﴾، فيعمون الأرض فينحاز منهم المسلمون حتى تصير بقية المسلمين في مدائنهم وحصونهم ويمضون إليهم مواشيهم حتى إنهم ليمرون بالنهر فيشربونه حتى مايذروا فيه شيئا فيمر آخرهم على آثارهم فيقول قائل لقد كان المكان مدة للماء ويظهرون على الأرض).

***“Za a buɗe wa Yajuju da Majuju ƙofa su fita kamar yadda Allah Ya faɗa. Kowane tudu za su hau, ma'ana za a same su, su cika bayan ƙasa, har Musulmi su ji tsoron su, har sai su ɓuya a cikin biranensu tare da dabbobinsu, ya kai halin da idan Yajuju da Majuju suka zo bakin rafi ko kogi, sai su shanye duk ruwan da ke cikin su, ba za su bar koda ɗigo ɗaya ba, na bayansu idan sun iso sai su ce da nan akwai ruwa kuwa. Haka dai za su cika ƙasa”.***

Muslim ya fitar daga Abubakar bini Abu Shaiba da Bini Majah lafazin Hadisin na Bini Majah ne. A wata ruwayar Hadisi:

(فلايمرون بماء إلا شربوه ولاشيئا إلا أفسدوه).

***"Ba za su wuce wani rafi ba, sai sun shanye shi, ko kuma wani wuri sai sun ɓata shi."***

**<u>5- Yadda Allah (swt) Zai Halaka Yajuju da Majuju</u>**

Amma game da bayanin, abin da Allah Zai halakar da su da shi, Kurɗabi ya ce a **Attazkira** Ka'abul Ahbar ya ce: "Su Yajuju da Majuju, za su harba kibansu wajen sama, sai su ce "Mun fi ƙarfin wanda ke sama, kamar yadda muka fi ƙarfin wanda ke ƙasa." Sai Allah Ya tura masu wata dabba mai suna **Na'afu** sai ta kama su ta yi ta kashe su.

A wani Hadisi na Nawasu bini Sama'an (rta) ya ce "Yajuju da Majuju za su ce mun fi ƙarfin wanda ke ƙasa, saboda haka mu himmatu mu fi ƙarfin wanda ke sama, sai su harba kibansu sama, sai Allah Ya dawo masu da kibansu, sun kwaɓe da jini, sai su ce mun ci nasara ga jama'ar sama, sai Annabin Allah Isah (as) ya roƙi Allah, sai ya aiko masu da wata dabba mai suna **Na'af u** ta sauka a wuyansu, gari na wayewa sai ka same su kwance matattu. A wani Hadisin wanda Hakim ya ruwaito a cikin mustaɗarik daga bini Mas'udu daga Manzon Allah (saw) ya ce:

(فيصبحون موتى أجمعين وينتن الأرض منهم فيؤذون الناس بنتنهم فيستغيثون الله عز وجل فيبعث الله ريحا عاتية غبراء ويكشف مابهم بعد ثلاث وقد قذفت جميعهم في البحر لايلبثون إلا قليلا حتى تطلع الشمس من مغربها).

***"Sai gari ya waye masu suna matattu gaba ɗayansu, duniya ta cika da warinsu. Mutane su shiga damuwa, saboda warinsu, sai Allah Ya tayar da wata iska mai ƙura, ga ta kuma da ƙarfi, sai ta kwashe abin da ya damu mutane a cikin kwana uku, ta jefa duk gawarwakin cikin Teku, kuma ba za a daɗe ba sai rana ta fito daga mafaɗarta."***

Dukkan dacewa tana ga Allah kaɗai.

## FASALI NA TAKWAS

## Ɗauke Alƙur'ani

A nan zan zo da abubuwa guda uku ne, kaɗai:

**Na Farko:** Bayanin cewa Alƙur'ani za a ɗauke shi cikin dare ɗaya babu abin da zai saura ko da aya ɗaya ce.

**Na Biyu:** Bayanin cewa duk abin da ke cikin ƙirjin mutane na haddar Alƙur'ani za a ɗauke shi, kamar yadda ake ɗauke littafi.

**Na Uku:** Bayanin cewa wannan zai auku ne, bayan tafiyar Annabi Isah (as); Dukkan muwafaƙa tana ga Allah Shi kaɗai.

### 1- Ɗauke Alƙur'ani Cikin Dare Ɗaya

Amma game da bayanin ɗauke A1ƙur'ani cikin dare ɗaya, ba abin da zai saura, an ruwaito daga Bini Majah daga Hadisin Huzaifa ya ce "Musulunci zai tsufa kamar yadda tufafi ke tsufa, har ya kai halin da ba a san mene ne Azumi ko sallah, ko yadda ake yanka, ko zakka ba. Wannan tsufan zai yi naso har ga Alƙur'ani . Sai a tashi da safe ba shi ko da aya ɗaya. Sai ka ga tsohon mutum ko mace suna cewa mun sami iyayemmu suna cewa "la-ilaha illallahu" mu ma muna cewa, amma ba mu san ta ba sai 'Saltu' ya ce, "To, ai wannan-la-ilahaillallahu ba za ta yi amfani ba ke nan tun da ba su san Azumi ko yanka ko zakka ba." Sai Huzaifa ya kawar da kansa, Saltu ya maimaita kalimarsu har sau uku, Huzaifa na kawar da kansa, sai ya ce kai Salta ai ita kalima (la-ilaha illalahu) za ta tsirar da su daga shiga wuta.

### 2- Bayanin Yadda Za A Ɗauke Abin da Ke Kirjin Mahaddata Na Alƙur'ani

Amma bayanin ɗauke abin da ke ƙirjin mahaddata, kamar yadda ake ɗauke littafi, Baihaƙi ya ruwaito a littafi mai suna; **'Shu'abul-iman'** daga Bini Mas'udu ya ce; "Ku karanta A1ƙur'ani kafin a ɗauke shi, saboda ba za a yi tashin ƙiyama ba sai an ɗauke shi." Sai suka ce, "Wannan rubutun na Alƙur'ani . To, yaya za a yi da na ƙirjin mahadatta?" Sai ya ce "Ai cikin dare ɗaya Allah Zai ɗauke shi, sai su wayi gari ba kome sai su ce ina abin da muka haddace." Sai dai su yi ta waƙoƙi.

3- Bayanin Aukuwar Haka Bayan Tafiyar Annabi Isah (as)

Amma bayanin cewa wannan zai auku ne bayan tafiyar Annabi Isah (as), Kurɗabi ya ce a **Attazkira** ɗauke Alƙur'ani zai zo ne bayan tafiyar Annabi Isah (as), bayan shi kuma sai mutanen Habasha su rusa ɗakin Ka'aba.

Abu Shehu ya fitar a littafin **Al-Fitanu** daga Abu Huraira (rta) ya ce Manzon Allah (saw) ya ce:

(ينزل عيسى ابن مريم ويقتل الدجال ويمكث أربعين عاما يحكم فيهم بكتاب الله وسنتي ويموت فيستخلفون رجلا من بني تميم يقال له المقعد وذلك بأمر عيسى عليه السلام وإذا مات المقعد لم يأت على الناس ثلاث سنين حتى يرتفع القرآن من صدورهم ومصاحفهم).

***"Isah Ɗan Maryam zai sauko, ya kashe Dujal, ya zauna a duniya shekaru arba'in ya jagoranci jama'a da littafin Allah da sunnata, sai ya rasu, sai a ba da halifanci ga wani mutum cikin ƙabilar Tamimu mai suna Maƙa'adu, za a ba shi da umurnin Isah (as), idan Maƙa'adu ya rasu, ba za a yi shekaru uku ba, sai a ɗauke Alƙur'ani a cikin ƙirjin mahaddata."***

Dukkan muwafaka tana ga Allah.

## FASALI NA TARA

### Fitar Dabba

Za mu zo da abubuwa guda biyar ne a wannan fasali:

**Na Farko:** Bayanin lokacin fitowarta.

**Na Biyu:** Bayanin wajen fitowarta.

**Na Uku:** Bayanin yawan fitarta.

**Na Huɗu:** Bayanin me ke tare da ita, idan ta fito.

**Na Biyar:** Bayanin siffarta.

### a) Lokacin Fitowar Dabba

Game da bayanin lokacin fitowarta; Haƙiƙa, Allah Ya ce:

﴿ وَإِذَا وَقَعَ الْقَوْلُ عَلَيْهِمْ أَخْرَجْنَا لَهُمْ دَابَّةً مِّنَ الْأَرْضِ تُكَلِّمُهُمْ ﴾ النمل: ٨٢

***"Idan zance ya tabbata sai mu fitar da wata dabba a bayan ƙasa, da za ta riƙa magana da mutane."*** **Alƙur'ani 27:82**

Kurɗabi ya ce a **Attazkira**, Imam Bagawi Abul-Kasim Abdullahi bini Muhammad bini Abdul'Azeez ya ruwaito daga ɗan Umar (rta) ya ce: "Dabba za ta fito daga wata kafa a jikin Ka'aba, saurinta kamar gudun Doki, amma a tsawon kwana uku, ko da sulusinta (1/3) bai fito ba Mawashi. Ya ambata daga Abu-Huraira (rta) daga Manzon Allah (saw) ya ce: "Dabba za ta fito daga Jiyad har ta kai Rukunul Yamani.

### b) Wajen Da Dabbar Za Ta Fito

Amma wutsiyarta ba ta fito ba. An ruwaito daga Hadisin Hashim bini Yusuf Alƙali daga Abu-Huraira (rta) ya ce Manzon Allah (saw) ya ce:

(بيس الشعب جياد).

***"Faɗa man garin Jiyadu ya halaka."*** **Alƙur'ani 27:82**

Suka ce, saboda mene ya Rasulul-llahi? Ya ce:

(تخرج منه الدابة فيصرخ ثلاثة صرخات فيسمعها من بين الخافقين).

***"A nan ne dabba za ta fito, za ta yi kururuwa sau uku dukkan gefen duniya za su ji."***

An samu daga Amr bini Ass: ya ce "Dabba za ta fito daga Makka a lokacin aikin Hajji, kanta zai kai cikin girgije, amma kafafuwnta ba su gama fita daga ƙarƙashin ƙasa ba."

Malam Atabi ya ambata a cikin littafinsa **Uyunul-Akhbar**. Abdullahi Ɗan Umar (rta) ya ce, "Dabba za ta fito daga dutsen Safa a Makka, sai ya tsage biyu sai ta fito daga gare shi." Abdullahi bini Umar ya faɗi irin haka sai ya ce, "Da na so in sanya ƙafata a wurin da za ta fito da na sanya." An ruwaito daga Katada, cewa ita dabbar za ta fito ne daga garin Tahama. An kuma ruwaito cewa za ta fito ne daga masallacin Kufa, daga inda ruwan ɗufana na tandar Annabi Nuhu ya cika. Wasu kuma sun ce daga garin Ɗa'ifa

**c) Yawan Fitar Dabbar**

Amma bayanin yawan fitar da za ta yi, Abu Dauda Dayalisi ya faɗa a musnadinsa daga Huzaifa (rta) ya ce, Manzon Allah (saw) ya ambaci Dabbar sai ya ce;

**(لها ثلاثة خرجات من الدهر فتخرج في أقصى البادية ولايدخل ذكرها القرية** (يعنى مكة)، **ثم تمكث زمانا طويلا ثم تخرج خرجة أخرى دون ذلك فيفشو ذكرها في البادية لايدخل ذكرها القرية** (يعنى مكة) **ثم تمكث زمانا طويلا ثم تخرج خرجة أخرى دون ذلك فيفشو ذكرها في البادية ولايدخل ذكرها القرية** (يعنى مكة).

***"Za ta fito sau uku ne, a zamaninta. Na farko za ta fito a wani ƙauye mai nisa ga gari, har labarinta ba zai shiga cikin gari ba, sannan ta zauna tsawon lokaci. Sannan ta ƙara fita na biyu a nan duk ƙauyen za su sami labarin ta, amma ba za ta shiga cikin gari ba, yana nufin garin Makka."***

Sai Manzon Allah (saw) ya ce:

**(بينما الناس في أعظم المساجد على الله حرمة وخيرها وأكرمها على الله المسجد الحرام لم يرعهم إلا وهي ترغو بين الركن والمقام تنفض عن رأسها التراب).**

***"Mutane suna cikin babban Masallaci mai alfarma ga Allah, kuma ma fi alhairin masallatai, mafi girma ga Allah, watau masallaci mai alfarma, sai kawai mutane su gan ta a firgice, tsakanin Rukunul yamani da Maƙamu Ibrahima, tana share ƙasa a kanta."***

**<u>d) Abin da Ke Tare da Dabbar</u>**

Amma game da bayanin abin da ke tare da ita, idan ta fito. Haƙiƙa, Bini Majah ya fitar daga Abu Huraira (rta) ya ce, Manzon Allah (saw) ya ce;

**(تخرج الدابة ومعها خاتم سليمان بن داود وعصى موسى بن عمران فتجلو وجه المؤمن بالعصى وتخطم أنف الكافر بالخاتم حتى أن أهل الإخوان ليجتمعون فيقول هذا يامؤمن ويقول هذا ياكافر).**

***"Dabba za ta fito tare da ita akwai zoben Annabi Suleimana ɗan Dauda da sandar Musa Ɗan Imrana, sanda za ta nuna fuskar Mumini ta kuma cokale hancin kafiri da zoben har ta kai 'yan'uwa biyu sun haɗu, wannan na kiran wancan kafiri wannan mumini."*** Tirmizi ya fitar.

Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**: "Haƙiƙa, an ce, tana hura wata alama ga mutane biyu sai ta ga mumini, sai ta yi busa a fuskar mumini kuma ta yi busa a fuskar kafiri. Ta ce "Ya Kafir." Sai Kurɗabi ya ce da busawa da alamtawa a lokaci guda ne, kowane sai ya dace da wurinsa. Ka ga maganar ba ta sukar juna ke nan. Allah kaɗai ne Masani.

**<u>e) Bayanin Siffar Dabbar</u>**

Amma bayanin siffarta, Abu-Zubair ya ruwaito kamar yadda yake a cikin littafin **Attazkira** na Kurɗabi cewa ita wannan dabba ta haɗa dukkan halitta na sauran dabbobi. Kanta dai kamar kan Ɓauna; tana da idon Alade; tana da bindin Giwa; tana da ƙahon Karakanda; tana da wuyan Jimina; tana da kirjin Zaki, tana da launin Damisa; tana da kwiɓin Kyanwa (Mage); tana da wutsiyar Rago; tana da ƙafar Raƙumi; tana da gaɓoɓi tsakaninsu kamu (zira'i) goma sha biyu; Haka Sa'alabi da Mawardi suka faɗa da wasunsu su.

An ruwaito cewa tana da gashi yamutsattse. An ruwaito cewa ita Dabbar ita ce Jassasa, kamar yadda ta zo a cikin Hadisin Fatima binti Kaisi, wanda Muslim ya fitar.

A taiƙaice, amma ta hanyar Muslim. Haƙiƙa, an ce ita, wannan dabba wadda za ta fito, ita, 'yar taguwar (Raƙumar) Annabi Salihu (as) lokacin da aka soke mahaifiyarta, ta gudu ta yi wajen wani dutse ta hura shi, ya tsage biyu ta shige cikinsa, sai ya haɗe. Tana nan a cikin dutsen har lokacin fitarta ya zo sai ta fito da yardar Allah. Sai Kurɗabi ya ce, "Wannan magana tana shiga cikin riwayar Huzaifa (rta) inda ya ce, tana kuka irin na Raƙumi." Allah kaɗai Masani.

## FASALI NA GOMA

### Fitowar Rana Daga Mafaɗarta

Za mu zo da abubuwa guda biyar su ma a wannan Fasali:

**Na Farko:** Bayanin tsawon daren da rana za ta fito daga mafaɗarta.

**Na Biyu:** Bayanin cewa za a rufe ƙofar tuba lokacin da rana ta fito daga mafaɗarta.

**Na Uku:** Bayanin hikimar fitar da rana za ta yi daga mafaɗarta.

**Na Huɗu:** Bayani mafi rinjaye idan aka haɗa labarin da farkon ayoyin shin shi ne wannan fitar, ko kuma waninsa ne?

**Na biyar:** Tsawon da ya rage na mutane a duniya bayan fitowar rana daga mafaɗarta.

### 1) Tsawon Daren da Rana Za Ta Fito Daga Mafaɗarta

Amma bayani game da tsawon daren da rana za ta fito daga mafaɗarta, Baihaƙi ya fitar a cikin littafinsa **Shu'ab** daga Abdullahi ɗan Umar ya ce; Rana za ta faɗi ta yi sujuda, ta yi sallama, ta nemi izini, sai a ƙi yi mata izini har sau biyu, ko uku na kwanaki, sai a ce mata "Koma daga inda kika fito." Abdul bini Humaid ya fitar a tafsirinsa daga Hadisin Abdullahi bini Abi Aufa ya ce, "Dare zai zo wa mutane na tsawon kwana uku, ba mai sanin haka sai masu sallar dare, saboda ya karanta hizbinsa ya kwanta mutane su cakuɗe da junansu, idan suka yi sallar subahi suka zauna, sai kawai su ga rana ta fito daga mafaɗarta, sai mutane su fashe da kuka, idan ranar ta zo tsakiya, sai ta koma, ta ci gaba da yadda ta saba; wannan Hadisi na wasu shaida ne amma Marfu'ai."

Abu Is'haƙa Sa'alabi ya ce da waninsa, masana tafsirin Hadisi, "Za a yawaita saɓo a bayan ƙasa, abin kirki ya tafi ba mai yin umurni da shi, abin ƙi (munkar) ya watsu ga kowa. Ba masu hana munkar, ko da na kwana ɗaya ne. Sai rana ta yi sujuda ta kuma nemi izini wajen Allah. Ta ina za ta fito? Ba za a amsa mata ba, har kamar na kwana uku. Wata shi kuma kamar na kwana biyu, ba wanda ya san wannan abu ya auku sai masu yin sallar dare. Su kuma 'yan kaɗan ne a gururuwan Musulmi. Idan aka cika waɗannan kwanakin, sai Allah Ya aiko wa Jibrilu (as) cewa, Allah Ya karɓi jawabinsu, amma Yana umurtar su da su koma su fito daga mafaɗarsu, su kuma fito ba tare da haske ga rana ba, wata ba tare da annuri ba. Kamar suna cikin halin kusufi. Shi ne inda Allah Ya ce masu:

﴿ وَجُمِعَ ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ ﴾ القيامة: ٩

***"Idan Muka haɗa rana da wata."*** **Alƙur'ani 75:9**

Da kuma inda Ya ce:

﴿ إِذَا ٱلشَّمۡسُ كُوِّرَتۡ ﴾ التكوير: ١

***"Idan kuma aka shafe hasken rana."*** **Alƙur'ani 81:1**

Haka nan kuma za su fito su yi sama ba haske gare su kamar Raƙuma. Ko kamar Dawaki. Idan rana da wata suka kai cibiyar sama, wato rabin sama, sai Jibirilu (as) ya zo masu, ya kama ƙahonninsu, ya koma da su inda suka saba faɗuwa, amma ta kofar tuba zai kai su.

Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**, "Sannan rana da wata za a sanya masu haskensu da annurinsu, su ci gaba da fitowa da faɗuwa yadda aka saba.

## 2) Bayanin Rufe Kofar Tuba Lokacin da Rana Ta Fito Daga Mafaɗarta

Amma bayanin cewa ƙofar tuba za a rufe ta, lokacin da rana ta fito daga mafaɗarta, Bukhari da Muslim sun ruwaito daga Abu Huraira Manzon Allah (saw) ya ce:

(لاتقوم الساعة حتى تطلع الشمس من مغربها فإذا طلعت ورآها الناس آمنوا أجمعون وذلك حين لاينفع نفس إيمانها لم تكن آمنت من قبل أوكسبت في إيمانها خيرا).

***"Ba za a yi tashin ƙiyama ba sai rana ta fito daga mafaɗarta. Idan ta fito a haka, sai mutane su yi imani gaba ɗayansu,a lokacin ne imani ba ya da amfani, wanda ba a riga an yi ba, ko kuma wani aikin alhairin da ba a riga an yi ba."***

Muslim ya ruwaito daga Hadisin Abu Huraira game da tashin ƙiyama

(من تاب قبل أن تطلع الشمس من مغربها تاب الله عليه).

***"Duk wanda ya tuba kafin fitar rana daga mafaɗarta, to, Allah Zai karɓi tubansa."***

Tirmizi ya fitar da Darul ƙuɗini daga Safwan bini Usala Maradiyyi ya ce na ji Manzon Allah (saw) ya ce:

(إن بالمغرب بابا مفتوحا للتوبة مسيرة سبعين سنة لايغلق حتى تطلع الشمس من نحوه).

***"A nan yamma akwai wata ƙofa buɗaɗɗiya domin karɓar tuba, ta kai faɗin tafiyar yini saba'in."***

Ba za a rufe ta ba har sai rana ta fito daga mafaɗarta. Kurɗabi a cikin **Attazkira** ya ce, "Malamai sun ce abin da ya sa imanin ba zai yi amfani ba, daga lokacin da rana ta fito daga mafaɗarta. Saboda tsoro ya rufe zuciyarsu. Wannan tsoron ya kawar da dukkan sha'awar duniya: jiki ya zama ba ƙarfi a gare shi. Saboda ganin tabbas na tashin alƙiyama, sai ya zama kamar mutumin da ya faɗa wa gargarar mutuwa ne, saboda yankewar nau'o'in saɓon Allah daga zuciyarsu da jikinsu. Duk wanda ya tuba a wannan halin ba a karɓi, tubansa ba kamar yadda ba a karɓar tuban wanda mutuwa ta same shi.

Manzon Allah (saw) ya ce:

(إن الله يقبل توبة لعبد مالم يغرغر).

***"Allah Yana karɓar tuban bawa, idan bai kai halin gargara ba."***

Ma'anarsa ruhinsa ya kai ga fita daga maƙogoronsa. A lokacin an riga an nuna masa makomarsa. Ko dai cikin Aljanna ko kuma cikin Wuta. Shi kawai ganin rana daga mafaɗarta kamar haka yake.

## 3) Hikimar Fitar da Rana Daga Mafaɗarta

Amma game da bayanai a kan hikimar fitar rana daga mafaɗarta, Haƙiƙa, Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira**: "An ce hikimar ita ce Annabi Ibrahim (as) ya ce wa Namarudu:

﴿فَإِنَّ ٱللَّهَ يَأْتِي بِٱلشَّمْسِ مِنَ ٱلْمَشْرِقِ فَأْتِ بِهَا مِنَ ٱلْمَغْرِبِ فَبُهِتَ ٱلَّذِي كَفَرَ﴾ البقرة: ٢٥٨

***"Allah Yana fito da rana daga gabas, kai kuma sai ka fito da ita daga yamma, sai kafiri ya ruɗe."*** **Alƙur'ani 2:258**

Saboda haka ne masu musun addini da masu ilimin taurari suke musun fitar rana daga yamma. Suna cewa wannan abu ba zai yi wu ba, sai Allah Ya ƙaryata su. Saboda haka Zai fito da rana daga yamma, domin masu musu su ga ikon Allah cewa, rana tana cikin mallakarSa ne, idan Ya so Ya fito da ita daga yamma, idan Ya so Ya fito da ita daga gabas.

## 4) Shin Fitar Rana Ce Ko Kuma Waninta Ne?

Amma bayani game da mene ne farkon ayar sa zai nuna tashin ƙiyama, kuma mene ne aka yi ijima'i a kansa. Shin wai fitar rana ce ko kowannensa ne?

Kurɗabi ya ce a cikin **Attazkira** "Ruwayoyi sun saɓa, cewa mene ne farkon alamomin tashin alƙiyama. Wasu sun ruwaito cewa fitar rana, ita ce ta farko kamar yadda ya zo a Hadisin Muslim. A wannan babin, wasu suka ce bayyanar Dujal. Wannan magana ita ta fi a cikin zantuttukan, ta fi kuma inganta, kamar yadda Manzon Allah (saw) ya ce:

(إن الدجال خارج فيكم لامحالة)

***"Dujal zai fito a cikinku ba makawa."***

Har zuwa ƙarshen Hadisin da tsawonsa. Da a ce a lokacin rana har ta riga ta fito daga yamma da Yahudu imaninsu ba zai yi masu amfani ba, a lokacin zuwan Annabi Isah (as) da kuma bai yi amfani ba, da addini bai zama guda ɗaya ba, saboda musuluntar da suka yi.

An ce a cikin **Attazkira**, a wani wurin daban, "Alamomin tashin ƙiyama sun zo a jere." Hadisin Huzaifa ya ce: "Muna tare da Manzon Allah (saw) a wani ɗaki, muna gangare, sai Manzon Allah ya zo mana ya ce kan me kuke magana? Muka ce a kan tashin ƙiyama sai ya ce:

(إن الساعة لاتقوم حتى ترو عشرة آيات: خسف بالمشرق، وخسف بالمغرب، وخسف بجزيرة العرب، والدخان، والدجال، ودابة الأرض، ويأجوج ومأجوج، وطلوع الشمس من مغربها، ونار تخرج من قعر عدن ترحل الناس)." ثم قال بعض الرواة في العاشرة: (ونزول عيسى ابن مريم). وقال بعضهم: (وريح تلقى الناس في البحر).

***"Kiyama ba za ta tashi ba sai kun ga alamomi guda goma: Kusufi a gabas da Kusufi a yamma da Kusufi a Jazirar Larabawa da hayaƘI da Dujal da Dabbar ƙasa da Yajuju da Majuju, fitar rana daga yamma, wuta ta fito daga garin Adan tana korar mutane, sannan sashen wani ruwaya ya ji a na goma zuwan Annabi Isahɗan Maryam (as). Wasu suka ce ta goma, iskar da za ta riƙa jefa mutane cikin Teku."***

Muslim ya fitar. Sannan ya ce, "Farkon alamar tashin ƙiyama a wannan ruwaya, kusufi guda uku. A nan Hadisin ya faɗi dabba kafin Yajuju da Majuju, amma ba haka ba ne ta farko ita ce bayyanar Dujal, sai Annabi Isah (as), sai Yajuju da Majuju. Idan Allah Ya kashe su da tsutsar **Anafu** a wuyansu Allah Ya karɓi Annabinsa Isa (as), aka bar duniya ba kome, kwanaki suka yi tsawo ga jama'a, harkar addini ta ɓace, mutane suka shiga komawa zuwa ga halinsu, suka ƙagi kafirci da fasiƙanci, kamar yadda suka yi a da, sai Allah ya kama su da hujja.

Sai ya fitar da dabba daga ƙasa tana nuna ɗan'Aljanna da ɗan-wuta, domin ko kafiri ya daina kafircinsa ya dawo hanyar ƙwarai. Mai fasiƙanci ya

bar fasikancinsa, domin su faɗaka, su dawo ga hanyar ƙwarai, sai dabbar ta ɓace masu, a kuma sami tsawon lokaci. Idan suka sake komawa ga laifi sai rana ta fito daga mafaɗarta, daga nan ba za a karɓi tuban kafiri ko na fasiƙi ba.

Idan ka yi tambaya ka ce ta yaya za a haɗa da ruwayar Muslim daga Abdullahi Dan Umar (rta) ya ce na haddace daga Manzon Allah (saw):

(إن أول آية خروجا طلوع الشمس من مغربها، وخروج الدابة على الناس ضحى).

***"Farkon alamar tashin ƙiyama fitar rana daga yamma sai fitar dabba ga mutane a lokacin waluha."***

Duk wadda ta fara fita 'yar'uwarta na biye. Da kuma abin da Bukhari ya ruwaito daga Anas bini Malik (rta) ya ce "Manzon Allah (saw) ya ce:

(أول أشراط الساعة نار تحشر الناس من المشرق إلى المغرب).

***"Farkon alamar tashin alƙiyama, fitar wuta daga gabas zuwa yamma tana korar mutane."***

Amsa a kan wannan shi ne kamar yadda Shehul Islam Bini Hijir, Askalani ya ce a cikin sharhin Bukhari abin da dai aka fi rinjayar wa shi ne. Abu mafi girma wanda zai cuci mutane, kuma ya sauya masu hali shi ne bayyanar Dujal sai saukar Annabi Isah (as), sai fitar Yajuju da Majuju a lokacin Annabi Isah (as) yana duniya, dukkan waɗannan sai sun zo sannan fitar rana daga yamma.

Sannan babbar alama kuma, wadda za ta sauya halin halittar sama, ita ce fitar rana daga yamma, bayan bayyanar dabba, a wannan rana, ko kusa da wannan rana.

Sannan babbar alama mai sanarwa game da tashin ƙiyama, ita ce tashin wuta kamar yadda ya zo a Hadisin Anas a cikin Sahihul Bukhari ya ce:

(أول أشراط الساعة نار تحشر الناس من المشرق إلى المغرب).

***"Farkon alamun tashin alƙiyama wutar da za ta kori mutane daga gabas zuwa yamma."***

Ta haka ne ake iya haɗa Hadisan.

Amma game da bayanin tsawon lokacin zaman mutane bayan fitar rana daga yamma, Bini Abu Shahiba ya ruwaito daga Abdullahi Ɗan Umar (rta), "Mutane za su ƙara zama a duniya bayan fitar rana daga yamma shekaru ɗari da ashirin (120), sai na ce amma mutanen lalatattu ne watau **Ashaƙarai** Bini

Abi Shaiba ya ruwaito, kuma a Musannarifi daga Abdullahi Ɗan Umar (rta) ya ce **Ashaƙaran** mutane suna da shekaru ɗari da ashirin bayan wucewar na kirki. Abu Nu'aim ya fitar kuma a littafin **Alfitari.**

Abu-Nu'aim ya kuma fitar daga Abdullahi Ɗan Umar (rta) ya ce, "Ba za a yi tashin ƙiyama ba sai Larabawa sun koma ga bautar gumaka, kamar yadda kakanninsu suka yi, za su yi wannan bauta ta shekara ɗari da ashirin, yana nufin bayan fitar rana daga yamma. Bayan waɗannan shekaru (120) babu abin da ya rage sai busa ƙaho, domin kashe halitta, sai busawa ta biyu ta rayar da halitta, tsakaninsu shekara arba'in ne Bukhari da Muslim sun fitar daga Abu-Huraira (rta) ya ce; Manzon Allah (saw) ya ce:

(بين النفختين أربعون سنة).

***"Tsakanin busar ƙaho ta farko da ta biyu akwai shekara arba'in."***

Ɗan Mubarak ya fitar a littafin nan mai suna **Zuhud** daga Hassan ya ce tsakanin busar kaho ta farko da ta biyu shekara arba'in ne.

A ta farko, Allah Zai kashe duk wani abu mai rai, a busa ta biyu Allah Zai rayar da duk wanda aka kashe. A nan ne muka zo ƙarshen littafin ***Faɗakar Da Al'umma Game Da Kusantar Sharuɗɗan Tashin Kiyam.***

Godiya ta tabbata ga Allah mafificin salati da cikakken aminci ya tabbata ga shugabammu, Muhammad da Iyalansa da sahabbansa baki ɗaya. Allah Ya yarda da shugabanni, tabi'ai da malamai masu aiki da iliminsu da shugabanni guda huɗu (Malik da Shafi'i da Hanbali da Abu Hanifa) da masu koyi da su, har ranar tashin ƙiyama.

Allah Ya yi salati ga shugabammu, Muhammadu da Iyalansa da Sahabbansa da aminci.

# طريق الجنة

# HANYAR ALJANNAH

Na

**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

**Mai Fassara**

**Malam Muhammadu Muhammad**

**Edita**

**Ahmed Abdullahi Sokoto (A.A. Sokoto)**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mallafi ........................................................................ 103
BABI NA ƊAYA: Tuba ...................................................................... 105
BABI NA BIYU : Zuhudu .................................................................. 107
BABI NA UKU: Kiyayi Abubuwa Biyu ............................................... 109
BABI NA HUDU : Yaƙi Da Shaiɗan ................................................... 111
BABI NA BIYAR: Yaƙar Zuciya ........................................................ 115
BABI NA SHIDA: Yaƙi da Ciki .......................................................... 121
BABI NA BAKWAI : Kiyaye Aukawa Cikin Haram Ko Shubuha ........... 122
BABI NA TAKWAS: Kiyayi Arziki .................................................... 125
BABI NA TARA : Ibada...................................................................... 131
BABI NA GOMA: Ikhilasi da Riya...................................................... 136
BABI NA GOMA SHA ƊAYA: Godiya Ga Allah................................. 139

## GABATARWAR MALLAFI

### Da Suna Allah Mai Rahma Mai Jin-Kai

Allah Ka yi salati da tsira da aminci a bisa Shugabammu, Annabi Muhammadu da iyalansa da sahabbansa da kyakkyawar amincewa, bawa mai tsananin buƙatuwar rahama zuwa ga Ubangijinsa, mai ƙarancin aiki, mai tsoro da fargaba, saboda mummunan aikin da ya aikata, Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu mai dangantaka da Fulani, mai mazhabar Maliki, mai koyi da Ash'airi ya ce: "Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da aminci su tabbata bisa ga Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi).

Wannan littafi, **Kitabu Ɗarikul-Aljannatu,** na taƙaita shi ne daga cikin asiran maganganun Abu Hamid Al-Gazzali (Allah Ya yi masa rahama). Ina faɗar cewa Allah Ya datar da mu. Ya ɗan'uwana ina horon ka da cewa farko dai Allah Ya datar da kai da neman ilimi da zagayawa a cikin neman sa. Kuma ka sani cewa ilimi da ibada, abubuwa ne masu tsada. Saboda su ne ma Allah Ya saukar da littattafai, kuma Ya aiko da manzanni. Babu makawa ga bawa ya kasance yana da rabo ga waɗannan al'amura guda biyu.

Sai dai cewa ita ibada bat a, samuwa sai da ilimi, don haka ya wajaba a gabatar da ilimi mai amfani kafin aiki. Kuma ka sani duk wanda ya nemi ilimi domin ya juyar da shi ga mutane, to, wannan kasuwancinsa bai yi riba ba. Ka tsarkake zuciyarka daga gilli da hassada da girman kai da riya da jiji-da-kai da kuma son duniya, domin ilimi ya zamo maka mai amfani. Ya ɗan'uwana lalle ilimin da ake nema na wajibi guda uku ne: Ilimin Tauhidi da ilimin Shari'a da kuma ilimin Sirri. Abin da muke nufi da shi, ilimin, da ya ta'allaƙa da zuciya, kuma yake taimakon ta. Amma iyaka cikin kowane ɗaya daga cikinsu, za mu yi maka bayaninsa da yardar Allah.

Wanda ya zama wajibi a kanka dangane da tauhidi, shi ne gwargwadon abin da za ka san asalin addini da shi, kuma ya lazimce ka, ka san ɓangarorin ilimin tauhidi. Amma ilimi na shari'a shi ne duk abin da ya wajaba ka aikata shi. To, haka ya zamo wajibi ka san shi, domin ka aikata shi, kamar tsarki da Azumi da Salla. To, Hajji da jihadi da zakka idan sun zamo maka wajibi, yana wajaba ka san yadda za ka aikata su. Idan kuma ba ka sani ba, to, kar ka yi su, ba su yi ba. Kuma abin da ya wajaba a kanka, ka aikata na ilimin sirri, to, sanin sa da abin da ke wajaba game da shi da abin da aka yi hani a kansa dole ne a kanka, domin ya sanya ka sanin yadda za ka girmama Allah da yin aiki domin Sa da yin niyya mai kyau da kuma aiki kuɓutacce. Dukkan waɗannan za su zo cikin wannan taƙaitaccen littafi. Wannan shi ne iyakacin abin da bawa zai sani na ilimi da babu makawa a kan haka. Abubuwa nawa ne da suka zama

wajibi a kansa na ilimi kuma suka wuce cikin ƙuruciya. A ƙarshe, su koma masa yana ɗan shekara saba'in. Dukkan al'amura dai suna a hannun Allah Mabuwayi da ɗaukaka.

## BABI NA ƊAYA

### Tuba

Ina horon ka ya ɗan'uwana da ka tuba a kan al'amura guda biyu. Na farkonsu, domin ka sami dacewar yin biyayya ga Allah. Shi'umci na zunubai yana gadar da haram. Zunubi yana taƙaita mutum ga aikata alherai da nishaɗi wajen jin biyayya ga Allah. Na biyun, tuba yana lazimtar ka domin karɓar aikinka na ibada. Domin mai bin bashi ba ya karɓar kyauta. Amma abubuwan da za su sanya ka tuba guda uku ne, su ne tunawa da munanan zunubai da tunawa da tsananin azabar Allah da tunawa da raunin jikinka. Idan ka himmatu da tunawa da su, zai sanya ka riƙa tuba na gaskiya.

Amma iyakar tuba shi ne rainon zuciya daga barin aikata zunubai da girmama Allah Mabuwayi da ɗaukaka da tsorata daga fushin Allah da kwaɗayin duniya, ko kuma tsoron mutane, ko neman yabo daga wurin mutane, ko kuma rauni. Sannan kuma ka sani cewa zunubai a dunƙule, kashi uku ne.

**Na Farkonsu:** Barin abubuwa wajibai da Allah Ya wajabta maka na daga salloli, ko Azumi, ko zakka, ko kaffara, ko kuma wanin haka, sai ka biya bashin da ake bin ka game da su.

**Na Biyu:** Zunuban da ka aikata tsakanin ka da Allah kurum. Kamar shangiya da kaɗa kayan kaɗe-kaɗe da cin riba da makamantansu. Sai ka yi nadama game da aikata su, kuma ka lamunce a cikin zuci, ba za ka sake komawa ga aikata su ba, ko aikata makamantasu har abada.

**Na Ukunsu:** Zunubai tsakanin ka da bayin Allah. Wannan shi ya fi wahala. Shi ma kuma ya rarrabu. Yana kasancewa a cikin dukiya, ko a kan rai, ko a cikin mutunci, ko ga iyali, ko kuma ga addini.

Ba zai yiwu ka biya dukkan abubuwan da aka ambata ba. To, abin da ba ka iya ba, sai ka koma ga Allah, kana mai ƙanƙan da kai a gare Shi da yin sadaka, domin Ya yarda da kai a ranar Alƙiyama. Ka tafi ka wanke tufafinka, ka yi wanka, ka yi Salla raka'a huɗu, ka ɗora fuskarka a ƙasa a wurin da babu kowa, kuma babu mai ganin ka sai Allah Mai tsarki da ɗaukaka. Ka sanya turɓaya a kanka, ka riƙa goga fuskarka a ƙasa wadda ita ta fi kowace gaɓa daga cikin gaɓoɓinka daraja; kana yi kana zubar da hawaye, kuma zuciyarka na cike da baƙin ciki. Kana ɗaga murya, kana ambaton zunubanka ɗaya bayan ɗaya, waɗanda ka iya tunawa, kana mai zargin kanka da aikata laifuffuka. Kana zargin ranka da cewa shin kai rai ba ka jin kunya? Yanzu ne za ka tuba?

Za ka iya ɗaukar azabar Allah? Kana da buƙatar fushin Allah? Ka yi ta ambaton waɗannan da yawa kana kuka.

Sannan ka ɗaga hannayenka sama zuwa ga Ubangijin tausayi ka ce: Ya Ubangijina, bawanKa da ya guje maKa, ya dawo ga ƙofarKa, bawanKa mai laifi ya dawo ga neman sulhu, Ubangijina, bawanKa mai zunubai ya zo maKa da uzuri, Ka yafe mani da kyautarKa; Ka karɓe ni da falalarKa; Ka dube ni da rahamarKa. Ya Allah Ka gafarta mani abin da ya wuce na zunubai; Ka kare ni daga abin da yayi saura na rayuwata, domin lalle alhairai gaba ɗaya a hannunKa suke. Kuma Kai a gare mu, Mai tausayi ne Mai jinƙai.

Ka yi addu'a mai tsanani ita ce: Zamo kuma sai ya zamo, Kana kewaye da zunubbammu. Kai ne Mai ajiye su ya Wanda ke ajiya ga kowane tsanani, na zo ina neman ajiya a wannan lokaci lalle Kai ne Mai karɓar tuba, kuma Mai tausayi. Ka yawaita kuka da nuna ƙasƙanci kuma sai ka ce; ya Wanda ji ba ya shagaltar da Shi daga wani jin, ya Wanda matsaloli ba sa ɓullowa gare Shi; ya Wanda ba Ya karɓawa, domin zurfafawa. Mun ɗanɗana daɗin rangwamenKa. Lalle Kai mai iko ne a bisa kome. Sai ka yi wa Annabi salati; ka nemi gafarar Allah ga kanka da sauran muminai, maza da mata, gaba ɗaya sai ka koma ga yin biyayya ga Allah Mabuwayi da ɗaukaka. Ya kasance ke nan ka tuba, tuba na gaskiya.

Kuma lalle daga wannan lokaci ka fita daga cikin zunubanka, ka zama mai tsarki kamar yau mahaifiyarka ta haife ka. Kuma Allah Mai tsarki Ya so ka, Ya ba ka lada da sakamako mai kyau. Kuma Ya saukar da albarka a gare ka da rahama, wadda siffantawar mai siffanfawa ba zai iya kiyayewa da ita ba, sannan aminci da tsarki su tabbata a gare ka. Kuma ka tsira daga zaluncin mai saɓo, ka rabu da shi duniya da lahira. Allah Shi ne Majiɓincin shiriya da dacewa da kyautarSa da kuma falalarSa.

## BABI NA BIYU

## Zuhudu

Ina horon ka ya kai ɗan'uwana da yin zuhudu a cikin duniya a kan al'amura biyu:

**Na Farkonsu:** Domin ibadarka ta tsayu, kuma ta yawaita, domin kwaɗayinta zai shagaltar da kai daga Allah. Ko dai a bayyane wajen shagaltuwa da aiki, ko kuma a ɓoye wajen shagaltuwa da tunani. Ko dai ka yi nufin su a ɓoye. Su duka biyun suna hana yin ibada, domin rai ɗaya ne zuciya ma ɗaya ce. Idan ka shagaltu da wani abu, za ka yanku da kishiyarsa.

**Na Biyu:** Daga ala'mura guda biyu, ka yawaita kyautata ayyukanka. Idan aka ce da kai mene ne ma'anar zuhudu a duniya da yadda haƙiƙaninsa yake? To, ka sani lalle zuhudu ya kasu kashi biyu. Zuhudu da aka ƙaddara ga bawa da zuhudun da ba a ƙaddara shi ga bawa ba. Wanda ake da iko shi ne abubuwa guda uku: Barin abin duniya da barin tara su da barin nufin duniya da zaɓarta. Amma zuhudun da ba a ƙaddara wa bawa ba shi ne gudun duniya cikin zuciyar mai zuhudu. Sai dai yin haka gabatarwa ne ga wannan, idan aka ƙaddara ga haka zai haifar masa da jin daɗin duniya a zuciyarsa, domin Allah Maɗaukaki da girman sakamakonSa.

Ka sani cewa mafi wahalar al'amura ita ce barin nufi da zuciya. Mutum nawa za ka tara cewa sun bar duniya a bayyane, amma kuma suna son ta a zuciya a ɓoye. Sai dai cewa wanda ya tsayu a kan guda biyun; farko, ana tsammanin ya dace da falalar Allah. Ya datar da shi wajen tunkuɗe wannan nufin a zuci da zaɓin son zuciya, domin Shi Allah Mai mafificin girma da buwaya ne.

Wanda ya kula da waɗancan na farko da aka ambata, zai riƙa tunawa da aibobin duniya. Zance dai mafi isuwa a cikin haka shi ne cewa ita dai duniya, maƙiyiya ce ta Allah Mabuwayi da ɗaukaka, kai kuma masoyinSa ne, Wanda yake son ɗaya, zai kasance maƙiyi ga ɗayan. Idan aka ce da kai: Mene ne hukuncin zuhudu a duniya, shin farilla ne ko kuwa nafila ne? To, ka sani cewa lalle zuhudu a cikin haramun dole ne, amma a cikin halal, nafila ne.

Idan aka ce da kai: Babu makawa mu nemi duniya, domin mu tsayu da kanmu. To, yaya za mu guje mata? To, ka sani cewa shi, zuhudu, yana kasancewa ne a ragowar abin da ba dole ba, wanda babu buƙatuwarsa domin mu rayu. Abin nufi da tsayuwa da ƙarfi shi ne yadda za ka bauta wa Allah

Maɗaukaki, ba ka ci ko ka sha, ka ji daɗi ba. Idan Allah Ya so Zai tsayar da ita rayuwar taka, ta wani dalili ko kuma ba tare da wani dalili ba.

Kamar yadda Ya halicci Mala'iku babu ci ba sha. Kuma idan Ya so Ya tsayar ma da rayuwarka da wani abu da ka aikata, ko ka nema ka samu. In Ya so kuma da wani abu na daban da ya faru gare ka, ba tare da ka nema ba, kuma ba tare da ka yi aiki ba. Saboda haka ba ka da buƙatuwar nema ko nufinSa, idan ba ka ji tsoron Allah ba dangane da haka. Ka nema kuma ka yi nufi. To, ka yi niyyar cewa, za ka ci abinci ne ko ka sha domin ka sami ƙarfin yin ibada ga Allah ba domin sha'awa ba ne. Ga Allah ne muke neman dacewa.

## BABI NA UKU

**Kiyayi Abubuwa Biyu**

Kuma ina horon ka ya kai ɗan'uwana da kaɗaituwa daga halittu a kan al'amura guda biyu.

**Na Farkonsu:** Cewa waɗannan al'amura guda biyu suna shagaltar da kai daga bauta wa Allah Mai tsarki da ɗaukaka.

**Na Biyu:** Na ɓata ibadar da ka aikata idan ba Allah ne Ya kare ka ba, saboda riya da adantuwa da ita. Ka sani ya kai ɗan'uwana cewa, lalle Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi) ya siffanta zamanin lalacewa, kuma ya yi bayanin siffarsa da siffar 'yan-zamanin. Kuma ya yi umurni a cikin wannan zamani da kaɗaicewa. Ya kasance babu makawa a san su da abin da zai zama gyara da nasiha daga gare mu a kammu.

Manyan malamai kuma manyan malamai magabata (Allah Ya yarda da su gaba ɗaya) sun haɗu a kan tsoratarwa da'yan wannan zamani, waɗanda suka zaɓi taɓewa, kuma suka yi umurni da haka, kuma suka yi wasiyya da ita. Babu shakka lalle su, sun ga hakan kuma suka yi nasiha, cewa zamanin ba zai wuce a gare su da alheri ba, sai dai ma ya zama mafi sharri, kuma al'amari ne da za ka gan shi da idanuwanka.

Idan aka ce da kai: Ka yi mana bayanin hukuncin Azalah da nisantar mutane da iyakar yadda ya wajaba ya kasance. To, ka sani cewa lalle mutane ta wannan kafar, mutane biyu ne: Akwai mutumin da ba ya buƙatuwar jama'a a tare da shi a cikin ilimi da bayanin hukunci. Abin da ya fi ga wannan mutumin shi ne kaɗaicewa daga mutane, kada ya yi cuɗanya da su sai ranar Juma'a, ko cikin Jam'i, ko ranar Idi, ko a aikin Hajji, ko gurin zaman neman ilimi na sanin sunnah, ko kuma wata buƙata ta rayuwa. In ba wannan ba, to, ya ware ya kuma keɓe kansa.

Ya ɗauki kansa bai sani ba kuma ba zai san wasu abubuwa na lalacewa ba, idan yana so ya yanke daga gare su gaba ɗaya. To, wannan ba zai wadatar da shi ba sai da al'amura guda biyu. Ko dai ya tafi inda waɗannan abubuwa ba dole ba ne, kamar kan duwatsu manya-manya, ko kuma cikin daji, ko kuma ya tabbatar cewa, lalle larurar da ya haɗu da ita, ta cuɗanya da mutane ta dalilin waɗannan farillai ita tafi a kan barin ta.

Sai dai kuma hanyar adalci a cikin haka ita ce ta farko, cewa ya riƙa haɗuwa da mutane a cikin abin da suka yi tarayya cikinsa na umurni. To, mutum na biyu; mutumin da zai koyar da ilimi ta yadda mutane za su buƙace shi dangane da al'amarin addininsu, domin su yi bayanin gaskiya, ko su yi

raddi a kan abubuwa na bidi'a ko kuma yin kira zuwa ga aikin alheri ta yin aiki, ko magana. To, wannan mutumi ƙauracewa ba za ta wadatar da shi ba, sai dai zai sanya kansa a tsakaninsu mai nasiha ga bayin Allah, ma'abucin kira zuwa ga addinin Allah, mai yin bayanin hukunce-hukuncen Allah Maɗaukaki.

Sai dai kuma yana buƙatar al'amura guda biyu wajen yin abota da su.

**Na Farkonsu**: Ilimi mai zurfi da dogon haƙuri da kallo mai sauƙi da kuma neman taimakon Allah a kodayaushe.

**Na Biyunsu:** Ya kasance ya kaɗaitu daga gare su in ya kasance yana cikinsu ne. Duk da haka akwai buƙatar ya dubi kansa a matsayin mai rabo daga cikin ibada keɓantacciya mai tsarki.

Idan aka ce da kai: Me za ka ce game da makarantun malaman lahira da kasancewa a cikinsu? To, ka sani cewa wancan wata hanya ce abar misali dangane da wannan sha'ani ga dukkan masu ilimi da ƙoƙarin bincike. Idan aka ce da kai; Mene ne hukuncin mai ijitihadin da yake son fita daga malaman lahira da makarantunsu, domin wani gyara da ya gani a kansa? To, ka sani cewa wannan wasu makarantu ne da suke da wata kariya mai kyau wadda mai ijitihadi zai katangu da ita daga yankewa da kuma sacewa, domin wanda ya fita daga matsayin karkata shi yana da dama guda biyu na Shaiɗanu za su kewaya a kansa.

To, don haka mai rauni bai da wani abu face ya lazimci kariya. To, amma mutum mai basira wanda abokan gaba ba su yi rinjaye a kansa ba, kuma ya sami daidaito ga kariya, to, ba shi da laifi, idan ya fita sai dai kasancewarsa tare da kariya ya fi daga samun wata illa a kodayaushe. Saboda haka kasancewa tare da mutanen Allah da yin haƙuri, a kan wahalar abokantakar ya fi sai dai kuma babu makawa a sami tsoron Allah cikakke wanda zai tabbatar da kasancewa a cikinsu maimakon kaɗaicewa daga gare su.

Idan aka ce da kai: Me za ka faɗa game da ziyarar yan'uwa a cikin soyayya ga Allah Mabuwayi da ɗaukaka da haɗuwa da abokai a cikin abin da ya shafi zikiri? To, ka sani yin haka yana daga cikin ibadar Allah Mai daraja, sai dai kuma da sharuɗɗa biyu:

**Na Farkonsu**: Rashin yawaitawa.

**Na Biyunsu:** Nisantar riya da yin ado da faɗar kalimomin lagawu da gulma.

To, amma abin da zai sa ka kaɗaitu daga mutane, al'amura uku ne: Na farko, Nutsar da lokuta cikin ibada. Na biyu: Yanke natsuwa da su. Na uku: Abin da ka sani na laifuffukansu. Ga Allah ne muke neman dacewa.

## BABI NA HUDU

### Yaƙi Da Shaiɗan

Kuma ina horon ka ya ɗan'uwana da yaƙar Shaiɗan da rinjayarsa ta ɓangarori biyu:

**Na Farkonsu:** Shi, maƙiyin Allah ne, ba zai bar ka ba face ya halaka ka. Ta bangare.

**Na Biyu:** Kuma, cewa shi mai bayyana ƙiyayya ne a kanka, kuma mai kafuwa ne domin yaƙi da kai har abada. To, yaya hali zai kasance idan ka zamo mujtahidi (mai ƙoƙari) a cikin ibadarka ga Allah da kiran halittu zuwa ga bauta wa Allah Mai tsarki da ɗaukaka ta ayyukanka da maganganunka? Wannan kishiyar aikinsa ne (Shaiɗan). Duk lokacin da za ka nuna tsananin fushinka ga Shaiɗan, shi kuma shirye yake da ya yaƙe ka. Idan yana nuna ƙiyayya a kan mutane gaba ɗaya, yana kuma nuna ƙiyayyarsa a gare ka musamman. Kuma yana da mataimaka a kanka, mafi tsananinsu, ranka da son zuciyarka. Kai kana shagalce, shi kuma Shaiɗan babu kome a tare da shi.

Shi yana ganin ka, kai kuma ba ka ganin sa, Kana mantawa da shi, shi kuma ba ya mantawa da kai. Don haka ke nan babu makawa ka yaƙe shi; ka rinjaye shi. Idan kuwa ba haka ba, ba za ka amintu daga ɓarna ba. Idan na ce da kai, da me zan yaƙi Shaiɗan kuma da me zan rinjaye shi? To, ka sani cewa, dangane da haka akwai hanyoyi guda biyu. Ta farkonsu: Lura da neman tsarin Allah daga gare shi domin shi, Shaiɗan, Kare ne da Allah Ya ɗora shi a kanka.

**Ta Biyunsu:** Tsayuwa a kansa wajen tunkuɗe shi da kuma saɓa masa, bayan neman tsarin da ka yi gurin Allah, domin Shi ne Mai kare ka daga sharrinsa ba kai ba. Kuma ka sani cewa yaƙar Shaiɗan da rinjayarsa a cikin abubuwa uku ne:

**Na ɗaya:** Ka dawwama da ambaton Allah a harshenka da zuciyarka

**Na biyu:** Ka kame daga kiran sa, kada ma zuciyarka ta ta'allaƙa da haka. Kuma kada ka bi shi.

**Na uku:** Ka san makircinsa da dabararsa.

Idan aka ce da kai, to, yaya za mu yi mu san haka? To, ka sani cewa ƙa'idojinsa yana da waswasi ta ɓangaren harbi da kibiyarsa idan ya harba ta. Kuma yana da dabara wadda ita ce kwarinsa wanda idan ya harba kibiyarsa, kuma yana bara wadda ita ce kwarinsa wanda idan ya ɗana ta, shi ne sai ya sanya maka wasi-wasi ta sanar da kai haɗarori, sannan ya bayyanar maka da

dabararsa ta sanar da kai ƙa'idojinsa. Waɗancan haɗarorin guda huɗu ne suka kasu.

**Kaso na Farko:** Wanda ya fuskanci Allah, Ya kasance yana aikata alheri da girmama jama'a, kuma ya lazimci neman hujja. Sai ya kasance ya jarabce ka da sharri da kausasa mu'amala. Alamarsa ita ce, mutum ya zama kurma mai fuska biyu ɗauke da halaye guda. Ɗayan kason kuma ya zo da matsayi na Mala'ika ba ya yin kome sai alheri. Ya nuna maka mai nasiha ne, shi mai shiryarwa ne. Ba a aiko shi ba sai domin haka. Alamar wannan kuma ita ce ya sanya maka kokwanto, amma fa a matsayin shi mai nasiha ne. Zai shigo maka ta kowace fuska. Ya riƙa bijiro maka da nasihohi, yana neman karɓawarka da kwaɗayinka ga alheri. Ɗayan kason da zai zo maka a matsayin Shaiɗan, ba zai kasance gare ka ba, sai domin sharri.

Duk abin da babu alheri a cikinsa, zai aikata shi. Alamarsa ita ce ya sanya mutum kamar kurma mai cike da sha'awa da jin daɗin yadda ya kasance. Waɗannan kashe-kashe guda huɗu suna da wasu alamomi na abin da ya kasance na alheri ta fuskar ijitihadi, ko ya kasance na sharri ta fuskar ijitihadi, ko ya kasance na sharri ta fuskar zunubai. To, waɗannan duka daga Allah ne.

Sai dai abin da ya kasance na sharri, shi yana sanya raunin ambaton Allah. Ko kuma da farko ya kasance sharri a ƙarshe ya zama zunubi. To, wannan daga Shaiɗan ne. Abin da kuma ya fara da alheri, to, wannan daga Mala'ika ne; abin da ya fara da sharri, amma bai sanya rauni ba wajen ambaton Allah, to, wannan abu daga son zuciya ne.

Ma'aunai guda uku ne. Idan kana son ka rarrabe haɗarin alheri sake, kada ka bibiye shi. Shi kuwa haɗarin sharri a yanke, ka nisance shi.

**Na ɗaya:** Sharrin da ya dace da alheri.

**Na biyu:** Yarda da abin kirkin da ya dace da alheri.

**Na uku:** Sanya rai kan haɗarin abin da zai kaɗaituwa da alheri.

To, yanzu lalle ka san akasin kowane ɗaya daga cikinsu. Wannan shi ne iyakar abin da ya lazimce ka, ka san shi na haɗarori. Ka ni'imtar da ganinka cikinsu gwargwadon iko, domin suna daga cikin ilimi mai sauƙi da asirai maɗaukaka. Allah ne muke neman dacewarSa da falalarSa. Amma dabarun Shaiɗan a kanka guda bakwai ne:

**Ta ɗaya:** Ya hana ka biyayya ga Allah sai ya sanya maka wasiwasi Allah Ya kare ka, domin kana da buƙatuwa ga wannan biyayya, domin ka yi gurin lahira da wannan duniyar wadda ba ta da lokacin ƙarewa.

**Ta biyu:** Ya Umarce ka da tasawif. Ya sanya maka taraddudi in Allah Ya tsare ka, ya ce lokacin mutuwarka ai ba hannunka yake ba.

**Ta uku:** Ya umurce ka da gaggautawa. Sai ya ce da kai, ka gaggauta, domin ka sami kaza da kaza. Ya sanya kokwanto a gare ka yana mai cewa: Aiki kaɗan tare da cikar alheri na tare da tauye aiki da rage shi.

**Ta huɗu:** Ya umurce ka da cewa cikar aiki, ita ce riya. Ya sanya kokwanto gare ka in Allah Ya kare ka, cewa ganin Allah Ya ishe ka.

**Ta biyar:** Ya jefa ka cikin jiji-da-kai. Sai ya riƙa cewa da kai da girmanka me zai tayar da kai? In Allah Ya tsare ka sai ya sanya maka kokwanto cewa biyayyarka ga Allah wata baiwa ce daga Allah wanda wani ba shi da ita, ba domin falalar Allah ba. Yaya matsayin wannan aiki ta bangaren ni'imar Allah Maɗaukaki?

**Ta shida**: Ita ce mafi girmansu. Ita ce ya ce da kai, ka yi ƙoƙari a ɓoye, Allah Zai bayyanar maka da shi. Idan Allah Ya kare ka sai ya sanya maka kokwanto cewa ai kai bawan Allah ne shi ne shugabanka. In ya so sai ya bayyanar maka da shi, in ya so sai ya ɓoye shi a gare ka. In ya so sai ya sanya ka haɗari. In ya so sai ya sanya ka wulaƙantacce. Duk wannan na gare shi kar ka damu in ya bayyana haka ga mutane, ko kuma bai bayyana shi ba, ba su da kome a hannunsu.

**Ta bakwai:** Ya ce da kai babu buƙata ga wannan aiki cewa idan an halicce ka mai arziki, barin aiki ba zai cutar da kai da kome ba. Idan kuma an halicce ka ɗan-wuta ne, aikata aiki ba zai amfane ka da kome ba. Idan Allah Ya kare ka sai ya sanya maka kokwanto cewa kai bawa ne a matsayin bawa kake gudanar da al'amarin kana bauta masa. To shi, Ubangiji Shi ne Ya dace da bauta watau rububiya. Wannan aiki zai amfane ka ta kowane hali, in an halicce ka ɗan aljanna, to, zai amfane ka da samun ƙarin lada. In kuwa kai ba ɗan Aljanna ba ne, Allah Zai yi maka uƙuba, saboda biyayyarka a gare Shi ta kowane hali.

Babu abin da zai cutar da kai in Ya shigar da kai wuta alhali kana mai biyayya, ya fi Ya shigar da kai ita kana mai saɓo. Yaya za ka shiga wuta alhali alƙawarin Allah gaskiya ne; maganarSa gaskiya ce. Haƙiƙa, Ya yi wa wanda Ya yi maSa biyayya alƙawari da sakamako mai kyau. Wanda ya haɗu da Allah Yana da imani da biyayya gare Shi, ba Zai shiga wuta ba fau-fau. Cancantar

Aljanna dangane da alƙawarin Allah na gaskiya ba saboda aiki ba ne. Da wannan ma'anar ne Allah Ya ba mu labari da cewa:

﴿وَقَالُوا۟ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى صَدَقَنَا وَعْدَهُۥ وَأَوْرَثَنَا ٱلْأَرْضَ نَتَبَوَّأُ مِنَ ٱلْجَنَّةِ حَيْثُ نَشَآءُ﴾ الزمر: ٧٤

***"Godiya ta tabbata ga Allah Wanda muka gasgata alƙawarinSa. Ya gadar da mu ƙasa; muna juyawa cikin Aljanna yadda muka so".*** **Alƙur'ani 39:74**

Ka farka ya ɗan'uwana domin yadda al'amari yake kamar yadda ka ga ni ne. Muna neman timakon Allah; muna neman tsarinSa domin lalle al'amari yana hannunSa daga gare Shi ne dacewa take. Babu dabara babu karfi sai ga Allah Maɗaukaki Mai girma.

# BABI NA BIYAR

## Yaƙar Zuciya

Ina horon ka ya ɗan'uwana da ka yaƙi zuciyarka, kuma ka tsoratar da ita da al'amura guda biyu;

Na ɗayansu cewa ita, maƙiya ce a cikin gida. Na biyunsu cewa shi miƙiyi ne, kuma maƙiyi ne wanda ake so, shi kuwa mutum makaho ne ga aibin masoyinsa. Idan aka ce da kai mene ne maganin zuciya?

To, ka sani cewa, wannan wata hanya ce daga cikin hanyoyi guda biyu. Suna ƙarfi ne gwargwadon abin da kake aikatawa na alheri, suna raunana a tsare ta wuri guda ba ta ci gaba ba. Ka sani ya ɗan'uwana cewa ka ƙasƙantar da ita sai ka karya sha'awarta daga bin inda take so da abubuwa guda uku, daga cikinsu akwai hana ta sha'awa da ɗaukar ayyukan ibada masu nauyi da neman tsarin Allah daga Shaiɗan. Idan ba ka yi haka ba, to, babu ikhlasi ke nan ga aiki.

Da abin da muka ambata ne za ka iya yi wa rai linzami da linzamin jin tsoron Allah. Linzaman jin tsoron Allah guda uku ne: Jin tsoron shirka da jin tsoron aikata bidi'a da kuma jin tsoron aikin laifi. Gazzali ya ƙara da cewa: "Jin tsoron Allah, ma'anarsa shi ne nisantar abin da ba a umurce ka ba. Iyakar jin tsoron Allah ita ce, nisantar abin da kake tsoron ya cutar da kai a cikin addininka."

Idan aka ce da kai: Ka rarrabe mana wannan bayani na son rai domin mu san yadda za mu magance shi da jin tsoron Allah. Sai nake cewa; Rarrabewa a cikinsa shi ne ka tashi ka tsayu da ƙwarin himma, don ka hana ta aikata laifuffuka; ka hana ta faɗawa cikin abin da ba a sa ta ba. To, amma abin da babu makawa ka aikata shi, shi ne ka ce wanda yake son jin tsoron Allah, to, ya tsare gaɓoɓinsa daga abubuwa guda biyar, domin su ne tushensu ne idanuwa da kunnuwa da harshe da zuciya da kuma ciki. Sai ya yi ƙoƙarin kiyaye su daga aikata abin da yake tsoron cutawarsa a cikin addini na daga laifuffuka da haramun da aikata abin da babu shi a cikin addini. A koma zuwa ga halal.

Idan kai ya kiyaye gaɓɓai daga waɗannan laifuffuka, to, muna fatar sauran rukunan sun isar maka saboda haka ne, nake horon ka da kiyaye idanuwa domin kulawa da al'amuran guda uku. Allah Mabuwayi da ɗaukaka Ya ce:

﴿قُل لِّلْمُؤْمِنِينَ﴾ النور: ٣٠

*"Ka faɗa wa muminai."* Alƙur'ani 24:30

Zuwa ƙarshen aya. Kuma Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata gare shi) ya ce:

(النظر من محاسن المرأة سهم مسموم من سهام إبليس فمن تركها أذاقه الله طعم عبادة تسره)،

***"Kallon kyawon mace, kibiya ce mai guba daga kibiyoyin shaiɗan watau iblis, wanda ya bar shi, Allah Zai ɗanɗana masa daɗin ibada, wadda za ta faranta masa rai."***

Kasancewar ido, an halicce shi ne, domin gani zuwa ga zatin Allah Mabuwayi da ɗaukaka ba domin kallon haramun ba.

Ina yin horo gare ka ya kai ɗan'uwana da ka kiyaye kunne daga wadatuwa da jin abin da ba a umurce shi, ya ji ba da al'amura guda biyu. Na farko; Tarayya da mai magana cikin zunubi. Na biyu; Rabuwa da tunani da waswasi a cikin zuciya.

Ina horon ka ya ɗan'uwana da ka kiyaye harshe domin shi ya fi tsanani a kansu duka. Idan aka lura da al'amura guda biyar

**Na Ɗaya:** Karkacewar gaɓɓai da karkacewarsa.

**Na Biyu:** Tozarta lokacinka in ka yi amfani da shi.

**Na Uku:** Tafiyar da kyawawan ayyukanka, idan ka yi amfani da shi wajen gulma zuwa ga wanda ka yi gulmar da shi.

**Na Huɗu :**Rashin amintuwa da laifuffuka in kana amfani da shi.

**Na Biyar:** Cancantarka da azabar Allah in ka faɗi wani abin ƙyama. Ka kiyaye shi kuma daga halartar abubuwa guda huɗu:

**Na Farko:** Shagaltar da marubutan nan guda biyu (Atidu da Raƙibu) da rubuta abubuwan da babu alheri a cikinsu.

**Na Biyu:** Kiyaye kai littafinka ga Allah Mabuwayi da ɗaukaka ga aikata lagawu da ayyukan ƙazanta.

**Na Uku:** Ka kiyaye cewa za ka karanta shi a gaban manyan mala'iku masu ƙarfi a ranar tashin Alƙiyama.

**Na Huɗu:** Ka kiyaye shi da yawan zargi da aibata mutane.

Ina horon ka ya ɗan'uwana da kiyaye zuciya da gyara ta. Domin ita ta fi girman haɗari, ta fi wuyar al'amari, kuma ta fi wahalar gyaruwa idan aka lura da al'amuran nan guda biyar;

**Na Ɗaya:** Faɗar Allah Mai girma da ɗaukaka;

﴿يَعۡلَمُ مَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ فَٱحۡذَرُوهُۚ﴾ البقرة: ٢٣٥

***"Ya san abin da ke cikin zukatanku, ku kiyaye shi"*** **Alƙur'ani 2:235**

Da makamantansa.

**Na Biyu:** Faɗar Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi).

(إن الله تعالى لا ينظر إلى صوركم وأبشاركم وإنما ينظر إلى قلوبكم...)

***"Allah ba Ya duban surarku, ko fatar jikinku, sai dai Yana duban zukatanku ne."***

**Na Uku:** Ita ce ta mallaki dukkan gaɓɓai. Idan ta gyaru, dukkansu sun gyaru. Idan ta ɓaci su ma gaɓɓai sun ɓaci.

**Na Huɗu:** Kuma ita, zuciya, taska ce ga duk abu mai daraja kamar hankali da ilimi. To, gaskiyar misalin wannan taskar, kuɓutar da ita daga ƙazanta.

**Na Biyar:** Idan ka yi aiki da ita, za ka sami halaye guda biyar ba wanin haka ba.

**Na Farko:** Kada ya yi nufin Shaiɗan da mallaka, sai dai gare shi.

**Na Biyu:** Cewa shagaltuwa da shi fiye da ƙima, to, zai bar son zuciya da rundunarsa. Hankali da rundunarsa suna yaƙi a tsakaninsu har abada.

**Na Uku:** kuma haɗuransa kamar kibiyarsa, ba zai gushe ba yana auka wa aiki ba dare ba rana, kuma ba za ka iya hana shi ba.

**Na Huɗu:** Maganinsa a ɓoye yake, domin abu ne da ya ɓoyu gare ka.

**Na Biyar:** Kuma yana da gaggawar juyawa da samun iko da rinjaye.

Idan aka ce da kai al'amarin wannan zuciya yana da muhimmancin gaske, to, ka ba mu labarin ma'anar yadda za a gyara ta da kuma laifuffukan da za su ɓata ta da tsammanin cewa, Allah Ya datar da mu yin ƙoƙari ga aiki domin haka. To, ka sani malaman lahira sun ambace ta cewa sun kai saba'in na halaye ababen yabo a ƙarƙashinsu, kuma akwai kishiyoyinsu ababen zargi.

Gazzali ya ce: Mafi muhimmancin rayuwata, al'amari ne na addini da farkawa daga barcin marafkana da duban kansa ga masu bin Allah Maɗaukaki. Ba zai kasance ya kai ga haka ba cikin sauƙi, akwai ayyuka masu yawa a kanka, idan Allah Ya datar da kai. Amma yanzu za mu ambata maka guda huɗu; kuma babu makawa mu ambace su saboda samun warakar zuciya, suna cikin **Madahidul Abidina**. Guda huɗu kuma suna ciki, akwai tsara aikin ibada da kuma gyaran zuciya. To, amma laifuffuka guda huɗu, Buri da gaggawa da hassada da kuma girman kai. To, waɗannan su ne asalin abubuwan da suke ɓata zuciya.

To, amma kishiyoyin waɗannan su ne Taƙaita buri da bin al'amura da natsuwa babu gaggawa da yin nasiha ga halittu da tawali'u. To, waɗannan su ne asalin abubuwan da ke gyara zuciya. To, ka yada ƙoƙarinka wajen gargaɗuwa da al'amarin juriya da kaiwa ga abubuwan can da suke gyara zuciya. Za ka sami cikar burin gaskiya da yardar Allah Mabuwayi da ɗaukaka.

To, amma iyakar buri shi ne nufin rayuwa zuwa ga wani lokaci wanda ya hukunta wa kansa, wannan shi ne buri. Kuma ma'anar tabbatar da shi a zuciya. Yin wasa da gabatar da al'amari da farkon haɗarinsa ba tare da samun dacewa a cikinsa ba. Wannan shi ne gaggawa. Kuma nufin gushewar ni'imar Allah Maɗaukaki daga ɗan'uwanku, Musulmi. Wannan ita ce hassada. Tunanin ɗaukaka kai da girmama kai. Wannan shi ne yin girman kai. Akasinsu da iyakarsu kuma su ne, kishiyoyinsu masu kyau. To, ka guje su ya ɗan'uwana matuƙar gujewa, domin idan burinka ya tsawaita, kana buƙatar abubuwa guda huɗu.

**Na Farko:** Barin yin biyayya ga Allah, domin a kodayaushe za ka riƙa cewa da sannu zan aikata ayyukan ƙwarai ai da sauran lokaci da sauran kwanaki masu yawa.

**Na Biyu:** Jinkirta tuba. Ka riƙa cewa da sannu zan tuba, ai kwanaki da yawa ai ni yaro ne shekaruna kaɗan ne.

**Na Uku:** Kwaɗayin tara dukiya da shagaltuwa da duniya da barin lahira, domin za ka riƙa cewa, ina tsoron talauci idan na manyanta. To, zai yiwu in yi rauni da neman dukiya, babu makawa in ajiye wani abu domin tsufa.

**Na Huɗu:** Bushewar zuciya, domin idan ka tsawaita buri, ba za ka tuna da mutuwa da ƙabari ba da rashin buri ne ake samun kishiyoyinsa masu kyau.

Amma gaggawa ita ce kasancewa cikin laifuffuka. Kuma tana da laifuffuka guda huɗu:

**Na Farko:** Kudurce dawwama wajen gaggauta wani aiki na alheri da tsayuwa a kai da kuma yin ƙoƙari, akwai yiwuwar ya gaggauta cikin aiwatarwa, amma kuma ba lokacin yin hakan ba ne. Ko dai ya aikata ya kuskure, ya yanke ƙauna da samun sa, ya bar ƙoƙarin aikatawa kuma yin haka, zai sanya a haramta masa samun lada. Ko kuma ya zurfafa wajen ƙoƙari har ya gajiyar da ransa, sai a yanke shi daga wancan matsayi. Zai kasance ya dawwama tsakanin yin sakaci da yin ƙari ga aikin ƙwarai da yin sakaci wajen rage ayyuka marasa kyau. Dukkansu guda biyun, sakamako ne na gaggawa.

**Na Biyunsu:** Ya kasance bawa na da buƙata sai ya roƙi Allah Maɗaukaki game da ita. Ya yawaita yin addu'a, akwai yiwuwar gaggauta karɓa masa kafin lokacin ya yi, sai ya ƙagara ya ƙosa sai ya bar addu'a, sai a hana shi wannan buƙatar.

**Na Uku:** Wani mutum ya zalunce shi, ya sanya shi baƙin ciki sai ya gaggauta yin addu'a a kansa, sai wannan Musulmi ya mutu saboda shi, ta yiwu ba za a yi masa haddi ba, sai ya kasance cikin laifi.

**Na Huɗu:** Asalin ibada shi ne idan mutum ya kasance mai gaggawa, zai kasance ya faɗa cikin cin abincin haram ko shubuha sai tsantseni ya wuce shi. Amma Ita, hassada, tana lalata aikin lada da sanya gyara kurakurai, kuma ita cuta ce mai halakarwa wadda masu karatu da malamai da yawa aka jarrabe su da ita da kuma da yawa daga jahilan mutane. Tana ƙunshe da abubuwa guda biyar:

**Na ɗaya:** Tana ɓata ayyukan lada.

**Na biyu:** Aiki ne na saɓo

**Na uku:** Gajiya babu faida

**Na huɗu:** Makancewar zuciya

**Na biyar:** Haramcinta.

Amma girman kai shi ne ɗaukaka kai. Shi ba shi da wani matsayi kamar sauran ɓangarorin, waɗanda suke cutar da sauran ɓangarorin. Sai dai ana cutuwa da shi a asali. Idan ya yi ƙarfi kuma ya yi rinjaye ba za ka iya riskuwa daga gare shi ba. Muna neman tsarin Allah Maɗaukaki. Ya ƙunshi abubuwa guda huɗu na laifuffuka:

**Na Farkonsu:** Haramcin gaskiya da makantar zuciya game da sanin ayoyin Allah, saboda faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿ سَأَصْرِفُ عَنْ ءَايَٰتِيَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ فِي ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ﴾ الأعراف: ١٤٦

*"Zan sarrafa ayoyiNa ga waɗanda suke yin girman kai a bayan ƙasa ba tare da haƙƙi ba."* Alƙur'ani 7:146

**Na biyu:** Fushin Allah a gare shi.

**Na uku:** Taɓewa a nan duniya.

**Na huɗu:** Shiga wuta da azabar Allah a lahira.

Waɗannan su ne abubuwan da muka tsamo daga cikin laifuffukan girman kai. Ɗaya daga cikinsu ya isar wa mai hankali kauce wa waɗancan abubuwan idan ka himmatu wajen aikata su da komawa ga aikata abubuwan da addini ya yarda da su. Allah ne muke neman dacewarSa da rahamarSa.

## BABI NA SHIDA

### Yaƙi da Ciki

Ina horon ka ya ɗan'uwa da ka kiyaye ciki daga haramun da shubuha.

**Da Farko**: Kuma da kiyaye shi da cin abin da addini ya hana a ci.

**Abu na Biyu:** Ka himmatu wajen yin biyayya ga Allah. Kuma ka lazimci bincike a kan haramun da shubuha daga al'amura guda uku:

**Na ɗaya:** Tsorata daga wutar jahannama

**Na biyu:** Mai cin haramun da shubuha zai zama korarre daga rahamar Allah, kuma ba ya dacewa da ibada.

**Na uku:** Mai cin su korarre ne daga rahama ba a karɓar sa.

Amma raguwar halal tana da laifuffuka goma su ne, bushewar zuciya da fitinar gaɓɓai da ƙarancin fahimtar ilimi da ƙarancin ibada da rashin jin daɗin ibada da haɗarin aukawa cikin shubuha da haramun da shagaltuwar zuciya da jiki daga ibada da tsananin magagin mutuwa da tauye lada a lahira da wasoso cikin hisabi. Waɗannan abubuwa guda goma; guda ɗaya na isarwa.

## BABI NA BAKWAI

### Kiyaye Aukawa Cikin Haram Ko Shubuha

Ya ɗan'uwana ina horon ka da ka dage da ƙarfinka ka kewaye daga aukawa cikin haram ko shubuha. Kuma ka taƙaitu ga cin halal iyakar kasancewarka ga ibada. Idan aka ce da kai: Mene ne haram kuma mene ne shubuha? To, ka sani cewa, sashen malamai sun ce haramun shi ne duk abin da ka tabbatar mallakar wani ne a shari'a, sai ka hana shi. To wannan shi ne haram. To, amma idan ba ka tabbatar ba, sai dai kana zato ne mafi rinjaye, to, wannan ita ce shubuha. Ita ce abin da zatonka ya rinjaya cewa na wani ne, amma ka hana shi.

Ita kuma shabuha, idan al'amura biyu suka yi daidai, sai ya kasance ana kokwanto, har ya zama wani bai rinjaya ba daga cikinsu a gare ka. To, wannan ita ce shubuha a cikin maganganu guda biyu a wurin Gazzali. Kuma hanuwa daga haram dole ne, kuma hanuwa daga shubuha shi ne tsoron Allah da tsantseni.

Idan aka ce da kai, me za ka ce game da kyaututtukan da Sarakunan wannan zamani suke bayarwa? To, ka sani cewa, lalle malamai sun yi saɓani a cikinsa. Wasu jama'a sun ce duk abin da ba a tabbatar da haramcinsa ba, to, a iya karɓa. Wasu kuma suka ce ba ya halatta a karɓi duk abin da ba a tabbatar da halaccinsa ba. Mafi rinjayen malaman a gare su haramun ne. Wasu jama'a sun ce ya halatta mawadaci ko talaka ya karɓa matuƙar ba a tabbatar cewa haramun ba ne. Sai dai abin da ya biyo baya na laifi yana ga wanda ya bayar.

Wasu kuma sun ce ba ya halatta a karɓi kome na daga dukiyoyin Sarakunan wannan zamani domin azzalumai ne, kuma mafi rinjayen dukiyoyinsu haramun ne. Hukunci a ɓoye yake, domin haka ya lazimce ka da ka nisance ta. Wasu kuma suka ce abin da ba a tabbatar da haramcinsa ba, to, ya halatta talaka ya karɓa, amma ban da wadatacce. Sai dai idan talakan ya san cewa, akwai zalunci a cikin dukiyar.

Gazzali ya ce wannan matsala ba a ba da fatawa da ita. Idan aka ce da kai mene ne hukuncin karɓar sadakar 'yan kasuwa ko wasunsu? To, amsa ita ce abin da a bayyane ya kasance mai kyau ne, babu laifi a karɓi sadakarsa. Idan kuma ba a karɓa ba, babu kome. To, amma ka sani cewa a cikin wannan al'amari akwai abubuwa biyu. Watau hukuncin shari'a shi ne karɓar abin da a bayyanensa mai kyau ne, kada ka tambaya sai dai in ka tabbatar akwai zalunci a ciki, ko kuma haramun a bayyane da kuma hukuncin tsantseni shi ne cewa

kada ka karɓi kome har sai ka yi matuƙar bincike. Ka tabbatar da cewa, babu shubuha cikinsa a wannan yanayi. Idan kuwa akwai, to, kada ka karɓa.

Idan aka ce da kai: Shin tsantseni ya saɓa wa shari'a da hukuncinsa. To, ka sani cewa, lalle shari'a ita, wani darasi, ne mai sauƙi. Kuma tsantseni, darasi ne mai tsanantawa da kewayewa. Kuma tsantseni yana daga cikin shari'a. Kuma guda biyun daga tushe guda ne, sai dai shari'a tana da hukunce-hukunce guda biyu. Hukunci na halacci da hukunci mafifici ga wanda ya kewaye.

**Na Farko:** Hukuncin shari'a, da kuma

**Na Biyu:** Hukuncin tsantseni.

Idan aka ce da kai idan ana bincike game da kome, al'amari zai ta'azzara ga mai tsantseni yayin da kuma babu makawa ya kai ga matuƙar biyayya ga Allah. To, ka sani cewa, hanyar tsantseni tana da tsanani. To, lalle wanda ya yi nufin kyautata ɗabi'arsa, to, sharaɗin yin haka, shi ne yin haƙuri da tsanani. Idan kuwa ba haka ba, to, hakan ba zai samu ga mai tsantseni ba. Domin haka ne da yawa daga cikin masu tsantseni suka tafi dutsen Labanon da waninsa, suka taƙaitu a kan cin ciyawa da 'ya'yan itatuwa waɗanda babu shubuha a cikinsu.

Sai ka yi koyi da irin hanyarsu in kana son samun matsayin tsantsenin da ya fi.

To, amma idan ka zauna cikin mutane kana cin abin da yake juyawa a hannayensu na dukiya, to, wannan zai kai ka ga mutuwa. Kada ka ci abin da ke hannayensu sai in akwai larura. Wannan zai kasance ne ya kai ga biyayyarka ga Allah. Idan aka ce da kai mene ne halal, kuma mene ne iyakar abin da aka hane ka wanda hisabi zai lazimce ka da bincike? Mene ne gwargwadon abin da bawa zai yi riƙo da shi har abada? To, ka sani cewa, halayen shari'a da ta amince guda uku ne;

**Na Farkonsu**: Shi ne bawa ya yi riƙo da alfahari da tara dukiya da kuma riya. Wannan na wajabta wuta da azabar Allah Mai girma.

**Kashi na Biyu:** Karɓar halal domin sha'awar ransa. Wannan na wajabta hisabi da bincike.

**Kashi na Uku:** Karɓar halal lokacin uzuri gwargwadon abin da zai taimake shi. Ya gudanar da ibada ga Allah. Wannan shi ya fi alheri da kuma kyau da lada, kuma babu hisabi a kansa, kuma babu uƙuba. Sai dai akwai lada da yabo. Tsayuwa a kan kiyaye wannan ladabi, tana buƙatar basira da nufi.

Domin ba zai sami duniya ba, sai da ibada ga Allah Maɗaukaki. Idan ka manta ba ka tuna da buƙatar ba, to, nufinka da ka yi, ya isar maka a dunƙule.

Ina horon ka ya ɗan'uwana da ka yaɗa da ƙoƙarinka a cikin waɗannan rabe-rabe guda huɗu da gargaɗuwa da su a duniyance da ɗabi'ance da nisantar Shaiɗan da son zuciya. Wanda ya halaka, ya halaka ta dalilin waɗannan rabe-rabe. Kuma ka sani ya ɗan'uwa cewa a nan ne tushensu yake. Shi ne cewa, ibada na da sharuɗɗa guda biyu. Aikata biyayya ga Allah da nisantar aikata saɓo. Himmar waɗanda suke matakin farko shi ne su azumci yininsu, kuma su yi tsayuwar dare.

To, amma himmar masu basira ita ce su kiyaye zukatansu daga karkata ga wanin Allah da kiyaye cikinsu daga cin haramun, su kuma kiyaye harsunansu daga maganganu yasassu, suna kuma kiyaye ganinsu daga kallon abin da bai shafe shi ba. To, idan kasancewa ɓangaren nisanta ya fi, to, ka kuɓuta. Idan ba za ka wadatu ba sai da ɗayansu, to, zaɓi nisantar sai ka ƙuɓuta idan ba za ka ƙuntata ba. Idan kuma ba haka ba, to, ka yi asarar guda biyun gaba ɗaya.

## BABI NA TAKWAS

### Kiyayi Arziki

Kuma ina horon ka ya ɗan'uwana da kauce wa duk abin da zai bijiro maka, ya shagaltar da kai daga bautar Allah Maɗaukaki. Waɗannan abubuwa masu bijirowa guda huɗu ne, arziki da tunane-tunane da ramuwa da masifu da tsanani. Kauce wa arziki shi ne tawakkali. To, ina horon ka da yin tawakkali ga Allah Mai tsarki da ɗaukaka, dangane da fagen arziki da buƙata a kowane samun faragar yin ibada.

**Na biyu:** Kodayake barin sa haɗari ne mai girma. Allah Ya nuna mana cewa arziki kamar halitta yake. Faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ ثُمَّ رَزَقَكُمۡ﴾ الروم: ٤٠

***"Allah Shi ne Ya halicce ku, sannan kuma Ya azurta ku."*** **Alƙur'ani 30:40**

Har zuwa inda Ya yi alƙawari inda Ya ce:

﴿وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا﴾ هود: ٦

***"Babu wata dabba a bayan ƙasa, face arzikinta na wurin Allah."***
**Alƙur'ani 11:6**

Sannan Bai tsaya ga alƙawari ba sai da ma Ya lamunce wa halittu da cewa:

﴿وَعَلَى ٱللَّهِ فَتَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ﴾ المائدة: ٢٣

***"Kuma ga Allah ne za ku dogara in kun kasance muminai."*** **Alƙur'ani 5:23**

Sannan Bai tsaya ga lamuncewa kaɗai ba har sai da ma Ya rantse, inda Allah Ya ce:

﴿فَوَرَبِّ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ إِنَّهُۥ لَحَقّٞ مِّثۡلَ مَآ أَنَّكُمۡ تَنطِقُونَ﴾ الذاريات: ٢٣

***"Ina rantsuwa da Ubangijin sama da ƙasa cewa lalle shi, arziki, gaskiya ne, kwatankwancin abin da kuke faɗa."*** **Alƙur'ani 51:23**

Haka ba zai isa ba har sai ya yi umurni, kuma ya isar da saƙo, ya yi gargaɗi. Kuma mai tawwakali yana ƙudurta al'amura ne da ƙarfin basira da cikar yarda da alƙawarin Allah Mai tsarki, ba ya waiwayen tsoron mutum, ko kuma Shaiɗan ya sanya masa waswasi.

Ya ɗan'uwana, ba ka duban waɗanda suka jiɓinci al'amarin duniya watau 'yan duniya? Amma Sarakuna, kai tsaye sun fuskanci mulki, ko dai su sami mulki, ko kuma su halaka. To amma 'yan-kasuwa sun sanya kawunansu cikin ɗayan al'amura guda biyu. Ko dai su rasa rayukansu, ko kuma su ci riba.

Amma mutanen lahira, babban al'amarinsu shi ne tawakkali ga abin da ya samu. Suna kaɗaituwa da bautar Allah, kuma suna yin abin da suke iyawa ga halitta. Idan an munana masu sai su yafe. Su ne suke mallakar ƙasa suna yin yadda suka so, kuma suna tafiya cikinta yadda suke so. Dukkan halittu a gurinsu ɗaya ne, kuma kowane zamani ɗaya ne a gare su.

To, amma tawakkali shi ne kasancewa tsayuwarka kan sanin kome daga Allah ne Mabuwayi da ɗaukaka ba daga waninSa ba. Kuma ba daga wani dalili ba ne na duniya, kuma ba wani dalili ba ne daga cikin dalilai. Amma tayar da kai, wata lamincewa ce ta Allah Maɗaukaki da cikar iliminSa da ikonSa da kuma tsarkake Shi da dukkan abin da ya saɓa wa waɗannan siffofi kamar rafkanuwa da kasawa. Wurarensa guda uku ne wurin kaso da wurin hasara da kuma wurin arziki da buƙata. Lamunce wa Allah ga waɗannan wurare ya tsayu ne ga yadda aka halicce ka domin bautarSa.

Kuma ka sani cewa shi, arziki, ya kasu gida huɗu. Wanda aka lamunce shi ne kamar abinci da abin da jikinka zai ginu da shi, ba tare da sauran dalilai sun taru da shi ba da wanda aka raba da kuma wanda ka mallaka, sannan da wanda aka alƙawarta shi. Amma wanda aka raba, shi ne wanda yake rubuce a lauhul mahfuz. Wannan kuwa ya haɗa da abin da zai ci da abin da zai sha da tufafin da zai sa duka a wani lokaci iyakantattu ne, waɗanda ba a ƙarawa kuma ba a ragewa.

Amma wanda aka mallaka shi ne abin da kowane mutun yake samu na dukiya daga cikin dukiyoyi, a nan duniya gwargwadon abin da Allah Maɗaukaki Ya ƙaddara. To, amma wanda aka alƙawarta shi ne abin da Allah Ya yi alƙawari ga bayinSa, masu jin tsoronSa, saboda tsayawa ga halal ba tare da wahala ba.

Idan aka ce da kai: Shin Ya lazimce mu, mu nemi arziki ta kowane hali? To, ka sani cewa shi, arzikin da aka lamunce, shi ne abinci wanda ba za mu iya neman sa ba, domin wannan aikin Allah ne ga bawa kamar rayuwa ce da mutuwa. To, amma wanda aka raba ba ya lazimtuwa a neme shi, idan bawa ba ya buƙatar sa, shi buƙatarsa waɗanda aka lamunce, kuma ita daga Allah ne cikin abubuwan da Ya lamunce ga bawa. Idan aka ce da kai shin wannan arziki da aka lamunce ga bawa yana da wasu dalilai da za a bi domin samun sa?

To, ka sani cewa ba ya lazimtar mu, domin aikin Allah Mai tsarki ne. Yana aikatawa a bisa dalilai, ko kuma babu dalili, abin da ya lazimce mu shi ne neman dalili. Kuma lalle Allah Maɗaukaki Ya lamunce mana shi yanke, ba tare da sharɗanta neman dalili ba ko kuma aikatawa. Haƙiƙa, ya bayyana a gare ka cewa neman arziki da dalilinsa ba al'amari ba ne da aka lazimta.

Idan aka ce da kai: Shin na shiga ƙauye ba tare da guzuri ba? To, ka sani idan kana da ƙarfin zuciya ga Allah da isasshen amince wa alƙawarin Allah Maɗaukaki, to, sai ka shiga. Idan kuwa ba haka ba, to, sai ka zama kamar sauran amawa, domin duk wanda ke gudanar da rayuwarsa kamar ta al'adar jama'a, to, Allah Zai gudanar da shi tare da su a bisa abin da ke wurinsa.

Idan aka ce da kai: Shin mai tawakkali zai riƙi wani guzuri tare da shi a cikin tafiya? To, ka sani cewa, zai iya ɗaukar guzuri sai dai ba zai ta'allaƙa zuciyarsa a kansa ba, domin babu makawa ya sami arzikinsa. Kawai ya ta'allaƙanta zuciyarsa ga Allah Maɗaukaki, kuma zai iya ɗaukar guzuri da wata niyya ta daban, kamar ya taimaki Musulmi ko makamantan haka. Shi sha'anin ba na ɗaukar guzuri ba ne ko barin sa, sai da cewa, sha'anin a zuciya yake. Idan aka ce da kai: Ɗaukar guzuri ya fi ko barin sa? To, ka sani cewa, idan ka kaɗaitu da ƙarfin zuciya ga Allah Mai tsarki, zai shagaltar da kai game da ɗaukar guzuri a kan bautar Allah, don haka barin ɗaukar sa ya fi.

Idan kuwa ya kasance domin taimakon Musulmi ne, to, ɗaukar guzurin sa ya fi. Muna neman dacewar Allah.

Abu na biyu: Tunane-tunane, abin da yake maganinsu, shi ne, mayar da al'amari ga Allah. Ina horon ka da mayar da al'amari gaba ɗaya ga Allah Mai tsarki da ɗaukaka da abubuwa guda biyu: Na farkonsu: natsuwar zuciya. Na biyunsu: Wanzuwar abu mai kyau da alheri a gaba.

Idan aka ce da kai; ka yi mana bayanin mayar da al'amari ga Allah da gurbinsa. To, ka sani cewa lalle mayar da al'amari ga Allah nufi ne da Allah Zai kiyaye maka matsalolinka cikin abin da ba ka amintu ba. Amma gurbinsa, shi ne a cikin nafilfili da abubuwan da suka halatta. To, ba ka buƙatar sa yanke sai dai da togaciya da kuma sharaɗin alheri da gyara. Idan ka iyakance niyyarka da togacciya, to, su ne mayar da al'amari ga Allah. To, amma abin da za a tashe ka a kansa shi ne tunawa da haɗarin al'amura da yiwuwar halaka da ɓarna a cikinsa. Abin da za a tashe ka a kansa shi ne abin da ka kasa kamewa a kansa, saboda larura.

Idan aka ce da kai: Wane tunani ne zai wajaba a mayar da al'amari ga Allah a kansa? To, ka sani cewa shi, tunani, ya kasu gida biyu. Tunanin da

kake shakkar faruwarsa, ko kuma rashin faruwarsa, ko kuma za ka same shi, ko kuma a'a. To, wannan yana da buƙatuwar togacciya wajen niyyarsa, ko burin samuwarsa. Kuma tunani maras kyau shi ne ka ƙi tabbatar da shi domin amfaninka To, wannan yana buƙatar mayar da shi ga Allah. Idan aka ce da kai shin mai tawakkali zai iya amintuwa da halaka, ko ɓarna, ko cutarwar wani abu mai cutarwa? To, ka sani abin da yake mafi rinjaye ba a aikata shi da mayar da al'amari, sai dai gyara.

Abu na Uku: Hukunci da nau'o'insa; shi kuma maganinsa shi ne yarda. To, ina horon ka da yarda da hukuncin Allah Maɗaukaki ga al'amura guda biyu: Na farkonsu. Tabbatuwa ga bautar Allah, domin idan ba ka yarda da hukuncin Allah ba, za ka kasance cikin shagaltuwa da himmantuwar zuciya har abada, domin me, ba ka kasance kaza ba? Ko me ya sanya kaza bai faru ba. Na biyunsu: Tunani cikin fushin Allah daga fushin Allah Mai tsarki. Idan aka ce da kai: Mene ne ma'anar yarda da hukumcin Allah? To, ka sani cewa yarda, ita ce barin fushin Allah da tuna fushin abin da Allah Bai hukunta shi ba, domin yin haka shi ya fi kuma ya fi kyau a gare shi a cikin abin da bai tabbatar da lalacewarsa ba ko ingancinsa. Wannan sharaɗi ne a cikinsa.

Idan aka ce da kai: Shin sharri ba hukuncin Allah ba ne, kuma yaya bawa zai yarda da sharri? To, ka sani cewa yarda ita ce lazimtar hukunci. Shi kuwa hukuncin sharri ba sharri ba ne. Abin da ake ce wa sharri kaɗai shi ne abin da aka hukunta. Abubuwan hukuntawa guda huɗu ne su ne: Ni'ima da tsanani da alheri da kuma sharri. Ita, ni'ima, wajibi ne a yarda da cewa, hukunci ce da Allah Ya hukunta. Domin haka ya wajaba ya gode wa Allah ta inda ni'imar ta zo.

Shi kuma tsanani, wajibi ne a yarda da abin da aka faɗa game da shi. Yana wajaba kuma ya yi haƙuri a kansa da kuma daga inda tsananin ya zo. Shi kuma alheri shi ma yana wajaba a yarda da shi da abin da aka faɗa game da shi na baiwar cewa alheri ne. Shi kuma sharri yana wajaba a yarda da shi da abin da aka faɗa a kansa da yarda da hukunta shi a kanka daga ko'ina, kuma sharrin ya zo maka. Ka sani cewa, waɗannan al'amura, suna kasancewa ne a zuci.

Abu na huɗu: Tsanani da musifu, kuma abin da zai ishe ka game da su shi ne, haƙuri. Ina horon ka da haƙuri da al'amura. Sai dai wannan yana faruwa ne a kan al'amura guda biyu.

**Na farkonsa:** Nutsa cikin bautar Allah, Shi kuma yana ginuwa ne a kan haƙuri. Wanda ya ƙudurci bautar Allah, kuma ya ja zuciyarsa ga karɓar abubuwan da suke bijirowa na tsanani da musifu. Sai dai ita, ibada, kanta tana

da wahala ke nan. Ita, ibada, ba a yin ta sai da wahalar mafi wahalar al'amura. Yana lazimtar a kewaye su, domin kada ayyuka su ɓaci. Tabbatuwa a kan aiki ita ce mafi tsanani a kan yin aikin. Shi, gidan ni'ima, gida ne da babu makawa a sami jarraba a ciki na wahalhalu kashi-kashi da musifu kamar mutuwar iyali da makusanta da 'yan'uwa da abokai da kuma jarraba rayuka da rashin lafiya da ciwace-ciwace da kashe mutane.

Ina horon ka da natsuwa. Ina gargaɗin ka kuma da gulma da ƙarya da tafiya zuwa wurin Sarki. Kowace daga cikin waɗannan musifu tana da hadari. Mai neman lahira shi ya fi samun tsananin jarrabawa. Wanda ya kasance zuwa ga Allah Ya fi kusanci, to, zai samu musifu masu yawa a duniya. Ya kai ɗan'uwana, in kana son yanke hanyarka ta zuwa lahira, to, ka sanya wa kanka launukan mutuwa guda huɗu:- su ne fari watau yunwa da ja shi ne saɓa wa Shaiɗan, da baƙi shi ne zargin mutane da kore shi ne; auka wa sashensu a kan sashensu. Na biyu daga al'amura biyu, waɗanda suke cikin haƙuri na da ga alhairan duniya da na lahira.

Ya ɗan'uwana ina horon ka da ka yanke daga waɗannan al'amura guda huɗu.

Idan kuwa ka ƙi, to, shagaltuwa da ɗaya daga cikinsu, zai hana maka yin ibada sannan ma mafi girma da ɓatarwarsu shi ne al'amarin neman arziki, domin shi ke juya zukata gaba ɗaya waɗanda Allah Ya halitta. Annabawa da malamai ba su gushe ba suna yin wa'azi, duk da haka ba su shiryu ba. Ba haka ba ma, ba su gushe ba suna tsoron kada su rasa abinci. Asalin dukkan wannan rashin lura da ayoyin Allah da halittunSu. Da kuma barin lura da maganganun Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi) da rashin aiki da maganganun bayin Allah na ƙwarai tare da shiga cikin waswasin Shaiɗan da rinewa da maganganun jahilai da nutsa cikin al'adun gafalallu, har Shaiɗan ya sami iko a kansu, kuma al'adun su tabbata a cikin zukatansu, har wannan ya kai ga raunin zuciya.

Amma ma'abuta basira da ƙoƙari ba sa gajiyawa da dalilanka da riƙo da igiyar Allah, ba sa waiwaye ga waswasin Shaiɗan da ɗabi'a mai kyau da kuma tsarkin zuciya. Idan shaiɗan ya sanya waswasi a cikin zukatansu, ko ransu, ko cikin mutum, to, za su tsayu wajen tunkuɗewa da kuma saɓa wa Shaiɗan har zuwa su sami jiɓintar hali mai kyau a gare su kuma Shaiɗan ya gushe daga gare su da ransu, kuma ya jawu ga ayyukan ƙwarai.

Ya ɗan'uwana waɗancan ƙoƙarce-ƙoƙarce suna tsayuwa su tabbata ne da ƙarfin ilimi da hasken tabbatarwa. Kuma ka sani ya ɗan'uwana cewa, lamunce wa Allah ga ginuwar jiki ba tare da dalili ba, wannan al'amari ne na

Allah. Hakanan kuma samun ƙarfi ga masu zuhudu da hanyar tafiya, ko shigar darare cikin kwanaki ga Allah suke. Akwai waɗanda ba su cin abinci har tsawon kwanaki goma.

Akwai wasu kuma ba sa cin abinci har tsawon wata guda, ko watanni biyu, kuma suna nan da ƙarfinsu. Amma mayar al'amari ga Allah, ana amfani da su ta hanyoyi biyu. Na farkonsu: Ka san cewa shi, zaɓi ba ya inganta sai ga wanda yake masani da gaba ɗayan al'amuran bayyane da kuma ɓoye, yadda halinta yake da kuma ƙarshenta. Idan kuwa ba haka ba, to, ba a yarda da zaɓin ɓarna da halaka a bisa abin da yake alheri ne da gyara. To, wannan shi ne ingantaccen al'amari da ya kewaye ga ilimin Ubangijin talikai.

**Na biyunsu:** Da wani mutum zai ce da kai, ni na fi ka ƙarfi ga dukkan al'amarinka, kai kana da ilimin zamaninka da yana yin ƙarfinsu kuma gaskiyarsu, tana zaune cikin zuciyarka. To ke nan me ya same ka da ba za ka mayar da al'amarinka ga Allah Ubangijin talikai ba? Alhali Shi ne Yake canza al'amura daga sama zuwa ƙasa. Mafi sanin duniya Wanda Ya ƙaddara dukkan abubuwan ƙaddarawa, Mafi tausayin masu tausayi, Mafi wadatar masu wadata Ya yi maka zaɓin abin da ya fi.

To, amma ita, yarda da hukuncin Allah, ana amfani da asaloli guda biyu. Shi ma na farkonsu shi ne walwalar zuciya daga damuwa da samun lada daga Allah da yardarSa. Na biyunsu: Abin da akwai fushin Allah daga wani babban tunani da cutarwa. Haƙiƙa, sashen malaman da suka gabata sun yarda cewa idan aka ce da kai mece ce ubudiyya da rububibiyya? Sai ka ce; Ubangiji Yake hukunci kuma bawa ya yarda. Idan kuwa ba haka ba da babu rububiyya da ubudiyya. Amma shi, haƙuri, magani ne, kuma ana ƙyamar shan sa, kuma yana da albarka wadda ke jawo amfani kuma ta tunkuɗe dukkan abin da bai da dalili. Idan magani ya kasance da irin wannan sifa, to, mai hankali ba zai ƙyamar shan sa ba. Kuma, shi, haƙuri, kashi huɗu ne; yin haƙuri a kan bin Allah. Yin haƙuri daga saɓa wa Allah. Da yin haƙuri a kan tarkacen duniya. Da yin haƙuri a kan musifu.

Muna roƙon Allah Ya datar da mu da mafi kyawon ayyuka. Domin lalle al'amura hannun Allah suke. Shi ne Mafi tausayin masu tausayi. Babu dabara babu karfi sai ga Allah Maɗaukaki Mai girma.

## BABI NA TARA

### Ibada

Kuma ina horon ka ya ɗan'uwa da lazimtar tashi ga yin ibada. wadda ita ce jin tsoro da fata. To, amma shi, tsoro, yana wajaba a lazimce shi da al'amura biyu, yin gargaɗi daga laifuffuka.

**Na biyunsu:** Kada ka yi mamakin ayyukanka na ƙwarai sai ka halaka. Amma ita, fata, ana lazimtar ta da al'amura biyu. Ɗaya, tashi, domin gudanar da biyayya ga Allah. Na biyu: Ɗaukar dukkan tsananin da ya same ka da wahalhalu. Idan aka ce da kai mene ne tsoro da fata? To, ka sani cewa lalle shi, tsoro, da fata suna komawa ga tunani, kuma ba shi cikin ikon bawa. Abin da yake cikin iko ga bawa ya gabatar da su. Iyakar tsoro, tsawar da ke faruwa cikin zuciya daga zaton da ba a so, iyakar fata ita ce, haskaka wa zuciya sanin falalar Allah Wanda rahammarSa ta yalwatu.

Abubuwan da tsoro ke gabatarwa guda huɗu ne su ne Tunawa da zunuban da suka wuce da tunawa da tsananin azabar Allah da tunawa da raunin ranka da tunawa da ikon Allah Maɗaukaki duk lokacin da Ya so da yadda Ya so. Abubuwan da fata ke gabatarwa guda huɗu ne. Su ne tunawa da falalar Allah da Ya yi maka da tuna alƙawarin lada da Allah Ya yi maka ba tare da tabbatar wa kanka ladar aikin da ka yi ba da tunawa da ni'imar da Ya yi maka game da al'amarin addiininka da duniyarka a halin da kake ciki, ba tare da tabbatarwa ba ko tambaya da tunawa da yalwar rahamar Allah Maɗaukaki.

Ya kai ɗan'uwana, shi, tsoro da fata su ne hanyar adalci tsakanin hanyoyi biyu masu halakarwa. Su ne amincewa da ƙauna ko fata. Ka sani cewa hanyar ba ta gyara hali tare da rai mai kyau daga alheri, sai da kiyayewa da abubuwa guda uku, waɗanda su ne asali na har abada. Tunawa da maganganun Allah Mai tsarki a cikin tsoratarwa da kwaɗayi da tunawa da ayyukan Allah Mai tsarki da ɗaukaka a cikin roƙo da yafiya da tunawa da ladar da Zai bayar ga bayinSa a cikin alƙawarin da Ya yi wa bayinSa na lada da uƙuba daga cikin ayoyin kwaɗaitarwa, akwai inda Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ قُلْ يَٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ أَسْرَفُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُوا۟ مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ ﴾ الزمر: ٥٣

***"Ya ku bayiNa da kuka israfi a kan kawunanku, kada ku yanke ƙauna daga rahamar Allah, lalle Allah Yana gafarta zunubai gaba ɗaya."*** Alƙur'ani 39:53

Da kuma faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿وَمَن يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ﴾ آل عمران: ١٣٥

*"Babu mai gafarta zunubai sai Allah."* Alƙur'ani 3:135

Da faɗar Sa:

﴿غَافِرِ ٱلذَّنۢبِ وَقَابِلِ ٱلتَّوۡبِ﴾ غافر: ٣

*"Shi mai gafarta zunubai ne Mai karɓar tuba."* Alƙur'ani 40:3

Da faɗinSa:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَعۡفُواْ عَنِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ﴾ الشورى: ٢٥

*"Shi ne Wanda Yake karɓar tuba daga bayinSa, kuma Yake yafe munanan ayyuka."* Alƙur'ani 42:25

Kuma da faɗar Allah:

﴿كَتَبَ رَبُّكُمۡ عَلَىٰ نَفۡسِهِ ٱلرَّحۡمَةَ﴾ الأنعام: ٥٤

*"Allah Ubangijinku Ya tabbatar wa kanSa tausayi."* Alƙur'ani 6:54

Da kuma faɗar Allah:

﴿وَرَحۡمَتِى وَسِعَتۡ كُلَّ شَىۡءٍ﴾ الأعراف: ١٥٦

*"RahamaTa ta yalwaci kome."* Alƙur'ani 7:54

Waɗannan ayoyi da makamantansu na fata suna da yawa.

Daga cikin ayoyin tsoro, akwai faɗar Allah;

﴿يَٰعِبَادِ فَٱتَّقُونِ﴾ الزمر: ١٦

*"Ya ku bayiNa ku ji tsoro Na."* Alƙur'ani 39:54

Da faɗinsa:

﴿أَفَحَسِبۡتُمۡ أَنَّمَا خَلَقۡنَٰكُمۡ عَبَثًا﴾ المؤمنون: ١١٥

*"Kuna zaton Mun hallice ku ne don wasa?"* Alƙur'ani 23:54

Da kuma faɗar Allah:

﴿أَيَحۡسَبُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَن يُتۡرَكَ سُدًى﴾ القيامة: ٣٦

*"Shin mutum yana tsammanin Za mu bar shi haka sasakai?"* Alƙur'ani 75:54

Da makamantan waɗannan ayoyi da suke magana a game da tsoro.

Daga cikin ayoyin da suke magana a kan tsoro da fata akwai inda Allah Ya ce:

﴿نَبِّئۡ عِبَادِيٓ أَنِّيٓ أَنَا ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ﴾ الحجر: ٤٩

*"Ka ba bayiNa labari cewa, Ni Mai gafara ne kuma Mai tausayi."* Alƙur'ani 15:49

Sannan Ya faɗa a ƙarshe:

﴿وَأَنَّ عَذَابِي هُوَ ٱلۡعَذَابُ ٱلۡأَلِيمُ﴾ الحجر: ٥٠

"*Kuma lalle azabaTa, azaba ce mai raɗaɗi."* Alƙur'ani 15:50

Da kuma inda Allah Ya ce:

﴿شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ﴾ البقرة: ١٩٦

*"Mai tsananin uƙuba."* Alƙur'ani 2:196

Sannan a ƙarshe Ya ce:

﴿ذِي ٱلطَّوۡلِۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ﴾ غافر: ٣

*"Ma'abucin gafara, babu abin bautawa sai Shi kaɗai."*

Mafi ban mamaki game da haka, faɗar Allah Maɗaukaki;

﴿وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفۡسَهُۥ﴾ آل عمران: ٢٨

*"Allah Yana tsoratar da ku kanSa."* Alƙur'ani 3:27

Kuma Ya ƙara faɗa:

﴿وَٱللَّهُ رَءُوفُۢ بِٱلۡعِبَادِ﴾ آل عمران: ٣٠

*"Allah Mai rangwame ne ga bayinSa."* Alƙur'ani 3:30

Allah Ya ƙara faɗa:

قَالَ تَعَالَى: ﴿ مَّنْ خَشِيَ ٱلرَّحْمَٰنَ بِٱلْغَيْبِ ﴾ ق: ٣٣

*"Wanda yake tsoron Allah a ɓoye."* Alƙur'ani 50:33

Ya haɗa tsoro da sunan Mai rahama ba Mai tilastawa ba ko Mai ramuwa ko Mai girma da makamantansu ba, domin ya kasance ambaton tsoro ya zama tare da rahama.

Asali na biyu; A cikin aikin bawa, amma ta ɓangaren tsoro sai ya riƙa tunawa da al'amarin Iblis. Amma ta ɓangaren fata, ka tuna da sihirin Fir'auna da mutanen Kogo da Karensu.

Asali na Uku; A cikin ambaton abin da Ya yi alƙawari da wanda aka alƙawarta masa. A cikin abin da aka yi alƙawari za mu ambata maka wasu halaye dangane da haka, domin tsoronka ya ƙaru, fatarka ma ta ƙaru. Daga cikinsu akwai mutuwa da ƙabari da ranar Alƙiyama da Aljanna da wuta. Amma ita, mutuwa, sai mu ambaci halin wasu mutane guda biyu. Ɗayansu. Abin da aka ruwaito daga ɗan Shibrimat lalle ya ce: "Na shiga wurin maras lafiya tare da Sha'abi yana tare da wannan mutum. Yana lakana masa kalimar shahada, sai maras lafiyar ya yi magana: "Ni ba zan faɗa wannan kalima ba. Ya karanta kuma:

﴿ وَأَلْزَمَهُمْ كَلِمَةَ ٱلتَّقْوَىٰ وَكَانُوٓا۟ أَحَقَّ بِهَا وَأَهْلَهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا ﴾ الفتح: ٢٦

*"Aka lazimta masu kalimar tsoron Allah, kuma sun kasance sun fi cancanta da ita da mutanenta ko ma'abutanta."* Alƙur'ani 48:26

Sai Sha'abi ya ce: Na gode wa Allah da Ya tseratar da ni da abokinmu.

Ɗayan kuma shi ne abin da aka ruwaito cewa, wani almjiri maɗaukaki ɗan Iyad dai mutuwa ta zo masa sai Fadil ya shiga gare shi, sai ya zauna wurinsa da kansa, sai ya karanta masa suratu Yasin. Sai ya ce: "Ya malamina, kada ka karanta wannan surar ka yi shiru." Sai ya laƙana masa ita sai ya ce: "Ba zan karanta ta ba, domin ni ba na tare da ita," sai ya mutu a haka. Sai Fadil ya shiga gidan wannan mutum, sai ya yi ta kuka har tsawon kwana arba'in bai fita daga gidan ba.

Sai ya gan shi a cikin barcinsa yana ta iyo cikin wutar jahannama. Sai ya ce: "Da wane abu ne Allah Ya cire ma'arifa daga gare ka, alhali ka kasance almajirinSa?" Sai ya ce: "Daga abubuwa uku ne aka cire wannan ma'arifa daga gare ni. Su ne: Annamimanci da hassada da kuma shan giya."

Amma shi, ƙabari, da halin da ake shiga bayan mutuwa, zan faɗi halin wasu mazaje guda biyu, abin da sashen salihai suka ambata, ya ce "Na ga Safiyanu Assauri bayan mutuwarsa a cikin barci. Sai na ce da shi yaya halinka ya kasance ya Aba Abdullahi? Sai ya kawar da kansa daga gare ni, kuma na

ce. 'Wannan ba zamanin kunya ba ne, sai na ce da shi: Yaya halinka, ya Aba Abdullahi?" Sai ya yi waƙa. Yana cewa:

**Na ɗaya:** "Na yi duba zuwa ga Ubangijina sai Ya ce da ni
*Madalla da yardaTa a gare ka ya Ɗan Sa'id

**Na biyu:** Haƙiƙa, ka kasance kana tsayuwa idan dare ya yi
*Da tunani da lura mai tsanani da zuciya kafaffa.

**Na uku:** Na kusance ka daga nesa ka zaɓi abin da kake so
* ka ziyarce Ni ba Ni da nisa daga gare ka

Mutum na biyu: Shi ne wanda aka ɗaure wa hannaye bayan mutuwarsa. Sai aka ce da shi: Me ka aikata? Sai ya yi waƙa, yana cewa:

Wani lokaci ya wuce muna wasa da shi, to, wannan shi, lokacin da ya zo yana wasa da mu.

Amma dangane da tashin Alƙiyama, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَوْمَ نَحْشُرُ ٱلْمُتَّقِينَ إِلَى ٱلرَّحْمَٰنِ وَفْدًا ﴿٨٥﴾ وَنَسُوقُ ٱلْمُجْرِمِينَ إِلَىٰ جَهَنَّمَ وِرْدًا﴾ مريم: ٨٥ - ٨٦

***"Ranar da Za mu tara masu tsoron Allah zuwa ga Mai rahama jama'a-jama'a. Kuma Mu kora mijirimai zuwa wutar jahannama a gangara da su."***
**Alƙur'ani 19:85-86**

Amma dangane da Aljanna da wuta, an yi amfani da ayoyi biyu game da su. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَسَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ شَرَابًا طَهُورًا﴾ الإنسان: ٢١

***"Ubangijinsu Ya shayar da abin sha mai tsarki."*** **Alƙur'ani 76:21**

da kuma faɗar Allah Maɗaukaki;

﴿رَبَّنَآ أَخْرِجْنَا مِنْهَا فَإِنْ عُدْنَا فَإِنَّا ظَٰلِمُونَ﴾ المؤمنون: ١٠٧

***"Ya ubangiji Ka fitar da mu daga cikinta, idan mun koma ga aikata ayyukan laifi, to, lalle mun kasance azzalumai."*** **Alƙur'ani 23:107**

Ya ce: "Ku zaunar da su cikinta kuma kada ku yi magana." Yahya ɗan Mu'azu ya ce "Ba mu sani ba cewa wace musifa ce ta fi girma daga cikin musifu guda biyu, kuɓuce wa Aljanna, ko shiga cikin wuta. Amma ita, Aljanna, ba a iya haƙuri da ita. Amma wuta kuma ba a iya haƙurin zama cikinta. A bisa kowane hali dai kuɓuce wa Aljanna shi ya fi sauƙi daga azabobin wuta.

## BABI NA GOMA

### Ikhilasi da Riya

Ina horon ka ya ɗan'uwana da tunkuɗe abubuwa marasa kyau. Abin **farko maras kyau:** Riya; ana tunkuɗe ta da yin ikhlasi ga aiki, domin aiki ya samu karɓuwa. Idan aka ce da kai; ka ba mu labari haƙiƙanin ikhilasi da kuma riya. To, ka sani cewa shi, ikhilasi, ya kasu kashi biyu. Akwai ikhilasi na aiki da kuma ikhilasi na neman lahira da aikin alheri. To, amma ikhlasi na aiki shi ne aikin da ke kusantar da mai shi ga Allah Mai tsarki da ɗaukaka. To, amma ikhilasi na neman lahira shi ne aikin da ake yi domin neman amfanin lahira da aikin alheri.

Fadil ya ce: Shi, ikhilasi, shi ne dawwamar duba aiki da mantawa da rabauta a ciki dukkansa. Wannan shi ne cikakken bayani. Kishiyar ikhilasi ita ce riya. Ma'anarta ita ce neman amfanin duniya da aikin lahira. Kuma ita Riya, kashi biyu ce. Riya tsantsa da riya ta cuɗanyawa. Riya tsantsa ita ce nufin samun duniya da aikin lahira. Wadda aka cudanya kuma, ita ce nufin samun amfanin duniya da lahira.

Idan aka ce da kai mene ne gurbin ikhilasi kuma a wane ɓangaren biyayya take kuma ta wajaba? To, ka sani cewa su, ayyuka, sun kasu kashi uku: Ibadoji na bayyane da ayyuka na ɓoye da kuma wanda shari'a ta yarda a yi. A cikin ikhilasi guda biyu na farko da kuma guda ɗaya na ƙarshe, shi ne ikhilasi na neman lada ne. Idan aka ce da kai shi ne kowane aiki yana buƙatar ikhilasi na kaɗaitawa? To, ka sani cewa, lalle an yi saɓani a cikinsa. Aka ce yana wajaba ga kowane aiki a sami ikhilasin kaɗaitawa. Aka kuma ce ya halatta ne a sami ikhilasi ga ayyukan ibadoji a dunƙule.

Idan aka ce da kai idan ya yi nufin alheri ga Allah da aikinsa, kuma ba ya son yabon mutane, ko kuma mutane su ji, ko samun wani amfani daga wurin mutane. Wannan zai kasance riya ke nan? To, ka sani cewa, yin haka riya ne tsantsa, domin ba yin abin da yake so ba ne kurum. Sai dai kasancewa ka yi ne kana fatar samun wani alheri da amfani da wannan ga aiki naka na duniya, daidai ne ya kasance daga Allah ne ko kuwa mutane ke yi domin samun wani alheri a wurinsu. Idan aka ce da kai idan ya kasance nufinsa na duniya ne da yake son ya samu daga Allah Maɗaukaki, domin ya samu kamewa daga mutane, ya tsayu ga yin bautar Allah Maɗaukaki. Wannan ma zai kasance riya? To, ka sani cewa yin haka da abin da zai haɗu da al'amarin lahira, wannan babu riya a cikinsa.

Hakanan kuma, idan ya kasance ka yi ne domin mutane su girmama ka da samun soyayyar malamanka da shugabanni. Ko kuma nufinka ya kasance, domin tabbatar da ƙarfafa hanyar gaskiya da mayar da amsa ga 'yan-bidi'a da yaɗa ilimi, ko kwaɗaitar da mutane a kan ibada, ba kana nufin ɗaukaka kanka da su ba, ba kuma kana yi domin samun duniya ba. Wannan duka niyyoyi ne ababen yabo, ba a sanya su a ƙofar riya ba, domin nufin da aka yi da su na lahira ne a haƙiƙa.

**Abu maras kyau na biyu:** shi ne jiji-da-kai Yana wajaba ka nisance su cewa shi da al'aura guda biyu. Na farkonsu cewa shi, jiji-da-kai yana kange mai shi daga samun dacewar Allah. Na biyunsu cewa shi, jiji-da-kai, yana ɓata aikin ƙwarai, domin ba a yi shi domin Allah Mabuwayi da ɗaukaka ba. Kuma kishiyarsa ita ce tunawa da baiwar Allah. Ya tuna cewa shi ma daga dacewar Allah Mai tsarki aka samar da shi da girman ladarsa da ikon a gare shi ne na ambato abin da ya wajaba yayin neman maganin jiji-da-kai da yin nafila a cikin sauran lokuta.

Ka sani cewa lalle mutane dangane da jiji-da-kai sun kasu kashi uku: Safun da suke jiji-da-kai ta kowane hali. Su ne Mu'utazilawa da 'yan Kadariyya. Safu na biyu su ne masu tunawa da baiwar Allah a kowane hali. Su ne waɗanda suka tsayu a kan hanyar ƙwarai ba sa jiji-da-kai da kome na aiki. Safu na uku su ne masu cuɗanyawa. Su ne dukkan Ahalussuna, suna faɗakuwa a wani lokaci, kuma su rafkana a wani lokaci. Amma abin da zai sanya ka bar riya shi ne, ka tuna faɗar Allah Mai tsarki da ɗaukaka:

﴿ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ وَمِنَ ٱلْأَرْضِ مِثْلَهُنَّ يَتَنَزَّلُ ٱلْأَمْرُ بَيْنَهُنَّ لِتَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ وَأَنَّ ٱللَّهَ قَدْ أَحَاطَ بِكُلِّ شَىْءٍ عِلْمًۢا ﴾ الطلاق: ١٢

***"Allah ne Ya halicci sammai guda bakwai da ƙasa kwatankwancinsu, al'amari na sauka a tsakaninsu, domin ku san cewa lalle Allah Ya kewaye da kome da iliminSa."*** **Alƙur'ani 65:12**

Allah Mai tsarki da ɗaukaka Ya kasance Yana cewa:

إني خلقت السماوات والأرض وما بينهما،

***"Ni Na halicci sammai da ƙassai da abubuwan da ke tsakanin su."***

Ka yi dubi da ganinka, domin ka san salla raka'a biyu da abin da kake yi a cikinsu da taƙaitawa, ba tare da kana ganiNa ba sai dai da ilimiNa a gare ka da yaboNa a kanka da godiyaTa a gare ka, har ka so cewa halitta su sani

domin su yabe Ka da wannan aiki da Ka yi domin su so ka, shin ba ka da hankali?

Ka tuna cewa shin wanda ke da abu mai daraja da tsada zai iya karɓar kuɗaɗe, dubban zinari ya sayar da su 'yan kuɗi kaɗan? Wannan ashe ba zai kasance asara bayyananniya ba? Yardar Allah ita ta fi fifiko a kan duniya da lahira da abin da ke cikinsu. Kuma ka tuna da cewa abin halittar da kake yin aiki, domin sa da ya san cewa kana yin aiki ne domin sa da ya yi fushi da kai. In ka kasance ba ka yin aiki domin Allah, kana nufin yin aiki domin neman yardar wanin Allah. Allah Zai gusar da zukatansu daga gare ka, su kaɗaita daga gare ka, sai yin haka kuma ya haifar da zukatansu daga gare ka, su kaɗaita daga gare ka, sai yin haka kuma ya haifar da hushin Allah gare shi. Kuma dukkan mutane su yi fushi da shi.

Amma abin da zai sanya ka bar jiji-da-kai shi ne tunawa da cewa, shi, aikin bawa, yana gudana ne a kansa da kuma kasancewar ƙimar aikin yana aukuwa ne daga Allah Maɗaukaki ta gurbin yarda da karɓar aikin. Idan ba haka ba, ai kana ganin ɗan ƙwadago yana aiki iya tsawon yini da dirhami biyu kurum. Da za ka kimanta daren Allah Maɗaukaki da Ya ba ka abin da hankali ba zai iya tunawa ba, ba haka ba ma da za ka ba Allah awa ɗaya kurum kana salla a cikinsa raka'o'i biyu masu sauki, duk abu ɗaya za ka samu dangane da haka.

Ka tuna cewa shi, mulki, a duniya idan aka ba wani, tufafi ne ko abincin da zai taimaka masa gudanar da aikinsa, akwai yiwuwar wanda aka ba wannan mulki, ya aiwatar da ƙoƙarinsa ga wanda yake fito-na-fito da mulkinsa. Ka tuna kuma da Wanda Annabawa da Mala'iku suke yin sujada gare Shi. Idan aka ba wulakantacce izinin ya shiga cikin waɗancan masu hidima, domin ya lura da wannan kafa, to, ai an girmama hidimar wulakantacce.

Ya ɗan'uwana ka ɓoye ayyukanka masu kyau kamar yadda kake ɓoye ayyukanka munana. Idan kana son kaiwa ga Allah. To, ina horon ka da ƙasƙanci da talauci da lazimtar ƙofar da yin ƙanƙan da kai da yin kuka da dare da wani yanki na yini. Ka nemi taimakon Allah, domin Shi ne Mafificin masu taimako. Babu tsira daga wannan al'amari sai da rahamar Allah Shi ne mafificin masu tausayi. Babu dabara, babu ƙarfi, sai ga Allah Maɗaukaki Mai girma.

## BABI NA GOMA SHA ƊAYA

### Godiya Ga Allah

Ina horon ka ya ɗan'uwa cewa, bayan ka sami rabauta da nufin wannan ibadoji masu sauƙi na daga laifuffuka da ka gode wa Allah da al'amura biyu. Na farkonsu: Dawwamar ni'ima. Na biyu: Samun ƙaruwa. To, amma dawwamar ni'ima domin godiya, ni'ima ce da ita ne take dawwama da barin ta ne, kuma ni'imar ke gushewa. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُوا۟ مَا بِأَنفُسِهِمْ ۗ وَإِذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِقَوْمٍ سُوٓءًا فَلَا مَرَدَّ لَهُۥ ۚ وَمَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَالٍ﴾ الرعد: ١١

*"Lalle Allah ba Ya canza wa mutane abin da Ya ba su na ni'ima har sai sun canza abin da ke gare su."* Alƙur'ani 13:11

To, amma samun ƙari sai Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿لَئِن شَكَرْتُمْ لَأَزِيدَنَّكُمْ﴾ إبراهيم: ٧

*"Idan kun gode Zan ƙara maku."* Alƙur'ani 14:7

Kuma ita, ni'ima, ta kasu kashi biyu. Ni'imar duniya da ni'imar Lahira. Ni'imar duniya iri biyu ce. Ni'ima mai amfani da Ni'imar tunkuɗewa. Amma Ni'ima mai amfani ita ce a ba ka abin da za ka kyautata rayuwarka da kuma amfana da ita. Abubuwan amfana sun kasu kashi biyu. Daidaita halitta a cikin amincinta da lafiyarta da abin da kake jin daɗi na abinci da abin sha da tufatuwa da aure da sauransu. Ita kuma Ni'imar tunkuɗewa ita ce a juyar maka da abubuwa marasa kyau da kuma masu cutarwa. Kuma ita ma ta kasu kashi gida biyu:

**Na Farkonsu:** Rai tare da amincewarka a gare shi wajen abin da yake kwaɗayi da sauran laifuffuka da illoli.

**Na Biyu:** Tunkuɗe abin da za ka haɗu da shi na cutarwa na daga nau'o'in saɓawa ko mummunan nufi na mutum da Aljani da Zaki da dabbobi da makamantansu.

To, amma ni'imar addini ta rabu gida biyu; Ni'imar dacewar Allah da Ni'imar kariya. To, ni'imar dacewar Allah ita ce dacewar Musulunci da sunnar Annabi (saw) sannan biyayya ga Allah. Da kuma ni'imar karewa, cewa kange ka daga kafirci, ko shirka da bidi'a da ɓacewa da kuma kare ka cewa kange ka daga kafirci, ko shirka da bidi'a da ɓacewa da kuma kare ka daga sauran

laifuffuka. Bayanin haka sai Shugaban duniya wanda Ya yi maka ni'ima kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَإِن تَعُدُّوا نِعْمَةَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴾ النحل: ١٨

***"Idan za ku yi ta ƙirga ni'imomin Allah, ba za ku iya ƙidanye su, ba. Lalle Allah Mai gafara ne Mai tausayi."*** **Alƙur'ani 16:18**

Kuma dawwamar wannan ni'ima gabaɗayanta bayan Allah Ya yi maka baiwa da ita da yi maka ƙari a kansu ta kowace kafa daga cikinsu, wanda ba ka kai gare su ba, kuma dukkan ƙoƙarinka ya dogara ne daga abu guda, watau ita ce godiya da yabo ga Allah.

Tsantsar waɗannan abubuwa tana kasancewa ne ga kimanta su, ya kasance a cikinsu akwai kowane irin amfani, domin tabbatar da riƙo da su, ba tare da rafkanuwa ba ta kowane hali. Domin ita, dukiya ce mai tsada. Allah ne Ma'abucin dacewa da falalar. Idan aka ce da kai: Mene ne haƙiƙanin godiya da yabo? To, ka sani cewa lalle malamai sun rabu a **tsakaninsu** cewa ita, godiya, tana daga hailala da tasbihi. Amma godiya ita ce yin biyayya ga Allah da gaɓɓai gabaɗaya ga Ubangijin halittu.

Idan aka ce da kai: Mene ne gurbin godiya? To, ka sani cewa gurbinta shi ne ni'ima. Akwai ni'imar addini da ni'imar duniya. Amma tsanance-tsanance da masifu a cikin duniya a cikin rai, ko iyali, shin godiya ta halasta a kansu? To, akwai maganganu guda biyu. Akwai maganar da aka ce ba ta lazimtar godiya, sai dai shi, tsanani, a wani gefen ni'imar Allah ne. To, ya lazimci godiya a bisa wannan ni'imar da aka gwama su tare da shi. Da kuma inda aka ce. Suna lazimtar godiya. Domin waɗancan tsanance-tsanance ba su ne haƙiƙani ba da dalilin da ya jawo suna masu amfani na daga addu'o'in da ba a so na wata illa, sai ya kai ga samun lafiyar jiki. Idan aka ce da kai shin godiya ce ta fi, ko haƙuri ka sani. Haƙiƙa, an ce godiya ita ta fi, saboda faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿ وَقَلِيلٌ مِّنْ عِبَادِىَ ٱلشَّكُورُ ﴾ سبأ: ١٣

***"Kaɗan ne daga cikin bayiNa suke godiya."*** **Alƙur'ani 34:13**

An keɓe su ne daga cikin keɓantattun abubuwa. Kuma an ce: Ba haka ba ne haƙuri ya fi, domin shi ne mafi girman wahala. Kuma yana zama mafi girman lada, ya fi girman matsayi. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴾ الزمر: ١٠

*"Lalle Za mu cika wa masu haƙuri ladarsu ba tare da lissafi ba."*
**Alƙur'ani 39:10**

Gazzali ya ce: "Lalle ita, godiya yadda take, ba ta samuwa sai da haƙuri. Shi kuma yadda haƙuri yake ba ya samuwa sai ga mai godiya." An yi amfani da asaloli guda biyu ne:

**Na Farkonsu:** Lalle ni'ima, ana bayar da ita ne ga mai ƙaddara ta, kuma mai godiya shi ya san darajarta,

**Na Biyu:** Tana samun wanda bai san ƙimar ta ba. Watau wanda ya kafirce mata ba ya godiya game da ita.

Ina horon ka da ka yaɗa ƙoƙarinka har ka san kimanta ta. Idan Allah Ya yi maka ni'ima cikin addini, to, ina gargaɗin ka da waiwayen duniya. Ka sani bisa haƙiƙa, cewa kai da an halicce ka a farkon duniya, kuma ka sami godiya da Musulunci da farkon lokaci har zuwa abada da ba ka kasance haka ba. Sai dai ina horon ka da yaɗa ƙoƙorinka gwargwadon iyawarka.

Ya ɗan'uwana lalle al'amari fa yana da sauƙi ga wanda Allah Ya sauwaƙe ma. Yana ga bawa ya yi ƙoƙari, Allah ne kuma Mai shiryarwa. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ فِينَا لَنَهْدِيَنَّهُمْ سُبُلَنَاۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَمَعَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴾ العنكبوت: ٦٩

*"Waɗanda suka yi ƙoƙari a cikin al'amarinMu, Za mu shiryar da su hanyoyinMu, lalle Allah Yana tare da masu kyautatawa."*
**Alƙur'ani 29:69**

Ya ɗan'uwana, karamominka idan ka yi riƙo da wannan hanya da yi mata hidima, guda Arba'in ne. Guda ashirin a nan duniya suke; guda ashirin kuma a lahira suke. Amma waɗanda suke a nan duniya, su ne:

**Ta farko:** Ambaton Allah gare ka da yabon Sa.

**Ta biyu:** Godiyarka a gare Shi.

**Ta uku:** SoyayyarSa ga Allah.

**Ta huɗu:** KasancewarSa wakilin Sa (Allah).

**Ta biyar:** Ya kasance Allah ne Mai azurta ka.

**Ta shida:** Kasancewa Allah ne Mai taimakon ka.

**Ta bakwai:** Ya kasance Shi ne Mai natsar da kai.

**Ta takwas:** Buwayar rai ƙasƙanci, ba zai same ka ba.

**Ta tara:** Ɗaukakar himma.

**Ta Goma:** Wadatuwar zuciya.

**Ta goma Sha ɗaya**: Shiriyar zuciya da hasken Allah zuwa ga ilimomin da sirrace-sirrace.

**Ta goma sha biyu:** Buɗewar ƙirji ba za ta sami ƙunci ba daga wahalhalun duniya.

**Ta goma sha uku:** Samun kwarjini.

**Ta goma Sha huɗu:** Sanya son Sa cikin zukata.

**Ta goma Sha biyar:** Samun albarka ta gaba ɗaya da samun albarka da turɓaya da inda ka taka, ko ka zauna, wata rana da mutumin da ka yi abuta da shi.

**Ta goma sha shida:** Horewar ƙasa daga tudu da kogi har in kana so ka tafi cikin iska da tafiyarka a kan ruwa da yanke fuskar ƙasa cikin awa ɗaya.

**Ta goma sha bakwai:** Hore dabbobi daga Zaki da dabbar daji da dabbobin gida da waninsu.

**Ta goma sha takwas:** Kada ka tambayi kome wurin Allah sai abin da Ya ba ka.

**Ta goma sha tara:** Kawar da fuskantar ƙofar Allah Mabuwayi sai ya nemi wasila wurin halitta zuwa ga Allah da yin hidimarka da kai buƙata ga Allah da fuskarka da albarkarka.

**Ta Ashirin:** Karɓa kira daga Allah Maɗaukaki ko da tunaninka ya halartar da wani abu. Waɗannan su ne karamominka a nan duniya. Amma kuma guda ashirin da suke a lahira, su ne;

**Ta ashirin da ɗaya:** Sauwaƙe maka magagin mutuwa.

**Ta ashirin da biyu:** Tabbatar imani.

**Ta ashirin da uku:** Fitar da rai tare da bushara.

**Ta ashirin da huɗu:** Dawwama a Aljanna.

**Ta ashirin da biyar:** Rayuwarka a asirce tare da ranka shi, kuma jiki, a girmama shi da yi masa jana'iza.

**Ta ashirin da shida:** Amintuwa da fitinar tambayar ƙabari da haɗuwa da dacewa.

**Ta ashirin da bakwai**: Yalwatar ƙabari da haskaka shi.

**Ta ashirin da takwas:** Natsar da ranka da girmama shi da kasancewarka tare da bayin Allah nagari.

**Ta ashirin da tara:** A tashe ka cikin buwaya da girmamawa, za ka fita daga kabarinka; Mala'iku suna haɗuwa da kai da hular sarauta.

**Ta talatin:** Hasken fuska.

**Ta talatin da ɗaya:** Amintuwa daga wahalhalun Ranar Alƙiyama.

**Ta talatin da biyu:** Karɓar littafin a hannun dama.

**Ta talatin da uku:** Sauƙin hisabi.

**Ta talatin da huɗu:** Samun nauyin ma'auni.

**Ta talatin da biyar:** Tabbatar samun tafkin Annabi (saw).

**Ta talatin da shida:** Tsallake siraɗi da sauƙi.

**Ta talatin da bakwai:** Samun ceto.

**Ta talatin da takwas:** Tabbatuwa a Aljanna har abada.

**Ta talatin da tara:** Samun yarda mafi girma.

**Ta cikon arbai'in:** Haɗuwa da Ubangijin talikai abin bautawa na farko da na ƙarshe, ba tare da 'ya'ya ba Mai girma da ɗaukaka.

Waɗannan su ne karamominka alhaira.

Da cikarsu ne littafin ya kammala wanda na tsamo su daga littafin "**Asararul Kalamu Abi Hamida Gazzali.**" Allah Maɗaukaki Ya jiƙansa. Kuma Ya zubo mana daga cikin albarkarSa.

Godiya ta tabbata ga Allah da dukkan yabo a gare Shi wanda na sani daga cikinsu da wanda ban sani ba a bisa ni'imominSa duka. Ya Allah Ka yi salati da aminci da albarka a bisa shugabammu, Muhammadu da iyalansa da matansa da zuriyarsa, salati da aminci da albarka, waɗanda ba su da iyaka kamar yadda babu iyaka ga kamalar Allah. Tsira da aminci su ƙara tabbata ga Annabi Muhammadu wanda babu Annabi bayansa. Dukkan godiya ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

# تنبيه الغافلين

## وتنظيم الإخبار وبديع الآثار

# FAƊAKAR DA RAFKANANNU

Na

## Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Mallam Muhammad Bala Abubakar

**Edita**

Dr. Hamza A. Ainu

## GABATARWAR MAWALLAFI

**Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin-ƙai**

Allah Ya yi daɗin tsira a kan shugabanmu, Muhammadu da iyalansa da abokansa.

Bawa mabuƙacin rahamar Ubangijinsa, Usmanu Ɗan Muhammadu ɗan Usmanu, wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo, (Allah Ya lulluɓe shi da rahamarSa) yana cewa: Wannan littafi **Faɗakar Da Rafkanannu Da Tsara Labartawa Da Kyawawan Gurabu.**

Azzakiyu Muhammadu ɗan Mahmud Alwankari (Allah Ya yi masa rahama) ragowar magabata na ƙwarai, ya ba mu labari. Ya ce: "Allah Ya sanya dukkan alheri a cikin fahimtar Addini, kamar yadda dukkan sharri ke shiga a cikin jahilci domin jahili yana aikata wa kansa abin da maƙiyi ba zai yi wa maƙiyinsa ba.

Na yi mamakin wanda ke keɓance gidan ruɗu da hattara da makirci amma ba ya kyautata zaman ƙabari, domin hattara da macizai da kunami da tsutsa. Jin daɗin duniya kamar farin cikin mafarki ne, ƙarshen girmanta talauci ne, lallai wanda ya kama ta da gaske ya taɓe.

Kashedinka ya ɗan'uwana kar ka ɗauke ta da hannuwa biyu a'a. Ka ɗauke ta da hannu ɗaya. Farin cikinta yana gauraye da kuka ba ta da wata ni'ima face mai saurin gushewa. Ba don saboda wautar da ke gare ka ba, ta yaya kake neman farin cikinta da girma a gidan kurkuku.

Duniya kayan Shaiɗan ce. Kashedinka, kar ka yi masa almubazzaranci da kayansa sai ya kama ka ta inda ba ka sani ba. Ya shiga wuta tare da kai. Duniya gidan jarrabawa ce. Ka da ka bari Ubagijinka Ya riske ka, cikin jarababbu.

Wanda ya karanta Alƙur'ani a gidajen masu mulki da mawadata saboda kwaɗayin abin duniya, Allah Zai yi masa azaba da abubuwa huɗu: -

**Na Farko:** Zai mutu talaka;

**Na Biyu:** Zai zare alamar mutanen kirki daga fuskarsa;

**Na Uku:** Mala'iku za su riƙa ce masa maƙiyin Allah da ManzonSa;

**Na Huɗu:** Zai tashi a ranar ƙiyama, a matsayin la'ananne.

**<u>Alƙur'ani Takobi ne Da Ke Yanke Talauci Ga Wanda Ya Tsarkake Shi Ya Jawo Talauci Ga Wanda Ya Tozarta Shi.</u>**

Halaye uku suna jawo talauci: Yawan janaba da tozarta Alƙur'ani da zama a ƙofar ɗaki. Allah Ya tsine wa wanda ya yi wa waninSa sujada, Allah Ya tsine wa wanda ke fallasa asiran bayinSa. Babu hutu ga yawan bashi, makwaɗaici, matalauci ne koda ya mallaki duniya.

Mai kamun kai mawadaci ne koda talaka ne. Babu wadata ga wanda ba ya yarda da abin da ya samu. Wanda ya yi haƙuri, haƙiƙa, ya wadatu. Ilimi a wurin gajiyayye kamar madubi ne ga makaho. Dukiya a hannun marowaci kamar mai tatso nono ne a wajen wanda ba ya da dausayi ba ya da gida.

Da sannu lokaci zai zo wa al'ummata, za su musanya gaskiya ta zama ƙarya a wurinsu. Da sannu lokaci zai zo wa al'ummata talakawa suna mutuwa alhali mawadata ba za su tausaya musu ba. Duk wanda ya wahalar da makaho, babu makawa Mala'iku za su wahalar da shi a cikin siraɗi da ma'auni.

Wanda ya jawo shi (makaho) saboda Allah, daga faɗawa wurin cutarwa, Allah Maɗaukaki Zai sanya masa Mala'iku su tsirar da shi daga wuta. Kashedinka, kar ka tozarta iddar ɗan'uwanka Musulmi, shi ne ka kwanta da matarsa a cikin iddarsa domin zai yi jayayya da kai ranar ƙiyama, ranar kamunga. Babu jin daɗi ga rayuwar da ke jiran mutuwa, ku bautata wa Allah kar ku haɗa Shi da komai.

Zama da maƙiyi, yana tauye rayuwa. Mutuwa ta fi sauƙi fiye da zama da wanda zuciyarka ba ta so. Kar ka kusanci gulma. Gaggautawar mutuwa, ga mai kambun baka gaskiya ne. Niyyar salla a lokacinta tana yawaita farin ciki, tana kamunce arziki. Jinkirta salla a lokacinta yana nauyaya arziki kamar yadda yake nauyayawa da zina da barcin asuba.

Kar ka zama mai tsaya wa azzalumai. Allah Yana shigar da mai tsananin jayayya wuta tun kafin hisabi, shi ne mai yawan dabara a gidan mahukunta. Babu mai wa'azin da ya fi mutuwa tsanani. Lokaci shi ne abokin tafiyarka.

Rayukanku, kamar jingina ne a gare ku babu makawar yankewa dangane da wanda aka bai wa jingina. Babu makawa game da ma'abocin aiki game da samin sakamako da cikawa, babu cutar da ta fi talauci tsanani.

Aliyu Ɗan Abu Ɗalib ya ce: "Duniya za ta zo ranar ƙiyama a kan surar tsohuwa kuturwa mummuna mai jan ido. Tana mai bayyanar da haƙoranta a

cikin mafi munin halittarta. Sai ta hango talikai sai a ce musu: 'Shin ko kun san ta?' sai su ce: 'Muna neman kariyar Allah daga sanin wannan."

Sai a ce musu: "Wannan ita ce wadda kuke ƙiyayya da hassada a kanta. Kuna bin gurace-guracenta na ƙarya, waɗanda suke ruɗe ku, kuka yanke zumuncinku saboda ita. Yau Ubangijinku Zai yi  muku azaba kala-kala sahu-sahu.

Duniya kamar inuwa ce, tana gushewa tare da rana. Duniya kamar walƙiya ce mai fizgewa; jin daɗinta ba zai tsawaita ba face ya gushe ya koma ga waninka. Babu hutawa ga mai hassada; babu mutunci ga maƙaryaci; babu masoyi ga marowaci.

Aliyu Ɗan Abi Ɗalib ya ce: Mutane suna alfahari da dukiya da nasaba; mu kuma muna alfahari da ilimi da ladabi. Bin jahili kan gaskiya ya fi bin malami a cikin ɓarna. Babu mayarwa ga abin da Allah Ya hukunta. Wanda duk ya ce dukkan mutane iri ɗaya ne, babu magani ga wautarsa.

Zuciya kamar ƙasa ce, aiki kamar irin shuka ne, wanda ya yi shuka a cikinta, zai girbe nomansa. Mafificin irinta, aiki da addini; makomarta tsantseni; irinta, ijtihadi, lahira ita ce ranar girbi.

Duk wanda ya shuka zai girba, wanda bai shuka ba, ba zai girba ba. Barin sa rai ga abin hannun mutane, shi ne maganin ciwon zuciya. An tambayi Aliyu Ɗan Abi Ɗalib (Allah Ya ƙara masa yarda) daga abubuwa shida: "Mene ne ya fi kogi wadatuwa?" Mene ne ya fi dutse tauri? Mene ne ya fi wuta zafi? Mene ne ya fi sama nauyi? Mene ne ya fi hunturu sanyi? Mene ya fi guba ɗaci?

Sai Aliyu Bin Abu Ɗalib (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: "Zuciya mai gamsuwa da abin da Allah Ya ba shi, ta fi kogi wadatuwa; zuciyar kafiri ta fi dutse tauri; azzalumin shugaba ya fi wuta zafi; ƙage ya fi sama nauyi, annamiminci ya fi guba ɗaci, neman abu a hannun marowaci ya fi hunturu sanyi.

Dukiyar wanda za a azurta, tana cikin taskokin mutane. Babu wadatuwa sai wadatuwar zuci; babu alheri a soyayya da marashin arziƙi; babu aibin da ya fi rowa tsanani. Babu masoyi ga marowaci, babu ciwon da ya kai kwaɗayi tsanani. Masoyinka shi ne mai tausaya maka a lokacin tsanani, arziƙin mutum yana cikin hannunsa da harshensa. Babu ƙarshe mai kyau a cikin saɓon Allah. Kar ka kusanci wanda ya yi gaba da mahaifinka. Kar ka auri ɗiyar mazinaciya, lallai ne tana da wani abu daga halin uwarta.

Kaicon wanda ya bi halakakku suka halaka shi. Jin daɗinsu na tare da su, shi kuma halaka ne tare da shi. Duniya ba ta kai fiffiken sauro a wurin mai hankali ba. Asalin halaka shi ne kwaɗayi da son duniya.

Idan Allah Yana son bawanSa sai Ya yawaita masa baƙin ciki. Idan kuma Ya ƙi shi sai Ya buɗe masa duniya. Taurin bashi da rowa, hassada ce uwarsu. Girman kai da kasala, wauta ce uwarsu; kunya da haƙuri, imani ne ya haife su, sai haƙuri ya auri kunya, aka haifi hankali. Girman kai ya auri kasala, aka haifi talauci. Sa rai ya auri son duniya, aka haifi sata; Kasala da roƙo, uwarsu ɗaya ubansu ɗaya. Babu ibada mafi tsanani kamar gane addini. Annabi (saw) ya ce:

(انتظار الفرج بالصبر عبادة)

***"Sauraron samun kuɓuta tare da haƙuri, ibada ne."***

Ku yi koyi da mai gani, kar ku yi koyi da makaho. Haƙuri takobi ne mai yankewa, ba zai sauka a kan wani abu ba, face ya yanke shi.

Maroƙi, matalauci ne koda ya mallaki duniya. Maroƙi, matalauci, ne ko da ya zo a kan doki. Ka fi abotaka da mafificin mutane, kar ka yi abota da mafi ƙasƙancinsu. Kamar yadda kuke kamar yadda ake shugabantar ku. Babu ciwon da ya fi talauci tsanani. Arziƙi ya fi tsananin neman bawa fiye da ajalinsa.

Allah Ya raba wa bayi arzuƙansu tun kafin rayukansu da shekaru dubu sittin. Ya ƙaddara abin ƙaddarawa da shekaru dubu hamsin. Shugabannin ƙarshen zamaninmu, 'yan-leƙen asiri ne. Abokan ƙarshen zamaninmu, mayaudara ne. Babu mata gare mu sai matan jayayya. Kar ku nemi arziki ga wanda babu kyautatawa a gare shi. Ku bai wa talakawa aure da sannu Allah Zai wadata su. Wanda ya auri mace saboda wadatarta, ƙarshensa talauci.

Wanda ya ci bashi domin ya sami girma da shi, ƙarshensa talaucewa. Wanda ya ci bashi don sadar da zumunta, Allah Zai lamunce masa abin da zai biya bashin da shi. Wanda ke cutar da malamai, imani zai fita daga zuciyarsa. Hassada tana kawar da haske daga fuska kamar yadda kwaɗayi ke kawar da kunya.

Ɗan'Adama yana fita daga duniya kamar yadda ya shigo a talauce. Iblis yana tsoron malami ɗaya amma ba ya tsoron jahili dubu. Wanda ke nufin tsira ba tare da aiki mai kyau ba, babu magani ga wautarsa. Ka ji tsoron halaka ga malamai, a lokacin da suke hulɗa da sarakuna.

Gajeren ruku'i tare da ƙasƙantar da kai, ya fi dogon ruku'I tare da fajirci. Wanda ya nemi gaskiya a wajen mata, babu magani ga wautarsa. Managarciyar mace tana taimakawa ga addini, muguwar mace tana canza addinin mijinta. Wanda ya fi kowa wauta, shi ne wanda ya koma ga Allah da talauci, ya bar dukiyarsa mawadata suka gada. Babu hankali ga wanda ke zaune a alƙarya, babu ilimi.

Shugabannin ƙarshen zamaninmu, 'yan-leƙen asiri ne. Malamansu, kuraye ne. Wanda ya cire hannuwansa daga yi wa Allah biyayya, ya zama a cikin mafi ƙasƙancin ƙasƙantattu. Wanda sallarsa ta ƙaranta, haƙiƙa, arziƙinsa ya ƙaranta. Wanda ya rasa alwalarsa, lallai haskensa ya ƙaranta. Wanda ya kusanci sarki, haƙiƙa ya mallaki rabin halaka.

Haƙiƙa, mafi tsananin wautar mutane, wanda ya bar guzuri kafin tafiya. Duk wanda ke tsoron zafi, babu makawa gare shi daga maƙiyi. Kashedinka, kar ka kasance mai ɗaukar guzuri a tsakanin 'yan uwanka, suna tafiya ba su ɗauke da komai. Kai kana ɗauke da nauyi.

Kashedinka, kada ciyawar daji "bola" ta burge ka, tana da kyau ne amma ba ta da amfani. To, haka nan kyakkyawar mace ba tare da kula ba kamar abincin da ba gishiri ne. idan ka kiyayi mahaifanka, to, ɗanka zai kiyaye ka. Wanda bai kiyaye dattijo ba, babu alheri a ƙarshensa. Babu haske a cikin arziƙin marowaci.

Kashedinka, kar ka yi surukuta da ƙasƙantacciyar nasaba. Matan zamaninmu, abokan maza ne.

## KARSHE

Tsira da aminci su tabbata ga shugaban Larabawa da baubayi.

# سوق الصادقين إلى حضرة القدس

# KORA MASU GASKIYA

Na

## Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Mallam Is'haƙ Yunus Al-Mashgool Bauchi

**Edita**

**Dr. Hamza A. Ainu**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ........................................................................ 157

Bayanin Amfanin Yunwa Da Illolin Ƙoshi............................................ 160

Bayani A Kan Hanyar Da Mutum Zai Saba Da Karya Sha'awar Ciki ......... 163

Bayanin Saɓanin Hukuncin Yunwa da Darajarta da Saɓanin Halayyar Mutane ........................................................................................ 169

Bayanin Illar Riya Wadda Take Ƙwanƙwasawa Zuwa Ga Wanda Ya Bar Cin Sha'awace-Sha'awace ko ya Karanta cin Abinci................................ 170

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Allah Ka yi salati a bisa shugabammu, Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa da tsira da aminci.

Bawa mabuƙaci mai tsananin buƙata zuwa ga rahamar Ubangijinsa wato Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usman, Bafullatani kuma mai bin mazhabar Maliki mai koyi da Ash'ari: Ya ce godiya ga Allah. Tsira da aminci su tabbata a bisa Muhammadu, masoyin Allah, zaɓaɓɓe kuma da alayensa da sahabansa tsarkakku da waɗanda suka bi su da kyautatawa zuwa ranar tura masu ɗa'a zuwa Aljanna. Fajirai kuma zuwa wuta.

Amma bayan haka wannan littafi ne na tura masu gaskiya zuwa halarar nan ta tsarkaka.

A cikinsa akwai bayanin falalar yunwa da amfaninta da hanyar motsa jiki cikin da karya sha'awar ciki da bayanin saɓanin hukuncin yunwa da halayyar mutane da bayanin falalar yunwa da bayanin riya da barin shawa.

Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce:

(جاهدوا أنفسكم بالجوع والعطش فإن الأجر في ذلك كأجر المجاهد في سبيل الله وأنه ليس من عمل أحب إلى الله من جوع ومن عطش)،

***"Ku yaƙi kawunanku da yunwa da ƙishirwa domin lada a cikin yin haka kamar ladan wanda ya yi yaƙi wurin ɗaukaka kalmar Allah. Haƙiƙa, babu wani aiki da ya fi soyuwa a wurin Ubangiji face yunwa da ƙishirwa."***

Kuma daga Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يدخل ملكوت السماء من يملأ بطنه)

***"Duk wanda ya cika cikinsa ba zai shiga can fadar Ubangiji ba."***

Kuma aka ce ya Manzon Allah (saw) wane ne ya fi daraja a cikinmu ne sai ya ce

(من قل طعامه وضحكه ورضي بما يستر به عورته).

***"Wanda ya ƙaranta cinsa da dariyarsa kuma ya yarda da abin da ya suturta al'aurarsa da shi."***

Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أفضلكم منزلة عند الله أطولكم جوعا وتفكرا وأبغضكم إلى الله كل نئوم وأكول وشروب)،

***"Mafificin matsayinku a wurin Ubangiji ranar tashin alƙiyama wanda ya fi ku tsawon yunwa da zurfin tunani kuma mafi fushinku a wurin Ubangiji, duk wani abin da ake zargi da mai yawan ci da mai yawan sha."***

Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

"إن الله يباهي الملائكة بمن قل طعامه في الدنيا يقول: انظروا إلى عبدي إبتليته بالطعام والشراب في الدنيا وتركهما، اشهدوا يا ملائكتي ما من أكلة واحدة يدعها إلا أبدلته بها درجات في الجنة).

***"Lalle Allah Yana yi wa mala'iku alfahari ga wanda ya ƙaranta cinsa a cikin duniya. Ya ce ku duba zuwa ga bawaNa Na jarrabce shi da ci da sha cikin duniya kuma ya bar su, to, ku shaida ya mala'ikuNa babu wata loma ɗaya da zai bari face sai Na musanya masa da ita da wasu darajoji a cikin Aljanna."***

Haka kuma Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا تميتوا القلوب بكثرة الطعام والشراب فإن القلب كالزرع يموت إذا كثر عليه الماء)،

***"Kada ku kashe zukatanku da yawan ci da sha domin zuciya kamar tsiro take, tana mutuwa idan aka yawaita zuba mata ruwa a kanta."***

Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

وقال صلى الله عليه وسلم: (وما ملأ آدمي وعاء شرا من بطنه حسب ابن آدم لقميات يقمن صلبه فإن كان لابد له فثلث لطعامه وثلث لشرابه وثلث لنفسه). وفي خبر: "إن الشيطان يجري من ابن آدم مجري الدم فضيقوا مجاريه بالجوع والعطش".

***"Wani ɗan'Adam bai taɓa cika wata jaka ba mafi sharri a kansa da ta fi cikinsa, lomomi biyu sun ishi ɗan'Adam da su riƙe masa cikinsa. In ya zama ba makawa sai ya ci sai ya kasa cikinsa kashi uku. Ɗaya don cinsa, ɗaya don shansa ɗaya don numfashinsa." Ya ce a cikin wani labari: "Lalle ne shaiɗan yana gudana daga jikin ɗan'Adam magudanar jini. To, ku tsuke magudanarsa da yunwa da ƙishirwa."***

Saiyadatuna A'isha (Yardar Allah ta tabbata a gare ta) ta kasance tana cewa: "Lalle Manzon Allah (saw) bai taɓa ƙoshi ba." Lukman ya ce ga ɗansa: "Ya kai ɗana, idan jakar ciki ta cika, to, sai ƙwaƙwalwa ta yi barci kuma hikima ta dakushe kuma gaɓɓai su zauna daga barin yin ibada." Kuma Abu Sulaiman Addarani ya ce: "In bar loma ɗaya daga abincin dare ta fi soyuwa a gare ni daga in tsaya da dare har zuwa Asuba." Kuma Sahal ya kasance yakan bar kansa da yunwa kwana ashirin da 'yan kai ba ya cin komai. Ya kasance

yana girmama yunwa kuma yana kai matuƙa a yunwa har yake cewa, ranar ƙiyama ba zai zo da wani aiki na ɗa'a da ya fi yunwa da rashin ciye-ciye marasa amfani da koyi da Annabi (saw) a wurin cinsa. Ya ce kuma "Lalle masu daraja masu daraja ne saboda barin ciki ba komai da yin shiru da hana ido barci da keɓanta," kuma ya ce kan kowace ɗa'a tsakanin sama da ƙasa yunwa ce kuma haka kan kowane aikin saɓo, tsakaninsu, to, ƙoshi ne.

Ya kuma ce: "Wanda ya bar kansa da yunwa, to, wasiwasi zai yanku gare shi." Ya ce kuma: "Fuskantowar Allah a kan bawanSa yana zamanto ne da yunwa da rashin lafiya da bala'i." Ya ce: "Ku sani wannan wani zamani ne ba wanda zai samu tsira a cikinsa face wanda ya yanke kansa da yunwa da haƙuri da ƙoƙari." Ya kuma ce babu wani a doron ƙasa da ya sha daga wannan ruwa har ya ƙoshi ya kuɓuta daga barin saɓo koda ya gode wa Allah. To, ya ya ke nan idan ya ƙoshi da abinci!

AbdulWahid ɗan Zaidu yana rantsuwa da Allah cewa; Allah Bai taɓa tsarkake wani ba sai da yunwa; waliyai ba su taɓa tafiya a kan ruwa ba, face sai da yunwa kuma ba a naɗe musu ko rage musu nisan tafiya face da yunwa kuma Allah Bai jibince su sai da yunwa.

## 2. Bayanin Amfanin Yunwa Da Illolin Koshi

Kila ka ce wannan falala mai girma ga yunwa daga ina kuma mene ne sababinta? Ka sani lalle cikin yunwa akwai amfani goma!

1. **Amfani na Farko:** Tsarkakar zuciya da kuma washewar basira kuma lalle ƙoshi yana kawo daƙiƙanci kuma yana makantar da zuciya
2. **Amfani na Biyu:** Laushin zuciya da tsarkakarta ne mutum kan yi shiri da riskar daɗin ganawa da Ubangijinsa da kuma tasirantuwa da ambaton Ubangijinsa. Abu Sulaiman ya ce: "lokacin da ibada ta fi yi mini daɗi idan cikina ya tamuƙe da bayana. Ya kuma ce: Zuciya idan ta ji yunwa da ƙishirwa, to, sai ta tsarkaka, ta yi taushi amma da zarar ta ƙoshi sai ta makance ta rushe ko ta halaka."
3. **Amfani na Uku:** Karya da ƙasƙanci da gushewar taƙama ko alfahari wanda shi ne mafarin ɗagawa da gafala ga Allah Madaukakin Sarki. Rai ba ta karaya ko ƙasƙanta daga wani abu kamar yadda take ƙasƙantuwa da yunwa, gare ta ne ake samun natsuwa ga Ubangiji, ake ƙanƙan da kai, ake samun tsoronSa.
4. **Amfani na Huɗu:** Mutum ba zai manta da jarrabawar Allah da azabarSa ba kuma ba zai manta da ma'abota bala'i ba domin lalle wanda yake a ƙoshe yakan manta da masu jin yunwa kuma shi mai jin yunwa yakan tuna da bala'in lahira. Ya tuna da ƙishirwarsa da ƙishirwar halittu a filin alƙiyama sai ya tuna da yunwarsa da yunwar 'yan-wuta waɗanda idan suka ji yunwa, za a ciyar da su da wata itaciya ta cikin wuta mai suna zaƙƙum, da dari'i kuma a shayar da su da ruɓaɓɓen jini da narkakkiyar dalma. To, wannan ɗaya daga cikin dalilan da suke sauƙaƙa wa Annabawa da Waliyyai bala'i sai ya zama musu sauƙi idan suka tuna da lokacin suna cikin wani bala'i.
5. **Amfani na Biyar**: Yana daga cikin manyan amfanin yunwa wato karya Sha'awace-sha'awacen yin dukkan saɓo da rinjaye a kan rai mai yawan umarni da mummunan aiki domin mafarin yin saɓo dukkansa sha'awa ce. Sayyadatuna Aisha (Yardar Allah ta tabbata a gare ta) ta ce: "Farkon bidi'ar da ta faru bayan Manzon Allah (saw) shi ne ƙoshi."
6. **Amfani na Shida:** Yunwa takan tunkuɗe barci da dawwamar da hana ido barci domin wanda shansa ya yawaita, to, barcinsa zai yawaita saboda wannan ne wasu malamai suke cewa: "Ya ku taron ɗalibai kada ku ci da yawa. Idan kuka ci da yawa za ku sha da yawa kuma ku yi bacci da yawa, ku yi asara da yawa." Mutane daga cikin masu gaskiya saba'in sun haɗu bisa cewa, lalle ne yawan barci na daga yawan sha.

7. **Amfani na Bakwai:** Sauƙaƙa dagewa a kan ibada domin ci yana hana yawaita yin ibada. Haƙiƙa, Abu Sulaiman Addarani yayi nuni zuwa ga illoli shida daga cikin ƙoshi sai ya ce: "Duk wanda ya ƙoshi tam, to, illoli shida za su shige shi."

    i- Haƙiƙa, zai rasa zaƙin ibada.

    ii- Kasa tsare hikima.

    ii- A haramta masa tausayi a kan halittu domin shi, mutum, idan ya ƙoshi, zai yi zaton kowacce halitta a ƙoshe take.

    iv- Ya kuma sa shi nauyin yin ibada.

    v- Da ƙaruwar Sha'awace-sha'awace.

    vi- A yayin da sauran mumunai suke kai komo tsakanin masallatai su kuwa kosassu na kai komo a tsakanin ban-ɗakuna.

8. **Amfani na Takwas**: Karancin cin abinci shi ke kawo lafiyar jiki kuma haka ne wani likita daga cikin likitocin Ahlil Kitab ya anbaci faɗar Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi inda ya ce; "Mutum ya kasa cikinsa kashi uku; ɗaya domin ci, ɗaya domin sha, ɗaya domin numfashi." Sai ya yi mamakin wannan Magana har ma ya ce: "Ban taɓa jin wata magana game da ƙaranta cin abinci mafi hikima irin wannan. Lalle wannan magana ce mai hikima."

9. **Amfani na Tara:** Sauƙin nauyin lalura domin duk wanda ya saba da ƙaranta ci, to, dukiya kaɗan za ta ishe shi gwargwadon samunsa, wanda ko ya saba da ƙoshi, zai zamo cikinsa ya zamo kullum yana aza masa nauyi. Kullum cikinsa zai riƙa ce masa "me za ka ci yau?" To, sai ya buƙaci shiga nan, shiga can saboda neman abin da zai ci.

A dunƙule dai dalilin halakar mutane, kwaɗayinsu a kan duniya. Kuma dalilin kwaɗayinsu a kan duniya; kwaɗayinsu a kan ciki. Daga cikin ƙaranta abinci, abin da zai tunkuɗe waɗannan kofofi su ne ƙofofin wuta daga lokacin da ya tunkuɗe ƙofofin sai a buɗe masa ƙofofin aljanna. Kamar yadda Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

أديموا قرع باب الجنة بالجوع فمن قنع برغيف في كل يوم قنع في سائر الشهوات) أيضا:

***"Ku dawwama ƙwanƙwasa ƙofar Aljanna da yunwa." Duk wanda ya gamsu da gurasa ɗaya kowacce rana, to, zai gamsu da sauran sha'awace-sha'awace."***

Kuma ya ce:

(وصار حرا واستغنى عن الناس واستراح من التعب وتخلا لعبادة الله ودخل في الرجال الذين

لا تلهيهم تجارة ولا بيع عن ذكر الله).

***"Ya kasance ɗaya ya wadatu daga abin hannun mutane. Kuma ya keɓanta daga bautar Allah kuma ya shiga cikin mazajen nan waɗanda wani kasuwanci ko ciniki ba ya shagaltar da su daga ambaton Allah."***

10. **Amfani na Goma:** Za ta sa ya sadaukar da kai da yin sadaka na daga abin da ya rage daga abincinsa a kan marayu da miskinai sai ya kasance a ranar alƙiyama a cikin inuwar sadakarsa. Kamar yadda ya zo da shi a wani labari. Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya yi duba zuwa ga wani mutum mai ƙaton ciki sai Manzon Allah (saw) ya yi nuni da cikin wannan mutum da ɗan yatsansa Ya ce:

(لو كان هذا في غير هذا لكان خيرا لك)،

***"Da a ce wannan cikin naka ya kasance a ba haka ba da ya fi alheri gare ka."***

Wato da ka fifitar da shi don lahirarka da kuma sadaukar da shi ga waninka da ya fi maka.

An karɓo daga Alhasan ya ce: "Wallahi na rantse da Allah, mun riski wasu mutane; ɗayansu ya kasance yana tare da abincin da zai ishe shi da ya so zai cinye shi gaba ɗaya sai ya ce wallahi, ba zai sanya shi duka a cikinsa ba har sai ya sanya wani daga cikinsa domin Allah."

Waɗannan su ne fa'idojin yunwa guda goma. Fa'ida ɗaya tana yin rassan da babu iyaka. Yunwa taska ce mai girma ga fa'idojin lahira Saboda haka ne wani daga cikin magabata yake cewa; "Yunwa, mabuɗai ne na lahira kuma ƙofofin gudun duniya, Koshi kuwa mabuɗai ne na duniya kuma ƙofofin kwaɗayi."

## 3. Bayani A Kan Hanyar Da Mutum Zai Saba Da Karya Sha'awar Ciki

Ka sani shi, Ɗalibi, yana da matakai guda huɗu game da cikinsa da abin da zai ci:

1- **Martaba ta Farko:** Kada ya ci komai face halal domin ibada tare da cin haram kamar gini ne a kan kumfar ruwa, Matakai uku da suka rage sun keɓanta ne musamman ga cin abinci wato ƙimanta gwargwadon yawan abincin da mutum zai ci a cikin lokaci a hankali da kuma bayanin shawar abin da ko kuma barin sa (abinci).

2- **Amma martaba ta Biyu**: A kan ƙaranta abinci da hanyar neman daki-daki daga duk wanda ya saɓa wa cin abinci da yawa da baya koma cin kaɗan-kaɗan, to zai sami wuyar yin haka don haka wahala ya kamata ya bi mataki-mataki kaɗan-kaɗan kamar ya rage daga abincinsa da ya saba ci kodayaushe. Misali, in ya kasance yana cin gurasa biyu ne sai ya so ya canja zuwa gurasa ɗaya, to, sai ya rage yankin biyu bisa uku har ya dawo zuwa ga gurasa ɗaya a cikin wata ɗaya. To, wannan ba zai cutar da shi ba kuma tasirinsa ba zai bayyana ba. In ya so sai ya yi haka ta hanyar awo. In kuma ya so sai ya rage loma ta hanyar lura sai ya bar loma. Kowacce rana gwargwadon abin da ya ci jiya.

Tabin wannan hanya akwai matakai huɗu. Mafi nisansa ya mayar da ransa zuwa gwargwadon yadda cikinsa zai iya riƙe shi wanda ba zai rage waninsa ba. Wannan shi ne zaɓin Sahal domin ya ce; "Allah Ya bautar da bayinSa da abubuwa uku wato rayuwa da hankali da ƙarfi. Idan bawa ya ji tsoro a kan abubuwa biyu wato rayuwa da hankali, to, ya ci ya kuma aje koda ya kasance yana mai azumi. Amma idan ba ya jin tsoron wani abu a kansu wato rayuwar da hankalin sai dai yana tsoron kar ya rasa ƙarfinsa, to, sai ya ce ya kamata kada ya damu koda zai yi rauni ne har sai ya kai ga yin sallah a zaune.

An ruwaito cewa, yin sallarsa a zaune tare da raunin yunwa ta fi sallarsa a tsaye tare da ƙarfin ci.

**Daraja ta Biyu:** Ya mayar da ransa, ya sabar da shi a dare da yini zuwa ga rabin mudu wato gurasa ɗaya da wani ɗan abu. Wannan ya yi kama da gwargwadon ɗaya bisa ukun ciki. Wannan shi ne mafi yawan mutane ke aikatawa ne kamar yadda Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ambata cewa: "Haƙiƙa, ya kasance al'adar Sayyadina Umar (Yardar Allah ta tabbata a gare shi) yana cin loma bakwai ko loma tara a rana."

**Daraja ta Uku:** Ya mayar da kansa zuwa gwargwadon mudu ɗaya shi ne gurasa ɗaya da rabi kuma wannan ya ƙaru a bisa kaso ɗaya bisa ukun ciki, cikin haƙƙin mafi yawan jama'a, ya kusa ya zama zuwa biyu bisa ukun ciki. To, ya zama sauran ɗaya bisa ukun don sha. To, babu sauran abin da zai rage don ambaton Allah. A wani ƙauli an ce; ɗaya bisa uku don ambaton Allah maimakon don nunfashi.

**Daraja ta Huɗu:** Ya yi ƙari zuwa ga mudu, wannan kuwa ya yi kama da ya zama ɓarna wato almubazzaranci saɓanin faɗarSa, Ubangiji Maɗaukakin Sarki:

﴿وَلَا تُسْرِفُوٓاْ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلْمُسْرِفِينَ﴾ الأنعام: ١٤١

***"Kada ku yi almubazzaranci lalle Ubangiji ba Ya son masu almubazzaranci."***
**Alƙur'ani 6:141**

A nan ina nufin ga wasu mutane, gwargwadon abin da mutum yake buƙata na abinci, yana saɓawa da yanayin mutum da shekaru da aikin da mutum ke shagaltuwa da shi.

To, ga kuma wata hanya ta biyar, wato wadda ba ta kimantuwa, sai dai shi, wuri ne mai sarƙaƙiya shi ne ya ci idan ya gasganta yunwarsa. Sai dai duk da haka ya kame hannunsa alhalin yana mai sha'awar abincin. Sai dai mafi rinjaye ka da ya ci gurasa ɗaya ko biyu ba. To, idan kuwa ya ci wannan jin yunwarsa ta gaskiya bai tabbatar da ita. Wato ya yi kama da sha'awar ƙarya.

Haƙiƙa, an ambaci yunwa ta gaskiya da alamomi kamar haka. Ta farko: Ba zai tsaya neman miya ba sai dai kawai zai ci waina gayanta kawai. Duk wanda ya nemi waina da mahaɗinta wato miya, to, wannan ba mai jin yunwa ba ne. Wasu suka ce ko dai ya rikice kuma ƙuda ba zai faɗo cikin abincinsa ba. Wannan yana mai nuni zuwa ga zaman cikinsa babu komai. Sanin haka, wannan ba a fili yake ba. Ba a iya gane shi.

Abin da ya dace da ɗalibi, ya kimanta wa ransa gwargwadon yadda ba zai raunata shi da ibada ba wanda da ita ce babbar manufa da yake a kanta. Idan ya kai ƙarshen wannan gwargwadon sai ya tsaya koda sha'awarsa ta yi saura. A dunƙule, kimanta abinci ba mai yiwuwa ba ne saboda yana saɓa wa yanayin halayyar mutane.

Na'am, haƙiƙa, ya kasance wasu jama'a daga cikin sahabbai abincinsu sa'i ɗaya ne kowacce Jumma'a Mudu huɗu kuwa shi ne sa'i ɗaya. Sai ya kasance kowacce rana kusan rabin mudu (shi ne abin da muka ambata) cewa gwargwadon ɗaya bisa uku na kason ciki.

Haka kuma Abu Zarri (Yardar Allah ta tabbata a gare shi) ya kasance yana cewa, “abincina kowacce Jumma'a sa'i ɗaya ne na sha'ir a zamanin Manzon Allah (saw). Ya ce “Na rantse ba na ƙara komai har sai na haɗu da Allah. Lalle ni na ji shi yana cewa:

(أقربكم مني مجلسا وأحبكم إلي من مات على ما هو عليه اليوم).

***“Mafi kusancinku a wurin zamaNa, mafi soyuwarku a wuriNa wanda ya mutu a kan abin da yake a kai a yau bai canza ba.”***

Ya kasance yana cewa a inda yake inkarinsa a bisa wasu sahabbai” haƙiƙa kun canza kun musanya matsayinku an ba ku nau'o'in abinci kala-kala alhalin ba ku kasance haka ba a zamanin Manzon Allah (saw).

**Ahlil Siffa:** Abincinsu ya kasance mudu ɗaya na dabino a tsakanin mutum biyu kowacce rana, Alhassan ya kasance yana cewa: “Mumini tafi ɗaya na abinci yana isar sa da kuma danƙa ɗaya na gari yana isar sa da kuma kurɓa ɗaya na ruwa. Shi ko munafiki yana ci yana sha ya ƙoshi. Ba ya barin cikinsa da yunwa ba ya ba maƙwabcinsa, ba ya fifita ɗan'uwansa saura na abincin. Sahal ya ce; “Da a ce duniya ta kasance babu wani abincin mumini a cikinta domin cin da mumini yake yi sai a lalura. Yana ci ne abin da zai riƙe shi ne kawai.

**Martaba ta Uku:** A lokacin cin abinci da gwargwadon jin kirtawarsa a kan haka akwai kuma wasu darajoji. **Daraja maɗaukakiya**; Mutum ya ji yunwar kwana uku ko fiye da haka. Su koma ɗalibai waɗanda suka ɗaukarwa kansu ba iyakancewa har wasunsu za su kai zuwa ga kwana talatin ko arba'in. Haka kuma akwai wasu daga cikin malamai masu yawa. Daga cikinsu akwai: Sahal ɗan Abdullah da AbdurRahaman ɗan Ibrahim da Ibrahimut-taimy da Sulaimanul Khawas, Haƙiƙa, Sayyadina Abubakar Saddiƙ (Allah Ya yarda da shi) ya kasance yakan ji yunwa a farko al'amarinsa yakan kwashe kwana shida bai ci abinci ba.

Haka kuma Abdullahi ɗan Zubair shi ma ya kasance yakan kwashe kwana bakwai bai ci abinci ba haka ma Abu Jauza'a, abokin ɗan Abbas, shi ma yakan kwashe kwana bakwai bai ci komai ba. Dukkan waɗannan, manufarsu ta barin kai da yunwa suna yi ne a bisa hanyar neman lahira.

Haka sashin wasu malamai suka ce duk wanda ya hana kansa abinci har na tsawon kwana arba'in, to, iko na mulkin Allah zai bayyana a gare shi ana kuranye masa sirrori na Ubangiji. Haƙiƙa wani daga cikin wannan ƙungiya ya tsaya a kan wani mai bautar Yahudawa ko Nasara sai ya ambata masa halinsa. Ya yi kwaɗayin ya Musulunta, ya bar abin da yake a kai na ruɗi

Sai ya yi mishi magana a kan maganganu masu yawa har ya zo inda mai bautar nan yake cewa; “Lalle Annabi Isa (as) ya kasance yana hana cikinsa abinci har tsawon kwana arba'in. Wannan kuwa mu'ujiza ce ba ta kuma zamowa ga kowa face ga Annabi.”

Sai Sufi ya ce da shi idan na hana cikina abinci na tsawon kwana hamsin; za ka bar abin da kake a kai kuma ka shiga addinin Musulunci kuma ka sani lalle shi, gaskiya ne kuma kai kana kan ɓata, sai mai bautar nan ya ce 'e' sai ya zauna ba ya zuwa ko'ina sai inda yake ganinsa har ya kai tsawon kwana hamsin sai ya ce: Ko’in ƙara kwanaki har ya kai kwana Sittin, sai mai bautar nan, ya yi mamaki har sufin nan ya ce ban taɓa zaton za a sami wani mutun da zai wuce Annabi Isa (as) wurin hana cikinsa abinci ba. To, wannan ya kasance dalilin musuluntarsa. Wannan daraja ce mai girma kuma kaɗan ne waɗanda suke kaiwa gare ta.

**Daraja ta Biyu:** Ya ji yunwar kwana biyu zuwa uku. Wannan bai fita daga cikin al'adar da ya saba ba sai dai yana kusa. Wannan yana yiwuwa wannan darajar ta kai gare ta ta wajen ƙoƙartawa da dagewa.

**Daraja ta Uku:** Ita ce mafi ƙaranci shi ne ya taƙaita a kan ci ɗaya a cikin dare da yini. Wannan shi ne mafi ƙaranci. Abin da ya wuce haka ya zama ɓarna da zama ƙosasshe. Wannan hali ne na waɗanda ba su jin yunwa. Wanda kuwa ya nisanta daga sunnah. Kuma magabata sun kasance suna ci sau ɗaya a rana. Kuma Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce ga Aisha (Yardar Allah ta tabbata a gare ta):

(إياك والإسراف فإن أكلتين في يوم واحد من السرف).

***“Kashedin ki da ɓarna domin ci sau biyu a rana yana daga almubazzaranci.”***

Duk wanda ya taƙaita a kan ci sau ɗaya a rana an so a gare shi ya ci a lokacin jijjifi. Kuma an so ya ci abincin bayan ya yi sallar dare zai sami yunwar rana don azumi, yunwar dare don tsayuwar dare da natsuwar zuciya zuwa ga sanannen lokacinsa.

Kada idan zuciyar mai Azumi ta kasance tana karkata ga neman abinci bayan Magariba zai shagaltar da zuciyarsa zuwa ga sallolin dare, to, abin da ya fi gare shi ya kasa abincin gida biyu misali in ya kasance gurasa biyu ce, sai ya ci gurasa ɗaya lokacin buɗa baki, ɗaya lokacin sahur don zuciyarsa ta natsu kuma jikin ba zai yi sakwa-sakwa ba. Haka yunwarsa ba za ta yi “tsanani ba domin yin sahur ɗin nan da ya yi, sai ya nemi taimako da gurasa ɗaya a kan tsayuwar dare ta biyun kuma don azumi.

Wanda ya kasance yana azumi yau, gobe ya ajiye, to, babu laifi ya ci abinci da Azzahar. Kuma ranar da yake yin Azumi, ya ci lokacin sahur. To, wannan ita ce hanyar iyakance lokutan cin abinci, kusa da na nesa.

**Daraja ta Huɗu:** hanyar da mutum zai bi ta lahira ga cin abinci ƙin amfani da miya kodayaushe, da kuma barin sha'awace-sha'awacen duk abin da yake da daɗi wanda mutum yake sha'awa. Dalili kuwa shi ne dukan cin abin da mutum ke sha'awa ga rayuwarsa, to, zai tsirar da girman kai ko taƙama a ransa da ƙeƙashewar zuciya kuma zai haifar da ɗabi'ar son jin daɗin duniya har ya saba da shi. Ya ƙyamaci mutuwa da haɗuwarsa da Ubangiji. Duniya ta zama masa Aljanna, mutuwa kuwa ta zama masa kurkuku.

Idan ya hana zuciyarsa sha'awace-sha'awace; ya ƙuntata mata, ya haramta mata jin daɗinta, to, sai duniya ta zame masa kurkuku sai mutuwa ta zama masa 'yancin kai. Da wannan bayani ne Yahya ɗan Mu'azu ya yi nuni inda yake cewa: "Ya ku taron masu gaskiya, ku ji da kanku yunwa don samun cin walimar aljannar Firdausi domin sha'awar cin abinci tana ga gwargwadon yunwar mutum ce." Kuma Manzon Allah (saw) ya ce:

(أشرار أمتي الذين غذوا بالنعيم ونبتت عليه أجسامهم وإنما همتهم ألوان الطعام وأنواع اللباس يتشدقون في الكلام).

***"Mafi sharrin al'ummata su ne waɗanda aka ciyar da su daga ni'imomi har ni'imomin suka tsiro a jikinsu kuma lalle su abin da ya dame su shi ne iri-irin abinci da tufafi kala-kala suna ƙaƙale a magana."***

Haƙiƙa, tsoron magabata ya tsananta a kan cin abinci mai daɗi. Suna ganin wannan yana daga cikin alamar 'yan-wuta har ma an ruwaito cewa, Wahab ɗan Munbah ya ce: "Wasu mala'iku su biyu sun haɗu a cikin sama na huɗu sai ɗaya ya ce da ɗan'uwansa 'daga ina kake? Sai ya ce; "An umarce ni da in kora wani kifi cikin kogi da wani Bayahude ya yi sha'awar sa. Allah Ya la'ane shi." Sai ɗaya mala'ikan ya ce: "Ni kuma an umarce ni da in ƙona wani mai da wani bawa mai bauta ya yi sha'awar sa." Da wannan ne Sayyadina Umar ya hana kansa shan ruwa mai sanyi da zuma. Mai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إذا سددت كلب الجوع برغيف أو كوز من الماء القراح وعلى الدنيا وأهلها الدمار).

***"Idan mutum ya toshe yunwar cikinsa da gurasa ɗaya da kofi ɗaya na ruwa mai sanyi ko daɗi, to, duniya da mutanen ka bar su da sauran."***

Yana yin nuni da wannan magana da nufin cewa, ya mayar da zafin yunwa da kuma tunkuɗewar cuta ba tare da jin daɗin duniya ba.

Kuma an karɓo daga Musa Alasji; yana cewa; "Raina ya taɓa sha'awar cin gishiri a abinci tsawon shekara ashirin amma ban ci ba." Kuma Ahmad ɗan Khalifa ya ce: "Raina tsawon Shekara ashirin, ba a bin da yake nema a wurina face in shayar da ita ruwa ta sha ta ƙoshi amma har yanzu na ƙi shayar da ita. An ruwaito cewa wani mai bauta cikin masu ibada ya kira wani daga cikin 'yan'uwansa sai ya kawo masa gurasa sai ɗan'uwansa ya tura masa wannan gurasa domin ya zaɓa wadda ta fi kyawu, sai mai bautar ya ce da shi; me kake aikatawa? Shin ba ka san lalle ne a cikin wannan gurasar da ka yi sha'awar cin ta akwai hikima kaza-da-kaza kuma an cakuɗa kaza da kaza a cikinta bad a kuma wanda ya haɗa wannan gurasar?

Kuma ya zo a cikin labari cewa, ba ta taɓa yin wata gurasa curarra ba da ta kewaya ta gaban ka har domin ka ci face mutane ɗari uku da sittin sun yi aiki a cikin ta. Na farkonsu shi ne Mika'ilu, na ƙarshensu shi ne mai yin gurasa.

﴿ وَإِن تَعُدُّوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ ﴾النحل: ١٨

***"Da za ku ƙirga ni'imomin Allah, ba, za ku iya ƙirga su ba."*** **Alƙur'ani 16:18**

Duk wanda bai iya barin abin da yake sha'awa, to, ya kamata kada ya gafalar da ransa da nutsar da ita a wurin sha'awace-sha'awace. Ya isa ya zama ɓarna ga mutum ya ci dukkan abin da yake sha'awar sa. An so kuma kada mutum ya yi barci a lokacin da ya ƙoshi sai ya haɗa tsakanin gafaloli biyu sai ya saba da mutuwar jiki; zuciyarsa ta rinƙa gaggawa zuwa ga haka sai dai don ya yi sallah ko ya zauna don ambaton Allah Maɗaukakin Sarki. Wannan shi ne godiya mafi kusanci. Kuma a cikin wani hadisi ya zo cewa ya ce:

(أذيبوا طعامكم بالصلاة والذكر ولا تناموا عليه فتقسو قلوبكم).

***"Ku narkar da abincinku da yin sallah da ambaton Allah, kada ku yi barci a kansa sai zukatanku su ƙeƙashe."***

Kuma mafi ƙarancin haka ku yi sallah raka'o'i huɗu; ku yi tasbihi ɗari. Kuma Sufyan Assauri ya kasance idan ya ƙoshi, to, zai raya daren nan.

## 4. Bayanin Saɓanin Hukuncin Yunwa da Darajarta da Saɓanin Halayyar Mutane

Ka sani lalle abin da ake nema mafi nesa shi ne tsaka-tsaki ta yadda mafi alkhairin al'amura shi ne mutum ya tsaya a tsaka-tsaki. Kuma abin da muka yi raddi a kansa cikin falalar yunwa, haƙiƙa, yana nuni zuwa ga wuce iyaka cikin abin nema ga malami, ya riski abin da ake nufi wato tsaka-tsaki

Ka sani lalle abin da ya fi mutum ya ci ta yadda ba zai cika cikinsa ya yi nauyi ba, kuma mutum ba zai ji raɗaɗin yunwa ba domin abin da ake nufi mutum ya ci gaba da wanzar da rayuwarsa. Nauyin abinci a ciki yana hana ibada kuma raɗaɗin yunwa yana shagaltar da zuciya daga gare ta. Abin da ake nufi ya ci cin da ba ba zai bar wani tasiri ga wanda ya ci abincin ba don mutum ya yi koyi da Mala'iku domin su an tsarkake su daga nauyin abinci da raɗaɗin yunwa.

Kuma manufa ta mutum, koyi da su, amma a farkon al'amari idan rai ya kasance mai tsananin sha'awa ce kuma mai karkata ce zuwa ga wuce gona da iri, to, daidaitawa ba za ta amfane shi ba sai dai ba makawa ya zama dole ya kai matuƙar ya saɓa masa raɗaɗin yunwa kamar yadda zai horar da dabba da raɗaɗin yunwa da duka a farkon al'amari zuwa har ta daidaita. To, idan ta yarda ta daidaita sai mutum ya dawo zuwa ga daidaitawar, ya bar azabtar da ita da horar da ita.

Ya kasance a al'adar Ibrahim Kawas, ga horar da ɗalibi a yi. Ya na umurtar sa. Domin kada ya saƙa a cikin zuciyarsa cewa Shehin yana umartar sa da abin da ba ya da amfani gareshi, sai dai yana ingiza shi (Ɗalibi) da yin aikin da shi shaihin bai iya aikatawa, kashe masa jiki da wancan cikin aikin da ya sabar da shi.

Mai ƙarfin imani idan ya shagaltu da riyada da gyara wani, to, zai zo wannan aikin ya lazimtar da shi zuwa ga matsayi ko mataki na masu rauni domin yana me kamancecceni da su da kuma tausasa su da yake yi a wurin kora su da yake yi zuwa ga arzikin wato lahira. Wannan bala'i ga annabawa da waliyyai.

## 5. Bayanin Illar Riya Wadda Take Kwanƙwasawa Zuwa Ga Wanda Ya Bar Cin Sha'awace-Sha'awace ko ya Karanta cin Abinci

Ka sani lalle illoli biyu masu girma suna shiga ga mai barin sha'awace-sha'awace.

**Na Farkonta:** Wadda tafi girma; Ita ce mutum ya kasance yana ƙin abubuwan sha'awace-sha'awace. Sai dai ya ɓoye ba ya son a san cewa shi yana sha'awar abubuwan. To, sai kuma ya ci a keɓance, abin da ba zai ci cikin jama'a ba. To, wannan ita ce shirka ɓoyayya.

Haƙiƙa, wasu sashinsu sun kasance suna sayen kayayyakin sha'awa su rataya su cikin gidajen su alhali su suna daga masu gudun duniya. Sai dai bai kamata maganar Shaiɗan ta ruɗar da shi ba cewa, lalle idan ka nuna wa mutane sai wasu su yi koyi da kai ga. To, ka yi ɓoyo don Allah ba wai ga waninka ba.

**Illa ta Biyu;** Ya sami ikon barin sha'awace-sha'awace sai dai yana farin ciki a san cewa ya shahara da kamewa daga sha'awace-sha'awace. Haƙiƙa, wannan ya saɓa wa barin sha'awa mai rauni wato ita ce sha'awar abinci. Amma kuma ya yi ɗa'a ga sha'awa mafi sharri daga waccan wato sha'awar zuwa ga neman ɗaukaka. To, ita ce sha'awa ɓoyayya. Ko ta yaya mutum ya ji wannan irin sha'awa a cikin ransa, ya karya ta saboda wannan sha'awar mafi muhimmanci daga karya sha'awar cin abinci. Wannan kuwa ita ce hanya wurin ladabtar da rai a kan sha'awace-sha'awace ɓoyayyu.

A dunƙule, duk wanda ya bar sha'awar cin abinci ya faɗa cikin sha'awar riya, ya kasance kamar wanda ya guje wa kunama ya faɗa ga macijiya, saboda sha'awar riya ta fi cutarwa fiye daga sha'awar abinci.

Littafin ***Kora Masu Gaskiya.*** Ya Kare. Ina gode wa Allah game da kyakkyawan taimakonSa kuma ina yi wa Allah godiya wanda Ya yi ni'ima a kanmu da ni'imar imani da Musulunci kuma Ya shiryar da mu da shugabanmu, Muhamamdu daga Allah Maɗaukakin Sarki da mafificin salati da mafi tsarkakan aminci ya cika.

Ya Allah Ka yi mana gafara da dukkan Musulmai, maza da Musulmai mata da muminai maza da muminai mata rayayyu, daga cikinsu da matattunsu, amin.

# دالية ابن فودي

# DALIYAH TA YABON MANZON ALLAH

Na

**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

**<u>Mai Fassara</u>**

**Imam Musa Tanimu**

**<u>Edita</u>**

**Ahmed Abdullahi (A.A. Sokoto)**

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi (saw) Annabi mai karamci da alayensa da sahabbansa

### Waƙe

1. Shin ko zan sami damar tafiyar gaggawa zuwa Madina
Domin in ziyarci kabarinsa Hashimiyyu Muhammadu
2. A lokacin da kansa ya mamaye sansaninta
Kuma alhazai suka dumfari Muhammadu
3. Na yi kuka har na zubar da hawaye
Saboda begen wannan Annabi Muhammadu
4. Na rantse da Allah Sarkin tausayi
Ba wata gaɓa a jikina face akwai ƙauna ga Muhammadu
5. Ni na yi kama da wanda musibar bege ta kama shi
Sam ban jin daɗin rayuwa in ban tare da Muhammadu
6. Na kusa saboda tsananin bege in tashi fir zuwa ga kabarinsa
Lalle ba zan ji daɗi ba, sai na ziyarci Ahmadu
7. Shi ne; Rana mai haske, hular girma, tekun kyauta
Lalle babu alheri sai an bi Muhammadu
8. Shi ne ruwa mamako wanda ni'imarsa ta game halitta
Sannan dukkanin halitta suna bayan Muhammadu
9. Inda zan tafi Madina da na biya buƙatata
Domin in yi birgima a turɓayar takalmin Muhammadu
10. Kabarin Ahmadu yana can wani wuri mai tsarki
Yana samar da turaren almiski na ƙanshin Muhammadu
11. Rana ma ba kome ba ce, domin khusufi na samun ta
Amma khusufi bai samun hasken wannan Murshidi
12. Shin ko zuciyata ta zama tsuntsuwa ce ta tashi, domin ziyartar gidansa
Hawayena yana zuba, domin rashin wannan Murshidi
13. Hawaye na guduna in na tuna da bigirensa
Haƙiƙa, na rame domin son Annabi Muhammadu (saw)

14. Kuma idan an ce da ni wa kake mutuwar so a cikin talikai
Zan ce lalle ni ina mutuwar son Muhammadu

15. Hallaka ta tabbata ga wanda ya ƙi bin hanyarsa
Ya tsawon baƙin ciki ranar ƙiyama ga maƙiyin Muhammadu

16. Kai ku tashi da sauri mu tafi zuwa ga hasken shiriya
Mu keta daji don mu ziyarci kabarin Annabi Muhammadu

17. Ku sha damarar tafiya zuwa ga adon ƙiyama
Mu je mu yi birgima da turɓayar Masallacin Muhammadu

18. Wutar soyayya tana kurɗawa tsakanin haƙarƙarimmu
Kaunarmu da soyayyarmu tana ga Muhammadu

19. Muna taƙama da alfahari da shi a duk duniya
Kai mun narke cikin ƙaunar Annabi Muhammadu

20. Takubbansa sun fille kawunan ma'abuta shirka
Shin wa yake musun falalar Ahmadu

21. Haskensa ya dusar da na taurari, ɗaukakarsa ta ɗara tasu
Shin wa ya kai ga ɗaukaka irin ta Muhammadu

22. Babu natsuwa a gare mu sai fa mun ziyarci kabarinsa
Don babu tausayi sai a gefen Muhammadu

23. Mun ɗaukaka ne a kan talikai da ɗaukakarsa
Mun sami shugabanci ne da shugabancin Ahmadu

24. Don begensa ne muke zubar da hawaye
Kuma hawayen yana goge laifimmu ga Muhammadu

25. Da yawa mai ɗimuwa a cikin duhu ya shiryu da shi
Dukkan mumini ya sami hasken shiriyarsa ce ga Muhammadu

26. Ɗabi'unsa ba a ba wata halitta irin su ba
Wane ne zai iya tattara karamar Ahmadu

27. Wane ne ya isa ya ƙirga ayoyinsa
Mu'ujuzar ta kai kamar rairai a wajen yawa ta Muhammadu

28. Rundunarsa daga Al-arshin Mahaliccin talikai ne
Duk duniya babu tamkar ga Muhammadu a talikai

29. Lalle an rubuta a cikin Attaura siffar Annabimmu
Kai! Har ma da Zabura akwai siffa ta Muhammadu

30. Linjilar Isa ma tana shedar siffofinsa
Kai! Kukan tumaki ma yana nuni ga Muhammadu

31. Allah Ya sanya tsakuwa ta yi tasbihi a tafinsa
Kuma ruwa ya ɓuɓɓugo daga yatsun Ahmadu

32. Kyarkeci ma ya yi shedar aikensa da gaskiya
Barewar daji ma ta amsa kira ta Muhammadu

33. Damo ma ya amsa kiransa, sannan ya gasgata saƙonsa
Kai Itatuwa ma sun gudana zuwa ga Muhammadu

34. Jariri ma ya sheda manzancinsa tsakanin talikai
Kuma ruwa ya kwarara mai yawa domin ƙauna ga Muhammadu

35. Rana ta koma saboda addu'arsa
Wata ya tsage saboda alfarmar wannan shugaba

36. Kuma girgeje ya yi masa inuwa cikin tsakar rana
Kurciya ta yi sheƙa a maɓoya ta Muhammadu

37. Kuma gizo-gizo ya yi saƙa a bakin kogonsa don kariya
Kututture ya yi kukan rashin Sidi Muhammadu

38. Wane ne ya sha kaɗan sai ya yi yawa
Kuma katangar Kisira ta karye lokacin haihuwar Muhammadu

39. Ruwan ƙoramu sun zuƙe don mu'ujizar haihuwarsa
Hakanan wutar (Majusawa) ta mace alfarma ga Muhammadu

40. Ya taho duniya da kaciyarsa, gyaran Mahalicci Allah
Kuma cibiya yanke karama ga Muhammadu

41. Ya kai mai ƙoƙarin ƙirga mu'ujizar Muhammadu
Shin za ka iya ƙirga kumfar kogi

42. Ko kuwa za ka iya ƙirga yashin duniya
Duk sun yi kaɗan a bisa mu'ujizar Muhammadu

43. Tsarki ya tabbata ga Wanda Ya ba shi babbar baiwa
Shin wane ne ya isa ya ƙirga kalimomi na yabo ga Muhammadu

44. Kada ku yi inkarin abin da na faɗa maku
Ya ku mutane Don na yi koyi ne ga wanda yake koyi da Muhammadu

45. Ni, mai ƙetare haddi ne, kuma gajiyayye ne, ni, jahili ne
Sannan ni mai zunubi ne, sannan mai tsananin bege ne ga Muhammadu

46. Kuma ni na san ba ƙwararre ne ba
Wajen yabo na fiyayyen halitta Muhammadu

47. Ni dai ƙaunarsa ce ta cika zuciyata sai na bayyana ta
Ba wargi nake yi ba, kuma ba wasa nake yi ba, wajen yabo ga Muhammadu

48. Zunubina ya yi mini dabaibayi ta ko'ina! Dabaibayi mai nauyi
Ta yaya ɗaurarre zai miƙe ya yi yabo ga Muhammadu

49. Ni tabbas mai rauni ne da zunubi, mai lulluɓe ni da shi
Ina fatar kuɓuta don alfarmar wannan Sayyidi

50. Na ɓoye laifina amma Allah Yana ganin sa
Ya Allah Masanin asirrai Ka azurta mu da wannan daɗi na Muhammadu

51. Ni na narke cikin laifi, kuma na yawaita
Ba ni da mafaka sai domin falalar Muhammadu

52. In an tambaye ka wane ne mai laifi? Ka ce ni ne
Babu kwaɗayin tsira sai don alfarmar Muhammadu

53. Ya Rasulu! Kama hannun wannan bawan mai laifi kai ne ginshiƙina
Kai ne mafakata ya manufata ya Muhammadu

54. Ya Allah Mahaliccimmu ga mu mun zo ta ƙofarKa
Ka tsare mu daga kurkukun azaba, don alfarmar Muhammadu

55. Ya Allah idan ba Ka yafe mini ba, tabbas na hallaka
Ka tsare ni daga kurkukun azaba ta wuta, don darajar Muhammdu

56. Haƙiƙa, na san Mahaliccina Allah Mai buɗe ƙofarSa ne
Don baiwarSa ga duk mai nufin bin hanyar Muhammadu

57. Ya Allah Ka cece ni daga firgicin kabari
Ya Mahaliccina! Ya Mai cetona! Ya sayyadi

58. Allah Ka sauƙaƙa mana hanyar ziyarar Annabi, ya maulaNa
Ka sauƙaƙa mana ziyartar Ahmadu

59. Ya Abubakar Siddiƙu kama hannun damata
Don Allah gobe nan kai ni ga Muhammadu

60. Ya Ummaru Faruku kai mu kusa ga Annabi
Ya wanda sunansa ya dace da halinsa, goben nan kai mu ga Muhammadu

61. Ya kai Aliyyu mijin Fatima
Kama hannuna har sai ka haɗa hannuna ga Muhammadu

62. Da taimakon Allah Mahaliccin talikai na kammala wannan ƙasidar
Wadda na sanya adadinta kamar shekarun Muhammadu

63. A shekara ta dubu ɗaya da ɗari biyu in ka gane
Ta hijirar Hadi Annabi Muhammadu

المحذورات من علامات خروج المهدي

# Gargaɗi Ga Alamomin Fitowar Mahadi (ra)

Na

Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**<u>Mai Fassara</u>**

Imam Musa Tanimu

**<u>Edita</u>**

Dr. Sa'adiya Omar.

# ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ............................................................ 183

Babi Na Ɗaya ............................................................ 183

Babi Na Biyu ............................................................ 185

Babi Na Ƙarshe ............................................................ 187

## GABATARWAR MAWALLAFI

**Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai**

**Babi Na Ɗaya**

Allah Ka yi salati zuwa ga shugabammu, Muhammadu kuma Ka tabbatar da tsira da amincinKa zuwa ga Alayensa da Sahabbansa da. Wannan littafin, **Al Mahzurat Min Alamat Kurujul Mahadi** na shugabanmu, Usmanu ɗan Fodiyo ne. Allah Ya lullube shi da rahamarSa Amin. Haƙiƙa, Ahmad Zaruk ya faɗa cikin sharhin **Umadatul Marid Assadiƙ** yayin da ɗan Mahadi ya ce: "Ni zan ba ka labari na sharuɗɗa goma na fitowar Mahadi."

**Na Farko:** Yana daga cikin sharuɗɗan ɗaukewar malamai da sanya masu kwaɗayi, suna sanya rahamar Allah a ƙarƙashin dugadugansu, suna fifita son duniya.

**Na Biyu:** Alƙalai ba sa yin hukunci da abin da Allah Ya saukar.

**Na Uku:** Sanya yara shugabannin al'umma.

**Na Huɗu:** Mawadata ba sa tausayin talakawa.

**Na Biyar:** Zai kasance ashararai su ne shugabanni.

**Na Shida:** Talakawa ba sa yin haƙuri a bisa abin da Allah Ya hukunta musu.

**Na Bakwai:** Maƙwabci ba ya tausayin maƙwabcinsa.

**Na Takwas:** Ana tozartar da gaskiya, ana ayyanar da ƙarya. Za a sanya hassada a tsakanin al'umma, har sai sun kusa kai ga kashe kawunansu.

**Na Tara:** Za su kuma riƙa cin naman junansu babu dalili.

**Na Goma:** Rashin kunya daga ɓangarorin maza da mata.

Ka sani ya kai ɗan'uwa Musulmi lallai wannan al'umma muna neman tsari daga gare su. Su kuma suna barin abin da rayukansu ya kamata su damu da shi. Kullum suna bin musibun da ke tsakaninsu, har sai sun hallaka su. Kaɗan daga cikinsu ne ke tsira daga barin haka.

Domin su haƙiƙa sun canza hukunce-hukuncen Allah da ayoyinSa. Duk wanda kuwa ya canza ilimi, me zai hana azabar Allah ba za ta saukar

masa ba? Jin daɗi ba ya samuwa ga mutanen da suka dage a kan aikata miyagun ayyuka.

Ka sani ya kai ɗan'uwana cewa mabuɗan sanin gaibu biyar ne ba kuma wanda ya san su sai Allah.

**Na Farko:** Ilimin sanin labarin duniya da abin da ke cikinta.

**Na Biyu:** Sanin abin da Allah Zai aikata gobe

**Na Uku:** Sanin ƙasar da kowane rai zai mutu a cikinta.

**Na Huɗu:** Sanin ranar tashin alƙiyama. Saboda faɗar Allah Maɗaukaki.

﴿إِلَيْهِ يُرَدُّ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ﴾ فصلت: ٤٧

*"A gare Shi ilimin ranar tashin alƙiyama yake."* Alƙur'ani 41:47

Babu wanda ya san ta in ba shi ba, sai dai za mu sanar da kai sashen sharuɗɗanta. Mace ta haifi ɗan da zai dame ta.

Bawa ya zama kamar ɗa mai 'yanci, ba za a ga wani aikin alheri a cikinsu ba. Fasiƙi ya kasance shi ne mai matsayi cikin jama'a, matan banza za su yawaita. Sulaimanu Tazuli yana ce wa Abdulƙahir, idan ka ga malamai sun jefar da matsayinsu; shugabanni sun kasance jahilai; Alƙalai sun zama azzalumai, ba sa hani ga mummunan aiki ba sa hukunci da abin da Allah Ya saukar, kuma ba sa yin aiki da hukuncin Allah, to, waɗannan bala'o'i za su sauka gare su da masiba da ƙasƙanci, saboda kauce wa hanyar Allah.

Ka sani lalle Safiyanus Sauri (Allah Maɗaukaki Ya yi masa rahama) ya ce: Al'amarin Mahdi zai bayyana a kan ginshiƙan addini guda goma sha ɗaya masu jaddada addini, domin masu jaddada addini su goma sha biyu ne bayan Annabi (saw) na hijira 1568A.H ko kuma 1369A.H sai dai zan sanar da kai alamomin sharuɗɗanta:

BABI NA BIYU

**Na Farko:** Rashin taimako tsakanin Musulmi

**Na Biyu:** Rashin kunya a tsakaninsu a bayyane.

**Na uku:** Ba za ka gane malamai ba, face da sababbin tufafi.

**Na Huɗu:** Matan banza suna alfahari a tsakaninsu, cikin lamarin duniya.

**Na Biyar:** Masu fatara da miskinai suna cikin wahala a kan rashin taimako daga attajirai Musulmi.

**Na Shida:** Mawadata suna alfahari da fasiƙanci.

**Na Bakwai:** Alƙalai ba sa yin hukunci sai da kuɗi.

﴿ يَنقُضُونَ عَهْدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعْدِ مِيثَـٰقِهِۦ وَيَقْطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ ۚ أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَـٰسِرُونَ ﴾ البقرة: ٢٧

*"Kuma suna warware alƙawarin Allah bayan ƙulla shi, suna yanke abin da Allah Ya yi Umurni da sadar da shi, kuma suna yin ɓarna a cikin ƙasa. Waɗannan su ne masu hasara."* Alƙur'ani 2:27

Idan Allah Ya yi nufin halaka wata alƙarya da tsananin azaba sai Ya umurci shugabanninsu da fasiƙanci da ɓarna kuma talakawa su shiga cikin fasiƙanci da zina da cin dukiyar marayu a bisa zalunci. To, da haka ne sai Allah Ya saukar da masiba da azaba a kansu. Bayan wani lokaci sai Allah Ya aiko da ni'ima a kansu, har su shagaltu sannan sai Ya kama su da musiba wadda ba za ta yanke a kansu ba, har sai Allah Ya hallaka su da ita, ko kuma su tuba. Sai Allah Ya bayyanar da wani mai jaddada adddinin Musulunci a cikinsu, kowane mai jaddada Musulunci yana da masu taimakon sa.

Ka sani ya kai ɗan'uwana ɗan zamani wanda ya kasance cikin zamanin Dujjal, Allah Ya la'ance su, su ne waɗanda suke yin hukunci ba da abin da Allah Ya saukar ba. To, waɗannan su ne kafirai, ba sa yin jihadi don ɗaukaka kalimar Allah, ba sa ciyarwa don Allah, babu kunya a cikin idanu mazajensu da matansu.

Suna cin dukiyar mutane da ɓarna, kuma suna karkatar da mutane daga hanyar Allah, suna barin hanyar gaskiya, suna bin hanyar ƙarya. Mata su zama, kamar maza. Haka kuma maza su zama kamar mata. Za su riƙa ɓata

aurensu ta hanyar maganganunsu, suna halatta zina, kuma suna yin ta da idanunsu, sai ya kasance mai bautar Allah kamar kare a cikinsu.

Maɓarnaci ya zama shi ne mutumin kirki; shugabanni su ne ashararai; shugabanninsu su ne masu bincike, kuma su ne alƙalai. Malaman wannan zamanin ba su da haƙurin kwaɗayi a kan abin duniya; mawadata ba sa amfanar da talakawa, su kuma talakawa ba sa yin haƙuri da abin da Allah Ya ƙaddara musu.

Duk wanda ya riski wannan zamani sai ya yaƙi kansa don kada ya shagaltu da abin da ya gani a wurin mutane, saboda mutanen wannan zamani sun karkata zuwa ga duniya ne, ba su shagaltu da al'amarin addininsu ba, kai ka ce ba za su mutu ba. Sun manta da abin da Allah Ya faɗa musu a cikin Alƙur'ani Mai girma:

﴿كُلُّ شَيۡءٍ هَالِكٌ إِلَّا وَجۡهَهُۥۚ﴾ القصص: ٨٨

***"Kowane abu zai halaka in ban da zatin Allah."*** **Alƙur'ani 28:88**

To, lallai fasiƙanci da annamimanci da girman kai da aikata riya da ji da jiyarwa da hassada da ƙeta da ganin fifiko a kan wani su ne mabuɗan samun fushin Allah a kan bayinSa. Waɗannan za su yi jagorancin su zuwa ga azabar Allah, har su hallaka ta dalilin abin da hannayansu suka aikata. To, lallai su, azabar Allah za ta zo musu babu kokwanto, muna neman tsarin Allah daga samun fushinSa da uƙubarSa, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿مَا يَنظُرُونَ إِلَّا صَيۡحَةً وَٰحِدَةً تَأۡخُذُهُمۡ﴾ يس: ٤٩

***"Ba za su ga komai ba sai wata tsawa guda da za ta ɗauke su."***
**Alƙur'ani 36:49**

Abdul'Aziz ya ce: A cikin wani littafi, **Mafatihu Ulumus Sa'a** idan ka ga an yanke zumunta kuma an kawar da kunya a idanun mutane, kuma ka ga wanda ba ya ɓarna a cikinsu shi ne ƙasƙantacce ko mahaukaci ko wulaƙantacce, to, a wannan zamani Allah Zai aiko da yunwa a gare su. Kuma bayan fari, za a saukar da ni'ima a gare su shekara tara ba sa jin ko labarin yunwa, sai a cire wahala saboda ni'imar da aka saukar a gare su sai su shiga aikata saɓo a cikin ƙasa, su riƙa barin hanyar gaskiya domin za su karkata zuwa ga mata da dukiya da sha'awace-sha'awace da son duk abin da zai janyo su zuwa ga fushin Allah.

## BABI NA KARSHE

Sannan sai Allah Ya saukar da bawanSa a garesu da rundunoni su tsaya a Gabas da Yamma, dama da hagu da tsakiya da kuma alƙibilar Musulmai za su sha wahala mai girma har sai sun kai ga yin zaɓin mutuwa saboda fitintinu. A wannan lokaci ne sai Allah Ya kawo wa Musulmai taimako ga waɗanda Musulmai suka yi mishi mubaya'a. Su tsayar da jihadi don ɗaukaka kalmar Allah su kashe kafirai har su haɗu da masifar Dujjal (Allah Ya la'ane shi) su yi ta yin yaƙi har yaƙin ya tsananta. Dajjal wanda Allah Ya la'ane shi, ya riƙa cewa idan aka wayi gari "za mu hallaka wannan jama'a domin ni ina da ikon yin haka." A cikin dare sai Allah Ya saukar da Annabi Isa (alaihis salam) sai ya kashe Dajjal Allah Ya shafe kafirci a bayan ƙasa. Ka sani lallai Mahdi yana da mataimaka:

Allah Ka yi ƙarin salati zuwa ga shugabanmu na farko da na ƙarshe.

Littafin Ilimin Tsoratarwa Daga Alamomin Bayyanar Mahdi ya ƙare.

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai. Allah Ka yi salati zuwa ga Annabi mai girma (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi).

Sunayen masu jaddada addini a cikin shekaru ɗari biyu bayan ƙarnin Annabi Muhammad (saw)

1. Umar bini Abdul'Aziz
2. Al'Imamus Shafi'i
3. Al'Imamul Ash'ari
4. Abu Hamidal Ahazali
5. Abubakar Albakalani
6. Fakrur Razi
7. Bini Daƙiƙul Idiyi
8. Balƙini
9. AbdurRahman Assuyuɗi
10. Ahmad Baba
11. Usman Bini Fodiyo

Allah Ya ji-ƙansu gaba ɗaya, amin.

# أجوبة محررة عن أسئلة مقررة

# AMSA TATACCIYA A KAN TAMBAYA TABBATACCIYA

Na

**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

Mai Fassara

**Mal. Ishaƙ Yunus**

**Al-Mashgool Bauchi**

Edita

**Dr. Hamza A. Ainu**

## ABUBUWAN DAKE CIKI


Gabatarwar Mawallafi .......... 193

Tambaya Ta Ɗaya .......... 194

Tambaya Ta Biyu .......... 195

Tambaya Ta Uku .......... 197

Tambaya Ta Huɗu .......... 200

Tambaya Ta Biyar .......... 201

Tambaya Ta Shida .......... 202

Tambaya Ta Bakwai .......... 204

Tambaya Ta Takwas .......... 206

Tambaya Ta Tara .......... 208

Tambaya Ta Goma .......... 209

Tambaya Ta Sha Ɗaya .......... 211

Tambaya Ta Sha Biyu .......... 212

Tambaya Ta Sha Uku .......... 213

Tambaya Ta Sha Huɗu .......... 214

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu, Annabi Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

Wani bawa kuma mabuƙaci ga rahamar Ubangiji mai suna Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu ɗan Salihu ɗan Muhammadu wanda aka fi sani da suna ɗan Fodiyo, Allah Ya lulluɓe shi da rahmarSa, amin, ya ce:

Godiya da yabo sun tabbata ga Allah, Wanda Ya bayyana Sunna kuma Ya ɗaukaki hasumiyarta, kuma Ya kawar da samuwar bidi'a tare da dakushe haskenta, Ya kuma bayyana sirrinta tare da shafe hanyoyinta.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu, Annabi Muhammadu wanda ya bayyana hanya ta gaskiya tare da tsari na haƙiƙa. Ya kuma yi umurni da bin Sunnar Annabi Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya da tabi'in da malamai masu aiki da sani.

Bayan haka waɗannan su ne 'yantattun amsoshi game da tambayoyi tabbatattu cikin saƙon da AsShehu Shisumas Ibn Ahmad ya aiko mani, wanda ya nemi da in amsa su alhalin ban kai matsayin ba domin kasancewata mai ƙarancin ilimi.

Sai na ga ya kamata saboda ɗan abin da na kamfata daga kogin ilimi na malamai da shaihunnai sai na buƙaci da in amsa tambayoyin tare da taimakon Allah Mai girma da ɗaukaka. Allah Ya ba mu dacewa.

Lallai waɗannan tambayoyin goma sha huɗu ne, ba zan faɗi wata magana ba wajen bayar da amsar face na danganta ta zuwa inda na samo ta domin samun natsuwa da kwanciyar hankali.

## TAMBAYA TA ƊAYA

Mene ne hukuncin sarayar da yin umarni da kyakkyawan aiki da kuma yin hani da mummunan aiki, wanda aka yi umurni da shi?

**Amsa:** AsShehu Sanusi ya faɗi cikin **Sharhim Alwusata**: "Lallai wajibi ne yin umurni da kyakkyawan aiki da kuma hani da mummunan aiki."

Ibnul Hajj ya faɗi a cikin **'Madakhal'** ya ce: "Ba a wajabta wa mai umurni da kyakkyawan aiki ko hani ba da ya canza abin da aka umurce shi da ya canza da ƙarfin tsiya ba. Sai dai wajibi ne a gare shi yin magana a kan hakan. Ya faɗi zahirin hukunci. Idan an saurare shi kuma aka yi aiki da shi, to madalla. Idan ko ba a saurare shi ba, to, shi ya gama aikinsa domin har a wajen Allah ba shi da laifi, kuma ya sauke abin da Allah Ya ɗora masa kuma ya kuɓuta game da maƙalewar da mutumin zai yi masa ranar Ƙiyama."

An ruwaito cewa, wani mutum zai maƙale wa wani mutum ranar ƙiyama wanda bai san shi ba, sai ya ce da shi 'mene ne ya faru ka maƙale mani kuma ni ba wata alaƙa da ta taɓa haɗa ni da kai?' Sai ya ce: "Ai ka taɓa gani na ina aikata ɓarna, amma ba ka yi ƙoƙarin canza ni ba ko yin wa'azi. To, ka ga wannan haɗari ne wanda yake da wuya a samu kuɓuta a gare shi.' Amma da a ce malamin ya yi magana (wa'azi) zai samu tsira, kuma magana ba ta da wahala a kan abubuwan ƙi, musamman a wannan lokacin namu. Shi, malami, magana a ka ɗora masa ba aiki ba ne mai wahala ba, kuma babu tsoro a gare shi sai dai ana barin ta ne kawai don ci gaban mai haƙar rijiya; yana ƙara zurfi yana cewa ya ci gaba domin kwaikwayon aƙidar da iyayensu da suka gada da kuma gudun tashin hankali.

Wannan shi ne ya halakar da al'ummomin da suka gabata, wato yin shiru ga abin da ya zama wajibi a yi magana a kai.

## TAMBAYA TA BIYU

Mene ne ya halasta na daga bayi a garuruwan da aka yawaita cinikin 'ya'ya masu 'yanci da waɗanda ba su halasta a bautar da su ba?

**Amsa:** Lallai garuruwa sun kasu Kashi Uku:

1. Garuruwan da kafirci ya yi ƙarfi ko ya yi rinjaye a ciki. Misali, garin Mushi da Gurma da Busa da Bargu da Gumba da Kutulul da Tabangu da Bubula da Gambiya da makamantansu waɗanda kafirci ya yi rinjaye a cikinsu.

To, irin waɗannan garuruwa ya halasta a mallaki mutanen garin ba tare da wata tambaya ba sai dai idan an sami tabbacin cewa bayin da ake kamowa Musulmai ne asali kafin a mallake su. To, sai a sake su.

Asshehu Ahmad Baab ya faɗi cikin littafinsa **'Al-Kashfu wal Bayan li as naafil Majlubis Sudani'** ya ce: "Dukkansu kafirai ne matuƙar dai suna kan kafircinsu." Sannan ya ƙara da cewa, "Babu laifi a mallake su, a mai da su bayi."

2. Garuruwan da Musulunci ya yi ƙarfi a cikinsu, kamar Barno da Kano da Katsina da Zazzau da Sagi da sauran garuruwan da Musulunci ya kwarara. Duka waɗannan ba ya halasta a mallaki mutanen ƙasar sai dai idan an sami tabbacin cewa bayin ko mutanen da ake fitowa da su daga ƙasar kafirai ne, babu laifi a mallake su.

Ash-Shayk Ahmad Bab ya faɗi cikin littafinsa da ya gabata da cewa, "Ba ya halasta a mallaki mutanen wannan garin. Amma idan aka kamo bawa a irin waɗannan garuruwa na Musulmi, aka fito da shi za a sayar, sai bawan ya bayar da shaidar cewa shi, Musulmi, ne kuma ɗa ne. To, za a sake shi kuma a matsayin ɗa yake mai 'yanci. Kamar yadda malaman Andalus suka bayar da fatawar haka, irin su, Ibn Utab da wasunsu.

Ta wannan hanya ce Alƙalan Faas suka yi ta yin hukunci. Abil Abbas Bin Sahl al-Imamul Mash-hur ya faɗi cikin littafinsa **'Nawazil'**: "Duk bawan da ya yi da'awar shi ɗa ne mai 'yanci kuma ya ce shi ya fito ne daga garin da ake yawaita cinikin 'ya'ya, to, a nan mai sayen kuma ya bayar da shaidar cewa haka ne, ya sayo shi ne daga wannan garin."

Muhammad Bin Walid da Yahya Bin Abdul 'Aziz suka ce: “To, za a buƙaci mai sayen ya zo da shaidu cewa,wannan mutumin da ya sayo bawa ne ba ɗa ba ne.”

Shi ko Sahnun ya ce: Ibn Lubaba ya ce: “Bawan da ya yi da'awar shi ɗa ne mai 'yanci zai zo da shaida.”

Ibn Zarb ya ce: 'Mai sayen ne zai tabbatar da hujjar ingancin cewa ya sayo shi a wajen wane kaza a matsayin bawa.'

3. Su kuwa garuruwan da ba mu da masaniyar su, Musulmai ne ko Kafirai ne.

Al Faƙih Al Hafiz Makhluf Al Babali ya ce: 'Duk wanda yake son zaman lafiya ga kansa, to, kada ya sayi wani bawa sai idan an san garin da ya fito. Daga nan sai mai sayen ya duba ya gani daga garin Musulmai yake ko daga garin Kafirai ne.' Al Faƙih Al-hafiz abu Ishaƙ bin Hilal ya ce: 'Lallai kamewa game da mallakar bayin da ba a san taƙamaiman garin da suka fito ba, to, wannan yana daga cikin babin tsantseni.'

Asshehu Ahmad Baab ya faɗi cikin littafinsa: **‘Al-Kashfu wal Bayan li as naafil Majlubis Sudani’** cewa: “Ba ya halatta sayen Bafullatani don a mallake shi ko a mai da shi bawa, domin yawancin ƙabilar Fulani Musulmi ne, face wani labari da ya same mu cewa akwai wata ƙabila da ake kira 'Wara'a jinn.' Su kafirai, ne ba mu san asalinsu ba Musulmi ne ko ridda suka yi?”

Sai Shehu Usmanu ya ce: “Kammalalliyar magana game da mallakar Bafullatani ita ce; ba ya halasta a mallake shi, sai dai idan an sami tabbacin cewa kafiri ne na asali, domin mafi rinjayen ƙabilarsu Musulmi ne.”

## TAMBAYA TA UKU

Mene ne hukuncin kuskure game da lafuzzan Alƙur'ani da sunayen Annabawar (tsira da amincin Allah su tabbata a gare su)?

**Amsa:** Lallai wannan bai halasta ba. Amma yin lahani (kuskure) a cikin Alƙur'ani, to, haƙiƙa Shehu Abu Hafs Bin Jaz'i ya ce, lahani mummuna ya kasu gida biyu:

1. Akwai lahani bayyananne;
2. Akwai lahani ɓoyayye.

Lahani (Dulge) bayyananne shi ne wanda yake lalata jerantuwar kalmomi (Nahawun Jimlar).

Lahani ɓoyayye kuma shi ne wanda ba a ba haruffa haƙƙoƙinsu na furuci.

Muhammad Bin Umar Al-Jazari ya faɗi cikin muƙaddamarsa **'Almanzumati fi ilmi tajwidil Kur'an'**.

1. "Bayan haka lallai wannan muƙaddimar tana nuni ne ga makarancin Alƙur'ani da ya sani:
2. Waɗannan ƙa'idojin kafin ya fara karatun Alƙur'ani.
3. Ya san mafitar haruffa da siffofinsu domin ya iya furta su cikin fasaha."

Kuma wasu malamai suka ƙara da cewa:

1. Koyon Tajwidi dole ne, domin duk wanda ba ya kyautata karatun Alƙur'ani, to, wannan mai laifi ne.
2. Saboda haka Allah ya saukar haka kuma ya sadu zuwa gare mu.

Abu Yahya Zakariya-Ansari ya faɗi cikin littafinsa mai suna **'Daƙa'iƙul Muhkama;**, sharhin wannan muƙaddima ya ce: "Akwai lahani bayyananne da kuma lahani ɓoyayye," (Kamar yadda aka yi bayani a baya sai dai shi, wannan malamin, ga yadda ya bayar da tasa fahimtar).

Ya ce: "Lahani bayyananne shi ne wanda yake aukawa a kan lafazi kuma ya jirkita ma'ana kuma ya birkita tsarin jimlar ko kalmar, kamar barin yin Ikhfa'i ko Gunna."

Shi ko AbdurRahman Suyuɗi cewa ya yi a cikin littafinsa, **'Al-Itƙan'**: "Lallai yana da muhimmanci mutum ya koyi Tajwidin Alƙur'ani, kuma ya bi shi daki-daki, domin akwai malamai da dama waɗanda suka yi wallafe-wallafe a kan tajwidi. Akwai irin su, Asshehu Addani da sauransu."

AbdurRahman Suyuɗi ya ci gaba da cewa: "Babu shakka, lallai, kamar yadda al'umma suke bautarsu ta hanyar fahimtar Alƙur'ani da tsayawa a kan iyakokinsa, haka kuma ya zama dole su kiyaye lafuzzan Alƙur'anin da kuma furta haruffansa daidai da siffar da ta dace da su, wanda aka samo daga bakin makaranta kuma gwanaye wajen karanta shi. Shi, wannan ilimi na tajwidi, an samo shi daga zuwan Annabawa masu fasaha."

Kuma makarantan Alƙur'ani sun faɗa cewa, "Karatun Alƙur'ani babu tajwidi, lahani ne."

Kuma a cikin littafin **Manhul Hamiyyati fi sharhil Farid**: Sadiƙ, (Allah Ya ƙara masa yarda), ya ce, "Mutum ya rinƙa karatu yana cijewa, ya fi da ya riƙa yin lahani a ciki."

Ayyub Assakhtiyani ya yi kuskure wajen faɗin wani harafi, amma sai da ya ce "Astaghfirullah." Shi ko Ɗan Umar da Ɗan Abbas sun kasance suna dukan 'ya'yansu idan sun yi kuskure wajen karatun Alƙur'ani.

(Sai Shaihu Usmanu) ya ce: "Lahani bayyananne shi ne wanda yake faɗawa a kan lafazi sai ya canza ma'ana da li'rabi, kamar yi wa majruri ruf'a ko nasba amma lahnul khafiyya shi ne wanda sanin sa ya keɓanta ne kawai ga masana, shi ne rashin bai wa kowane harafi haƙƙinsa na furuci, saboda haka ba za a iya kallafa wa kowace ƙabila hakan ba, domin kowace ƙabila tana da al'adarta da kuma salon yadda take magana."

Imamul Gazali ya faɗi cikin littafinsa **Ihya'u**, "Ba a ƙallafa wa bayi wajen karatun Alƙur'ani yin furuci da haƙiƙanin haruffan sai dai yadda al'adarsu da harshensu yake."

Amma irin canje-canje da ake samu a sunayen Annabawa, ba su halatta ba, domin dukkan kuskure daga shaiɗan ne wanda yake cusa hakan a ƙirazan mutane domin ya karkatar da su don kada su samu albarkar sunayen.

Ibn Hajji ya faɗi a cikin littafinsa **'Madakhal'** cewa, duba ɗan'uwa, Allah Ya yi maka rahama, zuwa ga makircin shaiɗan, yadda ya yi jifa da dafi mai guba. Idan ka duba za ka ga cewa yawancin sunaye na shari'a akwai sunan Allah a ciki kamar Abdullahi, ko AbdulFatah, da sunan Annabawa, (tsira da amincin Allah su tabbata a gare su) ko kuma sunayen Sahabbai.

Ya zo a cikin Hadisi daga Aliyu, (Allah Ya ƙara masa yarda), ya ce: "Lallai Annabi, (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi)  Ya ce:

(ما من أهل بيت فيه إسم نبي إلا بعث الله تبارك وتعالى إليهم ملكا يقدسهم بالغداة والعشي).

***"Babu waɗansu masu gida da zai kasance akwai mai sunan Annabi a cikin gidan face Allah Ya tayar da wani Mala'ika a gare su, wanda zai riƙa tsarkake su da nema masu gafara, safiya da maraice."***

Haka kuma an samo daga Hasnul Basri ya ce, "Lallai Allah Zai tsayar da bawanSa a gabanSa ranar ƙiyama, shi wannan bawan sunansa Ahmad ko Muhammad, sai Allah Ya ce da shi, bawaNa ba ka jin kunyaTa ne ka yi ta saɓa mani a duniya, ga shi kuma sunanka ya yi daidai da sunan masoyina, Muhammadu (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi)?" Sai wannan bawan ya duƙar da kansa ƙasa saboda kunya, sai ya ce: "Ubangiji, haƙiƙa, na aikata," Sai Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ce: "Ya Jibrilu, kama hannun bawaNa, ka sanya shi cikin Aljanna domin ina jin kunyar in yi wa mai sunan masoyina azaba da wuta."

To, idan haka ake samun ɗaukaka ta ƙoli ga sanya sunayen Annabawa, ina ga sunayen Allah Mai girma da ɗaukaka? Ai sun isa su zama mafiya albarka, waɗanda za a riƙa kira ko sanya wa mutane sunaye da su.

A yayin da shaiɗan ya fahimci cikakkiyar albarkar da ke tattare da sunayen nan sai ya buƙaci ya kawar da ita a gare su da ɗabi'arsa ta shaiɗanci. Sai ya jefa su ga wani rami da yi wa kawunansu laƙubba daban-daban waɗanda aka hana, suka riƙa kiran Muhammad da laƙabin Hamuu, Ahmad kuma da laƙabin Hamad, Yusuf kuwa da musayar Yasuu, shi kuwa AbdurRahman da laƙabin Raha da dai sauransu.

Kamar yadda aka sani a al'adarsu a tsakaninsu ko wani yanki na ƙasa akwai abin da suke yin laƙabi da shi, a nan ne ya ƙare kuma ya isa amsar tambaya.

## TAMBAYA TA HUƊU

Ta wace hanya za a iya gyara asalin kuskuren da aka samo daga bakunan malamai?

**Amsa:** Lallai gyaran wannan kuskuren dole ne musamman ga malamin da bai san ƙa'idar Larabci ba (Nahawu) kuma bai da ilimin ruwayar Hadisi ba.

Amma idan kuskuren ya kasance a cikin ruwayar Hadisi ne, to, malamai sun yi saɓani a kai.

AbdurRahman Bin Husain Al-Iraƙi ya faɗi a cikin **Alfiyyarsa** ya ce:

1. "Idan aka samu kuskure tun asali, to, za a duba a ga ta ya ya aka same shi.
2. Idan kuskuren daga mazhabar mutanen ƙwarai ya fito, misalin Imamu Malik ko Ibn Hambal ko Shafi'i, to, sai a gyara.
3. A waɗansu lokuta lahani ba ya canza ma'ana sai dai idan ana gudun yin kuskure, to a yi wasali shi ya fi.
4. Kuma a bi abin da ya dace a sashin ya fi, haka mafi yawan malamai aka ciro a wajensu.
5. A fara da dacewa ya fi da kuma karfi kuma a gyara matani kamar yadda ya zo. Anan ma ansa ya gamsar.

## TAMBAYA TA BIYAR

Mene ne hukuncin malamin da yake bayar da karatu alhalin bai sami izini (ijaza) ba daga ainihin malaminsa musamman a cikin ilimin tafsiri da Hadisi?

**Amsa:** Lallai samun lasisin bayar da karatu daga malaminka, wannan ba sharaɗi ba ne. Sai dai yana daga cikin halacci a cikin fatawar malamai.

AbdurRahman Suyuɗi ya faɗi cikin littafinsa **'Al-Itƙaan'** ya ce: "Karɓar lasisin bayar da karatu daga Shehu, wannan ba sharaɗi ba ne, sai dai yana daga cikin halacci. Duk wanda ya ga ya cancanta kuma zai iya bayar da karatun, to, babu laifi ko da malaminsa bai ba shi lasisin (ijaza) ba, kuma a kan wannan ra'ayin malaman farko suke.

Kai, ba ma ilimin Tafsiri ko Hadisi ba, kowane fanni idan dai mutum ya ga ya cancanta, to, babu wani ijaza (izini), ya tafi ya koyar da shi.

Amma a wajen bayar da fatawa, malamai sun yi saɓani a kai, waɗansu sun ce bai halasta ba domin ba kowa ne ya kamata ya ba da fatawa ba, domin a wajen bayar da fatawa, ana son malami ya zamanto mai la'akari da nazari da lokaci da zamani da ƙasar da mutumin. Waɗannan abubuwan guda huɗu: Mai bayar da fatawa, dole ne ya kula da su don gudun kada ya daɓa a ƙasa.

Irin wannan dalilin ne ya sa malaman suka ce ba kowa ne zai ba da fatawa ba.

Amma game da amsar fatawa, akwai buƙatar mutane su duba cancanta domin yawancin mutane ba su duba cancanta. Idan dai an ce wannan malami ne sai kawai su karɓi fatawa a gare shi.

Shi ya sa a wani lokaci ake son malami ya sami (ijaza) izini domin yawancin mutane ba su san a wajen wa ya kamata su karɓi fatawa ba.

## TAMBAYA TA SHIDA

Mene ne hukunci game da yin kuskure a cikin Kiran Salla?

**Amsa:** Lallai dole ne mutum ya aminta daga duk wani lahani wanda zai janyo masa abin da shari'a ba ta halasta ba. Wannan wajibi ne a kan kowane mai kiran salla, musamman idan har ya kasance yana furta lafazi na kafirci a ciki, kamar yi wa ba'un madda (ja) a wajen kalmar Akbar, to, wannan laifi ne da kuma tsayawa a kan ilaha.

Amma duk kuskuren da bai kawo canjin lafazi ko canjin ma'ana ba, to wannan mustahabbi ne. Alƙurashi ya faɗi a cikin littafinsa, **'Sharhul Mukhtasar'** cewa: "Aminta daga duk wata ɓarna a cikin kiran salla mustahabbi ne."

Abu Hasanul Maliki ya faɗi cikin littafinsa, **'Tahƙiƙul Mubani' (Sharhin Risala)** sashin masu kiran salla suna cakuɗa kiran salla a wurare kamar haka:

Suna yi wa Ba'un madda wato suna jansa daga Akbar sai su mayar da shi zuwa Akbaar. Daga ciki akwai inda suke yin ja a wajen Ash'hadu sai su ce Aashahadu wannan kalmar tana nufin tambaya ce wato "Na shaida?" Saboda jan da aka yi maimakon ana so mai kiran salla ya ce Ash'hadu ma'ana "Na shaida."

Daga ciki akwai kuma inda suke tsayawa a kan La'ilaha maimakon ana son mai kiran sallah ya faɗe su bai ɗaya laa'ilaaha 'illal-laah. Ya faɗi cikin littafinsa, **'Tawdeeh'** da cewa wannan laifi ne.' Kuma ya ƙara da cewa, "yin haka kafirci ne a cikin littafinsa, **'Zakhira'**.

Daga cikin irin wannan kuskuren akwai rashin shigar da tanwini (faɗuwar wasulla) na sama a sunan Annabi Muhammadu, misali: Ash-hadu anna Muhammadarrasulullah : أشهد أن محمدًا رسول الله wato a ji tanwin tare da tasirinsa a kan ra'un, amma abin da aka hana kada mai kiran salla ya ce Ash-hadu annan Muhammadaa rasulullah أشهد أن محمدًا رسول الله

Ka ga a nan ya yi amfani da alu jaa ke nan wannan lahani ne ɓoyayye.

Daga ciki akwai rashin furuci da harafin Haa Karami a wajen Hayya alas-salah حي على الصلاة Bugu da ƙari, akwai kuma rashin furuci da harafin Haa

Karami a wajen حي على الفلاح Idan mutum ya yi ƙoƙarin furta wanin wannan harafin, to, yana kiran mutane ne zuwa ga wuta, a maimakon samun tsira.

Haka ma na biyun yana kira ne zuwa ga abin da ba shi ake nufi ba.

Daga cikin irin wannan kuskuren akwai yi wa Laamun Fataha "Rasulallah" a maimakon "Rasulullah." Domin cewar da ya yi Rasulallah, wannan cewa bai shaida da Manzancin Annabi ba, saboda a Nahawunce ya sanya lafazin Rasulullah a maimakon lafazin Muhammad domin bai zo da khabarin ba, wato labarin ba.

Kuma daga ciki akwai yadda Malam Shibrahit ya faɗi cikin sharhin **'Mukhtasar'** yi wa Hamza maddi (jaa) daga Akbar a koma da shi Akbaar, laifi ne; da yi wa nuunun fataha a wajen faɗin an laa'ilaha illallah, sai mutum ya ce analaa'ilaaha illalaah, laifi ne ko kuma yi wa haakuri (jaa) laa'ilahaa, ko yi wa sunan Annabi Muhammad ruf'a; ko jan kalmar Hayya alassalaat sai mutum ya ce Haaya alassalat, duk wannan laifi ne.

Amma yi wa hamza ibdali wajen faɗar Akbar ko harafin 'waawun', to, wannan an yi sauƙi a kansa, kamar yadda ya zo a cikin wani littafi mai suna **Ihram**, sai dai an fi so mutum ya faɗe shi kamar yadda aka yi umarni.

Kuma a cikin littafin **'Kitabul Muwaƙit'** taƙaita alifun na biyu wajen faɗar sunan Allah. Misali, Allah sai mutum ya ce Allah wannan bai halatta ba, sai dai an yarda a lalurar waƙa ko don gudun almubazzaranci maddi ba kai ba gindi, ko kuma idan mutum yana gudun kada ya fita daga iyakar maddin.

## TAMBAYA TA BAKWAI

Mene ne ya zama dole ga mutumin da yake da iyali waɗanda suka haɗa da matan aure da 'ya'ya da bayi, idan har sun kasance ba sa bin umurnin Allah. Ta wace hanya ya kamata ya hane su?

**Amsa:** Khalil Bin Is'haƙ ya faɗi a cikin littafin **'Mukhtasar'** cewa: "A yi wa wadda ta saɓa daga cikin mata wa'azi; sannan idan ta ƙi ji, ya ƙaurace mata idan ba ta ji ba, ya doke ta, idan har ya yi zaton dukan zai kawo alfanu." Shibrikhiti yana cewa: "Idan har ta daina yi masa ɗa'a, to, shi kuma sai ya bar kwanciya da ita ko jin daɗi da ita."

Idan kuma tana fita ba tare da izini ba, ko ta ƙi bin abin da Allah Ya wajabta masa a kanta na daga haƙƙin Allah da haƙƙinsa, to, sai ya ɗauki waɗancan matakan ɗaya bayan ɗaya. 'Shibrahiti' ya ce: "Kada miji ya canza zuwa wani mataki na ladabtarwa, sai idan wannan matakin bai yi fa'ida ba."

(Shehu Usmanu) ya ce: "Adadin kwanakin da aka ce mutum zai iya ƙaurace wa matarsa, wata ɗaya ne." Kamar yadda Ɗan Kasim ya ruwaito daga Malik.

Ibnul Arabi ya ce: "Dukan da ake magana, mutum zai iya yi wa matarsa a bisa sharaɗin kada ya kasance mai cutarwa, shi ne wanda ba za a samu karya wata gaɓa ko rauni ba." Ata'ullah Al-askandari ya faɗi a cikin littafinsa, **'Attanwir fi Isƙatit Tadbir'** wajen yin sharhi a kan wannan ayar:

﴿ وَأْمُرْ أَهْلَكَ بِالصَّلَوٰةِ وَاصْطَبِرْ عَلَيْهَا ۖ لَا نَسْـَٔلُكَ رِزْقًا ۖ نَّحْنُ نَرْزُقُكَ ۗ وَالْعَٰقِبَةُ لِلتَّقْوَىٰ ﴾ طه: ١٣٢

***"Ka umurci iyalanka da salla kuma ka dage a kanta, ba Mu tambaye ka wani arziƙi ba, domin Mu ne Muke azurtawa, kuma kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah." Alƙur'ani 20:132***

Ka sani ya kai ɗan'uwa, lallai Allah Ya umurce ka da ka umurci iyalanka da yin salla, yadda yake wajibi a gare ka sada zumunci, to, haka ya zama wajibi ka ɗora iyalanka a bisa tafarkin shiriya don yi wa Allah ɗa'a da nisantar da su game da saɓa wa Allah.

Kamar yadda ya zama kowane mutum yakan so ya ga iyalansa sun zama masu albarka a duniya, to, haka ma ana so ka fi su son su sami albarkar lahira domin ita ce madawwamiya, kuma su abin kiwo ne a gare ka.

Manzon Allah, (tsira da aminci su tabbata a gare shi) Ya ce:

كلكم راع وكلكم مسئول عن رعيته

***"Dukkanku masu kiwo ne kuma za a tambaye ku game da abin kiwonku."***

Idan ka duba ayar da ta gabata, Allah Ya yi umurni ga mutum Musulmi da ya umurci iyalansa kafin ya umurci kansa wajen yin haƙuri da nace wa Salla.

### Faɗakarwa

Ka sani, wajibi ne a gare ka da ka umurci iyalanka da yin salla tun daga matarka da baiwarka da 'yarka da sauransu. Kuma ka buge su, idan suka bar ta, domin ba ka da hujja a wajen Allah da har za ka ce ka umurce su, su ne ba su ji ba.

Da sun san cewa za su sadu da ɓacin rai idan suka bar ta da ba su bar ta ba, kamar yadda idan suka saɓa maka ko suka ɓarnata wani abinci ko suka yi wa wani aiki da ka sa su, ɗaukar sakainar kashi, za su samu ɓacin rai da tashin hankali. Sai dai kodayaushe kana umurtar su da tsare haƙƙin Allah.

Dukkan mutumin da yake kula da salla ba ya umurtar iyalinsa da ita, to, ba za a sanya shi cikin masu umurtar iyalai da salla ba, kuma za a tashe shi ranar lahira a cikin tawagar masu wulaƙanta salla.

Idan ka ce lallai kana umurtar su amma su ne ba su aikatawa, kuma ka yi musu wa'azi ba su ji ba, kai hatta ɓacin rai ka nuna musu, ba su ji ba, shi ke nan, sai ka ƙyale su, ka fita harkarsu, to, har yanzu ba ka tsira ba.

Lallai yadda al'amari yake shi ne ka ƙaurace wa duk wanda ya cancanta ka ƙaurace masa domin ya ƙi al'amarin Allah. Idan bawanka ne, to, ka sayar da shi. Idan ko matarka ce, to, ka sake ta. Ita ƙaurace wa don Allah tana haifar da shiriya da kuma daidaito.

## TAMBAYA TA TAKWAS

Mene ne hukuncin mutumin da ya tashi zuwa salla sai shaiɗan ya sanya mashi waswasi, yana ta tunane-tunane, yana da lada ko babu?

**Amsa:** Yana da lada cikakkiya idan har shi ma yana bakin ƙoƙarinsa wajen kawar da waswasin domin ba yin kansa ba ne.

Amma idan har shi ne ya janyo tunanin da kansa na daga al'amuran duniya, to, a nan ladansa ya ragu, sai dai kuma duk da haka sallarsa ba ta ɓaci ba, amma yana daga cikin abin da ba a so (makruhi).

Kuma a cikin littafin **'Mukhtasar al Khalil'**: "Yin tunani a cikin salla game da al'amuran duniya makruhi ne." Abu Zaidil Akhdari ya faɗi cikin babin rafkannuwa, inda ya ce: "Duk wanda tunaninsa ya tsawaita a cikin salla game da al'amuran duniya, to, ladar ta ragu, amma sallarsa ba ta ɓaci ba."

To, amma maganin waswasi a cikin salla shi ne kamar yadda Ɗan Aɗa'ullah ya faɗi a cikin littafinsa **'Al-minan'** ya ce malaminsa Abu Abbas al-Mursi, (Allah Ya ƙara masa yarda) ya kasance yana sanar da mai waswasi wannan addu'ar:

**سبحان الملك الخلاق إن يشأ يذهبكم ويأت بخلق جديد وما ذلك على الله بعزيز**

***"Subhanal Malikil Khallaaƙ in ya sha' yuzhibukum wa ya'ti bi khalƙin jadid wa maa zalika alal-laahi bi a'ziz."***

Shibrahiti ya ƙara da cewa a cikin sharhin **Mukhtasar**, Duk wanda waswasi ya aure shi, to, ya rubuta wannan ayar kamar haka;

﴿ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ ۚ إِنَّهُۥ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٠٠﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ إِذَا مَسَّهُمْ طَٰٓئِفٌ مِّنَ ٱلشَّيْطَٰنِ تَذَكَّرُوا۟ فَإِذَا هُم مُّبْصِرُونَ ﴾ الأعراف: ٢٠٠ - ٢٠١

***"Wa'imma yanzaghannaka minash-shaiɗani nazgun fasta'iz bil-laah, 'innahu sami'un 'aleem, 'Innal lazeenat-taƙau 'Izaa massahum ɗaa'ifatin minash-shaiɗani tazakkaru fa'izaa hum mubsirun." Alƙur'ani 7:200-201***

Duk wanda waswasi ya aure shi, to, ya rubuta wannan ayar a jikin ganyaye bakwai da za'faran ko ya rubuta da ruwa ko wardi a ranar Juma'a, kowace rana ya riƙa cinye ganye ɗaya. Sannan ana so, idan ya haɗiye, ya zuƙi ruwa sau ɗaya, zai sami waraka da 'iznin Allah.

Kuma ya ƙara da cewa: Usman bin Abil Ass, (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cewa shaiɗan yana sanya mani waswasi a cikin salla a yayin da nake karatu sai Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) Ya ce:

ذلك شيطان يقال له خنزب فإذا أحسست فتعوذ بالله منه واتفل عن يسارك ثلاثا

***"Wannan shaiɗan ne mai suna Khinzaab. Idan ka ji wannan waswasin sai ka ce: "A'uuzu billaahi minash-shaiɗanir-rajeem. Sai ka yi tofi sau uku a wajen hagunka."***

Sai na aikata haka, sai Allah Ya kawar mani da shi. Kuma ya ƙara faɗa da cewa, a cikin littafinsa **'Jazariyya,'** "Duk wanda waswasi ya zo masa, to, ya lazimci ambaton Allah. Duk wanda ya lazimci ambaton Allah, to, waswasi ko kambun baka ba zai cutar da shi ba."

Shi kuma AbdurRahman Assuyuɗi, ya faɗi a cikin littafinsa mai suna **'Annasa'ih wal Wasaaya'**, "Yawaitar waswasi a cikin ayyuka ko niyya, wannan yana nuni ne a kan mutuwar tsaye shi ne ruhi da zuciya."

Saboda haka ku roƙi Allah domin ya kawar maku da wannan a cikin ƙarshen dare na ƙarshe, kuma Zai kawar maku, in Allah Ya so.

## TAMBAYA TA TARA

Mene ne hukuncin mutumin da ya shaida da kalmar shahada, sai dai kuma ya yi wa al'amuran addini ɗaukar sakainar kashi, abin da ya fi damuwa da shi kawai shi ne al'amuransa na duniya?

**Amsa:** Lallai malaman Ahlussunna, (Allah Ya yarda da su), sun haɗu da cewa "Duk wanda ya yarda da kalmar shahada, to, wannan hukuncin shari'a ya hau kansa." AbdusSalam bin Ibrahim Alluƙani ya faɗi a cikin littafinsa, **'Ittihaful Murid bi Jauharatit-tauheed'** cewa; "Imani cikakke shi ne wanda ake yi tun a duniya ba sai a lahira ba, shi ake iƙrari. Duk wanda ya yi iƙrari da kalmar shahada, to, hukuncin Musulunci ya hau kansa, kuma ba za a kira shi kafiri ba sai dai idan ya bauta wa gunki."

(Usmanu Bin Fodiyo) ya ce: "Idan har dalili ya tabbata, lallai mutumin ya tabbatar da cewa bayar da zakka yana kawo asara da tawayar dukiya, to, lallai wannan mutumin ya kafirta domin ya yi shu'umci da wani abu a cikin addinin Allah. Haƙiƙa ya kafirta a bisa zance na malamai mafi shahara."

## TAMBAYA TA GOMA

Mene ne hukuncin mutanen da suka yi wa shugabansu mubaya'a suna yi masa ɗa'a suna girmama shi, daga baya suka riƙa wulaƙanta shi, tare da ƙasƙanta shi don kawai ya daina ba su abin da yake ba su?

Amsa: Lallai wannan mummunar al'ada ce kuma haramun ce a bisa taruwar malamai. Waliyyullah Bin Abi Hamza ya faɗi cikin littafinsa **'Bahjatun-Nufus'** sharhin Bukhari, cewa, "Lallai Annabi ya yi umurni da kiyaye bai'a (mubaya'a) kuma Manzon Allah ya ci gaba da cewa, "Ko da shugaban baƙar fata ne ƙirin kamar shuni, mummuna mai taɓaɓɓen hanci, lallai ne ku yi masa ɗa'a, kuma ku saurare shi ko da yana karɓe muku dukiya da yawan duka safiya da maraice."

Sai wani daga cikin Sahabbai ya ce, "Ya Manzon Allah, me za ka ce idan har aka ɗora mana shugaba azzalumi, yana karɓe mana dukiya, kuma ba ya ba mu haƙƙinmu? Sai Mai tsira da amincin Allah Ya ce:

(أعطوهم حقوقهم واطلبوا حقوقكم من الله فإن الله سائلهم عما استرعاهم).

***"Ku ba su haƙƙinsu na shugabanni, amma ku nemi haƙƙinku a wajen Allah, domin Allah Zai tambaye su ta wace hanya suka shugabance ku."***

Sannan ya ce: Hadisai da suka zo da wannan ma'ana suna da yawa saboda ɗaukakar Musulunci da rukunansa da karya ƙarfin maƙiya da baƙanta musu zuciya.

A cikin littafi mai suna **Kasidatuj-Jaza'ir:** "Ba a cire shugaba saboda ya zama fasiƙi sai dai idan kafirci ne ya bayyana, to, ya zama dole a cire shi."

Shehu Sanusi ya ce: "A cikin sharhin a wannan ƙasida a daidai wannan wuri Manzon Allah (saw) ya siffanta zamani lalattatu da shugabanninta kamar yadda ya shahara amma bai bada umarni da a cire su ba; sai dai ya ce ku ba su haƙƙinsu; ku kuma ku roƙi Allah haƙƙinku."

A cikin **Ida'atid-Dujunat** ya ce: zamowar **Fasiƙanci** ga shugaba bai ba da damar a cire shi ba sai dai idan kafirci ne, dole a cire shi.

Kamar yadda ya zo a wasu baiti na Waƙa:

1. Bai halatta cire shi idan fasiƙanci ko zalunci ya bayyana.
2. Bai fita sai dai idan kafirci ne ya same shi amma domin zalunci kawai babu...

A cikin littafin **Ra'hatu jannat** wajen sharhin wannan baiti na Shehu Isma'il Damshƙi, ya ce: Baƙalani Ya ce: Allah Ya yi mashi rahama bai halatta ba a garemu mu cire shugaba dalilin wani laifi idan ba kafirci ba ne, kowa ce irin laifi ne kuwa, idan dai ba halatta laifin ba a ɓoye ko a bayyane.

A nan muna fatar amsar ta wadatar, duk sawaba da dacewa na ga Allah.

## TAMBAYA TA SHAƊAYA

Mene ne hukuncin mutumin da yake riya cewa ya san wani abu daga ilimin gaibi?

**Amsa:** Muhammad bin Abdul Karim Almaghili ya ce: "Duk wanda ya riya cewa ya san wani abu daga ilimin gaibi ta hanyar bugun ƙasa ko taurari ko aljannu ko wani abu na sautin tsuntsaye ko yanayin tashinsu da makamantansu, to, wannan maƙaryaci ne kuma kafiri, kuma duk wanda ya gaskata shi, shi ma ya kafirta."

Ya ce: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce:

من صدق كاهنا فقد كفر بما أنزل على قلب محمد صلى الله عليه وسلم

***"Duk wanda ya gaskata boka, haƙika, ya kafirce wa abin da Allah Ya saukar ga Annabi Muhammadu."***

Shehu Usmanu ya ce: Muhammad bin Ahmad Bin Jari ya faɗi a cikin littafinsa, **'Kawaninul Ahkamush shar'iyyah wa Masa'ilil Furu'ul Fiƙhiyya'** cewa, "Duk wanda ya yi da'awar motsawar taurari daga wuri zuwa wuri da cewar wani abu zai auku, to, wannan kafiri ne. Wanda kuma ya yi da'awar gaibi, ɗan-bidi'a ne. Haka nan kuma duk wanda yake amfani da wata hanya wai na neman sanin gaibi shi ma ɗan-bidi'a ne.

## TAMBAYA TA SHA BIYU

Mene ne hukuncin mutanen da suke girmama itatuwa da duwatsu da aljannu da shaiɗanu ƙasƙantattu musamman ƙabilar Hausawa?

Amsa: Babu shakka waɗannan mutanen kafirai ne a bisa ijma'in malamai, wato taruwar malamai. Muhammadu Bin AbdulKarim Al-Maghili cewa yake yi, a cikin amsar tambayoyin da Amirul Hajj wanda ake wa laƙabi da suna Askiya ya yi masa: "Mene ne hukuncin mutanen da suke faɗar kalmar shahada kuma suna masu shaidawa da ita, duk da haka suna girmama sashin waɗansu itatuwa dad a yanka don ba da jini na musamman, kuma suna da gidaje da suka ware don aikata hakan (Gidan Bori) har ta kai ba sa naɗa sarki ko su aikata wani aiki ko su zartar da wani al'amari sai tare da umurnin abin da suke girmamawa?' Muhammadul Maghili ya ce: "Babu shakka waɗannan mushrikai ne, domin kafircinsu ya bayyana ƙuru-ƙuru (a fili)."

## TAMBAYA TA SHA UKU

Mene ne hukuncin cin dukiyar sarakuna (wato, kyautarsu)?

**Amsa:** Imamul Gazali ya faɗi a cikin littafinsa, **'Minhajil Abidin'** cewa, "Malamai sun yi saɓani a kan cin dukiyar sarakuna. Waɗansu malaman sun ce bai halatta ba ga talaka da mawadaci da ya ci dukiyar sarakuna domin azzalumai ne, saboda haka mafi akasarin dukiyarsu da abincinsu haramun ne. Saboda haka mafi rinjayen zance shi ne a nisance ta."

Waɗansu malaman kuma suka ce: ya halatta a ci ko talaka ko mawadaci, domin laifin yana ga mai zaluncin ne. Wasu kuma suka ce: Ya halatta ga talaka ya ci ban da mawadaci."

(Shehu Usman) ya ce, "Idan ka san dukiyar haramun ce, to, ba ya halatta a ijma'ance (wato haɗuwar malamai ka ci dukiyan). Amma idan ba ka sani ba, to, halas ne ka ci a bisa zancen malamai mafi rinjaye."

Muhammad Abubakar al-Barnawi ya faɗi, cin dukiyar da ka san yadda aka same ta, hanya ce ta haram, to, ba ya halatta. Sai dai a bisa niyya ta ƙyama. Amma wadda ba ka da masaniya game da ita, to, halas ne a gare ka da ka ci.

Ahmad Zaruƙ ya faɗi, a cikin littafinsa mai suna '**Miftahus Sadad**' sharhin **'Irshadus-saliki'** cewa, wasu malamai sun yanke cewa cin abincin azzaluman sarakuna haram ne sai **Izzidddin bn AbdusSalam** ya yi inkarin wannan. Ka dai bari ya fi amma ba haram ba ne. Nace (Shehu Usmanu); Cin abincinsu babu laifi, wannan shi ne ya shahara. "Cin abincin sarakuna ko cin dukiyarsu halas ne idan har ya kasance ba ka da cikakkiyar masaniya da cewa haram ce."

Muhammad Bin AbdulRahman Albarnawi ya faɗi, a cikin littafinsa, **'Manzumatu Shurbuz zilal'**: "Cin abincin sarakuna halas ne amma duk wanda yake gudun auka wa shubuha, idan ya guje mata, to, da ma hakan ake so."

Sannan ya ƙara da cewa: "Idan ka zo ka tarar ana cin abinci da shugabanni, to, kana da zaɓi ka ci ko ka bari."

## TAMBAYA TA SHA HUƊU

Mene ne hukunci game da irin lafuzzan da mutane ke furuci da su. Misali "Nidman Fallawil" cikin harshen Tawarik, haka kuma a cikin harshen Fulani "Midun Kalfini," haka a cikin harshen Hausa "Muna taulafi (wato, muna kamun ƙafa da albarkacin)."

**Amsa:** Irin waɗannan lafuzza sun halasta, amma a bisa babin kyautata zato da cewa shi wanda kake buƙatar tallafin nasa ko taimakon, ba zai iya aiwatar da komai ba, sai tare da horewar Ubangiji da kuma yardarSa, kamar yadda ya zo cikin faɗin Allah ta'ala,

﴿ يَوْمَ لَا يُغْنِي مَوْلًى عَن مَّوْلًى شَيْئًا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ۝٤١ إِلَّا مَن رَّحِمَ ٱللَّهُ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴾ الدخان: ٤١ - ٤٢

***"Ranar da wani majiɓinci ba zai iya amfanar da majiɓincinsa ba da komai, kuma ba za a taimake su ba face wanda Allah Ya yi wa rahama." Alƙur'ani 44:41-42***

Jalaluddin Almahalli ya faɗi, a cikin tafsirin wannan ayar cewa: "Ana nufin su ne muminai domin sashinsu za su ceci sashi da izinin Allah. Kuma Hadisi ya tabbata daga Manzon Allah, (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) cewa: "Lallai waliyyai da malamai da salihan bayi suna daga cikin waɗanda za su yi ceto ranar ƙiyama. To idan wannan muƙami ya tabbata a gare su za su yi ceto, me zai hana mutane su nemi wasila (taulafi) daga gare su don su zame masu tsani don samun tsira ranar ƙiyama?" (Shehu Usman) ya ce: "Sai dai ba ya halatta mutum ya ruɗi kansa da cewa wani zai cece shi ranar ƙiyama, ya bar nema wa kansa gafara. Wannan laifi ne."

AbdurRahman Sha'rani ya ce, a cikin littafin **'Annasa'ih wal Wasaya,'** "Ana buƙatar mutum ya yawaita ƙoƙari wajen ibada da neman gafara ga kansa saboda gudun sakankancewa da wani zai cece ka ranar ƙiyama."

Kamar yadda Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce wa mutumin da ya tambaye shi a kan haka:

أعنّي على نفسك بكثرة السجود

***"Ka zage dantse ga kanka da yawaita sujada."***

(Shehu Usmanu) ya ci gaba da cewa: “Wanda yake da makauniyar zuciya shi ne wanda zai sakankance da wasu za su cece shi, ya daina bauta. A irin wannan hali nasa, zai haɗu da Ubangijinsa.

Waɗansu daga cikin waliyyan saboda hidima da tsananin ƙaunar da muridansu suke nuna musu da kuma kyautata zaton da muridan suke masu, sai ka ji waliyyi ya ce: 'Na lamunce maku Aljanna (wato ba za su Aljannah).

Kamar yadda ya zo a cikin wani littafi, **‘Allahjati fi Takhlisi Bahjati.’** An ruwaito cewa Asshehu Abil Kasim Umarul Bazzar da wasunsa sun ce, Shehu AbdulKadir ya lamunce wa muridinsa da cewa ba zai mutu ba, sai a bisa tuba (wato yana yafaffe a wurin Allah).

Kumaimati da Bazzar sun ce, an tambayi Asshehu Muhyiddin AbdulKadir, idan aka kira sunan wani a gabanka, amma mutumin bai taɓa shimfiɗa ƙyalle ba kuma bai karɓa daga gare ka ba ko za a iya sa shi daga cikin mabiyanka?

Sai ya ce: “Duk wanda ya mallaka mani zuciyarsa.” Allah Zai karɓe shi.

Abdullahi Bin Muhammadul –Harushi ya faɗi a cikin littafinsa mai suna **Al-fathul Mubin** sharhin **Kanzul Asrar**, Imamul Waliyyi Sayyadi Aliyul Bakri Almisri (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: Duk wanda ya karanta wannan salatin, kuma bai shiga Aljanna ba, na ba shi izini ya cakume ni (ya ci kwalata) ranar ƙiyama a gaban Allah Ta'ala salatin shi ne:

اللهم صل على سيدنا محمد الفاتح لما أغلق والخاتم لما سبق ناصر الحق بالحق والهادي إلى صراطك المستقيم وعلى آله حق قدره ومقداره العظيم

Alhasanul Yusi ya faɗa a cikin **‘Mahasir’** da cewa Ibn Nasir ya kasance yana tunatar da talakawa game da zancen Imamul Sa'alabi ya ce: “Duk wanda ya gan ni har zuwa mutum na bakwai, to, na lamunce masa Aljanna, kuma zan yi masa shaida ranar Alƙiyama.”

Alhasanul Yusi ya ce: **“Ka sani, duk irin waɗannan abubuwan da ake faɗi, ana faɗin su ne kawai a kan tafarkin nuna ƙauna, wato kwaɗayi da kuma dacewa, amma ba wai lallai ba ne hakan ya faru.”** To, wannan ya halatta kuma hankali zai iya ɗauka kuma shari'a ba ta hana ba, domin faɗar Allah Mai girma cewa “Kuma su waliyyan Allah tamkar wata hanya ce da Allah Ya fitar da wannan falalar daga gare ta domin suna da matsayi a wajen Ubangijinsu Mai Girma.”

Kamar yadda ya zo cikin ƙissar Ibnu Hasuun da cewa, duk wanda ya gan shi, ya shiga Aljanna kuma wanda ya ga wanda ya gan shi har sau bakwai ko fiye, shi ma zai shiga Aljanna.

Alhasan Yusi ya ce: "Wani Faƙirin Malami ya ba ni labari da cewa wasu jama'a daga cikin mutanen Mubarak Attastawi sun je wajen shugabansu, Muhammad Ishlarfi, sai Muhammad Islarfi ya ce da su, "Ya ku Faƙirai, me shugabanku Ibn Mubarak ya ce da ku?" Sai suka ce ai ya faɗa mana cewa mutanen zamaninsa suna ƙarƙashin (zimmarsa) alhakinsa, kulawarsa, wuyansa, sai shugabana, Muhammadu Ishlarfi, ya ce da su ku shaida mu ma muna cikin zimmarsa."

Alhasanul Yusi ya ce, "Ku duba, ya ku 'yan'uwa zuwa irin wannan sallama wadda miƙa wuya ce, to, irin wannan sallamarwar ake so a yi wa duk wanda irin wannan falalar ta same shi, daga mutanen ƙwarai, ba wajibi ba ne amince wa makarun Allah Ta'ala, kuma ba a son mutum ya kawar da kai da nuna wadata ga abin da ya zama dole da ka san shi kuma ka yi aiki da shi.

A nan ne wannan littafi mai suna **'Ajwibatun Muharraraht An As'ilatin Muƙarraraht'** ya kawo ƙarshe, wanda Asshayka Alhaji Shisumas Ibn Ahmad ya aiko don in amsa masa.

Na amsa dukkan tambayoyin tare da godiya ga Allah, Wanda Ya hore mani wajen amsa su, gwargwadon ilimina da fahimtata. Na danganta duk wata amsa da na bayar zuwa zantuttukan malamai da kuma littattafai, kamar yadda na yi alƙawari a farkon littafin.

Dukkan godiya da yabo sun tabbata ga Allah, Wanda Ya shiryar da mu ga wannan aiki, ba mu zamanto masu shiryuwa ba, face da shiriyarSa a gare mu.

**اللهم صل على سيدنا محمد القاتح لما أغلق والخاتم لما سبق ناصر الحق بالحق والهادي إيى صراطك المستقيم**

**وعلى آله حق قدره ومقداره العظيم**

Wannan littafi ya cika da godiya ga Allah da kuma taimakonSa, Ya Allah Ka yi rahama ga al'ummar Annabi Muhammadu (tsira da aminci su tabbata a gareshi). Amin.

# بيان البدع الشيطانية

## التي أحدثها الناس في أبواب الملة المحمدية

# Bayani A Kan Bidi'o'in Shaiɗan

Na


## Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Muhammad Siraj Harith

**Edita**

Dr. Hamza A. Ainu.

## GABATARWAR MAWALLAFI

**Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai**

Allah Ya yi daɗin tsira ga shugabanmu, Muhammad da mutanen gidansa da sahabbansa da aminci da mai yawa.

Bawa mabuƙaci mai tsananin ɓukata ga rahamar Ubanigijinsa, watau Usman ɗan Muhammad ɗan Usman wanda aka fi sani da Ɗan Fodiyo. Allah Ya lulluɓe shi da rahamarSa, amin. Godiya ta tabbata ga Allah Ubanigijin halittu, tsira da aminci su tabbata ga ManzonSa da mutanen gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka: Wannan shi ne littafin **Bayanin Bid'o'in Shaiɗan** waɗanda mutane suka ƙirƙiro a cikin addinin Annabi Muhammadu (saw). In Allah Ya so zai amfanar da wanda ya dogara a kansa.

Akwai daga cikin abin da mutane suka ƙaga a cikin babin imani: Yin Kabilanci a cikin addini, wannan bidi'a ne haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Akwai daga cikin abubuwan da suka ƙirƙira ga wannan babi, akwai ɓatarwa aƙidojin Musulmi, shi ma bidi'a ne bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin wannan, akwai kutsawa a cikin abin da babu wata buƙata gare shi, na zurfafa bayanan masu falsafa, ita ma bidi'a ce muharrama bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Shiga bayi: Wato yin bayan gida a cikin ɗakin ibadar kafirai, shi ko bidi'a ce haramtacciya, bisa ga haɗuwar malamai, domin zai kai ga su ma su aikata irin wannan a massalatanmu.

Yana daga cikin abubuwan da suka ƙirƙiro a wannan babin shi ne tatso zakari da ƙarfi wurin fitsari, shi ma bidi'a ce wadda aka haramta bisa ga haɗuwar malamai. Saboda cutar da kai ne, haka kuma shi zakari kamar hantsa ne duk lokacin da aka tatsa shi, sai ya haifar da sanyi wanda zai zamo dalilin rashin tsarki. Kuma yana sassautar da mafitsara, wato wurin taruwar bawali.

Kuma yana daga cikin irin wannan bidi'o'i, fitowar mutum a tsakanin mutane domin yin tsarki; yana riƙe da zakarinsa a hannu, koda zakarin ya kasance a cikin tufafi ne. Wannan bidi'a ce makaruhiya, domin wannan lalacewa ce da rashin mutunci. Idan har ya kasance akwai lalurar ta haɗuwa da

mutane a wannan lokaci, to, ya sanya ƙyalle ya ɗaure zakarinsa da shi sannan ya fito. Idan ya ƙare lalurarsa sai ya yi tsarki a lokacin.

Yana daga cikin waɗannan bidi'o'i akwai shigar da yatsa a cikin dubura yayin tsarki, shi ma bida'a ce makaruhiya ko haramtacciya.

Yana daga cikin abin da aka tarar ana aikatawa, yin tsarki saboda tusa. Ita ma bidi'a ce makaruhiya, shi ne mafi shahara, ko kuma haramtacciya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Wanka: Yawaita kwara ruwa, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, ga wanda yake ƙudurce cewar wannan abu ne da ba makawa daga gare shi, kuma aikin addini ne na tilas. Kuma yin haka yana daga cikar aiki bisa ra'ayinsa ɓatacce. Idan bai yi nufin haka ba, to ya zama bidi'a makaruhiya.

Yana daga cikin abubuwan da suka ƙirƙiro, warware kitsattsen gashi yayin da ya kasance sako-sako ruwa na shiga tsakiyarsa. Idan bai zama haka ba, to, ba makawa ta warware shi. Amma warware wanda yake sako-sako bidi'a ce muharrama, ga wanda ya ƙudurce cewa ba makawa daga yin hakan, ko cewa hakan shi ne addini madaidaci, kuma shi ne cikar aikinsa da ra'ayinsa ɓatacce, in ko bai zama haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abubuwan da suka ƙirƙiro, wato zuba ruwa a cikin kafar kunne shi ma bidi'a ce haramtacciya, domin cutar da kai ne, kuma zai iya kai wa ga kurumta.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Alwala: Fitar da sauti wurin tofar da ruwan baki, shi ma bidi'a ce makaruhiya, kuma yana daga cikin ƙari a kan wanki uku, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Kuma isa matuƙa wurin shafar kunnuwa, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abubuwan da suka ƙaga, wato yawaita zuba ruwa ga alwala shi kuma bidi'a ce haramtacciya ga wanda ya ƙudurce hakan ba makawa daga gare shi, ko hakan shi ne addini madaidaici, ko shi ne cikar aikinsa da ra'ayinsa ɓatacce. In ko ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya kamar yadda ya gabata a cikin Babin Wanka.

Yana daga cikin abubuwan da suka ƙaga na bidi'o'i, shi ne bin waswasi a cikin natsuwar zuciya da ruwaitowar shaiɗan, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, ga wanda ya ƙudurce hakan ba makawa daga gare shi, ko kuma shi ne addini madaidaici, kuma shi ne cikar aikinsa bisa ra'ayinsa ɓatacce, in ko ba haka ba, to, bidia'ce makaruhiya kamar yadda ya gabata a cikin Babin Wanka.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga na bidi'o'i a cikin Babin Taimama. Kallafa wa kai yin alwala tare da samun lalura ta shari'a ta yin Taimama kamar tsoron mutuwa ko rashin lafiya ko ƙishi, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai domin cutar da kai ne. Yana daga ciki, barin taimama ga mai janabar da ya rasa ruwa har lokacin salla ya fita, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai in an jinkirta har lokacin mukhtari ya fita, shi ma bidi'a ce haramtacciya, bisa ga haduwar malamai in an jinkirta har lokacin muktari ya fita ban da laruri.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga, shi ne yin taimama ba tare da lalura ta shari'a ba, na rashin ruwa ko rashin ikon amfani da shi, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai, kuma sallar wanda ya yi ɓatacciya ce, bisa ga haɗuwar malamai, kuma ba a lissafa shi daga cikin masallata koda ya ɗauka da cewa, yana daga cikin masallata. Yana daga cikin abin da suka ƙaga, shi ne maimaita shafar gaɓoɓi bayan game su da shafa, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki abin da suka ƙaga a cikin Babin Haila da Istihala da Jinin Biƙi: Yin azumin mata a cikin kwanakin haila, bidi'a ce muharrama, bisa haɗuwar malamai. Yana daga cikin haka, yin sallar mace a cikin kwanakin haila da kuma rashin sallar mace a lokacin jinin Istihala, shi ma wannan bidi'a ce muharrama bisa ga haɗuwar malamai. Yana daga cikin bidi'a, mace ta nutsar da yatsunta a cikin farjinta domin wanke cikinsa bayan ɗaukewar jinin haila, shi ma bidia'ce muharrama, bisa ga haɗuwar malamai domin hakan cutarwa ne gare ta, da kuma mijinta, domin idan ruwa ya shiga cikin farjinta tare da yatsanta sai ya sassauta shi, ya faɗaɗa shi. Yana daga cikin haka, zaman mace bayan ɗaukewar haila ba tare da salla ba har sai ta wanke tufafinta, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin haka, abin da sashin mata suke aikatawa, shi ne macen da ta haihu za ta zauna kwana arba'in ba tare da wanka ko salla ba, ko da jininta ya ɗauke, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, domin jinin biƙi idan ya ɗauke, ko da ranar haihuwa ce sai ta yi wanka, ta yi salla in ya ci gaba, ta zauna watanni biyu (Bayan wata biyu sai ta yi wanka ta cigaba da salla, ko jinin biƙi bai ɗauke ba).

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Lokutan Salla: Gwamutsarsu (wato, yin salla ba tare da tabbatar da lokacinta ya yi ba), shi ma bidi'a ce haramtacciya. Bisa ga haɗuwar malamai domin zai iya yin salla kafin lokacinta, kuma sai ta kasance ɓatacciya. Yana daga ciki: Dogaro wajen shigar lokaci a kan masaukan taurari a bisa hanyar tabbatarwa, shi ma bidi'a ce

haramtacciya bisa haɗuwar malamai, domin masaukan taurari an shar'anta su don a gane kusantowar asuba.

Yana daga cikin bidi'a, jinkirta salla har lokacinta ya fita. Shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, idan an yi nufin lokaci na laruri ya wuce. Amma bisa magana shahararriya ko da in an yi nufin lokacin mukhtari.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Al'amuran masallata yawaita su a cikin unguwa ɗaya shi ko bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin bidi'o'i: Shimfiɗa shimfiɗu cikin masallatai, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Riƙon mafifitai a ciki shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Rubutun littafin Alƙur'ani ko na ilimi a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya yana daga ciki koyar da ƙananan yara a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya yayin da yaran ba sa yin wasa a cikin: Idan ko suna yin wasa, to, bidi'a ce haramtacciya bisa ga abin da aka sani. Yana daga ciki, ɗaga murya a ciki, koda da ilimi ne, shi ma bidi'a ce makaruhiya, sai dai in ya kasance ɗaga muryar da ilimi don isarwa ne.

Yana daga Ciki: Ba da ƙissoshi a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Saye da sayarwa a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Yin roƙo ko bara a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Cin abu mai yawa a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Aske gashi a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Yanke farce a ciki shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Yin ɗinki a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Yin alwala a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga Ciki: Barin dabbobi su shiga a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin bidi'a shi ne cigiyar ɓataccen abu a ciki, ita ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin kiran Salla da Iƙama. Kiran sallar ladanai jama'a da sauti ɗaya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki, yin marairaita, wato karkatse sauti da makyarkyata, shi ma bidi'a ce makaruhiya matuƙar bai yi muni ba amma idan ya yi muni, to, bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abubuwan bidi'a, shi ne yawaita kiran salla lokaci bayan lokaci, bayan fitowar alfijir a masallaci ɗaya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki kiran salla ba da lafazin Kiran sallar, ba kamar a shirya a halarto, shi ma bidi'a ce makaruhiya ko kuma mustahabbiya. Yana daga cikin bidi'a Yin istigfari kafin tayar da iƙama. Wato, ladan ya yi "Astagfirullaha" sau uku, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Salla. Rashin shirya sahu, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga cikin bidi'a yin sujjada a kan shimfiɗu (darduma) shi ma bidi'a ce makaruhiya, in ya kasance shimfiɗa mai taushi, amma yin sujjada a kan tabarma mai kauri, shi kam ya halatta, sai dai barin sujjada a kai, shi ya fi kyau, idan bai zama lalura ba kamar zafin rana ko sanyi ko kaushin ƙasa. Yana daga cikin bidi'a Cewa haramar salla, lokaci ya yi, ita ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin bidi'a: Bayyanar da niyya, shi ma bidi'a ce makaruhuya, sai dai saɓani a wurin lafazi ne, shin bidi'a ne ko a'a? Magana shahararriya ba bidi'a ba ce. Yana daga cikin bidi'a keɓance karatun wata sura a cikin salla da wata sura sananniya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga cikin bidi'a: Isarwar jama'a da sauti ɗaya, ita ma bidi'a ce makaruhiya. An yi saɓani a kan ko an yarda a yi ladani ɗaya? Mai jiyarwa. Shin halal ne ko a'a? Magana da aka dogara a kanta ita ce ya halatta da kuma halattar yin koyi da shi.

Yana daga cikin bidi'a yin ƙari a cikin tasbihi: 'Subhanallah, walhamdulillah wallahu akbar a kan talatin da uku, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga cikin bidi'a, yin addu'a bayan salloli da wata siffa sananniya, ita ce liman ya yi addu'a, mutanne suna cewa amin, shi ma bidi'a ce makaruhiya a cikin Mazahabar Imamu Malik. Amma wani cikin malamai ya ce bidi'a ce kyakkyawa. Waɗannan kuwa suka ce; kowa ya yiwa kansa addu'a. Asali shi ne kowa ya yi wa kansa addu'a sai dai ba a samu saɓani ba cewar ba a ga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) yana shimfiɗa da hannunsa yana addu'a, mamu suna cewa amin da dalilin addu'arsa ba, haka nan halifofinsa shiryayyu bayansa yardar Allah ta tabbata a gare su. Kuma duk abin da Annabi bai aikata ba, kuma wani daga cikin sahabbansa bai aikata ba, babu shakka barin sa ya fi aikata shi. Yana daga cikin bidi'a, yin musabaha bayan sallar asuba da Juma'a, kai bayan ƙare salloli' ma duka guda biyar, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin bidi'a: Salla ranar Alhamis ɗin farko ta watan Rajab da daren tsakiyar Sha'aban da daren ashirin da bakwai na watan Rajab da sallar ban-kwana da Ramalana, da sallar Ashura da sallar Kabari da sallar iyaye da

sallar mako. Dukkan waɗannan bidi'o'i ne ce makaruhai. Yana daga cikin abin da ake riskarwa da waɗannan bidi'o'i ɗaura carbi ga damtse, kamar yadda mace take ɗaure warwaro a hanunta ko kuma rataya shi a wuya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Amma shi carbi kansa halal ne.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin ramuwar kuɓutacciyar sallar. Rashin rama ta don dogaro da cewar nafilfili za su toshe kafar farillai. Shi bidi'a, ce haramtacciya a kan shahararriyar magana. Yana daga cikin bidi'a sallar da suke yi a Juma'ar ƙarshe daga Ramalana, suna riya cewa wanda ya sallace ta ta wadatar da shi daga ramuwar kuɓutattun salloli, ita ma bidi'a ce makaruhiya, cikin karan kanta, amma riyawar da suke cewa tana wadatarwa ga barin ramuwa, shi kam ƙarya ce daga wurinsu da kuma ƙirƙire.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Rafknuwa: Kawar da kai daga yin gyara ga sallar da aka yi rafkanuwa a cikinta, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Wani cikin malamai ya ce idan mai salla ya kawar da kai daga gyaran salla, sallar ba ta gushe ba ana bin sa bashi har sai ya gyarata.

Yana cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Sallar Matafiyi: Barin ƙasaru, shi ma bidi'a ce makaruhiya. A game da ra'ayin malaman da suka ce sallar ƙasaru wajiba ce barin yenta bidi'a ce haramtacciya. Kuma barin sallar ƙasaru bidi'a ce makaruhiya a kan ra'ayin waɗanda suka ce sallar ƙasaru sunna ce.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin babin Sallar Juma'a: Yawaita masallatan Juma'a a gari ɗaya, shi ma bidi'a ce haramtacciya a bisa magana shahararriya. Yana daga cikin bidi'a, ɗaukaka hasumiya sosai, shi ma bidi'a ce haramtacciya, bisa ga haɗuwar malamai. Idan an yi nufin alfahari da ita, to, bidi'a ce haramtacciya. Idan ba don alfahari ba ne, to, bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Ɗaukaka murya yayin huɗuba shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Yin nafila bayan sallar Juma'a a cikin masallacin, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin babin Sallar idi: Haɗuwar mutane a ƙofar gidan liman ranar Idi kafin a fita zuwa masallacin Idin, ita ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Buɗa murya da kabbara har maƙogwaro ya dishe shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Tafiyar da kabbarbari a murya ɗaya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Jinkirta sallar idan har sai ranar ta yi zafi, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Kodayake lokacin na miƙuwa har zuwa zawali.

Yana daga ciki: Yini a masallacin Idi, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin addu'a a ranar idi lokacin haɗuwa da juna, shi ma bidi'a ce

haramtacciya ko halattacciya, ko mustahabbiya, amma a farko shi ne daidai. Yana daga ciki: Tafiya a kan muryar wani a cikin kabbara a bayan salloli biyar na cikin ranakun Idi da kuma isarwar wanin liman ita ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga: Babin Jana'ida da maƙabarta. Wanda ke yi wa mamaci talƙinin ka ce La'ila ha Illallahu, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin zikiri yayin yi wa mamaci wanka, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki sanya auduga a duburar mamaci da cikin hancinsa da maƙogwaronsa shi ko bidi'a ce haramtacciya, domin keta alfarmar mamaci ce.

Yana daga ciki: Ayyana wani ɓangare da za a fara da shi wurin ɗaukar gawa, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Kururuwa mai girma da yin kuka yayin fitar da mamaci, ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga ciki: Sassarfar masu ɗauke da gawa ita ma bidi'a ce haramtacciya domin cutar da mamacin yana daga ciki; tafiyar masu ɗauke da gawa hankali da jinkiri, ita ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Yin zikiri yayin ɗaukar gawa, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Raka gawa zuwa maƙabarta da karatun ƙur'ani, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Takardar da ake maƙala wa mamaci a cikinta akwai ayoyin Alƙur'ani da sunayen Annabawa ko wanin haka, daga abin da yake da wata alfarma, ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa magana shahararriya domin sashin jikin mamaci zai cuɗanya da takardar a cikinta akwai ayoyin Alƙur'ani ko sunayen Allah ko na Annabawa, ko wanin wannan daga abin da yake maialfarma. Haƙiƙa, sashin malamai sun ga yana da kyau takardar da ake rubutawa ake kira na alƙawari, a sanya ta a ƙirjin mamaci a cikin ƙabari. Ta ƙare.

Na ce wannan yana daga cikin abin da bai kamata ba saboda abin da ambaton sa ya gabata na cewa sashin jikin mamacin zai cuɗanya da takardar, kuma a cikinta akwai ayoyin Alƙur'ani a ciki da sunayen Annabawa ko waninsa daga cikin abin da yake da alfarma. Magana ta daidai da a ce aikata shi ya kuɓuta a gina ƙabarin a gefen gabas daga gare shi, wanda zai nisantar da ita daga mamacin, sai a sanya takardar a cikin haka kamar yadda sashin malamai, sai dai aikata shi ba ya kuɓuta koda wannan dabara domin bidi'a ce alheri gaba ɗaya. Yana nan a cikin bin Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi.)

Yana daga ciki: Rashin amfani da ruwan gidan da mamaci ya mutu a ciki shi ma bidi'a ce. Yana daga ciki wanke gaɓɓai daga kufan mamaci yayin

dawowa daga binne shi kafin a shiga gida, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Keɓance ranakun ta'aziyya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Idan keɓance waɗannan kwanakin da haramcin ta'aziyya, ba a cikin kwanakin da yake ba su ba, in kuwa ya zama haka, to, bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai. Sashin wasu mutane suna yin wannan bidi'ar gaishe da mara lafiya, yana cewa ba a gaishe da mara lafiya ranar Asabar.

Yana daga ciki: Taruwar mutane don yin fidda'u, ita ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Abincin da iyalan mamaci suke yi sai mutane su tattaru domin haka, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Madalla da sadakar da za ta amfani mamaci amma idan ta dace da sunna, a yi sadakar gare shi ba tara mutane ba. Yana daga ciki: Yin gini a kan Kabari, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Idan ba a yi nufin alfahari da shi ba idan ko an yi nufin alfahari, to, bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai, saɓanin ɗora dutse a wurin kansa don yin alama, shi wannan sunna ne.

Yana daga ciki: Dasa bishiya a wurin Kabari don alama, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Riƙe Masallaci a wurin Kabari domin neman tabarruki da yin salla a ciki, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Kuma a wata maganar an ce halal ne, amma magana ta daidai ita ce ta farko. Yana daga ciki neman tabarruki da yin salla a kan ƙabari shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Shafar Kabari don neman tabarruki, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Yin shafa da ruwan da ke kan Kabari don neman tabarruki, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Ɗebo turɓaya daga Kabari don neman tabarruki shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Karanta Alƙur'ani da yin zikiri a kan Kabari, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Kuma an ce game da yin karatu a kan Kabari ko kuma sunna ce mutum ya zauna a kan Kabari bayan binnewa tare da shagaltuwa da karatun Alƙur'ani da zikiri don a ɗebe wa mamaci kewa da shi gwargwadon yadda za a soke raƙumi kuma a raba namansa.

Na ce: "Abin da ya ke daidai shi ne abin da ya gabata na karhancin haka domin Mazhabar Imam Malik, karhancin karanta Alƙur'ani a kan Kabari sai dai wasu cikin malamai sun so yin haka domin abin da ya inganta na samun bushara da saduwarta ga mutum. Na ce a bisa ga kuɓutar wannah bai kamata ba a karanta ayoyin azaba ko umarni ko hani don kada ta kasance hujja ga mamaci. Yana daga ciki: Ɗora Alƙur'ani a wurin Kabari don neman tabarruki, shi ma bidi'a ce makaruhiya ko kyakkyawa.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Zakka: Jinkirta bayar da ita bayan wajabtar ta sai zuwa ranar Ashura, shi ma bidi'a ce haramtacciya

bisa ga haɗuwar malamai domin yana wajaba a kan kowa ya bayar da zakkar dukiyarsa da cikar shekararsa. Yana daga ciki: Ɓoye ta don ciyar da baƙi, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai ta fuska biyu: Fuska ta farko, jinkirta ba da zakka ga wanda ya cancanta lokacin wajabci. Fuska ta biyu. Yiwuwar kasancewar wani baƙin ciki bai cancanta ya karɓe ta ba.

Yana daga ciki: Bayar da ita ga limamin sallar Ashan ya zama ladan limancinsa, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, domin haka ba ya isarwa, idan wanda aka ba ya cancanci a ba shi domin an ba shi ita ne a matsayin lada. Yana daga ciki: Bai wa makusancinsa da shi bai lazimce ta ba fiye da abin da zai ba waninsa, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Keɓance Na'ibi makusancin mai dukiya da ita da kuma fifita su, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Abin da suka ƙaga a cikin Azumi: Yin Azumin ranar shakka domin a gewaye da shi daga Ramalana shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Yin zikiri bayan kowacce sallama biyu daga sallar Asham, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin tashe, shi ma bidi'a ce makahuriya. Kuma an ce yin tashen halal ne kuma an ce mustahabbi ne, amma magana ta daidai ita ce ta farko.

Yana daga ciki: Haɗuwar mutane don sauke Alƙur'ani a daren ashirin da bakwai ga watan Ramalana, ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai, bisa ga abin da mutane suka saba da shi a cikin wannan zamani na cuɗanyar maza da mata da waƙe-waƙe masu muni cikin karatu da jayayya a cikinta a bisa fuskar fariya. Amma idan ya wofinta daga dukkan waɗannan abubuwan ƙyama, to, shi, bidi'a ce makaruhiya ko halastacciya. Yana daga ciki halarto kwanukan ruwa a cikin masallaci yayin saukar shi ma bidi'a ce makaruhiya.

To, idan ka ce mene ne hukuncin karatu da zikirin Jama'a a kan murya ɗaya? Na ce lallai yana daga bidi'a makaruhiya, a cikin Mazhabar Malikiya. Idan ka ce mene ne hukuncin abin da mutane suke yi a watan Rabi'ul Auwal a ranar Maulidi ko ranar bakwai daga maulidi na haɗuwar mutane don zikiri da abincin da suke yin shi don haka? Na ce lallai shi bidi'a, ce makaruhiya, idan ya wofinta daga dukkan saɓo.

Kuma an ce magana ta yi daidai cewa yin Maulidin Annabi mai daraja yana daga bidi'a kyakkyawa ko mustahabbiya idan ya wofinta daga dukkan saɓo, amma abin da mutane suka saba da shi a wannan zamani a ciki na cuɗanyar maza da mata. Muna neman tsarin Allah. Wani ya ce ya hallata.

To, idan ka ce mene ne hukuncin wanda ya yi abinci kawai a ranar Maulidi ya yi niyyar Maulidi da shi, ya kira yan'uwa tare da kuɓuta daga saɓo? Na ce shi kam bidi'a ce makaruhiya ko mustahabbiya kuma shi ne zaɓaɓɓe.

To, idan ka ce mene ne hukuncin abincin ranar Ashura? Na ce mustahabbi ne in ya kuɓuta daga ƙallafa wa kai da kuma riƙon shi sunna babu makawa daga gare shi. Idan ko ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya.

To, idan ka ce mene ne hukuncin abincin ranar Idi? Na ce lallai sunna ce in ya kuɓuta daga ƙallafa wa kai da kuma riƙon shi, sunnar da ba makawa daga gareta. In ko ba haka ba, to, ya zama bidi'a ce makaruhiya. To, idan ka ce mene ne hukuncin abincin ranar layya? Na ce ban tsayu a kan hukuncinsa ba sai dai zaton cewa, halal ne in ya kuɓuta daga ƙallafa wa kai da ƙin sunnar da ba makawa daga gareta da shagaltuwa da shi kafin sallar Idi da yanka layya idan ba haka ba, to, shi bidi'a ce makaruhiya. Abin da aka sani a wannan yini shi ne zubar da jini.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Hajji: Sumbantar Baƙin Dutse da fitar da sauti, shi, bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki, ɗora kumatu biyu da goshi a kan dutsen, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Shafar bangon Ka'aba ko bangon masallaci shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki yin talbiya a murya ɗaya, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Keɓantar wurare da keɓantattun addu'o'i, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Tafiya da baya da baya yayin fita daga masallacin Makka, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Haka nan tafiya da baya da baya yayin fitowa daga masallacin Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) yayin bankwana gare shi (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi.)

Yana daga ciki: Yin haka tare da manyansu da wurin ƙaburburan da suke girmamawa kuma suke girmama iyalansu, suna riya haka yana daga babin Ladabi. Kuma kwatankwacin wannan bidi'ar abin da sashinsu yake yi na ɗawafi a Kabarin Annabi (tsira Allah da amincinsa su tabbata a gareshi) haka nan tafiyar da suke a wurin gini suna jefa hankicinsu da tufafinsu. Wananan dukkansu bidi'a ce makaruhiya, domin neman tabarruki yana kasancewa da bin Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi), kuma ibadar Jahiliyya ga gumaka ba ta kasance ba sai ta wannan gefen.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Yanka mai keɓance masu surorin Alƙur'ani da yin yanka gare su, sai dai bisa nuna godiya ba bisa hanyar shirka ba, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Amma idan babu keɓancewa, to, babu mai zargi sai dai ma yana cikin abin da za a yaba, domin Umar ɗan

Khaɗɗab (Allah Ya ƙara masa yarda) ya soke ruƙumi yayin da ya haddace Suratul Baƙara domin godiya ga Allah.

Yana daga ciki begen rai ga yin musanya a cikin rabon naman layya na ya ba da naman don a ba shi tukuicin musanya a kan haka, bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai domin layya ba a bayar da musanyarta. Yana daga ciki: Taron mutane a wurin haƙiƙa (suna), shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Idan ka ce mene ne hukuncin fuskantowar mata da guɗa yayin haihuwa? Na ce lallai bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai a kan dogaron cewar muryarsu, al'aura ce bisa shahararriyar magana. Idan ka ce mene ne hukuncin abin da sashin mata suke yi na sanya wuƙar da aka yanke cibiyar abin da aka haifa a wurin kansa matuƙar mamansa tana zaune a wurin kansa, idan ta tashi sai ta ɗauke ta tare da ita har tsawon kwana arba'in, wai tana yin haka don kada aljani ya shafe shi! Na ce lallai wannan bidi'a ce makaruhiya.

To, idan ka ce mene ne hukuncin abincin haihuwa da ake bayarwa tun daga ranar haihuwa har zuwa ranar suna? Na ce lallai shi kam halal ne in ya kuɓuta daga ƙallafa wa kai da kuma alfahari in ko ba haka, to, bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai. To, idan ka ce mene ne lokacin sanya wa yaro suna? Na ce lokacin yanka dabbar suna. Kuma ya kamata in yaron za a yanka masa rago ba za a faɗi sunan ba sai yayin da za a yanka ragon in kuma ba za a yi masa yanka ba saboda talaucin mahaifinsa, to, a ambaci sunansa a duk lokacin da aka ga dama a rana ta bakwai.

To, idan ka ce mene ne hukuncin sanya waɗannan laƙubba? Wane addini kamar Zakiyyuddini da Mahyiddini Alamuddini da makamantan haka? Na ce lallai wannan bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai in an yi nufin alfahari da tsarkake kai, in ko ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya ko halastacciya. Suna sanya su ne ga malamai kawai a rashin alheri amma su sun kuɓuta daga yarda da su.

To, idan ka ce shin ya halatta malami ko wani babba da sunansa? Na ce lallai ya halatta kodayake saɓanin abin da ya dace ne idan ba a ga ƙyamar haka daga wurinsa ba, in ko ba haka ba, to, ya kasance ta hanyar kayar masa da mutunci domin saɓa wa abin ma da aka saba kiran su da wasu laƙubba. Idan ka ce mene ne hukuncin wasu laƙubba sanannu a ƙabila kaza kamar ya wane a maza, ya wance a mata? Na ce lallai waɗannan laƙubba halal ne a karan kansu domin babu ma'anar tsarkaka a cikinsu kodayake suna nufin

girmamawa da su, amma fusatar su ga wanda ya bar kiransu da su, ya kira su da sunansu na yanka da kuma zargin su gare shi bai halatta ba.

To, idan ka ce ba mu labarin alkunya ta shari'a. Na ce alkunya ta shari'a yi wa mutum alkunya da ɗansa ko ɗan waninsa haka nan ma mace ana yi mata alkunya da ɗanta ko ɗan waninta. Haka nan mace ana yi mata alkunya da ɗanta ko ɗan waninta. Haka nan kuma ya halatta a yi wa mutum alkunya da wani hali da ya siffantu da shi kamar baban Turɓaya da Baban 'Yarmage.

To, idan ka ce ana yi wa ƙaramin yaro alkunya? Na ce babu laifi da yin haka sai dai barin sa, shi ya fi. A zahirinsa na ba da labari da ƙarya domin yaro ba ya haɗa.

To, idan ka ce mene ne hukuncin sanya suna da sunan Mala'ika kamar Jibril da Mika'il da makamantansu? Na ce lallai wannan makaruhi, kamar yadda Imamu Malik ya tafi a kai. To, idan ka ce sunan Malik ya shiga cikin wannan karhancin? Domin Malik shi ma suna ne na Mala'iku? Na ce ba ya shiga domin ba ya ayyana ga Mala'iku kawai. To, idan ka ce mene ne hukuncin sanya suna da munanan sunaye kamar yaƙi da ci-guna? Na ce lallai wannan makaruhi ne.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Rantsuwa. Yin rantsuwa da Annabi ko Ka'aba ko waliyyi ko makamancin wannan. Ita, bidi'a ce haramtacciya, ita ce, shahararriyar magana ko kuma makaruhiya. Yana daga ciki: Gaggawar yin kaffarar rantsuwa da azumin kwana uku tare da yana da ikon 'yanta wuya ko tufatar da mutane goma ko ciyar da su ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai domin Allah Madaukaki Bai yi umarnin azumin kwana uku ba a cikin kaffarar rantsuwa sai bayan an kasa daga abubuwa uku.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Alwashi: Alwashi mai maituwa kamar alwashin azumin kowacce Alhamis ko Litinin, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin alwashi ratayayye kamar idan Allah Ya warkar da mara lafiya ne ,to, zan yi sadaka da kaza, shi ma bidi'a ce makaruhiya, ko halattacciya.

Yana daga ciki: Alwashin ko kuɓuta kamar 'yanta bawan da ɗawainiyarsa ta yi ma nauyi saboda ƙarancin amfaninsa domin kuɓuta daga gareshi, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Alwashin ƙuntata kamar alwashin abu mai yawa da zai wahalar, shi ma bidi'a ce makaruhiya, in ya kasance yana iyawa, idan ko ba haka ba, to, bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin babin Aure. Amsar shugabannin sadakin mata, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Walima da ake gwama ta da ɓarna, ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Amma ba don ana ƙyamar walimar aure ba ne, ai ita, sunna, ce a bisa fuskar shari'a. Yana daga ciki: Abin da mata take karba daga mijinta na haƙƙin shimfiɗa, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai domin ya yi kama da zina.

Yana daga ciki: Yin jima'i alhali idanuwa suna kallo, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa magana sananniya domin al'aura ya wajaba a rufe ta. Yana daga ciki: Zuwa mata alhali tana rafkane gabanin ya yi wasa da ita; ya yi mata barkwanci, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Guni da magana yasasshiya yayin jima'i, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Zuwa mata ta duburarta, shi kuma bidi'a ce haramtacciya. Yana daga ciki: Tsiraituwar miji da mata yayin jima'i shi ma bidi'a ce Makaruhiya. Yana daga ciki: Suranta wata mata, manisanciya yayin jima'i da matarsa, kamar sai yana jima'i da ita, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa sananniyar magana. Kuma haka hukuncin yake ga mata ta suranta wani mutum manisanci yayin haka kamar yana jima'i da ita.

Yana daga ciki: Bayar da labarin miji ga wani na abin da ya kasance tsakaninsa da matarsa yayin jima'i shi ma bidi'a ce makaruhiya, domin wannan zai farar mazaje manisanta da mata da soyayya, haka nan bayar da labarin wata mata daga cikin mata.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Ciniki. Barin jahili a cikin kasuwa yana sayarwa don kansa, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Umar (Allah Ya ƙara masa yarda) ya kasance yakan yi duka da kwagiri ga wanda yake yin haka alhalin shi, jahili, ne. Yana daga ciki: Wakilta jahili a kan ciniki, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai, domin shi bai san abin da ya halatta ko aka hana ba.

Yana daga cikin zaman maza a gida su kuma mata su fita zuwa kasuwanni suna gwamutsuwa da maza, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai kuma kamanceceniya ce da Turawa domin matansu suna saye da sayarwa a cikin shaguna, maza kuma na gida. Haƙiƙa, shari'a ta hana kamantuwa da su idan ya kasance iyalan mutum na da ɓuƙatar sayen tufafi ko kayayyakin kwalliya, yari ko wasunsu, to, sai ya jibinci wannan da kansa in ya kasance yana da masaniya a kai ko wanda zai tsaya matsayinsa da wannan bisa harshen ma'abuta ilimi. Kada ya ba su damar fita yanke ga waɗannan

abubuwan domin sa iya kaiwa ga bayyanannen makirci wanda da yawa daga cikinsu ke yi shi ne sakin fuska ga mazaje manisanta.

To, idan ka ce shin ya halatta fitar budurwa zuwa kasuwa domin saye da sayarwa idan ta kasance ta rufe jikinta kuma ta kaɗaita ta wofinta ta ko wane abu da shari'a ta ƙyamata. Misali, gwamutsuwa da maza da kuma sakar masu fuska! Na ce lallai wannan halal ne idan an rasa wanda zai wakilce ta daga miji ko muharrami. Idan aka samu haka, to, ba ya halatta gareta ta fita domin fitarta fitina ce. Idan kuma ba wadda za a fitunu da ita ba ce, to, an karhanta mata fita, domin hanin gamamme ne, sai dai abin da aka togace na tsohuwa wadda ba buƙatuwar maza zuwa gareta.

Idan mace ba ta samu wanda zai wakilce ta ba daga waɗanda ambatonsu ya gabata, to, ta aika wadda za ta wakilce ta daga cikin mata tsofaffi waɗanda ba a kallo zuwa gare su kuma ba a damuwa da su, babu fitina a cikin surarsu ko cikin maganarsu. Idan waɗannan duka suka gagara, to, buƙatar ta fita ko dai ta kasance ta dole ko dai kayayyakin abinci ko tufa waɗanda za ta rufe jikinta da su ko a'a. Idan ta kasance ta dole kamar wanda muka ambata, to, ta fita kuma fitarta ta kasance a kan yaddar shari'a ta yarda a fita.

Idan ko buƙatar ba ta dole ba ce kamar kayayyakin ƙawa, to, ta haƙura shi ne mafifici gare ta kuma mafi yawan lada.

To, idan ka ce mene ne hukuncin fitar mata a kan masu yawo suna sayar da auduga ko waninta a cikin ƙauye? Na ce lallai wannan haramun bisa haɗuwar malamai domin ba ya halatta ga mace sai dai ga mijinta ko muharraminta, saɓanin abin da mata suke yi a wannan zamani. Misalinsa, mai sayar da munduwa ko warwaro ko auduga ko tufafin ado ko wanin wannan na abubuwan buƙatarsu ya je ƙauye, wani lokaci zai kaɗaita da mace. Wannan haram ne bisa haɗuwar malamai.

Wani lokaci kuma ta zo da wata cikin mata sai su taru gare shi saboda haɗuwarsu sai fira da shi ta auku da dai abubuwan da aka hana a shari'a mai daraja domin da yawa daga cikinsu, za su fita ba tare da hijabi ba ko ya kasance ta gajerun kayayyaki da makamantansu daga abin da yake sananne ne daga al'adunsu munana a waɗannan zamuna.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Tsayar da Haddi. Tsayar da haddi a kan mara galihu kawai ban da mai daraja. Yana daga ciki: Yarɓar da yawa daga cikinsu, kamar haddin zina, jefewa, ko bulala a wadatu da kuɗi don kwaɗayi. Wannan bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Hukunce-Hukunce: Gabatar da Jahilai a kan malamai da jiɓintar da muƙamai na shari'a ta hanyar gado ga wanda bai dace da shi ba, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Yin hukunci a kan jahilci, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai domin jahilai ba a bin su.

Yana daga ciki: Yin hukunci a kan ƙabilanci don bin son rai, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Domin son rai ba a bin sa. Yana daga ciki: Yin hukunci bisa cin-hanci, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Gado: Karɓar da shugabanni ke yi na kayayyakin mamaci, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Mamayar babban magada a kan dukkan dukiya. Yana cewa "wannan dukiyar 'yan'uwana ce ni ina matsayin babansu" ya riƙa tasarrufi a cikin dukiyar yadda ya ga dama ba mai iya gitta masa magana a kan tsawon rayuwarsa, har idan ya mutu sai mai ƙarfi ya mamaye dukiyar.

Yana daga ciki: Ba da gado ga kawu, ko ɗan yar'uwa na dukiya tare da samun magada, su ba za a ba su komai ba, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Rashin ba da gado ga wata mata cikin mata, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Kaciya. Jinkirta ta zuwa balaga, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai domin kware al'aurarsa bayan balaga, haramun ne. Yana daga ciki: Tsorata yara don kar su yi kuka yayin kaciyar, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Saurara wa yaran da suka kai lokacin kaciya, har waɗanda suke ƙasa da su su kai lokacin sai a yi musu kaciya tare a rana guda, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Idan wannan sauraron ya kai ga balagarsu, in ko ba haka ba, bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Tattara yara a sahara, shi ma bidi'a ce haramtacciya, yayin da aka rasa aminci a saharar ko aka ji tsoron tozarta, in ko ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Tattara mata yayin yi musu kaciya a cikin daki guda suna wasa da bai halatta ba na waƙe-waƙensu da karkaɗa mundayensu da shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga cikin abin da wasu sashin shaiɗanu suke yi saboda abincin kaciya na wargi da wasanni da haɗuwar maza da mata. Wannan haramun ne bisa haɗuwar malamai. Amma yin wannan abincin idan bai gwamu da waɗancan abubuwan ƙyama ba, halal ne.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Aski. Aske kai baki ɗaya. Shi, bidi'a, ce makaruhiya. Idan babu wata musanya in ko ba haka ba, to, bayyananniyar mazhaba halarcinsa. Yana daga ciki: Yin tukkuwa shi ne a bar gashi a goshi babu komai na gashi a kai, haka nan tsaga kai wannan bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Aske gashin kai yayin tuba, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Daga cikin malamai akwai wanda ya halatta shi; ya yi ƙiyasinsa a kan askin mai aikin hajji kasancewar gashin, zunubi ne ya kamata a gusar da shi. Na ce abin da ke daidai barin sa domin shi, bidi'a ce. Alheri gaba ɗayansa yana cikin bin sunnar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi).

Yana daga cikin abubuwan da suka haddasa shi ne: Kin gyara gashin baki, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai, a Mazahabar Malikiyya ko kuma makaruhiya. Yana daga cikin wannan. Aske gemu da hana ƙarya, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa ga abin da aka sani ga mashahuriyar magana. Yana daga ciki: Aske ƙarƙashin haɓa, shi ma bidi'a ce makaruhiya sai dai babu laifi wurin yin haka don ƙawa.

Daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Tufafi. Tsawata hannun riga da faɗa ɗa shi, shi ma bidi'a ce makaruhiya ko kuma an ce wannan bidi'a ce halastacciya, ko kuma mustahabbiya, a cikin waɗannan zamunna ga limamai da Alƙalai da shugabanni. Na ce maganar daidai, an so ga namiji ya gajarta tufafi zuwa rabin ƙwaurinsa; ya halatta zuwa idon sawu, abin da ya ƙaru, in ya yi nufin taƙama, haramun ne. In ba haka ba, an Karhanta (Anƙi).

Domin abin da ake so ga tufafin namiji, tsarkakar tufafi da tsakaitawa a cikin jinsinsa da kasancewarsu tufafin ƙima ne ba masu kayar da mutuncin jinsinsa ba wanda ba zai kai ga fita dangi ba wanda ya shahara a ba sassa biyu. Haƙiƙa, shari'a ta zargi waɗannan sassan biyun. Amma ita mace ta samu ta ja zaninta a bayanta gwargwadon kamu guda ko kamun zira'i domin buƙata da ta kira zuwa yin hakan ita ce suturtawa. Saboda mace dukkaninta al'aura ce in ban da fuska da tafukan hannu.

Yana daga ciki. Kurman naɗin rawani, shi ne mutum ya naɗa rawani ba tare da ya saki jelar rawanin ba, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Wani daga cikin magabata ya ce rawani ba tare da jela ko tsoro ba, ba makaruhi ba ne. Na ce maganar daidai ita ce abin da ya gabata na cewa makaruhi ne.

Yana daga ciki: Naɗa rawani da girma, shi ma bidi'a ce makaruhiya domin gwargwadon rawani shi ne tsawon kamu bakwai faɗin kuwa kamu ɗaya. Annabi (tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) yana da farin rawani, tsawonsa kamu bakwai; faɗinsa, kamu ɗaya. Amma tsoron rawani ba

ya daga cikin rawanin. Kuma Annabi (tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) yana da baƙin rawani, tsawonsa kamu bakwai, faɗinsa kamu ɗaya. Tsoron rawani yana daga cikin tsawon rawanin.

Kuma an ce girman rawani ba makaruhi ba ne a waɗannan zamuna, sai dai ma yin hakan halal ne, ko mustahabbi ma, ga limamai da alƙalai da shugabanni. A kan wannan, aka ce ku girmama rawaninku kuma ku faɗaɗa hannuwan rigunanku domin ɗaukakawar addini.

Na ce abin da yake daidai shi ne wannan makaruhi ne, idan ya kai iyakar girma mai muni ga al'ada. To, idan ka ce mene ne gwargwadon abin da za a saki daga rawani? Na ce shi ne gwargwadon tsawon yatsa huɗu, sai dai magabata sun kasance suna sakin gwargwadon kamu guda da ma sama da haka kaɗan ko ƙasa da haka kaɗan. Kuma ana sakin gefen rawanin ta tsakanin kafaɗu biyu. Annabi (tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) yana yin rawani ya saki gefen rawaninsa tsakanin kafaɗunsa. An karɓo Hadisi daga Aliyu shi ya ce: Annabi (tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) ya naɗa mini rawani, ya saki gefensa a kan kafaɗata, kuma ya ce:

العمامة جائز بين المسلمين والمشركين.

***"Rawani shi ne bambamci a tsakanin Musulmi da mushrikai."***

Yana daga ciki: Namiji ya nannaɗe kansa, shi ne ya rufe kansa da mayafinsa, ya mayar da gefensa a kan ɗaya daga kafaɗunsa, shi ma bidi'a ce makaruhiya domin shi, wannan, ya keɓanta da mata ne sai fa in don lalura ce kamar zafi ko sanyi. Yana daga ciki: Rashin tsiraituwa daga tufafi yayin barci, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Domin sunna a kan shimfiɗa tsairatuwa daga tufafi matuƙar bai wuce shekara arba'in ba. Yana daga ciki: Zaman mace tare da mijinta da mafi munin tufafi, idan tana son fita ta duba ga mafi kyawun abin da ke gare ta na tufafi da kayayyakin ƙawa ta sanya su ta fita, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai.

Yana daga cikin abin da suka ƙirƙiro a cikin babin abinci da abin sha: Yin abinci na musamman ga maigida da kofuna keɓantacciya gare shi, shi ma bidi'a ce, haramtacciya bisa haɗuwar malamai idan ya yi nufin girman kai da shi. Yana daga ciki: Cin abinci da cokula ko waninsu, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Sai dai in ya kasance yana da uzuri domin babin masu uzuri suna da hukuncinsu da ya keɓanta da su.

Yana daga ciki: Yanko loma kafin ya haɗiye ta gabaninta, shi ma bidi'a ce Makaruhiya. Yana daga ciki: Karya waina da wuƙa da gatso ta da fizgar ta da haƙora, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin ba'a lokacin cin

abinci, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin labari a kan abinci ko kuma barin magana gaba ɗaya, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Cin abinci ba tare da halarto da ruwa ba, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Cin abinci mai zafi shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Fitar da sautin tauna shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: A cikinsa, kwankwaɗar ruwa, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Amma nono sai mutum yana da dammar ya kwankwaɗe shi, ko mutum yana da zaɓi tsakanin kwankwaɗa da tsotsa. Yana daga ciki: Yin amfanin da wasu mata ke yi na biɗar abubuwan da suke sa ƙiba, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai.

Amma idan abin ya kai ga rashin aiwatar daga cikin farillan Allah Maɗaukaki kuma ya farlanta ko cutar da kanta, in ko ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya. Abin day a fi dacewa ga wannan shi ne taƙaitawa saboda mafi alherin abubuwa matsakaitansu.

Yana daga ciki: Kallafa wa Kai don baƙo shi ne ya karɓo abu bashi saboda ya yi alheri ba shi da halin biyan bashi, kuma ya kasance wanda zai karɓo bashin a wurinsa ya ƙyamaci bayar da shi ko mai karɓar bashin zai yi wahala gare shi, to, wannan abu ya yi kama da shi kallafa wa kansa da aka hana masa, saboda haka wannan shi ne bidi'a ce makaruhiya. Amma idan wanda zai karɓo bashin daga wurinsa yana farin ciki da haka, mai karɓar bashin zai yi kuma farin ciki tare da kasancewar biyan yana da sauƙi gare shi, to, wannan ba ya daga cikin ƙallafawa daga komai, har ma abu ne da ya kasance mai girma idan aka yi don Allah.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Sallama. Yin rantsuwa da Allah a wannan lokaci, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin addu'a a wurin sallama, shi ma bidi'a ce Makaruhiya. Yana daga ciki: Sunkuyawar da kai a yayin sallama, ita ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Idan ya gaskata, cewa shi rukuni a shari'ance idan ba haka ba, to, bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Miƙewar da wasu daga cikinmu ke yiwa waɗansu a lokacin sallama. A wuraren zama ko wuraren biki yayin yin wannan sallama, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Kuma wasu sun ce bidi'a ce halastacciya. Magana ta daidai lallai wannan makaruhi ne. Misali, misalign wannan miƙewar ga zama makaruhi ita ce miƙewa ga Alƙur'ani  ita ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga ciki: Yin musafaha da gefen yatsu yayin wannan sallama, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Domin sunna ta tabbatar da hannu da hannu yin musafahar an halatta, ba hana ba ko kuma ba a karhanta ba. Yana daga ciki:

Cire hula da rawani yayin sallamar, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Yana daga ciki: Yin nuni da yatsu ko da tafi yayin yin sallama, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Domin sallamar Yahudawa shi ne nuni da yatsu kuma sallamar Kiristoci nuni da tafin hannu. Yana daga ciki: Isar da sallamar wani namiji ga wata mata shi ma bidi'a ce makaruhiya domin wannan zai haifar da soyayya tsakanin maza manisanta da mata manisanta.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Neman Izini: Neman izinin shiga gida da yin tasbihi, shi ma bidi'a ce makaruhiya. Sunna da ta zo a cikin neman izini ita ce Salamun Alaikum in shigo? Zai faɗe ta sau uku idan an ba shi izini sai ya shiga in ko a'a sai ya koma.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga cikin Babin Magani da Tawada. Yin magani da najasa kamar mushe ko makamancinsa, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. In ya kasance a cikin jiki ne, to, ya halatta bisa magana shahararriya in ya kasance a bayan jiki ne. Yana daga ciki: Yin magani da surkullen Ajamanci wadda ba a san ma'anarsa ba, shi ma bidi'a ce haramtacciya a Mazihabar Imam Malik. Yana daga ciki: Yin magani da ƙulle-ƙulle, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Mafarki. Gabatar mutum a kan aikatawa ko bari da zarar ya ga mafarki ba tare da ya gan shi a Alƙur'ani ko Sunnar Manzo (tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi) ko a kan ƙa'idojin magabata (Allah Ya ƙara musu yarda) ba. Shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yana daga ciki: Rashin kulawa da mafarki gaba ɗaya, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai domin mafarki, ba a watsi da shi yana daga cikin yankin Annabta. Yana daga ciki: Yin ijtihadi wurin istihara a kan abin da ya gani a mafarki ko aka ganar masa, shi ma bidi'a ce makaruhiya.

Yana daga cikin abin da suka ƙaga a cikin Babin Kyautatawa wanda shi ne Tasawwuf: Ɗaure sashinsu ko kansu da ƙarfe ko da igiya ko ya riƙa yi wa kansa lalas da wuta don tsanantawa wurin tarbiyyantar da kai shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai domin cutar da rayuwa ne. Yana daga ciki: Neman ɓoyewa da wani hali ba yardajje ba shi ne abin ya kasance haramun da aka haɗu a kai, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa abin da aka sani, E. An halatta neman ɓoyewa kai da abin da yake halal ne mai muni ga al'ada ko makaruhi.

Yana daga ciki: Sauraren kaɗe-kaɗe haramtattu a wurin taron malamai kamar sauraren yesga ko garaya shi ma bidi'a ce haramtacciya, bisa abin da aka sani. Yana daga ciki: Musun karamomin waliyyai, shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Malamai sun ce ana jin tsoro ga mai musantawa mummunan ƙarshe. Allah Ya yi mana tsari. Muna roƙon Allah lafiya da zaman lafiya.

Yana daga ciki: Da'awar mutum ga waɗannan karamomi alhali shi ba ya cikin ma'abotanta ita ma bidi'a ce haramtacciya. Malamai sun ce ana jin tsoro ga wanda yake da'awar ta alhali bai cancanta ba mummunan ƙarshe. Allah Ya tsare mu, muna roƙon Allah lafiya da zama lafiya.

Yana daga ciki: Yin nazari a cikin littattafan ma'abuta Kashafi ga wanda ba ya iya banbance tsakanin zarra da giwa shi ma bidi'a ce haramtacciya bisa haɗuwar malamai. Yin nazari a littafin ma'abuta kashafi ba ya halatta sai dai ga malamin da ya san Littafin Allah da sunnar Manzonsa (saw). Ya bar abin da bai bayyana gare shi ba. Yana mai sallamawa gare shi, ba mai yin aiki da shi ba ba don tawaya da ke ciki mafaɗinsa ba a'a don rashin a kan iliminsa. Domin ba ya ƙallafa wa kowa abin iliminsa bai tuƙe zuwa gare shi ba. Har ma bai halatta ka yi aiki da abin dab a ka sani ba.

﴿ وَلَا تَقْفُ مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ ﴾الإسراء: ٣٦

***"Kada kai magana a kan abin da iliminka bai kai gare shi ba."***
**Alƙur'ani 17:36**

Daga cikin abubuwan da suka haddasa a wannan babi shi ne aikata abubuwan da suka ɗarsu ga zuciya ko ilhama ko kuwa abin da ake ji na daga muryoyi ko kuwa kashfi ba tare da auna abin da Alƙur'ani da Sunnan Annabi (saw) suka ce ba. Yin haka bidi'a ce da aka haramta ga haɗuwar malamai.

Daga cikin abubuwan da suka ƙirƙiro a wannan babi akwai riya cewa Waliyyi ya kai ga wani mataki da ake ɗauke masa wasu ayyukan addini na zahiri waɗanda suke wajibi shi ma wannan bidi'a ce wadda aka haramta ga haɗuwar malamai.

## FAƊAKARWA

**Ta Ɗaya:-** Ina sanar da ku ya 'yan'uwana cewa, nau'o'in bidi'o'i daga cikinsu akwai waɗanda suka wajaba a Zabura don gusar da su. Daga cikinsu akwai mustahabbai ne; akwai waɗanda halal, ne akwai waɗanda aka haramta a kawar duk abin da aka sanan riskar cutuwa da shi, to, kai kana da yin musun sa. Idan ya kasance zai kai ga shi ga ɓarna dama abin ƙyamar da ya fi shi, girma, to, an hana ƙyamatarsa ba wai ta karan kansa ba, ta inda abin da zai jawo waɗannan zamani ne na Jarabta da fitinu babu hanya zuwa gitta wa al'amuran mafi yawan mutane suke aikatawa. Lalle wannan zai kai zuwa ɓaci da halaka. Ku bar malamai waɗanda suka kafa kansu domin karantarwa. Idan suka aikata sawaba lada nag are su, in kuma suka yi kuskure zunubi na kansu. Hanyarsu in sun dace na su ne in kuma sun kuskure, to, a kansu.

Wanda duk ke neman ilimi don ya yi hukunci da shi a kan mutane bisa hanyar tilasci da kausasawa, to, ba zai huta ba kuma ba za a huta da shi ba. Wanda ko ya koyi ilimi don kansa kuma don ya yi hukunci da shi ga mutane bisa hanyar tausasawa da harama, to, shi kam zai huta kuma za a huta da shi.

**Na Biyu:-** Ina sanar da ku cewa, dukkan fannonin ilimi na nan a wurin malamai daɗaɗɗu da fararru. Sai dai abin da aka rasa a waɗannan zamuna ilimin sunna da na bidi'a sai a wurin 'yan kaɗan daga cikinsu. Idan kun tsinkayi ɗaya daga cikinsu a waɗannan zamunna, to, ku riƙe shi sosai lallai ya zama samun irinsa, waɗannan zamunna kamar mai biɗar jan karmatako.

**Na Uku:** Ina sanar da ku cewa al'umma ba mai tsare ta daga bayyanar fitintinu sai rayuwar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) kuma ba abin da zai tsare na bayansa sai rayar da Sunnarsa, don haka na hore ku da raya tad a biyar ta.

A nan ne littafin **Bayanin Bidi'o'in Shaiɗan** waɗanda mutane suka ƙaga su a cikin babi na addinin Musulunci. Ya ƙare.

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da aminci su tabbata ga Manzon Allah, cikamakin Annabawa kuma shugaban Manzanni.

Rubutu ya cika da godiyar Allah da kyakkyawan taimakonSa da ɗatawarSa. Ranar Alhamis, kwana Ashirin da biyar da suka shuɗe na watan Rajab. Tsira ya tabbata ga shugaban Manzanni da mutanen gidansa da Sahabbansa baki ɗaya. Allah Ka gafarta mana da iyayenmu da dukkan al'ummar Annabi Muhammadu (saw).

# أصول العدل

## لولاة الأمور وأهل الفضل

# Tushen Adalci Ga Shugabanni da Masu Falala

Na


Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Abdurrahman Ɗan Abdul'aziz

**Edita**

Dr. Sa'adiya Omar.

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi .......... 245

Tushe Na Farko: Darajar Shugabanci .......... 246

Tushe Na Biyu: Soyayya Ga Malaman Addini Da Nasihohinsu .......... 248

Tushe Na Uku: Ladabtar Da Wanda Ya Yi Zalunci .......... 249

Tushe Na Huɗu: Yafe Laifi Da Rage Fushi .......... 250

Tushe Na Biyar: Son Abin Da Shugaba Ke So Ga Mabiyansa .......... 251

Tushe Na Shida: Taimaka wa Mabuƙata .......... 252

Tushe Na Bakwai: Guje Wa Sha'awa Da Sanya Tufafi Na Alfarma .......... 253

Tushe Na Takwas: Sassauta Al'amurra .......... 254

Tushe Na Tara: Tsayuwa Da Fargabar Kabari Da Matakansa Da Ambaton Fargabar Lahira Da Matakanta. .......... 254

Tushe Na Goma: Ambaton Manzon Allah (saw) .......... 256

Na Farko : Game Da Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki .......... 256

Al'amari Na Biyu: Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki Na Kyakkyawan Tsari. .......... 257

Al'amari Na Uku: Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki Tsara Daularsa. .......... 257

Al'amari Na Huɗu: Abin Da Ya Wajaba A Kan Sarki Na "Tsaron Gida Ko Cikin Tafiya.". .......... 257

Al'amari Na Biyar: Abin Da Ya Wajaba Sarki Ya Bayyanar Na Lamarin Sarauta.. .......... 258

Al'amari Na Shida: Adalci Da Bincike .......... 258

Al'amari Na Bakwai: Tattaro Kuɗi Ta Hanyar Halal. .......... 259

Al'amari Na Takwas: Cikin Dukiyoyin Allah. .......... 260

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Tsira da aminci su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu da Dangoginsa da Sahabbansa aminci da amincewa mai yawa.

Godiya ta tabbata ga Allah, Wanda Ya yi mana ni'ima da ni'imar imani da Musulunci. Ya kuma shiryar da mu da shugabammu jagorammu, Muhammadu. Mafificin salati da tsarkakakken aminci daga Allah su tabbata a gare shi.

Bayan Haka: Wannan Littafi Tushen Adalci Ga Shugabanni Da Ma'abuta Falala, sai in ce: Allah Ya sa mu dace. Ka sani, lalle tushen adalci goma ne, kamar yadda Gazali ya faɗa cikin wallafe- wallafensa. Ya zo da maganarsa ta fuskar rairayewa da taƙaitawa don gudun tsawaitawa wadda ke jawo ƙosawa.

## TUSHE NA FARKO

## Darajar Shugabanci

Ya kai sarki, ka san darajar shugabanci, ka san kuma haɗarinsa, domin shugabanci, ni'ima ne. Wanda ya tsayu da haƙƙinsa, ya sami arziƙin da ba shi da iyaka, kuma babu arziƙin da ya fi shi. Wanda ya tauye a kan yunƙurawa da haƙƙinsa, ya faɗa cikin halaka ba ta da iyaka, kuma babu halakar da ta fi ta. Sai dai kafirce wa Allah Maɗaukaki.

Daga cikin abin da yake nuna girman darajar shugabanci, idan sarkin mai adalci ne, faɗinsa (tsira da aminci su tabbata a gare shi):

(والذي نفس محمد بيده عدل السلطان يوما واحدا أفضل من عبادة سبعين سنة)

***"Na rantse da Wanda ran Muhammadu yake hannunSa. Adalcin sarki na wuni ɗaya ya fi ibadar talakansa na shekara saba'in."***

Da faɗinsa (tsira da aminci su tabbata a gare shi):

(والذي نفس محمد بيده إنه ليرفع عمل السلطان العدل إلى السماء مثل عمل جملة الرعية، وكل صلاة يصليها تعدل سبعين ألف صلاة)

***"Na rantse da Wanda ran Muhammadu yake hannunSa, lalle ana ɗaukaka aikin sarki mai adalci zuwa sama, kamar aikin waɗanda yake wa shugabanci a dunƙule. Kowace salla idan ya yi ta tana daidai da salla dubu saba'in."***

To, in ya kasance haka, babu ni'ima mafi girma fiye da a bai wa bawa darajar sarauta. Da faɗinsa (tsira da aminci su tabata a gare shi):

(المقسطون لله في الدنيا على منابر اللؤلؤ يوم القيامة).

***"Masoyan adalci don Allah a nan duniya, suna kan mumbarai na lu'u lu'u ranar tsayuwa."***

Daga cikin abin da yake nuna girman haɗarin shugabanci, faɗinsa (tsira da aminci su tabbata a gare shi):

: (يؤتى بالولاة يوم القيامة، فيقول الله تعالى: ((أنتم كنتم رعاية خليفتي، وخزنة مملكتي في أرضي))، ثم يقول لأحدهم: ((ضربت عبادي فوق الحدّ الذى أمرت به؟)) ". فيقول : "يا رب لأنهم عصوك وخالفوك(فيقول) ((لا ينبغي أن يسبق غضبك على غضبي) ثم : يقول لآخر: ((لم عاقبت عبادي أقل من الحد الذي أمرت به؟)). فيقول"يا رب رحمتهم" فيقول ((كيف تكون أرحم مني؟ خذوا الذي زاد والذي نقص فامشوا بهما زوايا جهنم)).

***"Za a zo da shugabanni ranar tsayuwa, sai Allah Maɗaukaki Ya ce: "Ku ne kuka kasance masu lura da abin mulkiNa da taskar abin mallakaTa a cikin ƙasaTa, sai Ya ce da ɗayansu, ka doki bayiNa fiye da haddin da Na yi umurni da shi?" Sai wannan sarkin ya ce: "Ya Ubangijina, saboda sun saɓa maKa, sun aikata saɓo, sai Allah Ya ce: "Bai kamata fushinka ya riga fushinNa ba." Sai Allah Ya ce da wani sarkin: "Me ya sa ka azabtar da bayiNa ƙasa da haddin da Na yi umurni da shi?" Sai sarkin ya ce: "Ya Allah, tausayinsu na yi," sai Allah Ya ce: "Ta yaya za ka fi Ni tausayi?" Ku kama wanda ya yi ƙari da wanda ya yi ragi, ku tafi da su magamar Jahannama."***

Da faɗarsa (tsira da aminci su tabbata a gare shi) :

: (أشد الناس عذابا يوم القيامة السلطان الظالم).

***"Wanda ya fi kowane mutum shan azaba ranar tsayuwa sarki macuci."***

Daga cikin abin da yake nuni a kan girman darajar shugabanci, da girman haɗarinsa, akwai faɗarsa (tsira da aminci su tabbata a gare shi):

(أحب الناس إلى الله وأقربهم منهم السلطان العادل، وأبغضهم إليه وأبعدهم منه السلطان الجائر).

***"Mafi soyuwar mutane da kusancinsa a wajen Allah, sarki mai adalci, wanda Allah Ya fi fushi da shi, ya kuma fi nisanta da shi, sarki (ja'iri)."***

To, idan ya kasance haka, babu ni'ima mafi girma fiye da a bai wa bawa darajar sarauta, kuma babu mafi haɗari fiye da ita.

## TUSHE NA BIYU

### Soyayya Ga Malaman Addini Da Nasihohinsu

Ya kai sarki, ka cika soyayya ga malaman addini, ka kuma kwaɗaitu a kan sauraron nasiharsu, kuma ka guji miyagun malamai masu kwaɗaitarwa a kan duniya, domin su za su yabe ka, su ƙarfafa ka, su nemi yardarka, don kwaɗayin abin hannunka.

Shi, malamin kirki, shi ne wanda ba ya kwaɗayin abin da ke hannunka na daga dukiya. Kuma zai yi maka adalci na wa'azi da maganganu.

Kamar yadda ake faɗi: Lalle Shaƙiƙul Balkhi (Allah Ya ji-ƙansa,) ya shiga wajen Sarkin muminai Haruna Rashid, sai Haruna Rashid ya ce da shi: "Kai ne Shaƙiƙu mai gudun duniyar nan?" Sai ya ce, "ni ne Shaƙiƙu, amma ban zamo mai gudun duniya ba." Sai sarki ya ce da shi: "To yi mini wasiyya" Sai ya ce da shi: "Lalle Allah Ya zaunar da kai a wurin Abubakar Assiddiƙ, kuma lalle yana nemanka da gaskiya irin ta Siddiƙ Ya ba ka wurin Umar ɗan Khaɗɗabi Alfaruƙ. To, yana nema a wurinka. Ka rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya. Ya kuma zaunar da kai a wurin Usman ɗan Affan (Zunnuraini,) kuma lalle yana nema daga gare ka kunya da karimci irin nasa. Ya kuma zaunar da kai wurin da Aliyu ɗan Abu Ɗalib ya zauna, yana nema a wurinka, ka zama mai ilimi da adalci."

Sarkin Muminai Umar ɗan Abdul'Aziz ya tambayi Muhammad ɗan Ka'abu, Allah Ya ƙara masu yarda, ya ce da shi: "Siffanta mini adalci? Sai ya ce: "Duk Musulmin da bai kai shekarunka ba, to, ka zamo Uba a gare shi, wanda ya girme ka kuma, ka zamo ɗa a gare shi, wanda kuma yake kamarka, ka zamo ɗan'uwa a gare shi, ka hukumta duk mai laifi gwargwadon laifinsa.

Umar Ɗan Abdul'Aziz ya tambayi Abu Hazim ya yi masa wa'azi, sai Abu Hazim ya ce: "Idan za ka yi barci, ka sanya mutuwa ƙarƙashin kanka, duk abin da ka zaɓa, mutuwa ta same ka a kansa, ba tare da damuwa ba. To, ka lazimce shi; duk abin da ba ka so mutuwa ta same ka kana kansa. To, ka ƙaurace masa, ta yiwu mutuwar tana kusa da kai."

Ya kamata ga wanda yake kan mulki ya sa waɗannan hikayoyi a gaban idonsa. Ya karɓi wa'azozin da aka yi wa waninsa. Duk kuma inda ya ga malami ya yi wa sarakuna wa'azi da irin waɗannan wa'azozin, kada ya ɓoye masu maganar gaskiya. Duk wanda ya ruɗe su, to, ya yi tarayya da su a cikin zaluncinsu.

TUSHE NA UKU

**Ladabtar Da Wanda Ya Yi Zalunci**

Ya kai sarki, kada ka gamsu da ɗauke hannunka a kan azzalumai. Amma ka ladabtar da yaranka da mashawartanka da ma'aikatanka da wakilanka. Kada ka yarda su yi zalunci, domin kai za a tambaya a kan zaluncinsu, kamar yadda za a tambaye ka a kan zaluncin kanka.

Umar Ɗan Khaɗɗab (Allah Ya ƙara masa yarda), ya rubuta takarda zuwa ga ma'aikacinsa, Abu Musa Al'Ash'ari: "Bayan haka, lalle mai arziƙin shugaba shi ne wanda jama'arsa suka azurta da shi, mafi halakar shugaba shi ne wanda jama'arsa suka wahala da shi. Kashedinka, kada ka yi zalunci, domin ma'aikatanka za su yi koyi da kai."

Yana rubuce a cikin Attaura: "Duk zaluncin da sarki ya san da shi ma'aikatansa suke yi, kuma ya yi shiru a kansa, wannan zaluncin zai kasance an dangana shi gare shi, za a kama shi da shi."

## TUSHE NA HUƊU

### Yafe Laifi Da Rage Fushi

Mafi rinjayen shugaba, yakan kasance mai girman kai. Kuma wanda ya yi girman kai, yakan yi fushi wanda zai ja shi zuwa ga ramuwar gayya. Shi, fushi, shi ne dodon hankali, kuma maƙiyinsa da kuma lalacewarsa. Ya kamata ya kai sarki, ka karkata zuwa ɓangaren yafiya cikin al'amura, ka saba da karimci a kai-a kai. Idan wannan ya zama ɗabi'a a gare ka, ka yi koyi da Annabawa da Waliyyai.

Duk yayin da ka sanya zartar da fushi ya zama ɗabi'arka, ka yi koyi da dabbobi da miyagun dabbobi. Kuma mafi yawan fushin sarakuna ya fi a kan wanda ya ambace su, ya tsawata harshensa a kansu, sai su sabar da jininsa.

Mai tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

(ويل لمن يغضب وينسى غضب الله تعالى عليه).

*"Azaba ta tabbata ga wanda ya yi fushi, ya manta da fushin Allah Maɗaukaki a kansa."*

Mai tsira da aminci ya ce:

: (ثلاث من كانت فيه فقد كمل إيمانه: من غضب وانصف في حالة رضاه وغضبه وعفى عند المقدرة)

*"Abubuwa uku waɗanda ya kasance tare da su,to, imaninsa ya cika, wanda ya yi fushi kuma ya yi adalci cikin halin yarjewarsa, ya kuma yi fushi ya kuma yafe inda yake da iko."*

Mai tsira aminci su tabbata a gare shi ya ce:

(قد يبلغ الرجل بحلمه وعفوه درجة الصائم القائم)

*"Haƙiƙa, mutum, yakan kai darajar mai azumi da tsayuwar dare, saboda haƙurinsa da yafewarsa."*

Zainul Abidina Aliyu Ɗan Husaini (Allah Ya ƙara masu yarda) ya fita wata-rana zuwa Masallaci, sai wani mutum ya zage shi, sai yaransa suka yi kan wannan mutum za su buge shi, su cutar da shi, sai Zainul Abidina ya hana su, ya ce: "Ku kame hannuwanku daga gare shi." Sannan sai ya waiga wajen wannan mutum ya ce: "Ya kai wannan, ai ni na wuce abin ma da ka faɗa, abin da ba ka sani ba ya fi abin da ka sani yawa, idan kana da wata buƙata da za ka ambata, ka ambata." Sai kunya ta kama mutumin ya ruɗe. Sai Zainul Abidina ya cire rigarsa ya ba shi, ya kuma yi umarni da a ba shi dirhami dubu. Sai mutumin ya wuce yana cewa: "Lalle wannan yaro lalle jikan Manzon Allah ne (tsira da aminci su tabbata a gare shi)."

## TUSHE NA BIYAR

## Son Abin Da Shugaba Ke So Ga Mabiyansa

Lalle kai kana cikin wata hatsaniya tana tasowa gare ka. Wani lokaci kuma tana kauce maka, ka ƙaddara cewa, kai ma kana daga ɗaya cikin waɗannan jama'a naka, kuma lalle akwai wani shugaban ba kai ba. To, duk abin da ba ka yarda da shi ga kanka ba, kar ka yarda da shi ga waninka daga cikin Musulmi.

Mai tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce*:*

لا (من أحب النجاة من النار والدخول في الجنة فينبغي أن يكون بحيث إذا جاءه الموت وجد كلمة الشهادة، وكل ما يرضاه لأحد من المسلمين). يرضى لنفسه لا

***"Wanda yake son kuɓuta daga wuta ya kuma shiga Aljanna. To, ya kamata ya kasance yana wajen da in mutuwa ta zo masa, zai samu yin 'Kalimar shahada,' kuma dukkan abin da bai yardar wa kansa ba, kada ya yarda a kan wani Musulmi."***

## TUSHE NA SHIDA

### Taimaka wa Mabuƙata

Kada ka raina taimakon da kake yi wa ma'abuta buƙata da kuma tsayuwarsu a ƙofarka. Ka kiyaye wannan haɗarin. Ko yaya Musulmi suka zo wajenka da buƙata, to, kada ka shagaltu da nafiloli na ibadarka, domin biyan buƙatun Musulmi ya fi nafilolin ibada.

Umar Ɗan Abdul'Aziz ya kasance wata-rana yana biyan buƙatun mutane, ya zauna har zuwa Azahar sai ya gaji ya shiga gidansa don ya huta saboda gajiyarsa, sai ɗansa ya ce masa: "Mene ne zai kuɓutar da kai idan mutuwarka ta zo maka yanzu? Kuma a ƙofar gidanka akwai mabuƙaci yana jiran ka. Ga ka, ka tauye masa haƙƙinsa?" Sai ya ce: "Ka yi gaskiya, ya ɗana." Sai ya yunƙura ya dawo majalisarsa.

## TUSHE NA BAKWAI

### Guje Wa Sha'awa Da Sanya Tufafi Na Alfarma

Ya kai sarki, kada ka saba wa kanka da sha'awace-sha'awace daga sanya tufa ta alfahari, da cin abinci mafi daɗi. Amma ka yi aiki da wadatar zuci cikin dukkan abubuwa, domin babu adalci in babu wadatar zuci.

Umar Ɗan Khattab (ra) ya tambayi mutumin kirki ya ce: "Shin ka ga wani abin ƙyama cikin halayena?" Sai ya ce: "Na ji an ce ka ajiye guntayen gurasa biyu a kan teburin abincinka, kuma kana da riga biyu ɗaya ta dare, ɗaya ta rana." Sai ya ce: "Bayan waɗannan akwai waɗansu?" Ya ce: "Babu," Sai ya ce: "Wallahi, waɗannan biyun ba za ka sake ganin su ba a wajena."

## TUSHE NA TAKWAS

<u>Sassauta Al'amurra</u>

Ya kai wannan sarki! Idan zai yiwu a gare ka, ka aikata al'amura da sauƙi da sassauci, kada ka aikata su da tsanani da tursasawa.

Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi) ya ce: "Wanda ba ya tausaya wa jama'arsa Allah ba Zai tausaya masa ranar tsayuwa ba."

Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi) ya ce*:*

: (من ولي شيئا من أمر أمتي فشق عليهم اللهم شق عليه، ومن ولي شيئا من أمر أمتي فرفق بهم، اللهم ارفق به).

***"Wanda aka jiɓinta masa wani abu na al'amarin al'ummata, sai ya tsananta masu, ya Allah, Ka tsananta masa: Wanda aka jiɓinta masa wani abu na al'amarin al'ummata, sai ya tausaya masu, ya Allah, Ka tausaya masa."***

## TUSHE NA TARA

<u>Tsayuwa Da Fargabar Kabari Da Matakansa Da Ambaton Fargabar Lahira Da Matakanta.</u>

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩٠﴾ فَسَلَٰمٌ لَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩١﴾ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٩٢﴾ فَنُزُلٌ مِّنْ حَمِيمٍ ﴾ الواقعة: ٩٠ - ٩٣

***"To, Idan ya kasance daga cikin makusanta, to, sai hutawa da abinci da Aljannar ni'ima, in kuma ya kasance daga ma'abuta dama, to aminci ya tabbata daga ma'abuta dama. Idan kuma ya kasance daga cikin masu ƙaryatawa, ɓatattu, to, yana da liyafa ta ruwan zafi da ƙonuwar wutar Jahimu."***
**Alƙur'ani 56:90-93**

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَخْبَتُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّهِمْ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ﴾ هود: ٢٣

***"Lalle waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki na ƙwarai, suka marairaita zuwa ga Ubangijinsu, waɗannan su ne 'yan' Aljanna."***
**Alƙur'ani 11:23**

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَفِي ٱلْآخِرَةِ عَذَابٌ شَدِيدٌ وَمَغْفِرَةٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنٌ﴾ الحديد: ٢٠

*"Kuma a lahira akwai azaba mai tsanani da gafara daga Allah da yarjewa."* Alƙur'ani 57:20

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلِكُلٍّ دَرَجَٰتٌ مِّمَّا عَمِلُوا۟﴾ الأحقاف: ١٩

*"Kowane yana da darajoji, na abin da suka aikata."* Alƙur'ani 46:19

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلَلْآخِرَةُ أَكْبَرُ دَرَجَٰتٍ وَأَكْبَرُ تَفْضِيلًا﴾ الإسراء: ٢١

*"Kuma lalle lahira ta fi girman darajoji, kuma mafi girman falala."* Alƙur'ani 17:21

## TUSHE NA GOMA

### Ambaton Manzon Allah (saw)

Lalle Maɗaukaki bayan Ya sanya ayyukan mutum, daga cikinsu akwai abin da yake zama dalilin halakar mutum, akwai kuma wanda ke zama dalilin tsira ga mutum. Kuma shi, mutum, ba zai iya sanin haka ba da ƙashin kansa. Allah Maɗaukaki da hikimarSa da falalarSa da rahamarSa sai Ya halicci Mala'iku, Ya kuma aika su zuwa ga mutane. Haƙiƙa, Ya hukunta su da arziƙi tun fil'azal.

Kuma su ma Annabawa (tsira da amincin Allah su tabbata a gare su,) sai Ya aike su zuwa ga halitta don su bayyana masu hanyar arziƙi da ta halaka.

Don mutane su sami hujja wajen Allah, Ya aiko Annabimmu Muhammadu (tsira da aminci su tabbata a gare shi). A ƙarshe, Ya sanya shi mai bushara da gargaɗi, ya sadar da annabtakarsa zuwa cikakkiyar daraja, har ya zama babu sauran wajen ƙari ko daɗi. Saboda haka, Ya sanya shi cikamakon Annabawa (Aminci ya tabbata a gare shi). To, wannan shi ne tushen adalci Al-Gazal ya ambata kamar yadda ya faɗa cikin wasu wallafe-wallafensa. Ya kamata ga kowane sarki ya kiyaye da fahimtarsu tare da yin aiki da su.

Ya kamata gare shi kuma ya kiyaye al'amura takwas waɗanda Muhammad Ɗan Abdulkarim Tilmisani ya ambace su cikin sashen wallafarsa. Ya zo da zancensa ta fuskar rairayewa da taƙaitawa don gudun tsawaitawa wadda take jawo ƙosawa.

### Na Farko Game Da Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki

Ya kai sarki, ka dogara ga Allah. Ka nemi taimakonSa cikin al'amarinka, kuma dukkansu ka yi don Allah. Duk ayyukanka ya zama don neman yardar Allah ne. Ka tunatar da kanka cewa kai ma ɗaya ne daga cikin halittar Allah. Kuma akwai waɗanda suka fi ka ƙarfi da yawa, ba domin taimakon Allah ba, Ya zama duk kwaɗayinka na Allah ne, tsoronka duka na Allah ne, kuma don ingantar da halittar Allah. Allah Bai shugabantar da kai a kansu ba don more masu, sai dai Ya shugabantar da kai ne don ka gyara masu addininsu da duniyarsu.

Ni'imar Allah ce gare ka, ka gode maSa, ka kyautata kamar yadda Allah Ya kyautata a gare ka. Kada ka yanke ƙauna daga rahamar Allah, Allah Ya kuranye baƙin ciki mai yawa.

## Al'amari Na Biyu

## Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki Na Kyakkyawan Tsari

Ya zama dole ga dukkan sarki ya tufata da tufa mai kwarjini a gida da waje. Ka bayyanar, ya kai sarki, da son alheri da masu alheri. Ka ƙi sharri da masu sharri, ka ƙawata jikinka da ƙanshinka watau turare. Ka kyautata tufafinka na adon maza da halal, kada ka yi ado da Zinare ko Azurfa ko Alhariri. Ka yi zaman haɗa ƙafafu in ka zauna. Ka natsu gwargwadon iyawarka. Idan za ka yi magana, ka faɗi gaskiya. Idan ka yi alƙawari, ka cika. Idan da ka yi umurni ko hani a kan wani abu, to, ka hanu, kada ka rafkana har sai ka cimma nufinka. Kada ka kusanci hidimarka ko majalisarka, kana da ƙananan mutane watau marasa mutunci, domin martabar shugaba saboda haka ka zaɓi na kirki cikin mutane.

## Al'amari Na Uku

## Abin Da Ya Wajaba Ga Sarki Tsara Daularsa

Dole ne kowane sarki ya tsara masarutarsa a kan abin da zai kasance gyara ga abin sarautarsa. Daga ciki akwai wazirai da ba sa tsoron kowa sai Allah da alƙalai amintattu. Su karkasu da shugabannin 'yan sanda su tsawatar da masu yaƙe-yaƙe, masu yaye baƙin ciki da kwaranniya da malamai amintattu, su ne masu shiryarwa da marubuta suna kiyayewa da shugabannin fifitattu suna taruwa da ma'aikata suna ba da haƙƙin Allah da 'yan aike- cikin garuruwan Musulunci da 'yan-leƙen asiri zuwa garin maƙiya da masu hidima a gida suna komowa da garu ginanne mai isarwa don tattalin abinci da ruwa da kasuwa.

## Al'amari Na Huɗu

## Abin Da Ya Wajaba A Kan Sarki Na Tsaron Gida Ko Cikin Tafiya

Ya kai sarki! Ka kula da abincinka da abin shanka da tufafinka. Kada ka rabu da makami kada wani ya kusance ka sai ma'abuta amana da kintsi.

## Al'amari Na Biyar

## Abin Da Ya Wajaba Sarki Ya Bayyanar Na Lamarin Sarauta

Dole ne ga kowane sarki ya ba da wani sashen al'amura gwargwadon iko. Wannan kuma ya haɗa duk lamarin da ake da haɗari. Idan an yi shi ya riƙa wannan a tambaya a kan duk abin da ya jahilta daga masu adalci da amintattu masu mutunci a gaba gare shi da masu wasiyya. Kuma ya fitar da haƙƙi a kan duk maras galihu daga marayu da wawaye. Ya yi umurni a ɗaga su don a sami mai jiɓintar su. Daga nan kuma ya kiyaye Baitalmali da dukiyar ma'aikata da duk abin da yake shi ne abinci don bincikensa na kuɗi ko wanin kuɗin.

Daga cikin wannan, ya bincika halin ma'aikatansa. Ya duba ayyukansu a kowane lokaci. Duk wanda aka same shi da kasawa, ya yi masa tsawa. Duk wanda yake jin tsoron cuta daga gare shi, ya cire shi. Duk wanda ya maimaita laifi har aka kawo ƙorarsa, kuma babu wani bayani, in an sami mai canjin sa sai ya canza shi.

Daga cikin wannan, ya binciki labarin abokan gaba da 'yan-leƙen asiri amintattu daga cikin haka. Ya binciki zargin masu zargi da yabon masu yabo, saboda sukan iya nesanta na kusa ko kuma nesanta na kusa Da yawa sukan so abokin gaba da yawa sukan ƙi masoya. Daga cikinsu akwai wanda zai yi yabo mai yawa, sannan ya yi zargi ko ya yi zargi mai yawa sannan ya yi yabo don a daina tuhumar sa idan ya yi zargi ko ya yi yabo.

## Al'amari Na Shida

## Adalci Da Bincike

Ya wajabta ga shugaba ya yi adalci cikin mahukuntan sarki, ma'abuta adalci da kyautattawa. Shi, adalci, shi ne a ba kowane mai haƙƙi haƙƙinsa na kansa da waninsa da kyautatawa. Kyautatawa, ita ce mutum ya bugi ƙirji a kan al'amarin waninsa. Daga cikin adalci, ya daidaita tsarin masu rigima a tashi kewayowar maganar. Babu makawa sarki, babba kullum sai ya zauna ya yi bincike har a kan mata da yara, abin da Alƙalai suka binciko bai isa ba, ko Ma'aikata domin ƙorarraki na jama'a suna kasancewa mafi yawa dole, kuma a kansa ya tsawatar da su.

## Al'amari Na Bakwai

## Tattaro Kuɗi Ta Hanyar Halal

Ya zama dole a kan kowane sarki kada ya tara kuɗi sai ta hanyar da Allah Ya halasta masa. Daga cikin kuɗin da Allah Ya halasta masa ya karɓa, ya kuma kashe akwai: Zakkar kuɗi da kayan noma da dabbobi da ma'adinai da zakkar kono da ɗaya bisa biyar na dukiyar da aka binne a ƙasa da ɗaya bisa biyar na ganima da kuɗin kariya da na sulhu da abin da ake karɓowa wajen 'yan-kasuwa waɗanda aka yi wa waɗancan salhu da dukiyar da ba ta da magaji da abin da Allah Ya taro masa na ganimar Fai'u. Idan sarki ya kasance mai adalci wajen gudanar da dukiyar Allah, to, ya zama dole ga wanda a kansa akwai wani abu na misalin zakkar kuɗi ko waninta ya miƙa ta gare shi, don ya sarrafa ta.

Daga cikin dukiyar da Allah Ya haramta wa Sarakuna da waninsu: Dukkan zalunci: Daga cikin zalunci akwai abin da yake karɓa a kan yin hukunci ko waninsa. Wannan haramun ne a ijma'in malaman Musulmi, kuma hanya ce ta ɓata addini da buɗe ƙofofin cin hanci da rinjayar miskinai domin su, shugabanni, suna karɓar kuɗin, ba makawa sai an karɓi dukiya daga talakawa.

Daga cikin zalunci kuma toshiyar baki, ita ma haramun ce bisa ijma'i, ba ya halatta ga sarki ko waninsa daga Alƙalai ko ma'aikata su karɓi wani abu daga wajen wani abokin ƙara kafin su yi hukunci ko bayan hukunci. Ba ya karɓar kyauta daga talakawa sai in ta kasance saboda 'yan'uwantaka ne, to, ta halatta, kamar dangantakarku ta auratayya, ko don soyayya da take tsakaninsu ko don neman lada a wajensa.

Yana daga cikin zalunci kuma azabtarwa da dukiya kamar karɓar kuɗin ɓarawo ko mazinaci. Ita ma haramun ce a kan kowane hali, sai dai idan ta kasance laifi ne mai rataya da wannan dukiyar kamar nono a haɗa shi da ruwa da bayar da shi sadaka ya halatta.

Daga cikin zaluncin kuma karɓar ushira ko waninta daga ma'abuta haƙƙi da kayan gado ita ma haramun ce bisa ijma'in Musulmi. Idan wata masiba ta faɗa wa mutane ana neman kuɗi babu kome a Baitul Mali, ba za a iya tunkuɗe cutarwar daga kansu sai da dukiyarsu, to, wajibi ne a taimake su gwargwadon halinsu, ba tare da an ciyar da yin haka ɗin gaba, ba kamar faɗuwar garu a wajen da ake tsoro.

## Al'amari Na Takwas

## Dukiyoyin Allah

Ya zama dole ga wanda hannunsa akwai wani abu na dukiyar Allah, kada ya ɓatar da ita sai wajen masaufi shari'ar Allah. Dukiyar Allah wadda Ya sanya ta arziƙin bayinSa kashi biyar: Kaso ɗaya na wasu jama'a sanannu; kaso ɗaya cikin gudanarwar shugaba don mas'alolinsu. To, kaso na farko, zakkar kuɗi da noma da dabbobi da zakkar ma'adini da zakkar kono, ana gudanar da ita ban da zakkar kono ga nau'i takwas wanda ke cikin faɗin Allah Maɗaukaki.

﴿إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ﴾ التوبة: ٦٠

***"Ita, zakka, kawai ta faƙirai ce da talakawa da masu aiki a kanta da waɗanda ake jawo hankalinsu zuwa Musulunci da kuma bayi da masu bashi da fi sabilillahi da matafiya."*** **Alƙur'ani 9:60**

Gudanar da zakkar kono ta jinsi biyu na farko kawai ne.

Kashi na Biyu: Shi ne Fai'u, kamar kumusin bisa ɗaya bisa biyar na ganima da abin da aka karɓa a wajen kafiran amana da ma'abuta kirki da abin da aka karɓa wajen 'yan kasuwarsu da ɓarayin ƙasa da dukiyar gadon da babu mai cin ta da abin da Allah Ya bai wa muminai na daga abokan yaƙi ba tare da an yi yaƙi ba. Duk hukuncin wannan na wajen shugaba, ya gudanar da shi da tsoron Allah.

Kuma mafi haƙƙin mutane wajen wadatawa a kansa dukiyar da ganimar Fai'u su ne masu kare addini daga mafifitan Musulmi da malamai masu tsoron Allah da shiryayyun mutane a kowane gari su suka fi cancanta da shi a kan waninsu, sai in buƙata ta saukar masu, sai a ɗauka a kai masu daga cikinta bayan an bai wa masu ita, abin da zai ishe su ta fuskar bincike. Idan ya kasance ba mutanen garin ba ne, suka fi buƙata fiye da mutanen garin sai a ɗauko masu mafi-yawa bisa ga bincike.

Rayuwar shugabanni masu adalci suna raba dukiyar Fai'u, sai su fara toshe shi kamar toshe ginin garu ko gyara makamai ko wanin su, sannan a ciyar da Malamai da Alƙalai da masu kiran sallah da duk wanda akwai wata mas'laha ta Musulmi a hannunsa, kamar mayaƙa, sannan talakawa. Idan dukiyar ta wadata, sai shugaba ya rage wani abu a Baitul-mali don gudun abin da zai iya aukuwa na annoba ko gina masallatai da fansar bayi da biyan

basussuka da taimakon marasa aure don su yi aure da taimakon alhazai da wanin haka na fuskokin buƙata.

Ya kuma fifita iyalan gidan Manzon Allah (tsira da amincin su tabbata a gare shi) wajen kasa dukiyar da dukkan haƙƙoƙi. Haƙiƙa, Umar ɗan Abdul'Aziz (Allah Ya ƙara masa yarda), ya kasance yana kwaɗaitar da 'ya'yan Fatima (Allah Ya ƙara mata yarda) a kowace shekara da Dinari dubu goma sha biyu, ban da abin da yake bai wa waɗansunsu na makusanta. To, wannan shi ne sunnar kashe dukiyar Allah Mai girma da Buwaya ga Musulmi.

Nan ne littafi na 'Tushen Adalci Na Shugabanni' ya cika da taimakon Allah Mai girma da Buwaya. Yau, Laraba, lokacin Azahar, bakwai ga Jimada Auwal Shekara ta Sharkaci bayan hijirar Annabi (tsira da aminci su tabbata a gare shi.)

Godiya ta tabbata ga Allah, Wanda Ya shiryar da mu ga wannan, ba mu kasance masu shiryuwa ba, sai dai don Allah Ya shiryar da mu mafificin salati da cikakken aminci su tabbata ga shugabammu, Muhammadu (tsira da aminci su tabbata a gare shi) da Sahabbansa gaba ɗayansu. Yardar Allah ta tabbata ga Tabi'ai da malamai masu aiki da shugabannin nan su huɗu masu ƙoƙari da kuma masu koyi da su har zuwa ranar sakamako.

﴿ رَبَّنَآ إِنَّنَا سَمِعۡنَا مُنَادِيٗا يُنَادِي لِلۡإِيمَٰنِ أَنۡ ءَامِنُواْ بِرَبِّكُمۡ فَـَٔامَنَّاۚ رَبَّنَا فَٱغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا وَكَفِّرۡ عَنَّا سَيِّـَٔاتِنَا وَتَوَفَّنَا
مَعَ ٱلۡأَبۡرَارِ ١٩٣ رَبَّنَا وَءَاتِنَا مَا وَعَدتَّنَا عَلَىٰ رُسُلِكَ وَلَا تُخۡزِنَا يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ إِنَّكَ لَا تُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ﴾

آل عمران: ١٩٣ - ١٩٤

***"Ya Ubangijimmu, lalle mun ji wani mai yekuwa yana yekuwa kan imani cewa, lalle ku yi imani da Ubangijinku. To, mun yi imani ya Ubangijimmu. Ka gafarta mana zunubammu, kuma Ka kankare mana kurakurammu, kuma Ka karɓi rammu tare da masu nagarta. Ya Ubangijimmu, Ka ba mu abin da Ka yi mana alƙawari a wajen ManzanninKa, kuma kada Ka kunyata mu, ranar tsayuwa lalle Kai ba aka saɓa alƙawari."***

**Alƙur'ani 3:193-194**

Da kyakkyawan taimakon Allah, littafi ya cika. Tsira da aminci su tabbata ga Manzon Allah da amincewa, Amin.

# سراج الإخوان

## في أهم ما يحتاج إليه في هذا الزمان

# Haskakawa 'Yan'uwa Muhimman Abubuwa

Na


**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

**Mai Fassara**

**Mal Ishaƙ Yunus**

**Al-Mashgool Bauchi**

**Edita**

**Ahmed Abdullahi  Sokoto (A.A. Sokoto)**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi .................................................................... 267

FASALI NA FARKO: Bambancin Musulmi da Kafirai .......................... 269

FASALI NA BIYU: Bambanci Tsakanin Malamai Masu Taimakon Shaiɗan. ........................................................................................ 271

FASALI NA UKU: Hukuncin Waɗanda Suke Furta Kalimar Shahada A Kan Al'ada Ba Su San Kome Na Ayyukan Musulunci Ba. ...................... 277

FASALI NA HUƊU: Hukuncin Yaƙar Mutanen Da Suka Furta Kalmar Shahada Kuma Suna Aikata Ayyukan Musulunci Sai Dai Suna Gaurayawa Da Ayyukan Kafirci. ........................................................ 280

FASALI NA BIYAR: Hukuncin Yaƙar Masu Taimakon Kafirai Daga Cikin Malamai Da Ɗalibai Da Jahilai .................................................. 283

FASALI NA SHIDA: Hukuncin Yaƙar Musulmi Masu Sakaci (Jinkiri) Waɗanda Ba Su Shiga Mubayi'ar Wani Shugaba Daga Shugaban Musulunci Ba. ........................................................................ 285

FASALI NA BAKWAI: Hukuncin Yaƙar Masu Yaƙar Musulmi. ........... 287

FASALI NA TAKWAS: Hukuncin Yaƙar Azzalumai Daga Cikin Shugabannin Musulmi .......................................................................... 289

FASALI NA TARA: Abubuwan Da Suka Wajaba A Kan Shugabannin Musulunci Na Tsayar Da Dokokin Musulunci Da Gyara Garuruwa Da Canza Munanan Ayyuka ...................................................................... 291

FASALI NA GOMA: Haƙiƙanin Halal Da Haram Da Rarrabewar Shubuha Daga Asalin Halal ................................................................ 298

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu (saw) da iyalan gidansa da Sahabbansa

Bawa mabuƙaci ga rahamar UbangijinSa: Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu wanda aka fi sani da Ɗan Fodiyo (Allah Ya lulluɓe shi da rahamarSa Amin). Ya ce: "Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu, kuma mafificin salati cikakke da cikakakken aminci su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu (saw) da iyalan gidansa da sahabbansa gaba ɗaya, kuma Allah Ya ƙara yarda ga shugabanni Tabi'ai da malamai masu aiki da iliminsu, da shugabannin nan guda huɗu masu ƙoƙarin ijtihadi (Abu Hanifa da Maliki da Shafi'i da Ahmadu) da mabiyansu har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka wannan littafi, **'Sirajul Ikhwan'**, yana daga cikin mafiya muhimman ayyuka da ake buƙata a wannan zamani, kuma na sanya shi a fasaloli guda goma.

**Fasali na Farko**: Bayanin bambanci tsakanin Musulmi da kafirai.

**Fasali na Biyu:** Bayanin bambancin malaman addini masu ambaton Allah kuma masu taimakon Allah da miyagun malamai rafkanannu, mataimaka Shaiɗan.

**Fasali na Uku**: Hukuncin yaƙar mutanen da suke furta kalimar Shahada a kan al'ada, kuma ba su aikata kome na Musulunci.

**Fasali na Huɗu:** Hukuncin yaƙar mutanen da suke furta kalimar Shahada, kuma suna aikata aikin Musulunci sai dai suna gaurayawa da ayyukan kafirci.

**Fasali na Biyar:** Hukuncin yaƙar waɗanda suke taimakon kafirai daga cikin malamai da ɗalibai da jahilai.

**Fasali na Shida:** Hukuncin yaƙar Musulmi masu sakaci (jinkiri) waɗanda ba su shiga ƙarƙashin mubaya'ar wani shugaba daga cikin shugabannin Musulmi.

**Fasali na Bakwai:** Hukuncin yaƙar masu yaƙar Musulmi da kuma ƙwace musu kaya.

**Fasali na Takwas:** Hukuncin yaƙar azzalumai daga cikin shugabannin Musulmi.

**Fasali na Tara:** A cikin abin da yake wajaba ga shugabannin Musulunci na tsayar da dokokin Musulunci da gyara garuruwa da canza munanan abubuwa.

**Fasali na Goma:** A cikin bayanin haƙiƙanin halal da haram da shubuha (ruɗani) daga asalin halal.

## FASALI NA FARKO

### Bambancin Musulmi da Kafirai

Ina cewa: "Ga Allah nake neman dacewa, ku sani ya ku 'yan'uwa Musulmai lalle haƙiƙanin Musulmi, a shari'a su ne waɗanda suka furta kalimar shahada, kuma suke yin aiki na Musulunci. Kuma ba a ji kome daga gare su ba, waɗanda suke inkarin (musun) wani abu wanda aka sani yau da gobe ba shari'a ko da wani abin da aka sani a cikin addini, kuma ba a ji daga gare su sun yi izgilanci da addinin Allah da waɗansu lafuzza na kafirci ba.

Kuma ba a ganin su suna gauraya (cuɗanya) ayyukan Musulunci da na kafirci. Abin sani shi ne: sharaɗin ingancin Musulunci shi ne kada a yi wani inkarin (musun) wani abu da aka sani a cikin addini, domin duk wanda ya yi inkarin haka kafiri ne na haƙiƙa. Ya zo a cikin **Idwa'atid Dajina'** cewa: "Duk wanda ya yi jayayyar (musun) abin da aka sani a cikin addini, ya tafi da kafirci (ya kafirta), kuma ruɗinsa ya ƙaru". Kuma ya zo a cikin **Kaukabus Saɗi'u** "Wanda ya yi musun wani ilimin da aka yi tarayya a kansa, to, lalle shi ba Musulmi ba ne."

Kuma abin sani a nan shi ne: dukkan sharuɗɗan ingancin Musulunci, su ne, barin yin izgilanci ga addinin Allah da lafuzza na kafirci, domin duk wanda ya yi izgilanci ga addinin Allah, haƙiƙa, kafiri ne ko da kuwa bai ƙudurci haka ba a zuciyarsa. Kuma ya zo a cikin **Bada'ul Amal** cewa: "Yin lafazi na kafirci ba tare da mutum ya ƙudurci haka ba a zuciya, ridda ce a cikin addini a faƙaice." Abin sani shi ne, sharaɗin ingancin Musulunci, barin gauraya ayyukan Musulunci da na kafirci, domin duk wanda ya gauraya ayyukan Musulunci da ayyukan kafirci, haƙiƙa, kafiri ne.

Kuma ya zo a cikin **Kasidatul Jaza'iriyya** cewa: Kuma ga misalinsu duk ma'abucin shirka (haɗa Allah da wani wurin bauta) ko da sun jingina kansu da addini, kafirai ne. Kuma kada ka kawo mini wata hujja a kan abin da muka tabbatar. Duk wanda ya yi musun abin da aka sani a cikin addini, ko ya yi izgilanci ga addinin Allah, ko kuma ya gauraya ayyukan Musulunci da ayyukan kafirci, haƙiƙa kafiri ne ko da yana addinin da irin addinin Musulunci. Wannan shi ne bambanci tsakanin waɗannan Musulmi da kafirai.

Amma duk wanda yake gauraya ayyukan Musulunci da ayyukan saɓo da bidi'a, ba ya zama kafiri ga dukkan Ahlus Sunna. Abin sani kawai shi dai mai saɓon Allah ne da ManzonSa, kuma fasiƙi ne ko da yana aikata manyan zunubai, kuma ya doge a kan ƙananan zunubai.

Kuma ya zo a cikin **'Dararul Kala'id'** cewa: "Duk wanda ya saɓa wa Allah da manyan zunubai ko ya doge a kan ƙanana, to, fasiƙi ne, kuma a cikin laifin ma ya zurfafa." Kuma ya zo a cikin **Risala** cewa: "Duk wanda ya aikata wani zunubi daga cikin Musulmi, ba ya zama kafiri." Kuma Imam Bukhari (ra) ya yi masa Babi a cikin **Sahih Al-Bukhari** cewa: "Saɓo yana daga cikin ayyukan jahiliyya ba a kafirta mai yin sa."

## FASALI NA BIYU

**Bambanci Tsakanin Malamai Masu Ambaton Allah Kuma Masu Taimakon Allah Da Miyagun Malamai Rafkanannu Masu Taimakon Shaiɗan**

Ina cewa: "Ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya ku 'yan'uwana! Lalle bambanci tsakanin malamai masu ambato ko masu taimakon Allah da miyagun malamai rafkanannu masu taimakon Shaiɗan, shi ne duk wanda ya haɗa siffofi guda biyu, Ilimi da tsoron Allah, to, wannan yana daga cikin malamai masu ambaton Allah kuma masu taimakon Allah. Kuma duk wanda bai haɗa waɗannan suffofi guda biyu ba, to, yana daga cikin mugayen malamai rafkanannu, masu taimakon Shaiɗan.

Kuma ya zo a cikin **Ajwaba** (amsoshi) na Shehu Muhammadu ɗan Abdul-Kareem, Al-Magili Al-Tilmisaniy game da tammbayoyin da Amirin (shugaban) Hajj Baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya a lokacin da ya tambaye shi: Bambanci tsakanin malaman addini masu ambaton Allah, waɗanda su ne mafi albarka a mutanen duniya da mugayen malamai rafkanannu, waɗanda aka ambace su, su ne mafi muni ga mutanen duniya.

Sai ya amsa da cewa: "Bayan haka Ya Allah muna neman taimakonKa da kiyayewarKa a kan abin da muka tanada na shari'o'inKa. Lalle Kai Ka tambaye ni, sai na ce, tun lokacin da Allah Ya yi mana baiwa da Musulunci, wata musiba ta shafe mu a wannan garin na rashin amana ga wanda za a jingina masa ilimi daga makarantan ƙasarmu. Yana daga cikin siffarsu, Ajmawa (waɗanda ba su jin harshen Larabci) ba su fahimtar harshen Larabci, face kaɗan daga cikin maganar Larabawa na rubuce-rubucensu da karkatarwarsu. Kuma abin ya girma ta yadda ba su san manufar malaman, ko kuma wurin da aka kwafo shi (rubuto shi) da karkarwa.

Amma duk da haka suna da wasu littattafai waɗanda suke karantarwa, Hikaya da Labaru, suna maganganu a ckin addinin Allah, kuma suna riya cewa: "Su ne magadan Annabawa, kuma wai yana wajaba a gare mu mu yi koyi da su." Kuma ina neman Allah (swt) ya taimake mu, a kan ɗaukar wannan nauyi, wanda sammai da ƙassai, suka ƙi ɗauka. Kuma ina nema a gare ka (Amir), ka taimake ni a kan abin da Allah Ya sanar da kai game da waɗannan makaranta. Shin yana halatta a gare ni, in yi aiki da maganarsu a cikin addini, kuma **Taƙalidanci** (bin su) da su zai kuɓutar da ni a wurin Allah ko hakan ba ya halasta gare ni? Wajibi ne a yi bincike game da wanda za mu damƙa masa hukunci, kuma mu yi taƙalidanci (koyi) a cikin al'amuran addini.

To, za ka bayyana mana siffar wanda ya dace da haka a shari'ance? Kuma ka sani Allah Ya taimake mu, lalle mulki na Allah ne kuma babu wata nasara face daga wurin Allah. Ka kasance bawan Allah ga yi maSa ɗa'a; Zai kasance Ubangiji a gare ka da kiyayewarSa da taimakonSa.

Ka sani kai bawa ne wanda aka mallaka, ba ka mallakar kome. Haƙiƙa, majiɓincinKa Ya ɗaukaka ka a mafi yawa daga bayinSa, domin ka gyara masu addininsu da duniyarsu ba domin ka zamo shugaba ba ko majiɓincinsu, kai a cikin dukkanin abin da kake mulka, mai kiwo ne ba mai mallaka ba. Kuma dukkan mai kiwo za a tambaye shi game da kiwonSa.

To, idan ka san haka ya kai shugaba, to, ina umurtar ka da abubuwa guda biyu. Na farko: Ka nesantar da kanka daga masharranta daga gare ka, ka kusanto da masu alheri gare ka. Na biyu: Ka tambayi malamai masu ambaton Allah a kan dukkan abin da ba ka san hukuncinsa ba, a dukkan abubuwanka, domin ka yi hukunci da abin da Allah Ya saukar. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿فَسْـَٔلُوٓاْ أَهْلَ ٱلذِّكْرِ إِن كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ﴾ النحل: ٤٣

***"Ku tambayi waɗanda suka sani, in dai kun kasance ba ku sani ba." Alƙur'ani 16:43***

Waɗanda suka sani da waɗanda suka haɗa siffofi biyu, ilimi da tsoron Allah domin da ilimi ne ake sanin shiriya daga ɓata, da tsoron Allah ne, ake umurni da shiriya daga ɓata kada ka yi taƙalidanci (koyi) da kowa a cikin addininka face wanda ya tabbata cewa lalle shi, mallami ne mai tsoron Allah, domin duk wanda bai tabbata cewa, shi, malami ba ne, to, ana tsoron kada ya ɓace, kuma ya ɓatar da jahilcinsa.

Kuma duk wanda bai tabbata cewa shi, mai tsoron Allah ba ne, ana tsoron kada ya ɓace, kuma ya ɓatar da son zuciyarsa. Shin ba ka gani ba ne faɗar Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلْأَحْبَارِ وَٱلرُّهْبَانِ لَيَأْكُلُونَ أَمْوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلْبَٰطِلِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۗ وَٱلَّذِينَ يَكْنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلْفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ﴾ التوبة: ٣٤

***"Ya ku waɗanda suka yi imani! Lalle masu yawa daga cikin malaman (Yahudawa) da Ruhbanawa (Nasara) suna cin dukiyar mutane da ɓarna, kuma suna kangewa daga hanyar Allah."*** **Alƙur'ani 9:34**

Kuma ya zo a cikin **Sahih Muslim** daga Abu Sa'idul Khudri (Allah Ya yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (saw) ya ce:

(لتتبعن سنن الذين من قبلكم شبرا بشبر ذراعا بذراع حتى لو دخلوا جحر ضب لا تبعتموهم).

***"Lalle za ku bi hanyoyin waɗanda ke gabaninku, taƙa da taƙa, zira'i da zira'i, da za su shiga ramin damo da lalle za ku bi su."***

Sai muka ce:

يا رسول الله اليهود والنصارى؟

***"Ya Manzon Allah! Yahudawa da Nasara?"***

Sai ya ce:

"فَمَنْ"

***"To, su wane ne (idan ba su ba)."***

Kuma ya tabbata lalle da yawa daga cikin malaman wannan al'umma da masu bautarsu suna cin dukiyoyin mutane da zalunci. Kuma suna kangewa ga bin tafarkin Allah, saboda waɗannan malaman da masu bautar. Ɓarna ta watsu a cikin dukkan garuruwa. Manzon Allah (saw) ya ce:

(هلاك أمتى عالم فاجر وعابد جاهل)

***"Halakar al'ummata yana daga mutum biyu: malami fajiri da mai bauta jahili."***

Kuma Manzon Allah (saw) ya ce:

(أنا من غير الدجال أخوف عليكم من الدجال).

***"Ni ba ina ji maku tsoro ba ne daga Dajjal."***

Sai suka ce:

"ممن يا رسول الله؟"

***"To, daga mene ne kake ji mana tsoro, ya Manzon Allah?"***

Sai ya ce:

(من علماء السوء).

***"Daga miyagun malamai."***

Kuma an ruwaito daga Khuzaifa ɗan Yaman (Allah Ya yarda da shi) ya ɗauki tsakuwoyi (ƙananan duwatsu), a cikin tafin hannunsa, sa'annan ya ce: "Lalle addini ya haskaka kamar haskakawar waɗannan". Sa'annan ya ɗibi

ƙasa cikin tafin hannunsa, ya sanya yana kewaye tsakuwoyin, har ya rufe su, sa'annan ya ce: "Ina rantsuwa da Wanda raina yake hannunSa, waɗansu mutane za su zo suna rufe addini kamar haka, kamar yadda na rufe waɗannan tsakuwoyin," Ahadith.

Sa'annan Muhammadu ɗan AbdulKareem Al-Magili Al-Tilmasaniy, haƙiƙa, ya bayyana daga littafin Allah da Sunna da ijma'in malamai lalle da yawa daga cikin makaranta na waɗannan al'umma. Su ne miyagun malamai, kuma mafiya cutarwa ga Musulmi daga dukkan maɓarnata.

Sa'annan, ya ce: "Bayan maganar, to, inda ka ce, haƙiƙa, na bayyana kuma na buɗa, lalle da yawa daga cikin malaman al'umma, ba sa cikin masu ilimi, masu ambaton Allah, abin sani kawai, su dai suna daga cikin mugayen malamai ɓatattu masu ɓatarwa. Sai duk daga cikinsu suna karanta Alƙur'ani, da Hadisai, kuma suna juyar da yawa daga cikin Alƙur'ani kuma suna riya cewa: "Ai su, daga malamai ne masu ilimi masu ambaton Allah, suna musun lalle shi daga miyagun malamai yake."

To, da wani aibi ne za mu bambance tsakanin malamai masu ilimi da mugayen malamai? To, amsa ga Allah muke neman dacewa, Ya daidaita halayen malamai masu ilimi waɗanda ba su gauraya da halayen mugayen malamai. A asali, magana da aiki.

Kuma babu makawa Allah Yakan sanya haske ga duk wani mai shiryarwa daga cikin malamai masu ilimi masu ambaton Allah; haske a kan haske, a cikin kowane zamani daga zamunna. Kuma bayanin haka yana daga cikin hikimar Allah. BaYa azabtar da mutane har sai Ya bayyana masu abin da suke jin tsoro. Wannan ita ce sunna ta Allah a kan mutanen farko da kuma mutanen ƙarshe. Domin kada su ce ranar alƙiyama:

﴿إِنَّا كُنَّا عَنْ هَٰذَا غَٰفِلِينَ﴾ الأعراف: ١٧٢

*"Lalle mun kasance mun gafala, daga wannan."* **Alƙur'ani 7:172**

Yana daga cikin hikimominSa, Mai girma da ɗaukaka. Ya sanya wannan bayani a kan harshen mutum daga Annabawan farko da malamai masu ilimi a ƙarshe.

Kuma Ya sanya wa kowane mai shiryawa daga cikinsu, maƙiya daga cikin mujurimai. Su ne Shaiɗanun mutane da Aljannu. Sashensu yana wahayi ga sashe. Suna kauce wa magana domin ruɗi. Babu makawa ga duk wanda zai bi haske mabayyani ba. To, zai san gaskiya mai shiryarwa da ƙaryar Shaiɗanu sai Allah Ya sanya wa Annabawa mu'ujiza. Su kuma malamai masu ilimi da

ayyuka na ƙwarai. Babu wani Annabi da Allah Ya aiko shi ga bayinSa, face Allah Ya sanya masa haske mabayyani a tsakanin mutane dukkansu, kuma yana kan gaskiya bayyananna.

Haƙiƙa, kuma duk wanda ya saɓa masa ko ya bijire masa, yana cikin ɓatattu masu ɓatarwa, hakanan kuma masu ilimi daga kowace al'umma, har zuwa ranar alƙiyama, domin Allah Ya sanya su saboda shiriya da tsayar da hujja a cikin wannan al'umma, kamar Annabawa a cikin al'ummomin da suka shuɗe.

Saboda haka ne aka ruwaito, lalle a cikin farkon kowane ƙarni, Allah Yana aiko malami ga mutane, domin ya sabunta masu addininsu. To, babu makawa ga wannan malami a kowane ƙarni halayensa su kasance a cikin umurni da kyakkyawan aiki da hani daga mummunan aiki da gyara al'amuran mutane da adalci a tsakaninsu da taimakon gaskiya a kan ƙarya da taimakon wanda aka zalunta a kan azzalumi, saɓanin halayen malaman zamanimmu.

Saboda haka sai ya kasance baƙo a tsakaninsu, domin kaɗaituwarsa a siffarsa da halayensa da ƙarancin ira-irensa. To, a wannan lokaci zai bayyana, ayyana, lalle shi yana daga cikin masu gyara. Kuma duk wanda ya saɓa masa, ya bijire masa, ya juyar da mutane daga gare shi, lalle shi yana daga cikin maɓarnata. Saboda faɗin Annabi (saw) cewa:

(بدء الإسلام غريبا وسيعود غريبا فطوبى للغرباء)

***"Musulunci ya fara baƙo, kuma zai ƙare baƙo, madalla da baƙin."***

Aka ce su wane ne baƙi ya Manzon Allah? Sai ya ce:

(الذين يصلحون عند فساد الزمان).

***"Su ne waɗanda suke gyarawa a lokacin da zamani ya lalace."***

To, wannan yana daga cikin mafi bayanan alamomin malamai masu ilimi waɗanda su ne Allah Yake bayyana wa mutane addininsu da su. Yana daga cikin alamomin mugayen malamai lalle su ba sa gyara, kuma ba sa barin wanda zai gyara ya gyara. Misalinsu, kamar misalin ƙaton dutse ne a bakin rafi, ba zai sha ba, kuma ba zai bar wanda zai sha, ya sha ba. Kowane ɗaya daga cikinsu, ya fi tsananin cutarwa a kan mutane, daga Shaiɗanu dubu, labari ba kamar gani ba. Idan ba ka fahimci abin da muka tabbatar ba, idan wani abu da muka faɗi ya rikice maka, dukkansu, suna nau'o'i uku ne:

**Na Farko:** Shi ne duk wanda ya bayyana maka cewa: shi, malami ne, mai tsoron Allah.

**Na Biyu:** Shi ne duk wanda ya bayyana maka cewa: shi ba malami ba ne, ko kuma malami ne, amma ba mai tsoron Allah ba ne.

**Na Uku:** Shi ne duk wanda kake shakka a cikin al'amarinsa ba ka sani ba, shin malami ko kuwa ba malami ba ne?

To, duk wanda ya bayyana maka cewa malami ne mai tsoron Allah, to, wannan yana cikin malamai masana masu ambaton Allah. To, ka tambaye shi game da addininka, kuma ka yi taƙalidanci (koyi) da shi. Zai tsirar da kai, kuma zai ishe maka kamar wanda ya riya cewa, yana bayar da labari a kan abin da ya shafi addini, sai ya bayyana maka babu shakka cewa, lalle shi masani, ne kuma amintacce ne.

Amma duk wanda ya bayyana maka cewa, shi ba masani (malami) ba ne, ko kuma shi ba mai tsoron Allah ba, to, ba ya cikin malamai masu imani. Kada ka yi taƙalidanci (koyi) da shi a cikin abin da ya shafi addininka. Kuma kada ka tambaye shi, kamar wanda ya riya cewa, yana ba da labari ga abin da ya shafi addini, sai ya bayyana maka cewa shi ba masani ba ne, kuma ba amintacce ba ne. Kuma duk wanda ba ka san halinsa ba, kuma ba ka sani ba, shin shi malami ne mai tsoron Allah ko a'a, to, shi ma ka dakata daga gare shi, kada ka yi taƙalidanci (koyi) da shi a kan abin da ya shafi addininka.

Kuma kada ka tambaye shi ko da ya kasance mai fasaha ne, kuma Balarabe, ya haddace duk abin da ke cikin littafi, har sai ya bayyana maka, babu shakka cewa shi, malami, ne mai tsoron Allah. Kamar wanda yake riya cewa, shi yana bayar da labari a kan abin da ya shafi addini, cewa shi, masani, ne amintacce, amma bai bayyana maka shin shi yana da gaskiya ko ƙarya yake yi ba.

To, idan ka san wannan al'amarin makaranta na wannan zamani ba zai rikice maka ba, wajibi ne a kanka ka nemi malami wanda yake mai ilimi a duk wajen da yake, domin malamai masu ilimi a cikin wannan al'umma kamar Annabawa ne a cikin al'ummar da ta shuɗe, wajibi ne a dogara gare su, kuma a tafi zuwa gare su, ko da suna nesa. Wannan shi ne ƙarshen magana, ga Allah muke neman dacewa da shiriya.

## FASALI NA UKU

## Hukuncin Waɗanda Suke Furta Kalimar Shahada A Kan Al'ada Ba Su San Kome Na Ayyukan Musulunci Ba

Ina cewa, ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya ku 'yan'uwana! Lalle hukuncin waɗannan da muka ambata, su ne kafirai, babu shakka za a yaƙe su; a kashe mazaje, kuma a kame zuriyarsu da matansu, a karɓe dukiyarsu, a bautar da su dukkansu, ba saɓani a kan haka.

Kuma ya zo a cikin **Ajwaba**, na Muhammadu ɗan AbdulKareem ɗan Muhammadu Al-Magili Al-Tilmasaniyy game da tambayoyin da Amir (shugaba) Al-hajj Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya yi masa, sai ya ce: "Lalle na shiga wannan gari bayan mulkin Sunni Ali. Mafi yawansu sun tara dukiyoyinsu da masu hidimarsu ta fuskoki daban-daban, na shugabance su a kan haka dukkansu, sai na bar duk wanda ya ce shi ɗa ne, kuma Musulmi, sai da yawa daga cikinsu sun fita.

Sa'annan bayan haka na yi tambaya game da halayen wani sashe daga cikinsu da garuruwansu, sai ga su suna masu shaidawa cewa: Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne. Amma kuma duk da haka, sun ƙudurci a cikin zuciyarsu, cewa akwai wani abu wanda yake amfanar da su, kuma ya cutar da su, wanda ba Allah Mai girma da Ɗaukaka ba.

Kuma suna da gumaka, kuma suna cewa, ƙila ya ce: kaza ko kaza zai kasance. To, idan kaza, ya kasance, to, kaza zai faru. Kuma suna girmama waɗansu itatuwa, suna yin yanka domin su. Suna da waɗansu gidaje waɗanda suke girmamawa a wurinsu, ba sa jiɓintar wani shugaba, kuma ba sa yanke wani al'amari ƙarami ko babba face da umurnin shugabannin waɗannan gidajen waɗanda suke girmamawa.

Sai na tsawatar da su game da haka, sai suka ƙi su bari face da takobi. Shin hakan zai kafirtar da su har in yaƙe su, kuma in karɓe dukiyarsu duk da suna faɗi da harshensu, cewa: Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, Muhammadu Manzon Allah ne. Abin da Sunni Ali, Sarkin, bai tambaye su ba, abin da aka nema a wurinsu na Musulunci, ba waninsa ba. Kuma ana kama su kamar yadda ake kama Musulmi, amma yau haƙiƙa na umurce su da su bar abin da suke kai. To, idan suka ƙi bari, me zan aikata game da su?"

To amsa dai, ga Allah muke neman dacewa: "Lalle dukkan hukunci yana ga Allah, farko da ƙarshe. Kuma ka gode wa ni'imar Allah a kan ka, ka ji

tsoron Shi, a cikin abin da Ya jiɓinta maka da Ya rataya maka na umurni. Kuma ka sani, lalle abin da Sarki Sunni Ali ya ɗauka, to, ya ɗauki nauyi ne wa kansa. Kuma duk abin da ya aikata ya aikata wa kansa ne har ajalinsa ya ƙare. Sai ya sanya wannan aiki a tsakaninku, kai sai ka ɗauke shi. To, ka yi aiki saboda kanka wurin ɗaukar wannan nauyi wanda kake fatar albarkarsa, wanda kake neman godiya a ƙarshensa, duniya da lahira.

Kuma kada ka ce ga duk wani abu da bai dace ba, wanda kake da ikon gusar da shi, bai lazimta a gare ni in gusar da shi ba, domin ba ni na aikata ba, ai wanina ne ya aikata. To, dukkan abin da waninka ya aikata, sa'annan ya zo zuwa gare ka, idan alheri ne, to, ka tabbatar da shi. Kuma idan sharri ne, to, ka gusar da shi, ko da an ɗauki tsawon lokaci ana yi, domin mulkin dukkansa na Allah ne, kuma hukunci na ga Allah. Kuma kai bawa ne na Allah, wajibi ne ka gyara dukkan abin da ya zo zuwa gare ka, saboda haka aikinka ga duk wanda ya ce shi, Musulmi, ne ɗa daidai ne. Kuma haka ne duk abin da ya ayyana ga Musulmi, to, wajibi ne ka komar da shi zuwa gare shi dukkansa.

Kuma amma dukiyoyi idan ka gauraya su, kuma ka kasa gane ainihinsu, to, na Baital-Mali, sai ka juya su a abin da kake ganin gyara ne ga addinin Allah. Wanda duk ya yi da'awar cewa, Sarki Sunni Ali ya sanya an karɓa masa misalin nauyin zinari ɗari ko azurfa, kuma ya tabbatar da haka da shaida ta adalci, to, ba abin da ya rage face ka mayar masa da dukiyarsa, wadda Sarki Sunni Ali ya bar ta a kan haka. Domin dukiyar nan wadda yake ƙara ba a samu wane ne mai ita ba. Kuma duk dukiyar da aka rasa mai ita wadda take da yawa, kuma tantancewar a ga mai ita, ta buwaya bale a raba ta a ɓangaren masu bin sa bashi, to, lalle irin wannan dukiyar tana a cikin Baital-Mali na Musulmai.

Amma waɗannan mutanen da na siffanta halayensu, to, babu shakka su mushirikai ne, domin kafircinsu a bayyane yake. A hukunce, kai zai ma kasance da abin da bai kai haka ba. Kuma babu shakka, lalle yaƙar su, shi ne ya fi dacewa da cancanta daga kafiran da ba sa cewa: "Babu abin bautawa da gaskiya, sai Allah," saboda waɗannan da na siffanta halayensu sun lulluɓe gaskiya da ƙarya. Mutane da yawa sun ɓata ta dalilinsu, saboda jahilcin Musulmi har suka kafirta, alhali ba su sani ba. To, su ya fi cancanta da a yaƙa daga kafiran da ba su kusanci Musulunci ba. Za a yaƙe su da kashe mazansu da kama matansu da karɓe dukiyarsu, idan suka kurumce (doge) a kan shirkarsu sai a ƙona gidajen shugabannin shirka da allolinsu da wuta, kamar yadda Khalid ɗan Walid ya aikata (Allah Ya yarda da shi), ga waɗansu sashe da suka yi ridda, wurin ƙin bayar da zakka. Sai ya ƙona su da umurnin Amir (shugaba) Mumminai Abubakar Siddiƙ (Allah Ya yarda da shi).

Kuma duk wanda ka bar shi daga cikinsu saboda riyawarsu cewa, wai shi ɗa ne, Musulmi, sai ya bayyana maka cewa, shi, kafiri, ne, to, ka dawo da shi cikin bauta. Kuma ka karɓi dukiyarsa, sai dai idan ya tuba, ya kyautata Musuluncinsa, to ka bar shi kamar yadda ka aikata a farko. Kuma duk wanda ya bar wani abu domin Allah, to, Allah Zai canza masa da abin da yake mafi alheri a gare shi. Allah Ya ce:

﴿وَلِلَّهِ خَزَآئِنُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ لَا يَفۡقَهُونَ﴾ المنافقون: ٧

***"Dukkan taskokin sammai da ƙasa na Allah ne, amma munafikai ba su fahimta."*** **Alƙur'ani 63:7**

## FASALI NA HUƊU

**Hukuncin Yaƙar Mutanen Da Suka Furta Kalmar Shahada Kuma Suna Aikata Ayyukan Musulunci Sai Dai Suna Gaurayawa Da Ayyukan Kafirci**

To, ina cewa, ga Allah nake neman da cewa: Ku sani ya 'yan'uwana! Lalle yaƙar waɗannan mutanen wajibi ne, a kan abin da magabata suka yi tarayya a kansa, domin su kafirai ne da ijma'i, domin Musulunci da shirka a tare ba a karɓar su. Ya zo a cikin **"Kasidatul Jaza'iriyyat,"** misalin duk wani mai shirka ko da ya jingina kansa ga addinin kafiri ne. To, da haka ne za ka san cewa: Sarakunan Hausa kafirai ne a kan abin da muka sani a wannan zamani, saboda gauraya ayyukan Musulunci da na kafirci, kamar girmama waɗansu wurare da itatuwa da duwatsu da yin yanka da sadaka, domin su da neman taimakon bokaye da masu tsafi. Kuma dukkan waɗannan ko shakka babu kafirai ne, kamar yadda bayaninsa zai zo a cikin wannan fasali da fasali na shida, idan Allah Ya yarda.

Kuma ya zo a cikin **Ajwaba** na Muhammadu ɗan Abdul-Kareem Al-Magili Al-Timasaniy game da tambayoyin da Amir (shugaba) Al-hajj baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar, wanda aka fi sani da Askiya, ya yi a lokacin da ya tambaye shi, a kan Sunni Ali da kuma halin shugabannin Songai. Sai ya ce: "Uwarsa ta kasance daga Kasar Farr, su mutane ne kafirai, suna bauta wa gumaka da itatuwa da duwatsu. Suna yin sadaka saboda su, suna roƙon buƙatunsu ba sa yanke wani abu har sai sun sharwace su. Idan suka dawo daga tafiya sai nufi wurinsu sai su sauka a wurin.

Kuma waɗannan gumaka suna da masu tsare su, waɗanda suke yi musu hidima. Daga cikinsu akwai bokaye da masu sihiri suna tsarkake su, haka suka sunnanta ga kowane ƙarami da babba suna tsayuwa a wurinsu, har ya ƙagu a tsakaninsu, har ya ɗabi'antu da ɗabi'o'insu, suka ɗauki abin shirkarsu, abin taimakonsu". Sa'annan bayan mutuwar baban sa sai ya nemi shugabancin Songai. Kuma ya yaƙe su har sai da ya yi galaba a kansu har ya shugabance su, kamar yadda babansa ya kasance a gabaninsa daga cikin Sarakunan Songai, sai dai shi, tasowarsa tun daga ƙaraminsa, zuwa girmansa, ya taso a tsakanin kawunnansa (ƙannen uwa ko yayyenta) yana da ɗabi'a daga ɗabi'o'insu.

Ya kasance daga cikin siffofinsa, yana furuci da kalimar shahada da makamantanta na lafuzzan Musulmi. Kuma yana azumin watan Ramadan, kuma yana sadaka sosai da yanka da makamantansu a wurin Masallaci, amma duk da haka yana girmama sashen wasu itatuwa da duwatsu da yanka, domin

su da sadaka da ƙanƙan da kai da yi masu alwashi da neman biyan buƙatunsa daga wurinsu. Kuma yana neman taimakon su da masu sihiri da bokaye a cikin dukkan al'amarinsa, ko kuma ma yawancinsu.

Kuma dai yana daga cikin siffarsa ba ya tsayuwa ga mata da aure, ko babu aure na sharruɗɗan Musulunci ba haka ba. Duk lokacin da mace ta ba shi sha'awa a cikin dukkan masauratarsa sai ya kama ta, ya shigar da ita gidansa. Kuma yana daga cikin siffofinsa, ya halasta karɓar ginin Musulmi da dukiyoyinsu, kuma a kan kashe makaranta da malaman Fiƙhu da masu bautar Allah da mata da yara ƙanana, waɗanda ake shayarwa da makamantansu.

Amma duk da haka bai gushe ba tsawon rayuwarsa har ya mutu sai bayansa. Amir (shugaba) Askiya ya shugabance su. Ya mallaki garin, ya hana su game da yin shirka da ɓarna. To, mene ne hukunci a kan Sarki Sunni Ali da dukkan mataimakansa na azzalumai, waɗanda sun kasance suna aiki da irin aikinsa, shin su kafirai ne ko kuwa a'a? Shin za a bautar da yaransu bayansu a 'yanta matansu da yaransu ko kuwa a'a?

"Amsa dai ga Allah muke neman dacewa, shi, Sarki Sunni Ali da dukkan mataimakansa da mabiyansa masu goya masa baya, babu shakka su ne mafi zaluncin azzalumai, fasiƙai, waɗanda suke yanke abin da Allah Ya umurta a sadar, suna ɓarna a kan ƙasa. To, yaƙar da Amir (shugaba) Askiya ya yi masu, ya karɓe shugabanci daga hannunsu yana daga cikin mafi falalar jihadi, kuma mafi muhimmanci.

Amma shin su, kafirai ne ko kuwa a'a?". "To, ba a kafirta wani daga cikin Musulmi saboda zunubai, amma kuma abin da kuka ambata, game da halin Sarki Sunni Ali wanda ya san abin da yake yi kafirci ne, idan al'amarin ya kasance kamar yadda kuka ambata ne, to, shi, kafiri, ne. Kuma hakanan duk wanda ya yi aiki da kwatankwancin aikinsa, to, wajibi ne aka kafirtar da wanda bai kai wannan ba, amma bautar da yaransu, ni ban ga haka ba, ko da ya tabbata an yi masu hukunci da kafirci, domin kafirai kashi uku ne:

**Na Farko:** Wanda ya kasance asalinsa kafiri ne, kamar Kiristoci da Majusawa (masu bautar wuta) da makamantansu waɗanda suka yi gadon kafirci daga iyayensu.

**Na Biyu:** Wanda ya kasance Musulmi ne sai ya yi ridda daga Musulunci, ridda wadda take bayyane, cewa, shi ya fita daga addinin Musulunci, ya shiga waninsa na addinin kafirai.

**Na Uku:** Wanda yake riya cewa shi, Musulmi ne, sai muka yi masa hukunci da kafirci, sai wani abu ya bayyana a gare shi, wanda a zahiri ba

wanda ke yinsa face kafirai, kamar abin da kuka ambata ga Sunni Ali. To, kafirai waɗanda suke na asali, ana kama zuriyarsu da matansu, kuma ana raba dukiyarsu. Wannan babu saɓanin a kan haka a wurin malamai.

Amma kafircin wanda ya yi ridda akwai saɓani. Ɗan Ƙasim, ya ce: "Waɗanda suke zaune a wurin da yake kewaye na Musulmi sai suka yi ridda daga addininsu zuwa kafirci, ba a kama yaransu da matansu, amma dukiyarsu ta zama ta Musulmi." Ɗan Rushdi ya ce: "Wannan shi ne abin da yake daidai idan aka duba, domin waɗanda suka yi ridda ai asalinsu 'ya'ya ne" ya ce a kan abin da Ɗan Kasim ya tafi game da waɗanda suka yi ridda, shi ne abin da mafi yawan malamai suka tafi a kai da shugabannin magabata.

To, idan ka san haka duk wanda ya aikata wani abu daga cikin waɗancan ayyukan, waɗanda suke wajabta, kafircin, to, za a neme shi da ya tuba. Idan ya tuba sai a bar shi, idan kuma ya ƙi tuba, za a kashe shi da takobi a matsayin kafiri, amma ba za a bautar da yaransu ba. Abin sani kawai za a tilasta musu yin musulunci, amma sayar da iyayen yaran waɗanda suka haifa, watan ummul walid yana daga cikin dukiyar Baital-mali. Ni ban ga wani laifi ba, ko duk da yaransu ba a bautar da su.

Kuma ya zo a cikin "**Mukhtasar**", idan jma'a suka yi ridda, kuma aka yaƙe su, to, kamar waɗanda suka yi ridda ne, Shibkhitiy, ya ce: "A wannan akwai wani muhalli na bayanin haka, za a nemi manyansu da su tuba, za a tilasta wa ƙananansu, kuma za a sanya dukiyarsu ta zamanto waƙafi, ba za a kama iyalansu ba, wannan shi ne abin da Umar (Allah Ya yarda da shi) ya aikata. Kuma shi ne a bin da da yawa daga cikin malamai suka tafi a kai da shugabanni magabata face kaɗan.

Asbagu ya ce: "Kamar kafirai ne abokan yaƙi, za a bautar da yaransu da iyalansu". Kuma na rantse haka ne umurnin yake, haka kuma Umar (ra) ya saɓa wa Abubakar (ra), game da waɗanda suka yi ridda daga Larabawa. Sai Abubakar (ra) ya sanya su daga cikin waɗanda suka warware alƙawari, sai ya kashe manyansu. Aka kama matansu da yara ƙanana, kuma aka sanya su cikin rabo. Haka kuma dukiyarsu. Wannan shi ne aikin Abubakar Siddiƙ (Allah Ya yarda da shi). Kuma ga Allah muke neman dacewa da shiriyarSa.

## FASALI NA BIYAR

### Hukuncin Yaƙar Masu Taimakon Kafirai Daga Cikin Malamai Da Ɗalibai Da Jahilai

Ina cewa, ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya 'ya'uwana! Lalle yaƙar waɗannan waɗanda na ambata wajibi ne da ijma'in malamai domin su, kafirai ne, ko shakka babu, ko da sun kasance suna lulluɓe ƙarya da gaskiya, saboda sun kasance suna halasta musu abin da Allah Ya haramta, ko kuma sun kasance mataimakansu ne a kan mumunai a cikin rundunoninsu.

Ya zo a cikin **Ajwaba** na Muhammadu ɗan AbdulKarim, ɗan Muhammadu Al-Magiliy Al-Tilimasiniyy game da tambayoyin da Amir (shugaba) Al-Hajj baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka sani da Askiya', a lokacin da ya tambaye shi, game da shugaba kamar wanda yake aikata haram kamar Miksu (mai karɓar haraji) da makamantansu.

Idan aka ce masa, wannan abin da kake aikatawa haramun ne sai ya ce, "Ai ni Allah Ya tsare ni daga haram, duk abin da nake aikatawa, halal ne, lalle mu mun fi ku sani", shi halinsa gauraya ƙarya da gaskiya. Yana da waɗansu malaman Fiƙihu waɗanda ya riƙe su. Saboda wannan, duk lokacin da ya yi nufin aikata wani abu, na son ransa sai ya kusanto da su ya ce; masu: "Shin kaza ba halal ba ne?" sai su ce: gaskiya ne, halal ne gare ka, sai su dace da shi a kan manufarsa, sai ya lulluɓe da su wajen aikata zalunci da fajirci.

Shin irin wannan shugaban azzalumi ne, ko kuma kafiri ne, saboda ya halatta abin da Allah Ya haramta, kuma haka waɗancan malaman? Sai ya amsa da faɗarsa: Duk wanda ya tabbata cewa ya halasta zama da jiɓintar kafirai da makamantansa, kamar cin dukiyar mutane da ɓarna, wajibi ne a yi masa hukunci da kafirci.

Haka kuma duk wanda ya yi musun gaskiya bayyananna, kuma ya lulluɓe ta da ƙarya. Ya faɗi a cikin littafinsa, **'Misbahul Arwah Fi Usul Falah'** a cikin bayanin kafircinsu, "Su kafirai ne a kan muminai." Abin da ke nunawa a kan rashin imani da nassin Alƙur'ani game da hani ga jiɓintar kafirai, saboda faɗarSa Maɗaukaki, cewa:

﴿ تَرَىٰ كَثِيرًا مِّنْهُمْ يَتَوَلَّوْنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ لَبِئْسَ مَا قَدَّمَتْ لَهُمْ أَنفُسُهُمْ أَن سَخِطَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ وَفِى
ٱلْعَذَابِ هُمْ خَٰلِدُونَ ﴿٨٠﴾ وَلَوْ كَانُوا۟ يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلنَّبِىِّ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ مَا ٱتَّخَذُوهُمْ أَوْلِيَآءَ وَلَٰكِنَّ
كَثِيرًا مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴾ المائدة: ٨٠ – ٨١

***"Kuma za ka ga masu yawa daga cikinsu (munafukai) suna jiɓintar waɗanda suka kafirta, to, lalle tir! Da abin da suka gabatar wa rayukansu, Allah Ya yi fushi a kansu, su a cikin azabar Allah masu dawwama ne, da sun kasance sun yi imani da Allah da AnnabinSa da abin da ya saukar gare shi (saw)da ba su riƙe su masoya ba, sai dai da yawa a cikinsu fasiƙai ne."***

**Alƙur'ani 5:80-81**

Ya ke cewa: "Domin dalilin da aka ambata a bayyane yake lalle duk wanda ya lazimci imani, za ka ga ba ya jiɓintar kafirai, sai ya lazimci duk wanda ya shaida Allah Mabuwayi ne. Shin kafirta duk wanda ya jiɓinci wani daga cikinsu, ko waninsa, a kowane lokaci, kuma a kowane wuri yana halatta, jiɓintar su shi ne taimakon su, domin mai jiɓinta shi ne mai taimako, ba a yi masa wani uzuri da abin da ya bayyana a gare shi na nufin amfanarwa?

Kamar wanda ya yi sujada ne ga gunki saboda da Dirhami dubu ɗari sai ya tuba. To, idan ya tuba sai ya bari. Idan kuwa ya ƙi, to, za a kashe shi da takobi. Idan ya mutu ko aka kashe shi kafin ya tuba, to, ya mutu kafiri, ba za a yi ma sa wanka ba, kuma ba za a yi ma sa sallah ba, kuma ba za a bizne shi a maƙabartar Musulmi ba, ko da ya kasance tsawon rayuwarsa yana furta kalimar Shahada; yana Sallah da Azumi da Hajji. Kuma yana aikata dukkan nau'ukan ayyuka na ɗa'a, domin babu wani aiki face da imani saboda halayen kafirci suna ɓata dubu daga halayen imani. Karshen Maganar ke nan.

Ni kuma na ce: "Sai ya tabbata da wannan duk wanda ya jiɓinci haka (ayyukan kafirci), yana daga cikin kafirai kowane ne shi, a kowane zamani, kuma a kowane wuri. To, ya yi ridda a addinin Musulunci. In Musuluncinsa ya inganta kafin haka, yaƙar su shi ya fi, ga kowane yaƙi. Kuma dukiyarsu ta zama ta Musulmi amma hukuncin bautar da su da bautar da yaransu da matansu." To, ya gabata a cikin bayanin saɓanin bautar da masu ridda. Lalle da yawa daga cikin malamai ba sa halasta hakan, saɓanin Asbag da waɗanda suka yi muwafaƙa ce da shi a cikin malamai a game da halasta hakan. Duk wanda ya yi duba da kyau a cikin wannan Fasali zai san cewa masu taimakon kafirai daga cikin malamai da ɗalibai da Jahilai, kafirai ne, domin sashensu suna rufe ƙarya da gaskiya, saboda su. Wannan kafirci ne, kamar yadda ya shuɗe. Kuma sashensu suna halasta musu abin da Allah Ya haramta, kuma shi ma kafirci ne kamar yadda ya shuɗe. Kuma wasu sashensu, suna jiɓintar su da taimakon su, cikin rundunoninsu, a kan rundunonin Musulmi. Wannan kafirci ne kamar yadda ya shuɗe. Allah ne Wanda ake neman dacewarSa da shiriyarSa.

## FASALI NA SHIDA

## A Cikin Hukuncin Yaƙar Musulmi Masu Sakaci (Jinkiri) Waɗanda Ba Su Shiga Mubayi'ar Wani Shugaba Daga Shugaban in Musulunci Ba

Ina cewa, ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya ku 'yan'uwa! Lalle yaƙar waɗannan waɗanda muka ambata wajibi ne a kan abin da magabata suka yi tarayya a kansa, har sai sun shiga ƙarƙashin mubayi'ar wani Amir (shugaba) na muminai, akan yi wa Allah ɗa'a da ManzonSa (saw). Idan aka kira su zuwa ga mubayi'a suka ƙi.

Kuma ya zo a cikin **Ajwaba** na Muhammadu ɗan AbdulKareem ɗan Muhammadu Al-Magili Al-Tilmasaniy game da tambayar da Amir (shugaba) Al-Hajj Baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya yi a lokacin da ya tambaye shi game da hukuncin waɗanda muka ambata sai ya ce: "Lalle waɗansu sashen Musulmi a gabas da mu da yamma da mu, sun saurare ni, suka nema da su shiga ƙarƙashin yi mana ɗa'a, shin za mu amsa masu a kansa? Ko kuma za mu tsaya a kan hukuncin garimmu wanda Allah Ya gadar mana da shi daga Sunni Ali?

Amsa a nan ita ce: "Allah ake neman dacewarSa, ka sani ba ya halatta ga wasu ƙungiya na Musulmi su kasance ba su da shugaba, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْ ﴾آل عمران: ١٠٣

***"Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku, kada ku rarraba."***
**Alƙur'ani 3:103**

Kuma ya zo a cikin **Sahih Muslim** daga ɗan Umar, Lalle shi ya ce: Ya ji Manzon Allah (saw) yana cewa:

(من خلع يدا من طاعة لقي الله يوم القيامة لا حجة له، ومن مات ليس في عنقه بيعة مات ميتة جاهلية)

***"Duk wanda ya cire (janye) hannunsa daga biyayya ga shugaba, lalle zai haɗu da Allah ranar ƙiyama babu wata hujja a gare shi. Kuma duk wanda ya mutu ba shi da mubaya'ar wani shugaba, to, lalle ya yi mutuwar Jahiliyya."***

Ka amsa masu zuwa ga mubayi'arsu da shiga ƙarƙashin ɗa'arka idan suka ƙi, ka tilasta masu a kai, gwargwadon iyawarka, kuma ka yaƙe su da takobi har sai dukkansu sun shiga ƙarƙashin ɗa'arka, akan yi wa Allah da ManzonSa ɗa'a. Wannan shi ne mafi falalar jihadi, kuma mafi muhimmanci.

Kuma ya ce: a game da garin da suke da Amir (shugaba) yana shugabantar su a wurin gyaran addininsu da duniyarsu gwargwadon iko a cikin wannan zamani. To, waɗannan ba su halatta ga wani daga cikinsu ya cire kansa daga cikin shugabancinsa ba, saboda shi ya fi cancanta da su daga waninsa, matuƙar yana shugabanci a kan yi wa Allah ɗa'a a cikin al'amuransa. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلَا تَنَازَعُوا فَتَفْشَلُوا وَتَذْهَبَ رِيحُكُمْ﴾ الأنفال: ٤٦

*"Kada ku yi jayayya, sai ku rarraba, sai ƙarfin ya tafi."* Alƙur'ani 8:46

Kuma ya zo a cikin **Sahih Muslim** daga Abu Sa'idul Khuduri (Allah Ya yarda da shi) ya ce; Manzon Allah (saw) ya ce:

"(إذا بويع الخليفتان فاقتلوا الآخر منهما)"

*"Idan aka yi wa khalifofi biyu mubayi'a, to, ku kashe na biyun."*

Karshen maganar ke nan. Allah Shi ne Wanda ake neman dacewarSa da shiriya.

## FASALI NA BAKWAI

### Hukuncin Yaƙar Masu Yaƙar Musulmi

Ina cewa, ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya ku 'yan'uwana! Lalle yaƙar waɗanda suke yaƙar Musulmi wajibi ne a ijma'in malamai. Kuma ya zo cikin **Ajwaba**, na Muhammadu ɗan Abdul-Karim, ɗan Muhammadu Al-Magili Al-Tilmasaniy game da tambayoyin da Amir (shugaba) al-Hajj, baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya ya yi a lokacin da ya tambaye shi game da yaƙar waɗanda suke yaƙar Musulmi. Ya ce: "Mene ne amsarku, waɗanda suke yaƙi a tare da su, mutanen da suke riya cewa su, Musulmi ne, kuma suna zaune tare da su a gida da halin tafiya. Kuma suna gaurayuwa da su a cikin dukkan halayensu da al'amuransu, a lokacin da su, waɗannan masu yaƙar mu, suka zo yaƙar mu, sai rundunarsu ta haɗu da su, sai suka zo da su zuwa gare mu, suka ce: "Mu, Musulmi ne."

Sai muka ce masu: "To, ta yaya za ku haɗu da waɗancan masu yaƙar mu? Sai suka ce: "Ba mu da ikon fita daga gare su, muna tsoron kada su kama mu, kuma idan kuka fita waɗansu za su kama mu, domin mu, miskinai ne, ba mu da ikon kare kanmu." Sai muka mayar masu da dukiyarsu. Kuma muka ce musu ku rabu da su. Shin za mu bar yaƙar waɗannan masu yaƙar mu, domin kada mu cutar da waɗancan Musulman, waɗanda suke tare da su, kuma suka ƙi rabuwa da su, ko kuwa babu makawa sai mun yaƙe su, ko da kuwa, cutarwa za ta samu waɗanda suke tare da su daga cikin Musulmi, waɗanda muka ambata. Haƙiƙa, waɗansu daga cikin malaman na garimmu sun ruɗar da ni, har sai da na dakata daga gare su?

Amsa a nan ita ce: Ga Allah muke neman dacewa ga daidai, amma waɗanda suke yaƙar Musulmi babu makawa za a yaƙe su, babu laifi a kanku, idan kuka samu wani a cikinsu wanda yake cikin waɗancan Musulmi, domin su sun zalunci kawunansu da suka zauna da su. Amma abin da ba ku sani ba daga cikinsu na rayukansu da dukiyoyinsu, har kuka ɓata babu kome a kanku game da shi. Amma wanda kuka sani kafin ku ɓata shi, to, ku nisance shi, ku mayar da shi zuwa ga masu shi, kuma hakan idan ba su zaɓi zama da su ba ne.

Amma waɗanda suka zaɓi zama da su ko kuma sun kasance suna taimakon su, a kan ɓarna, to, waɗannan suna cikinsu, ku kashe su, kuma ku karɓe dukiyarsu, kuma kada ku karɓi tubansu, idan Allah Ya ba ku sa'a a kansu. Baban Kasim Al-Barzaliy ya ambaci haka, abin da yake cewa: Haƙiƙa wani shugaba ya fanɗare da wasu ƙungiya a wani yanki na Afirika mafi yawansu sun zurfafa cikin kafiran amana, sai malamin mu ɗan Arfata ya ba da

fatawa cewa: “Dukiyarsu ta halatta”, aiki da mafi rinjayensu, har sai dai masana bambancin halal da haram, suka yi ƙoƙarin bambancewa a tsakaninsu.

Ya ce: Su masu saɓo ne saboda sun ƙara yawan masu yaƙar Musulmi da ƙara duhunsu, saboda haka ba su da wani hurumi (kariya), wai cewa su sun tsare kansu ba su gauraya da su ba, kuma haka idan ba a samu wani da zai nuna haka daga wurinsu ba. Idan kuwa ba haka ba, to, zai kasance kamar wanda aka matsa masa a garin da yake, cikin garin Biladul-Harbi (ƙasar da Musulmi suke yaƙar da kafirai) ta wurin da ba ya iya fita daga cikin garinsa, yana jin tsoron kansa da dukiyarsa da 'ya'yansa. Karshen maganar ke nan, Allah muke neman dacewarSa da shiriya.

## FASALI NA TAKWAS

### Hukuncin Yaƙar Azzalumai Daga Cikin Shugabannin Musulmi

Ina cewa ga Allah nake neman dacewa; ku sani ya ku 'yan'uwa! Lalle yaƙar azzaluman shugabannin Musulmi waɗanda suke karɓar dukiyar Musulmi da zalunci da nuna ƙarfi ko shakka babu wajibi ne, idan yaƙar nasu ya kasance saboda taimakon gaskiya ne a kan ƙarya, kuma taimakon wanda aka zalunta ne, a kan azzalumi, idan gusar da zaluncin zai yiwu ga Musulmi, ba tare da cutarwar da za ta fi wancan zaluncin ba.

Kuma ya zo a cikin **Ajwaba** na Muhammadu ɗan AbdulKareem, Al-Magiliy Al-Tilimisaniy game da tambayar da Amir (shugaba) Al-Hajj, baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya yi a lokacin da ya tambaye shi a kan haka sai ya ce, idan gari ya kasance akwai Musulmi, shugabanninsu suna karɓar dukiyarsu da zalunci da nuna ƙarfi, shin zan iya mayar da wannan zaluncin ko da kuwa zan kashe shi ko kuwa a'a? Kuma hakanan idan shugaba ya kasance yana karɓe kayan mazauni da miskini, kuma ba ya hana masu ɓarna, shin ni zan iya hana shi da yaƙar sa ko kashe shi ko kuwa a'a? Kuma har wayau shugaba azzalumi wanda yake zaluntar mutane a duk inda ya haɗu da Musulmi da wasu kaya a tare da su, ya ƙwace, kuma idan wani mutum baƙo ya mutu ko wanda ba baƙo ba, a garinsa sai ya karɓe dukiyarsa ko da kuwa waliyyansa suna nan ko ba sa nan, kuma yana tsare waɗansu matafiya waɗanda suka zo wucewa ta garinsa, ya zaunar da su, ya binciki kayayyakinsu, kuma ya binciki abin da yake ciki, sai ya karɓi abin da yake riya cewa zakka ne?

"Amsa a nan ita ce, ga Allah muke neman dacewa. Lalle duk wani shugaba daga cikin shugabannin da ka siffanta su, da suke riƙe Maski da zalunci da ɓarna da rashin gyara, idan za ka iya gusar da zaluncinsu daga Musulmi, ba tare da wata cutarwa ba a kansu (Musulmi), har mu tsayar masu da Amir (shugaba) adali, to, ka aikata haka.

Kuma idan haka ɗin ya kira zuwa ga yaƙi ko kuwa kashe da yawa daga cikin azzalumai da mataimakansu da kashe da yawa daga mataimakanka, domin duk wanda aka kashe daga cikinsu (azzalumai) shi ne mafi sharrin wanda aka kashe, kuma duk wanda aka kashe daga cikinku shi ne mafi alkhairin shahidai, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ ٱشۡتَرَىٰ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَنفُسَهُمۡ وَأَمۡوَٰلَهُم بِأَنَّ لَهُمُ ٱلۡجَنَّةَۚ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقۡتُلُونَ وَيُقۡتَلُونَ﴾ التوبة: ١١١

*"Lalle ne, Allah Ya saye daga muminai rayukansu da dukiyarsu cewa; lalle suna da sakamakon Aljanna, suna yaƙin nan cikin hanyar Allah, saboda haka suna kashewa ana kashe su."* Alƙur'ani 9:111

Yana daga cikin hanyoyin Allah tsare zalunci ga Musulmi da caccanza munanan ayyuka, to, yaƙar waɗanda suke yaƙar Musulmi da azzalumai daga cikin musulmi yana daga cikin mafi falalar jihadi. Idan ba za ka iya gusar da zaluncinsa ba, ga Musulmi, face da cutarwa a gare su (Musulmi), to, an samu cin karo na cuta guda biyu, to, ka kiyaye kada ka canza mummunan aiki da mummunan aiki irinsa, ko wanda ya fi shi, (muni) sai ka tambatar ana aikata mafi sauƙi daga cikin cututtukan nan guda biyu, domin aikata abin da ya fi sauƙi daga cikinsu, ƙa'ida ce shahararriya, kuma sunna ce wadda muka gada.

Kuma ba ya daga cikin munkar kashe azzalumai da maɓarnata da mataimaknsu, ko da kuwa sun kashe da yawa daga cikinku, idan kisan naku da suka yi ya kasance ne, domin taimakon gaskiya a kan ƙarya da taimakon wanda aka zalunta a kan azzalumi. Karshen maganar ke nan. Allah ne wanda ake neman dacewarSa da shiriya.

## FASALI NA TARA

### Abubuwan Da Suka Wajaba A Kan Shugabannin Musulunci Na Tsayar Da Dokokin Musulunci Da Gyara Garuruwa Da Canza Munanan Ayyuka

Ina cewa, ga Allah nake neman dacewa. Ku sani ya ku 'yan'uwana. Lalle yana daga ckin abin da yake wajaba a kan Amir (shugaba) na muminai da mataimakinsa a cikin garinsa, tsayar da dokokin Musulunci, kamar gina wurin taruwa domin sallar Jumma'a da masallatai (Na khamsu Salawat) da kuma tsayar da sallolin guda biyar a cikinsu da bayar da Zakka ga wanda ya cancanta da juya nau'o'in dukiya ta Allah (swt) a wurarenta, kamar yarda Ya shar'anta ga umurni da kyakkyawan aiki da hani daga mummunan aiki. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ﴿٤٠﴾ ﴾الحج: ٤٠

***"Haƙiƙa, Allah Zai taimaki wanda ya taimake Shi, lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi."*** **Alƙur'ani 22:40**

﴿ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُواْ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَنَهَوۡاْ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۗ ﴾ الحج: ٤١

***"Su ne waɗanda idan muka sanya su shugabanni a ƙasa, suna tsayar da Sallah, kuma suna bayar da Zakka, kuma suna umurni da kyakkyawan aiki, kuma suna hani daga mummunan aiki."*** **Alƙur'ani 22:40**

Yana daga cikin abin da ya wajaba ga shugaba da mataimakinsa a cikin garinsa kiyaye addini, ta inda ba za su bar wani ba, yana magana a cikin addinin Allah kamar karantarwa, ko hukunci, ko bayar da fatawa, har sai ya kasance daga cikin masu ilimi, masu tsoron Allah. Haƙiƙa, Amir (shugaba) Al-Hajj, baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar, wanda aka fi sani da Askiya, ya tambayi Muhammadu ɗan Abdul-Karim Al-Magili Al-Tilmasaniy game da hukuncin kiyaye addini a kan shugabannin Musulunci. Sai ya amsa da abin da aka ambata, sai ya ce: "Ashe ba yana daga ckin manyan wajibai a kan kowane Amir (shugaba) ya kore duk wani maɓarnaci daga kan hanyar duniya? To, ta yaya ba zai zama wajibi a kansa ba, ya kore su daga hanyar addini?

Yana daga cikin abin da ya wajaba a kan Amir (shugaba) na muminai da mataimakinsa su canza munanan abubuwa daga duk wanda yake riyawa daga cikin mutane cewa; Lalle shi ya san wani abu a ilimin gaibi ta hanyar yin

zane a kan yashi da makamantansu, ko kuma ta hanyar taurari, ko ta hanyar labarin Aljannu, ko da wani abu daga cikin kukan tsuntsaye, ko kuma tashinsu da makamantan haka.

Haƙiƙa, Al-Amir (shugaba) Al-Hajj baban Abdullhi Muhammadu ɗan Abdul-Karim wanda aka fi sani da Askiya, ya tambayi Muhammadu ɗan Abdul-Karim ɗan Muhammadu, Al-Magili, Al-Tilmasaniy, ga dukkan abin da muka ambata sai ya amsa da cewarsa: "Wajibi ne a kan shugaban Musulmi da kuma duk wanda yake da iko daga cikin muminai da su canza wanɗancan munanan ayyuka daga duk wanda yake riya cewa; Lalle shi ya san wani abu daga ilimin gaibi da wani abu daga waɗancan al'amura ko wasunsu. To, shi maƙaryaci ne, kafiri, kuma duk wanda ya gaskata shi ya kafirta. Wajibi ne a tsayar da su domin tuba tare da takobi. Duk wanda ya tuba, a bar shi, kuma duk wanda ya ƙi, to, a kashe shi da takobi kafiri ne, ba za a yi masa wanka ba, kuma ba za a sanya masa likkafani ba, kuma ba za a bisne (turbuɗe) shi a cikin maƙabartar Musulmi ba." Kuma Manzon Allah (saw) ya ce:

(من صدق كاهنا فقد كفر بما أنزل على قلب محمد صلى الله عليه وسلم).

***"Duk wanda ya gaskata boka, to, haƙiƙa ya kafirta da abin da aka saukar wa Muhammadu (saw)."***

Yana daga cikin abubuwan da suka wajaba a kan shugaba da mataimakinsa, a cikin garinsa, canza munanan ayyuka. Duk wanda yake riya cewa, yana rubutu saboda janyo wani alheri, ko yalwar arziki, ko so, ko kuma kare ɓarna kamar watsa maƙiya a yaƙi da hana ƙarfe yanka (tauri) da hana kibiya cutarwa (kauda-bara) da makamantansu, na magungunan Masirhira da ayyukansu. Haƙiƙa, Amir (shugaba) al-Hajj, baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya tambayi Muhammadu ɗan Abdul-Karim ɗan Muhammadu Al-Magili Al-Tilmasaniy, a kan duk abin da muka ambata, sai ya amsa da cewarsa, "Za a tsayar da kowane ɗan sihiri da 'yar sihiri da duk wanda yake riya cewa, lalle yana da wani Sinadarin gano gaibi da wasu kalimomi waɗanda ba sunayen Allah ba ne da makamantansu waɗanda suke cewa, suna janyo arziki da shi, suna wargaza maƙiya da shi, ko makamancin haka, a gaban takobi. Duk wanda ya tuba daga cikinsu a bar shi, kuma duk wanda ya ƙi, a kashe shi."

Kuma duk wanda ya riya cewa abin da yake rubutawa da makamantansu daga cikin Littafin Allah ne, kuma yana daga cikin daɗaɗan maganganu, kada ku gastakata shi. Abin sani kawai maƙaryaci ne. Abin da ya zama wajibi a tsoratar da shi, idan ya ƙi bari, to, sai a azabtar da shi, azaba ta

kwatanci ga 'yan-baya, domin ya zamanto an toshe ɓaraka, kuma an kiyaye shari'a da aƙida. Karshen maganar ke nan.

Kuma na ce: abin da muka ambata (na mugun malami mai sihiri) cewa: haka ba ya lazimtar da haramcin aiki da abin da ya dace da shari'a, a'a ya halatta a yi aiki da duk abin da ya dace da shari'a, daidai ne abin ya kasance ta hanyar janyo amfani ne, ko ta hanyar tsare cutarwa, kuma duk ɗaya ne daga cikin abubuwan da ake sha ne, ko kuma abin da ake ratayawa na magani, amma abin da aka haramta kawai, abin da ya kasance ta hanyar masu sihiri na wasu Sinadarin sihiri da sunayen da ba sunayen Allah ba, kamar yadda ya bayyana da makamantansu na abubuwan da ba su dace da shari'a ba.

Yana daga cikin abubuwan da suka wajaba a kan shugaba da mataimakinsa a cikin garinsa, canza munanan abubuwa kamar buɗe al'aura, ga 'ya'ya da bayi da kuma gauraya maza da mata a cikin kasuwanni da hanyoyi da rashin katange mace ga ɗan'uwan mijinta, ko abokinsa, ko ɗan baffansa, (ɗan wan Uba ko ƙanin Uba). Haƙiƙa, Amir (shugaba) Al-Hajj baban Abdullahi Muhammadu ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya yi tambaya game da duk abin da muka ambata, a wurin Muhammadu ɗan Abdul-Kareem ɗan Muhammadu Al-Magili Al-Tilmasaniy.

Sai ya amsa da faɗarsa cewa: Yana daga cikin abubuwa mafiya muni, abin da ka ambata na haɗuwar maza da mata da buɗe al'aura, to, wajibi ne, a kan shugaban Musulmi ya yi ƙoƙari wurin hana waɗannan abubuwa gwargwadon ikonsa. Kuma ya sanya waɗanda aka amince musu, a kan wannan aiki dare da yini bayyane da ɓoye. Wannan ba wai yana daga cikin tajassus (watau: bin diddigi) ga Musulmi ba ne. Wannan yana daga cikin mafi kyawon shugabanci da kore masu laifi, musamman ma idan ɓarna ta watsu a cikin gari. Kuma yana daga cikin abubuwan da suka dace, waɗanda yake kuma wajibi ne a kare mace daga duk wani wuri na tuhuma. Ko kuma shugaba ya sanya amintattu suna kewayawa dare da yini a kan hanyoyi, duk wanda suka gani yana magana da matar da ba ta halatta ba ya yi magana da ita, ko yana shiga wuri, ko kuma yana kallon ta, to, su kama shi, su zo da shi.

Wanda aka jiɓinta masa shugaban Hizba, a cikin wannan da makamatansa sai ya abzatar da shi. Kuma ya tsorata shi a abin da ya dace da irin sa, bisa gwargwadon munanan ayyukansa. Wannan ba wani haddi ba ne da aka iyakance, kuma ba wata doka ce ƙayyadajjiya ba. Wannan kawai an sanya shi ga wanda aka wakilta, sai shugaba ya duba ya ga abin da ya dace. Kuma ya ji tsoron Allah, ya yi doka a wurin hana ɓarna da kawo wa ƙasa alheri. Ya kawo gyara da tsoron Allah ba da bin son rai ba. To, idan ka ce wani amintacce ne wanda ya cancanta da haka, wanda za a amince masa, har

shugaba ya sanya wannan al'amarin a hannunsa, kuma ya jiɓinta shi zuwa gare shi, babu shi wannan zamani, musamman a wannan lokaci.

Sai na ce: “Aikata abin da ya fi sauƙi, idan abubuwa biyu masu cutarwa suka haɗu, wajibi ne, da ijma'in malamai, kuma cutarwa da aikin Hizba zai aukar, ya fi sauƙi a kan barin waɗannan laifuffuka su yaɗu, don cutarwa da za a samu daga haka. Idan aka bari fasiƙai suna laifi, kuma babu shakka a kan haka. Kuma ai ɓarnar kallon (matar da ta ba ta halatta ba) za a iya hanawa ta hanyar nisantarwa da masu wannan laifi daga wuraren tuhuma, kamar tafiya cikin dare da makamantansa da keɓancewa. Babu cutarwa mafi girma a kan mutane, idan akwai nisantar haka a mafi rinjayen wannan.”

Amma barin ɓarna da ke cikin barin masu aikin Hizba a kan fasiƙai maza da mata, musamman a wurin keɓancewa da wurin da yake a bayyane da wurin tuhuma, to, babu wata hanya ta hana aikin Hizba face zartarwa, musammam ma a wannan lokaci namu wanda sharri ya yawaita, kuma a cikin wannan gari na ƙasar Hausa da makamantansu.

Kuma daga cikin abubuwa waɗanda suke bibiya masu gudana, tsarin siyasar shugabanci a cikin mafi-yawa a garururwa na Musulunci, lalle bayan sallar Isha'i da lokaci kaɗan, shuagaba yakan kewaya cikin gari da mataimakansa, a kowane dare, duk wanda ya haɗu da shi a kan hanya sai su kama shi, su kulle shi a cikin Kurkuku har zuwa gobe, sai su bincika game da shi, Shin sun kama shi ne a wurin da ake tuhuma, ko kuma waninsa face mutumin da aka san shi da alheri, amma ya fita cikin daren saboda wata buƙata mai girma. Kuma da dare babu wata mata da za ta fita, ko da baiwa ce ko namiji face wanda aka san shi da alheri, ko ya fita saboda wata buƙata mai girma. Saboda haka yakan sanya kariya daga ɓarnar ma'abuta sharri, ko da ya cutar da yawa daga wasu waɗanda ba su ba (ma'abutan sharri), saboda aikata ɗaya daga cikin abubuwa masu cutarwa da a gusar da ɗaya shi ne doka.

Kuma yana daga cikin abin da ya wajaba a kan shugaba mumini da mataimakinsa a cikin garinsa, ya canza makircin 'yan-kasuwa, domin daga cikinsu akwai masu tauye sikeli da ma'auni da ƙari da ragi, daga cikinsu akwai masu algussu na zinari da azurfa da dussar azurfa ko kuma ya ƙi tsabtace dunƙulallen zinare daga turɓaya, ko kuma ya hura nama ko kuwa masu gauraya nono da ruwa. Daga cikinsu akwai wanda yake kama kayan mutum, a matsayin ya saya zai je ya sayar, ba zai bayar da kuɗin ba sai ya tafi da kayan, idan ya yi nadama ko bai samu wanda zai sanya masa riba ba ya dawo da shi. Ko kuma mai kayan ya nemi kuɗinsa a wurinsa sai ya ce, masa, karɓi kayanka ko kuma ka yi haƙuri har sai na sayar tukuna.

Daga cikinsu akwai wanda yake sayar da baiwa, kuma har wanda ya saya ya sadu da ita, ba sa damuwa da istibra'i. Idan ciki ya bayyana gare ta, sai su riƙa jayayya.

Haƙiƙa, Amir (shugaba) Al-Hajj baba Abdullahi ɗan Abdul-Karim Muhammadu Al-Magili, Al-Tilmasaniy da aka tambaya, sai ya amsa masa, amma tauye ma'auni haramun ne, a cikin littafin Allah (swt) da Hadisai da abin da al'umma suka yi tarayya a kansa. To, wajibi ne a kan shugaba ya sanya amintacce a kan kasuwanni tare da kiyaye ma'auni. Su gyara ma'aunan kowane gari, a kan ma'auni guda da tsayar da sikeli. Kuma awo ya kasance daga abin awo sananne kamar mudu (abin awo), ko da za a rarraba mudu kwatankwacin awon mudu ɗari za a iske su dukkansu daidai babu tauyewa. Kuma idan aka haɗa su wuri guda awon bai ƙaruwa, face abin da babu makawa na ƙaramin ƙari ko ragi.

Kuma ba ya wajaba a yi tarayya a dukkan garuruwa a kan ma'auni iri guda, da sikeli. Abin da ya halatta daidaita ma'aunan kowane gari, da sikelinsu, ya kasanace iri guda, kuma babu makawa, sai an dinga kawo ma'auni da sikeli, a dinga dubawa a kowace shekara. Duk wanda ha'inci ya bayyana a gare shi na wani abu a cikin ma'auninsa da sikelinsa, to, a azabtar da shi, a kuma fitar da shi daga cikin kasuwannin Musulmi. Siffar ma'aunin ita ce, a shimfiɗa fata a kansa lafiyayya mai taushi mai santsi sai a tsayar da mizanin (ma'aunin) har sai ya daidaita. Idan ya daidaita sai a sanya zinari ko azurfa wanda ba a san nauyinsu ba, a hankali, da sanju, sai a ɗauke shi ba tare da karkatarwa ba, ko lanƙwasawa, ko dabara, kuma ba zai yi wayon girgizawa ba, ko ya girgiza, sa'annan ya fitar da hannunsa, kuma ya ƙaru ko ya ragu, har sai shi, mizanin, ya daidaita a cikin tsakiyar abin awo, a hankali, ba tare da wata dabara ba. Sai ya bayar da abin da ke cikin abin awo ga mai shi, kuma ya tattara abin da ya faɗi a kan fata, ya mayar da shi zuwa ga asalinsa.

Kuma siffar awon: Mai awon ya shimfiɗa (ajiye) sikeli (fatar awo) daidaitacce mai santsi (wanda ba su tauye haƙƙi). Sa'annan a ɗora masa abin da za a auna a hankali, har sai ya cika sosai, kuma ba girgizawa ba karkatawa, ba kuma wata dabara, abin sani kawai ana daidaita ma'auni ne a wurin ajiye shi. Kuma a zuba masa abin da za a zuba na tarin (dunƙulen) zinariya ko azurfa, kuma har sai ya cika cikinsa. Sikelin sanju yana daidaita su babu tauyewa, kuma babu wata hila (yaudara) a karkata ko girgiza.

Amma dukkan nau'o'in algussu haramun ne a cikin littafin Allah da Hadisai da ijma'in malamai. To, wajibi ne a kan shugaba ya tsoratar da masu algussu da yaudara a mafi girman tsoratarwa. Duk wanda ya samu dukiya ta wannan hanyar, to ya zamanto Fai'u. Shugaba zai sanya ta, domin gyaran

al'ummar Musulmi. Ciniki yana ƙulluwa ne da magana, sa'annan da karɓeɓeniya.

To, wajibi ne ga duk wanda ya saya, ya bayar da abin da yake kansa na kuɗi. Idan ya ƙi za a karɓa ko da ba ya so, idan ba a samu kome a wurinsa ba, face wannan abin da ya saya, daga wurin wanda yake bin sa bashi, to, shugaba zai karɓa ya sayar da shi, a maimakonsa, sai nan ya biya wanda yake bin sa bashi. Idan wani abu ya yi saura, to, nasa. Idan kuma wani abu ya rage, to, zai biya, kuma zai bi shi bashi, ba zai dawo da shi zuwa ga wanda ya saya ba, face da yardarsa, ko kuma da wani aibi.

Duk wanda ya sayar da baiwa, kafin ta yi isbtira'i, daga gare shi, ya sallama ta ga wanda ya saya, to, yana daga cikin fasiƙai waɗanda suke yanke abin da Allah Ya umurta da su sadar, kuma suke ɓarna a cikin ƙasa, kuma wajibi ne a tsoratar a kan haka, na yin uƙuba mai tsanani gare shi (ga mai aikata haka) da waninsa. Kuma idan ya ce bai sadu da ita (baiwar) ba, ba za a gaskata shi ba, sai idan suna cikin wani hali na muni wanda ba zai iya saduwa da ita ba, kuma bai taɓa faɗin cewa ya sadu da ita ba, kuma ba ta yi shaida a kansa ba, to, sai a gaskata shi, a kan cewa bai sadu da ita ba.

Kuma ya wajaba ga shugaba ya lazimta wa masu cinikin bayi da su bar su, su yi istibira'i kafin sayarwa, waɗanda ake kwanciya da su, ko mai ita, ya yi musun saduwa da ita, ko aka samu tabbas, ko da tana da muni, ko ya yi da'awar istibira'i. Muwala'a shi ne a bar ta wajen aminin mutum har sai ta yi haila, haila ɗaya ma ta isa ga mai sayarwa ko mai saye.

Yana daga cikin abin da ya wajaba a kan shugaba da mataimakinsa a cikin garinsa, canza munanan abubuwa, na mutane, waɗanda ba su rabon gado a kan littafin Allah da hadisan AnnabinSa (saw). Abin sani kawai ƙanen uwa ne ko, wan uwa da ɗan 'yar'uwa suke gado. Waɗansun ma, babbansu shi ne zai riƙe abin da mamaci ya bari, kuma ya riƙa cewa: ai wannan dukiyar 'yan'uwana ce, ai ni kamar babansu (ubansu) nake, ai za mu tsare musu ita, kuma za mu tarbiyyantar da su. Waɗansu, su kuma ba sa bai wa mace gado, ko wata daga cikin mata.

Haƙiƙa, ya yi tambaya ga wajen shugaba Al-Hajj baban Abdullahi ɗan Abu Bakar wanda aka fi sani da Askiya, ya tambayi Muhammadu ɗan Abdull-Karim ɗan Muhammadu, Al-Magili Al-Tilmasaniy a kan abin da muka ambata, sai ya amsa da faɗarsa cewa: "Mutanen da su sha'aninsu, ba sa rabon gado a kan littafin Allah da sunnanr AnnabinSa (saw), su kawai gado a wurinsu ƙanen uwa ko wan uwa, ko ɗan 'yar'uwa, suke gado, idan sun ga cewa halal ne, to, su kam sun kafirta, ko kuma suna yin musun, shari'o'i na

gadon, amma sai suka tabbatar cewa, su masu saɓo ne, to, sai a umurce su da su tuba. Idan sun ƙi shugaba zai karɓe dukkan dukiyoyinsu baki ɗaya. Idan suka tuba sai ya bar masu abin da yake nasu daga cikin dukiyar, waɗanda ya tabbata aiki suka yi suka samu, na halal. Kuma ya raba masu abin da ba wannan ba. To, ya karɓi rabi, kuma ya bar musu rabi.

Amma wanda babba daga cikinsu yake karɓe dukiyar da aka mutu aka bari, yana cewa: "Wannan dukiyar 'yan'uwana ce, ni kuma kamar ubansu ne, zan tsare musu, za mu tarbiyyantar da su, to, za a umurce su, da su tuba". Kuma lalle shugaba ya karɓe haƙƙoƙin masu rauni daga masu ƙarfi daga cikinsu, ya tsaya wa duk wanda aka zalunta a kan haƙƙinsa, kuma shugaba zai yi adalci ga wanda ake bi bashi, amma waɗanda ba su bai wa matan aure gado, ko wata daga cikin mata, to, su kamar kashi na farko ne a kan wannan rarrabewa. Ƙarshen maganar ke nan. Ga Allah muke neman dacewa da shiriya.

## FASALI NA GOMA

**Haƙiƙanin Halal Da Haram Da Rarrabewar Shubuha Daga Asalin Halal**

Ina cewa ga Allah kawai nake neman dacewa. Ku sani ya 'yan'uwana! Lalle halal shi ne abin da aka jahilci asalinsa amma haram shi ne abin da aka tabbata mallakar wani ne, shubuha kuwa ita ce duk abin da bai ayyana cewa: halal ba ne ko haram.

Ahmad Ar-Razuƙu ya ce a cikin littafinsa, '**Miftahu Sadad**' Sharhin Irshadus Saliki: "Halal shi ne duk abin da ya kuɓuta daga neman haƙƙin Allah, ko haƙƙin bayi. Haram kuma, dukkan abin da aka jahilci asalinsa a kan magana mafi inganci, amma shubuha, ita ce abin da hallaccinsa ko haramcinsa bai ayyana ba."

Gazzali ya ce a cikin littafinsa, **'Minhajul Abidin'** ya ce: "Haram, duk wani abin da ya tabbata mallakar wani ne, amma asalin halal yana da yawa, amma mai 'Shurbi Zilal'u ya tsara su a cikin waƙe, inda yake cewa:

1. Asalin halal fita biɗa (nema) da noma*
   Da kasuwanci da sana'a.
2. Da tsantsani da gaskiya a cikin mu'amala*
   Da ilimi a wurin biɗa (nema) da haɗin guiwa.
3. Kuma dukkan haƙƙoƙi an warware su *
   Haka masu bi ma'abuta halal ya zama halal.
4. Babu haƙƙin Ubangijimmu haka babu haƙƙin waninsa *
   Kuma babu rataya da shi lalle ka san haka.
5. Haka dukiyar Baital-Mali, Khumusi da Ushuri*
   Da Jiziya da haraji da ganimar Fai'u cikakke.
6. Haka dukkan abin da ka jahilci masu shi daga dukiya *
   Daga masu gado kuma babu ma'abucinsa.
7. Waɗannan abubuwa bakwai na Baital-Mali *
   Ga wanda yake da wata mashiga a cikin faɗar halali.
8. Shin asalinsa da asalin farkonsa lalle ka nemi sani *
   Ko wanda aka jahilci asalinsa ya tsira.

9. Wasu sun ce: asalin halal shi ne dukiyar fatauci *
Wadda aka yi ta da gaskiya, sa'annan aka yi nasiha cikin fatauci.

10. Haka kuma dukiyar farauta a kan tudu, ko cikin teku in aka raba *
Da adalci.

11. Haka ganimar Fai'u da ta gado su ne, masu tsarki ga asalinsu, sa'annan ruwan tukwane (kogi) biyu *
Masu gudana cikin shukar daji wadda babu mai ita, kuma babu dashen wani.

12. Kuma dukiyar sadaki halali ce ga mata *
Misali abin da aka bayar ga danginta saboda ita, ka fahimci haka.

13. Roƙon mabuƙaci, idan an ba shi ya zama halali, haka kyautar sulhu *
Waɗannan su ne goma a maganar nasiha.

14. Kuma dukkan abin da asalinsa bai bayyana ba *
Shi ne halal dukkan sa ga ma'abuta halali.

15. Ka karɓe shi a kan zahirin shari'a babu kome *
Kuma ba tare da ka tambaya ina asalin ba, don tsoron laifi.

16. Wannan shi ne ya fi sauƙin ban da wanda ya ce *
Ana neman sanin asalin ka kiyaye wajen jidali a kan haka.

17. Bai dacewa da yawan tambaya a zamanin yau *
Saboda mafi yawan asali an ɓarnata su, saboda haƙiƙa sun ce.

18. Mai riƙon (tsaron) rai da iyalai *
Yana iya cin haram gwargwadon buƙata daga dukiya.

19. Ba tare da ɓarna, ko ƙari a kan *
Buƙatarsa ba wajen ciyarwa.

20. Wannan ba'a ƙidaya shi daga maciya haram *
Haka kuma ba shubuha ba ce ga duk wanda haka ya auku, kamar yadda ya zo cikin.

21. Alfakihani mai sharhin Risala *
Haƙiƙa ya ambaci haka, lalle ka kiyaye abin da ya ce.

22. Wasu kuma sun tsananta a kan haka, wasu suka sassauta*
Cewa addini sauƙi ne, haka wanda ya yi adalcin magana ya ce.

23. Da duniya abin da yake cikinta ya zama haram *
Duk da haka nan abincin mutum sai ya zama halas.

Wannan littafi ya ƙare a nan daga abin da muka shirya daga waƙen Shurbu Zilal kuma shi ne ƙarshen Littafin Sirajul Ikhwan Fi Ahammi Ma Yuhtaju Ilaih Fi Hadha Zaman. Muna neman taimakon Allah Mai baiwa, Mai kyauta, ƙarewar wallafa a lokacin La'asar ranar Laraba sha biyar (15) ga Watan Sha'aban 1226AH.

Na gode wa Allah Wanda Ya shiryar da mu zuwa ga wannan addinin, ba domin shiriyarSa ba da ba mu shiryu ba, mafificin salati da aminci su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu, da iyalansa da sahabbansa baki daya, Allah kuma Ya yarda da shugabanni tabi'ai da malamai masu aiki da iliminsu da shugabanni guda huɗu masu ijtihadi da musu koyi da su har zuwa ranar ƙiyama. Allah Ka jiƙan Al'ummar Manzon Allah Muhammadu gamammen jinƙai, domin alfarmar Manzon Allah a wajenKa, Amin.

# تحذير الإخوان

## من ادعاء المهدية الموعودة في آخر الزمان

## Gargaɗi Ga ‘Yan’uwa Game Da Da'awar Mahdi (RA) Mai Bayyana  A Karshen Zamani

Na


Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

Malam Muntaƙa Muhammad Bilbis

**Edita**

Dr. Hamza A. Ainu

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Ƙai

Ina farawa da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabammu, Annabi Muhammadu tare da Alayensa da Sahabbansa.

Faƙirin bawan nan na Allah mai matsananciyar buƙatuwa zuwa ga rahamar Ubangijinsa, Usmanu ɗan Muhammadu wanda aka fi sani da suna Ɗanfodiyo, Allah Ya lulluɓe shi da rahamarSa, amin, ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya ni'imta mu da baiwar imani da kuma Musulunci kuma Ya fifita mu da shugaba majiɓincin al'amurranmu, Muhammadu, (tsira da aminci su tabbata a gare shi).

Bayan haka, wannan littafi, Gargaɗin 'yan'uwa ne game da da'awar Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa a ƙarshen zamani.

Ina farawa tare da neman dacewa a wurin Allah. Ya 'yan'uwana ku sani cewa da'awar Mahdi na daga cikin abubuwan da aka jarabci mutane da shi tun zamanin da ya shuɗe har zuwa yanzu. Alhassan Al-Yusi ya faɗi a cikin wata lacca tasa cewa: "Lallai ka sani (kai sauraro) wannan al'amari na da'awar ƙarya, bala'i ne wanda waɗansu Malamai sun yi nuni da shi tun da daɗewa."

Ku kuma ku sani ya 'yan'uwana cewa bayyanar Mahdi tabbatacciya ce, kuma kasancewar shi daga zuriyar Faɗimatu, ɗiyar Manzon Allah (saw) shi ne mafi inganci a ra'ayin jamhurun Malamai. Kurɗabi ya faɗi cikin **'Al-Tazkirah'** cewa Abul-Hassan Muhammad bin Al-Husain bin Ibrahim Asimul Sajzi ya ce: Haƙiƙa, labaru da damar gaske daga Manzon Allah, (Sallallahu alaihi wa sallam), sun tabbatar da zuwan Mahdi.

Amma dangane da kasancewar shi (Mahdi) sharifi ne shi ma Hadisai ingantattu da dama sun tabbatar da shi. Haka nan ma babban Shehin Malamin nan, Ahmad bin Hajar, ya yi bayanin cewa, Al-Muttaƙa ya labarta masa cikin littafin **'Al-Burhan.'**

Kuma dangane da kasancewarsa daga cikin zuriyar Faɗimatu, ɗiyar Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi), to, lallai Hadisai ingantattu sun bayyana haka. Al-Kurɗabi ya faɗa a cikin **'al-Tazkirah'** cewa: "Hadisai daga Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) sun tabbatar da cewa, (maganar bayyanar) Mahadi daga zuriyar shi (Annabi) ta hanyar Faɗimatu, tabbatacciya ce.

Al-Sharif al-Samhudi ya faɗi a cikin **'Jawahirul Aƙadain fi Fadhlish Sharifain'** bayan ya ambaci waɗannan Hadisan cewa: Ya tabbata ke nan daga waɗannan Hadisai cewa, Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya bayar da labarin bayyanar Mahdi, kuma ya tabbatar da kasancewar shi daga 'ya'yan Faɗimah (Allah Ya ƙara mata yarda).

Ku kuma sani ya 'yan'uwana cewa, waɗannan labaran da Hadisan suna fa nuna kusancin lokacin bayyanar shi ne kamar yadda ya zo a cikin **'Alwardi Fi Akhbaril Mahdi'** na AbdulRahman al-Suyuɗi da kuma 'Al-burhan fi alamatil Mahdi Fi Akhiriz-zaman', na Aliyu bn Husamid deen, wanda aka fi sani da Al-Muttaƙi. Amma dai ba a yi maganar ainihin lokacin bayyanarsa ba daga cikin labaran ko alamomin, kamar yadda sauran alamomin tashin ƙiyama ma suka nuna babu wanda ya san lokacin faruwarsu sai Allah. Haka kuma ita kanta tsayuwar ƙiyamar, babu wanda ya san lokacinta.

Al-Kurɗabi ya faɗi a cikin **'Al-Tazkirah'**: Iyakar abin da ya kamata a faɗi game da wannan (bayyanar Mahdi) shi ne labarin da Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi), ke cewa bayyanar Mahadi tana daga cikin fitintinun ƙarshen zamani. Amma koyaushe ne lokacin bayyanarsa? To, ya kamata a ba da hanzari a take (na rashin amsar wannan tambaya saboda rashin hanyoyin labaru ingantattu da za a iya dogaro da su).

Saboda haka bai wuci a ce (zancen) bayyanar Mahdi kamar na tashin ƙiyama ne ba, babu wanda ya san shekarar ko watan aukuwarsa. Duk da cewa, an san a ranar Juma'a za ta kasance, to, amma a wace Juma'ar? Sanin ainihin ranar sai Allah Mabuwayi Maɗaukaki Wanda Ba shi da abokin tarayya. Haka kuma al'amarin yake dangane da sanin lokacin faruwar sauran alamomi na tashin ƙiyama.

Ku sani kuma ya ku 'yan'uwana cewa ba ni ne Al-Imam al-Mahdi ba. Kuma ban taɓa yin da'awar Mahdiyya ni ba. Kodayake ana jin (daga cikin mutane) masu faɗin haka. Ni kuma ina mai tsanantawa wajen kwaɓon su daga yin haka. Haƙiƙa, na tabbatar da rashin yarda ta da wannan (maganar) a cikin waɗansu littattafai da na wallafa da harshen Larabci da harsunanmu na gida. Yana daga cikin misali magana da na yi a cikin ɗaya daga cikin littafina da Larabci mai suna **'Al-khbar al-Mahady ila Ummuril Imanil Mahdi min Ahli baitin Nabiy'**, (sallallahu alaihii wasallam): Da haka ne za ka fahimci cewa, ni ba Imamu Mahdi ba ne, kamar yadda marasa sanin Hadisan Manzon Allah, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) suke zato. Domin shi, Mahdi, sharifi ne daga cikin 'ya'yan ɗiyarsa, Faɗimah (Allah Ya ƙara mata yarda), wannan tabbatacce ne. Ni kuma ban san da haka a cikin nawa nasabar ba.

Haka nan kuma daga cikin ire-iren littattafaina na Larabci na yi magana a cikin littafin: **'Annaba'ul hadi ila umuril-Imanil Mahdi'**, cewa: "Ba na wallafa wannan littafin domin in yi iƙirarin cewa ni, Mahadi, ne ba. Manufata dai da wallafa shi ita ce domin in bayyana maku cewa, Allah Maɗaukakin Sarki Ya yi mani baiwar dacewar yanayina da na Imamu Mahdi waɗanda Malamai suka bayyana a cikin littattafansu, Allah Ya ƙara masu yarda. Haka kuma da na yi koyi ne da faɗin Allah Maɗaukaki

﴿وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ﴾ الضحى: ١١

*"Amma da ni'imar da Allah Ya yi maka ka faɗa (domin godiya)."*
**Alƙur'ani 93:11**

Bayan na ambaci waɗannan halaye sai na ce: Imamu Mahdi dai yana da siffofi da asirai waɗanda ba zai yiwu wani daban ya siffantu da su ba.

Daga cikin misali har wa yau a cikin littattafaina da harshenmu na gida, na ambaci abubuwa kamar talatin da uku daga cikin ɗabi'un Mahdi waɗanda aka yi mani bayaninsu sai kuma aka dangata ni da shi ta fuskar ɗabi'unsa. (a kawo Fassarar waƙen cikin fillanci)

Ina dalilin in yi da'awar ni ne Mahdi alhali an haife ni ne a ƙasar Sudan (baƙaƙe) a wurin da ake kira Maratta, kuma an sani daga cikin Hadisan Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) cewa shi, Mahadi, a Madina ne za a haife shi.

Al-sharif Al-Samhudiy ya faɗi a cikin littafin **'Jawahirul Aƙadain Fi Fadhlish-Sharifin** cewa:

An karɓo daga Nu'aimu bin Hammad cewa: Sayyadina Aliyu, (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: "Za a haifi Al-Mahdi ne a Madina." Sai Ali bn Hishamid deen, wanda aka fi sani da Al-Muttaƙi a cikin littafin **'Al-Burhan Fi Alamatil Mahdi Akhiraz-zaman'** ya ce: Nu'aimu ɗan Abi Ɗalibi (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: Madina ce za ta kasance mahaifar Al-Mahdi. Ta ya ya zan yi da'awar ni ne Al-Mahdi, alhali suna na bai zo ɗaya da na Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ba. Saboda ni suna na Usmanu, kuma sunan mahaifina bai zo ɗaya da sunan mahaifinsa (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ba. Domin sunan mahaifina, Muhammadu. Alhali an sani a cikin hadisan Annabi cewa, shi, Al-Mahdi, sunansa zai zo ɗaya ne da sunan Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi). Haka kuma sunan mahaifinsa zai zo ɗaya da sunan mahaifin Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Al-sharif Al-Samhudiyy ya faɗi a cikin '**Jawahirul Aƙadain Fi Fadlish'** sharifaini a lokacin da zai kawo Hadisin Abu Dawuda wanda aka ruwaito daga Ɗan Mas'ud, ya ce:

(المهدي يواطئ إسمه إسمي واسم أبيه إسم أبي).

***"Al-Mahdi sunansa zai zo ɗaya ne da sunana, kuma sunan mahaifinsa zai zo ɗaya da sunan mahaifina."***

Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Ya kuma ce Tirmizi ma ya ruwaito Hadisin tare da inganta shi.

Ni kuma ina mai cewa AbdulRahman As-Suyuɗi shi ma ya ruwaito wannan hadisin a cikin **'Tarikhul Khulafa'**. Kuma Aliyu ɗan Hishamud-deen wanda aka fi sani da (suna) Al-muttaƙi, ya faɗi a cikin littafin **Al-Burhan Fi Alamatil Mahdi fi Akhiriz-zaman** cewa Tirmizi ya ba da labarin a cikin ingantattun Hadisansa kamar haka:

An karɓo daga Ɗan Mas'ud daga Annabi, (Tsira da amincin Allah su tababta a gare shi) ya ce:

(يولد رجل من أهل بيتي يواطئ اسمه اسمي واسم أبيه اسم أبي).

***"Za a haifi wani mutum (bayana) daga cikin mutanen gidana, sunansa zai zo ɗaya da sunana, kuma sunan mahaifinsa zai zo ɗaya da sunan mahaifina."***

Ina dalilin in yi da'awar ni ne Al-Mahdi? Alhalin na san cewa, da yawa daga cikin siffofina sun saɓa da abin da ya zo dangane da al'amarin Al-Mahdi cikin hadisan Annabi da maganganun Sahabbai da Tabi'ai. Allah Shi ƙara masu yarda. Wannan kuma shi ne ma'aunin gaskiya na ƙaryata duk wani wanda zai yi da'awar shi ne Al-Mahdi.

Na ga wani abin mamaki, wani mutum daga cikin jama'ar gari ya yi da'awar walittaka. Ko da ya ziyarce mu ba mu hana shi yin da'awarsa ba. Saboda rashin damuwarmu da wannan. Da ya koma ziyartar mu karo na biyu yana mai da'awar shi ne Al-Mahdi sai muka hana shi ci gaba da yin haka. Sai ya koma inda ya fito ya ci gaba da da'awarsa bai daina ba har al'amarinsa ya yaɗu a tsakanin Toronkawa, ya zame masu matsala.

Wannan ya sa suka aiko mana da wasiƙar neman bayani game da al'amarinsa. Shin shi ne Al-Mahdi ko ba shi ba ne? Ga ma nassin wasiƙar da suka rubuto mana:

"Daga ƙasƙantaccen bawan Allah mai ƙarancin sani, Yusufu ɗan Usama, zuwa ga babban masoyi masanin Allah, shugaban Muminai Usmanu

wanda aka fi sani da suna Ɗan Fodiyo kuma zuwa ga ɗan uwansa Abdullahi, tauraron ilimi kuma zuwa ga jama'ar Musulmi gaba ɗaya. Dalilin rubuta waɗannan kalmomi zuwa gare ka shi ne domin in jaddada gaisuwa da roƙon addu'ar neman gafara da shiriya da dacewa.

Dalili na biyu kuma shi ne don mu ƙara jaddada mubaya'armu a gare ka, muna masu jin kiranka da biyayya gare ka, a cikin halin ƙunci da yalwa da daɗi da rashin daɗi. Mun ɗauki wannan alƙawari da harsunanmu da zukatanmu. Kuma ka amince muna daga cikin mabiyanka. Mun miƙa al'amurranmu zuwa gare ka, ka yi lissafin mu cikin jama'arka da iyalanka. Ka umarce mu da duk abin da kake so, ka hane mu daga duk abin da kake ƙi, ka nuna mana abin da ke da maslaha a gare mu duniya da lahira.

Haka kuma yana daga cikin dalilan (rubuta) wannan takarda mu sanar da kai wani lamari mai tayar da hankali da ya iso gare mu ta hanyar wani matashin saurayi daga cikin danginmu. Ya ba mu labarin cewa, wani mutum daga cikin Musulmi mai suna Muhammadu (yana nufin wannan mutumin Hamɓe ne da ke zaune a garin Magage) ya faɗa masa cewa, haƙiƙa, shi ne Al-Mahdi.

Al'amarin wannan mutumin ya sanya mu cikin ruɗani. Sai muka aika masa da wani saurayi matashi wanda muka yarda da addininsa muke kuma yaba hankalinsa da fahimtarsa da kuma iliminsa, don ya je ya binciki mutumin nan, ya tabbatar mana da da'awar da muka ji yana yi.

Da saurayin nan ya dawo gare mu sai muka nemi ya ba mu labarin dukkan abubuwan da ya gano daga lamarin wannan mutumi (mai da'awar shi ne Al-Mahdi) sai ya faɗa mana dukkan abubuwan da ya gani na al'amuransa da zantuttukansa (ƙasidu) sai kuwa muka samu tabbacin cewa lallai shi ne Al-Mahdi. Daga bisani muka yi ittifaƙi a kan miƙa al'amarin zuwa gare ka ya Usmanu. Domin kai ne shugabanmu, mai kyautata mana da nasiha, kuma masoyinmu, kai ne ka san haƙiƙanin Al-Mahdi da siffofinsa da alamomin da ake iya gane shi da su.

Babbar buƙatarmu daga gare ka ita ce ka rubuta mana littafi mai gamsarwa wanda zai yaye mana jahilcin da muke ciki dangane da al'amarin wannan mutumin, mu sami tabbacin ko shi ne Al-Mahdi ko ba shi ba ne."

Wannan ita ce tambayarsu da buƙatarsu. A dalilin haka ne kuma na wallafa wannan littafin. Saboda haka nake bayar da amsar wannan tambaya da cewa:

"A bayyane yake cewa, wannan mutumin ba shi ba ne Mahdi, domin yana a matsayin mai biya ne: matsayin malamai kuwa sama yake da matsayin ɗalibai: Mujtahidi mai iya rinjayar da wani ra'ayi a kan wani. Shi kuma sama yake da matsayin Malamai, shi kuma mujtahidi mai iya fitar da rassan mas'ala, sama yake da mujtahidi mai rinjayarwa; haka kuma matsayin mujtahidi mai mayar da mas'aloli zuwa ga tushensu sama yake da mai fitar da rassa. Shi kuma Al-Mahdi yana daga cikin mujtahidai masu assasa tushe saboda kasancewarsa mujtahidi sakakke ba mai ƙaidi da wani mazhaba daga cikin mazhabobi ba.

AbdulWahab As-Sha'arani ya faɗi cikin Al-Mizan: "Shi, Al-Mahdi, a zamaninsa zai rusa aiki da mazhabobin magabantansa. Malamai masu kashafi sun tabbatar da haka."

Abin mamaki ta ya ya wannan mutumin da ba kowa ba ne shi zai riƙa yin da'awar shi, Mahdi, ne, alhali nesa yake da wannan matsayin idan an ɗora shi a ma'aunin martabobin Malamai. Idan kuma za a ɗora shi da martabobin Sufaye ne, to, lallai wannan mutumin bai kai ga ma martabar Salikai ba, wanda shi kuma matsayin sama yake da martabar Musulmi masu biya. Matsayin Muridai kuma sama yake da na Salikai da Ammawa. Matsayin Arifai kuma sama yake da na Muhaƙƙiƙai, wanda shi kuma sama yake da matsayin Arufai. Shi ko Al-Imamul Mahdi, shugaban Kuɗuban zamaninsa ne.

Da ban mamaki ƙwarai wannan mutumin ya yi da'awar shi ne Mahdi alhalin tsakaninsa da wannan matsayi akwai martabobin girma da dama. Allah Ya kare mu daga jahilcin rashin sani. Cutar jahilci muninta ya isa. Babu wanda zai bi wannan jahilin mutumi cikin wannan jahilcin ban da jahili daga cikin sakararru. Su ne waɗanda Aliyu ɗan Abi Ɗalib ya siffanta su da sakararru, ƙasƙantattu mabiya duk wani mai kururuwar banza.

A can baya mun gabatar da mizani adili na ƙaryata duk wani mai da'awar shi ne Mahdi, wanda kuma siffofinsa sun saɓa da bayanan da ake da su a kan Al-Mahdi daga Hadisan Annabi (saw) da zantuttukan Sahabbai da Tabi'ai. Siffofin shi wannan mutumin kuma sun saɓa da abubuwan da aka ambata. Wannan shi ne dalilin ƙaryata shi. Duk wani marar zurfin fahimta ma zai gane wannan. Saboda babu wani kamanni komai ƙanƙantarsa da ka iya sa a yi zaton shi ne Mahdi.

In Allah Ya yarda za mu kawo hujjojin Malamai a cikin wannan littafin, waɗanda da su ne za mu yanke wuyan duk wani mai da'awar shi ne Mahdi gabanin bayyanar ainihin mai matsayin.

Mun ambata a farkon wannan littafin cewa, wannan irin da'awa (ta Mahdi) tana daga cikin musibu da aka jarabci mutane da su a zamanin da da na yanzu a ƙasashe dabam-dabam. Ɓangaren Imamiyya daga cikin Rawafilawa sun yi da'awar cewa, Muhammad ɗan Alhassan Al-Askari shi ne Al-Imamu Al-Mahdi.

Al-sharif As-Samhudi ya faɗi a cikin littafin **Jawahirul Aƙadaini Fi Fadhlish-Sharifaini** cewa, 'Rawafilawa ba su da hujjar cewa, Al-Mahdi shi ne Al-Imamu Muhammadu ɗan Alhassan Al-Askari. Sa'annan kuma ya ce jamhrun Malamai ban da 'yan Imamiyya suna kan batun cewa, Al-Mahdi ba shi ba ne wannan Muhammadu ɗan Alhassan, kuma shi Al-Mahdi zai bayyana ne a ƙarshen zamani.

Idan kum ka ce da ni; kai ma ka taimaka da ƙarfafa cewa Al-Mahdi zai yi dogon zamani, kuma shi ne Muhammadu ɗan Alhassan ɗin nan da ake zancensa a yayin da ka faɗi cikin littafin **Al-khabar Al-maddi ila Umuril Imamil Mahdi**, cewa Al-Mahdi zai yi dogon zamani, kamar yadda AbdulWahab Al-Sha'arani ya tabbatar cikin littafinsa (**Al-Yawakitu wal Jawahir Fi Ɗabaƙatil Akhyar**), har kuma ka ɗauko waɗansu maganganu daga cikin wannan littafi ka sako su cikin littafinka da na ambata, alhali jamhurun Malamai ba a kan wannan ra'ayi suke ba.

Amsata ga wannan tambayar ita ce: 'Na ambaci wancan maganar ce ba domin na dogara da ita ba, sai dai don in sanar da mutane cewa, shi AbdulWahab Al-Sha'arani ya zaɓi wannan ra'ayi cikin littafinsa wanda na ambata. Na kuma kawo maganarsa ne saboda ganin mutane sun kusa su fara musa alamomin tashin Kiyama. Ba kuma na zo da shi ba ne alhali ni kuma ina inkarin tsawon zamanin da Al-Mahdi zai yi ba. Saboda ba ni da hujjar yin haka. Kuma shi waliyyi ne daga cikin waliyyan Allah, waɗanda zancensu sirri ne abin ɓoyewa, babu mai iya bayyana shi sai su. Allah Shi ne Mafi sani da haƙiƙanin wannan.

Al-Sharif Al-Samhudi ya faɗi cikin **Jawahirul Aƙadaini**:

"Jamhurun Malamai in ban da 'yan Imamiyyah sun tsayu a kan cewa, ba wannan Muhammadu bn Alhassan ne Al-Mahdi ba, da kuma cewa, zai bayyana ne a ƙarshen zamani, ba tare da kowa ya iyakance zamanin ba, saboda yin haka ya saɓa wa al'ada. Da a ce shi ɗin ne, to da kuwa Manzon Allah, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya siffanta shi da siffofin da suka keɓance shi, kamar yadda ya bayar da labarin, tsawon zamanin Isa ɗan Maryamu da tsawon zamaninsa. Kuma Manzon Allah, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) bai bar duniya ba sai bayan ya tabbatar da shari'a

cikakkiya, bayan shi kuma wahayi ya yanke. Ta ina aka sami irin wannan shishshigi ga shari'a, ta wace hanyar suke samun irin waɗannan labaru?"

Haka kuma 'yan Zaidiyya, ya tabbata cewa, sun yi da'awar cewa Zaydu ɗan Aliyu ɗan Alhussain, jikan Manzon Allah, (Allah Ya ƙara masa yarda) shi ne Al-Mahdi. Sidi Alhassan Al-Yusi ya faɗi cikin wata lacca tasa:

Jama'ar Zaydu ɗan Aliyu sun yi masa da'awar shi ne Al-Mahdi. A lokacin da ya tabbatar da wannan da'awa ga Hisham sai Yusufu ɗan Umaru ya gicciye shi. Har ma aka faɗi cikin wasu waƙoƙi na Bani Marwana: (Mun gicciye maku Zaydun a jikin icen dabino. Mu ko ba mu ga cewa, za a gicciye Mahdi a jikin ice ba).

Al-Sharif Al-Samhudi ya kuma faɗi cikin **'Jawahirul Aƙadaini:'**

"Ba a lissafin 'yan-Rafidha daga cikin shugabannin mutanen Zayd ɗan Aliyu ɗan Al-Husaini, jikan Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi), wanda ake danganta Zaydiyya zuwa gare shi. Ya kasance shugaba ne mai girma a cikin sashin Tabi'ai na biyu, kamar yadda ɗan Mas'udu ya ce. Ya rayu a zamanin mulkin Hisham ɗan AbdulMalik, sai mutane da dama suka yi masa mubaya'a a Kufa. 'Yan Rafidha kuma suka neme shi da ya yi wa shehunnan nan biyu bara'a kafin su taimake shi, amma ya ƙi. Suka ce shi ke nan, sai dai mu ƙi ka. Shi kuma ya ce da su ku tafi ai ku ne ababen ƙi (Rafidha). Sai sunan ya bi su daga wannan lokaci."

Al-Sharif Al-Samhudi ya ci gaba da cewa, bayan ya kawo zancen Al-Hajjaju As-Saƙafi da jama'arsa:

"Sai aka rinjayi Zaydu, harbin kibiya ya same shi a goshinsa, sa'annan ya mutu. Jama'arsa suka bisne shi a ƙasan wata ƙorama ta yadda ruwa zai ci gaba da bi ta kansa. Amma kuma daga cikin waɗanda suka bisne shi ne waɗansu suka je suka nuna wa Hajjaju inda yake. Sai ya tono jikinsa, ya yanke kansa, ya kuma gicciye shi. Wannan ya faru a shekara ta ɗari da ashirin da ɗaya. Ya dawwama a wannan halin gicciyew har Hisham ya mutu, sai da Walidu ya gaji mulki ya bisne shi."

Ya kuma ci gaba da cewa, an ruwaito "Jariru ɗan Hazim ya ga Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) a cikin mafarki yana jingine da kututturen icen da aka gicciye Zayd a kai, yana cewa mutane: "Haka za ku yi da ɗana?" Haka kuma jama'a da dama sun ruwaito cewa, an gicciye shi ne tsirara, sai gizo gizo ya yi saƙa a daidai al'aurarsa a wannan ranar."

Haka kuma wani ɓangare na Shi'ah su ma sun yi da'awar Muhammadu ɗan Al-Ƙasim ɗan Aliyu ɗan Al-Hasan ɗan Aliyu ɗan Abi Ɗalibi shi ne Al-Mahdi. Al-sharif Al-Samhudi ya faɗi a cikin **Jawahirul Aƙadaini**:

Kamar yadda ya zo a cikin **Al-Muruj** na Al-Mas'udi: Wani ɓangare na Shi'ah sun yi da'awar jagoranci ga Muhammadu ɗan Al-Kasim ɗan Aliyu ɗan Alhasan ɗan Aliyu ɗan Abi Ɗalibi, har da kuma cewa, shi ne Al-Mahdi wanda ake sauraron bayyanarsa." Ya ƙare da cewa: "Ya kuma kasance daga cikin masu yawan ibada, da gudun duniya da tsantseni na ƙarshe. Ya kasance a Kufa sai Al-Mu'utasim ya nemi da ya tafi a shekara ta ɗari biyu da sha tara, sai ya tafi Khurasan. Da haka ne Al-Mu'utasim ya kama shi ya tsare. Daga bisani aka samu waɗansu mutane 'yan Shi'ah suka fitar da shi, suka tafi da shi wurin da babu wanda ya sani.

Wani ɓangaren kuma na ganin yana nan raye, Allah Yana azurta shi har zuwa ranar da zai bayyana domin ya cika duniya da adalci. Bayan an cika ta da ɓarna da zalunci.'

Haka kuma 'yan Kisaiyyah sun yi da'awar Muhammad ɗan Hanifa shi ne Al-Mahdi. Sharif As-Samhudi a cikin **Jawahirul Aƙadaini** yana cewa:

"Waɗancan kuma, wato reshen Shi'ah da na ambata suna cewa, Muhammad ɗan Hanifa shi ne Al-Mahdi bayan 'yan'uwansa biyu, waɗanda su ma jikokin Manzon Allah ne, Allah Ya ƙara musu yarda. Suka kuma yi da'awar yana raye a Hayara-Radhwa.

Wata ƙungiya kuma daga cikinsu suna a kan cewa, shi (Muhammadu ɗan Hanifa) shi ne shugaba bayan Aliyu (Allah Ya ƙara masa yarda), ba jikokin nan biyu ba. Wancan ra'ayi na farko shi ne (mutane daga cikinsu) da yawa suka tsaya a kai daga cikinsu ma akwai Abdur-Rahman."

Bayan wannan sai ya ce:

"Kuma ba a lissafin 'yan-Rafidha daga cikin jagororin jama'ar Is'haq ɗan Ja'afar As-Sadiq, duk da cewa, wani ɓangaren Shi'ah sun yarda da jagorancinsa. Kuma ya kasance mai daraja da falala da yawan ilimin Hadisi. Ya kuma kasance mafi kamanni da Manzon Allah, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi). Sufyanu ɗan Uyainah ya kasance idan zai ruwaici Haidisi daga gare shi yakan ce: "Na karɓo Hadisi daga amintacce yardajje Is'haq ɗan Ja'afar As-sadiq." Bayan ya kawo zantuttuka daɗaɗa game da waɗancan shugabanni magabata masu nuni ga rashin da'awar Mahdi ga shi ɗan Ja'afar, ya ce sukan nisanta shi ne ma daga wannan da'awa, duk da cewa, matsayinsa ya kai ya yi."

Daga cikin waɗanda suka yi da'awar Mahdiyanci akwai Ahmad ɗan Abdullahi ɗan Abi Muhalli. Alhasan Al-Yusi ya faɗi cikin wata lacca tasa cewa, "shi, Ahmad ɗan Abdullahi ya yi da'awar shi ne Al-Mahdi wanda ake sauraron bayyanarsa, ya ci gaba da jihadi, ya mallake zukatan jama'ar gari, suka bi shi har ya shiga garin Sajalmasah ya ci su da yaƙi. Ya samu kusanci da Sarakunan Sudaniyyah, har ya zo ya mallake su, ya fito da su zuwa Murakish, inda suka haɗu da Zaydu ɗan Ahmandu Al-Mansuf, suka kuma rinjaye shi, suka kore shi daga garin. Sai shi, Ahmadu, ya je ya nemi agajin mutanen garin. Al-Susi ta ƙurya, su kuma suka fito inda ɗan ibn Mahallii yake suka kashe shi, suka kuma rinjayi rundunarsa, suka fatattake su. Wannan shi ya kawo ƙarshen al'amarinsa. Sai Zaydu ya koma karagar mulkinsa"Shi kenan."

Daga cikin waɗanda suka yi da'awar Mahdi, akwai Abu Abdullahi ɗan Tumarta Al-Susi. Ya kuma kasance mutum ne mai ilimi. Ya tafi can Hiyal yana ta kira zuwa  ga addini, ya kuma samu mabiya masu yawa. Daga bisani kuma sai ya bayyana da'awarsa ta shi ne Al-Mahdi. A lokacin da mabiyansa suka ƙara yawa ya tilasta musu jihadi domin ɗaukaka kalmar Allah da yaƙin maɓarnata. Sai ya jagorance su zuwa yaƙar Murabiɗun da suka fi su yawa. A wannan yaƙin ne shi, Abu Abdullahi, ya mutu. Ya faɗi maganganu da Malamai suka yi inkarinsu kuma sun ɗauki mabiyansa ɓatattu ne.

Babu shakka game da kasancewar waɗancan mutane ɓatattu ne, ga duk wanda ya san maganar bayannar Mahdi a ƙarshen zamani.

Al-Jalal Al-Suyuɗiyu ya wallafa wasu littafai biyu masu suna '**Al-Urful Wardi Fi Akhbar Al-Mahdi**' da '**Kashfu Fi Majawazatil luɗfi li Haazihil Ummah**' A ciki ne ya yi bayani mai yawa da gamsarwa cewa, "Haƙiƙa, bayyanar Mahdi za ta samu jinkiri har zuwa ƙarshen zamani, lokacin ne Dujjal ma zai bayyana, kuma Annabi Isa ma zai sauka, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi). Amma tabbatacce ne cewa, Ɗan Tumarta ba shi ba ne Mahdi, haka kuma duk wani mai da'awar Mahdi tun wancan zamani har wannan zamani namu."

Ina godiya ga Allah da Ya sa na samu waɗannan littattafai biyu, waɗanda suka ƙunshi bayanai masu gamsarwa a kan bayyanar Mahdi zai kasance lokaci ɗaya ne da Dujjal da kuma saukowar Annabi Isa, (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Haka kuma Alhasan Al-Yusi, (Allah Ya ƙara masa yarda) ya faɗi a cikin wata muhadharah tasa cewa, wata ƙungiya kuma a ƙasar Indiya ta yi da'awar (cewa) Muhammadu ɗan Sidi Al-Janagwari shi ne Al-Mahdi.

Aliyu ɗan Hishamuddeen wanda aka fi sani da Al-muttaƙi ya yi bayani a kan Alamomin Mahdi a cikin littafin **Al-Burhan**: "Haƙiƙa, wata ƙungiya ta bayyana a ƙasar Indiya tana da'awar wani mutumi sharifi wanda aka haife shi a Indiya, mai suna Sidi Muhammadu ɗan Khal Al-Jonagwari, wanda ya mutu yana ɗan shekara arba'in, wai shi ne Al-Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa a ƙarshen zamani. Amma kuma siffofinsa sun saɓa da abin da ke cikin Hadisan Annabi da maganganun Sahabbai da Tabi'ai, yardar Allah ta ƙara tabbata a gare su duka dangane da al'amarin Mahdi.

A ganina akwai dalilai guda biyu masu sa mutane yin irin wannan da'awa. Dalilan kuma su ne:

1. Rashin bambantawa tsakanin Annabi da waliyyi. Alhali sananne ne cewa, akwai bambanci tsakanin su ta fuskoki da dama. Daga cikinsu shi ne kasancewar Annabi Ma'asumi ne (ba ya aikata saɓo). Shi kuma waliyyi ba ya kasancewa ma'asumi, sai dai ya zama mahfuzi (wanda kuskure ko tuntuɓe ka iya faruwa a gare shi), wanda yake hakan kuma baya faruwa ga Annabi. Haka mawallafin littafin '**Kawa'idul Ɗariƙa**' shi ma ya ce: "Waliyyi yana nan kan walittakarsa muddin bai zama fasiƙi ba. Idan kuma ya aikata fasiƙanci, wannan a zahiri ya warware kasancewar shi masoyin Allah da ManzonSa."

   Saboda haka nake cewa, mutum ba ya fita daga walittaka don ya yi furuci da magana wacce ake iya yi wa fahimta daban-daban. Saboda wannan yana daga cikin halayensu."

   Aliyu ɗan Hishamuddeen ya ci gaba da kawo dalili na biyu kamar haka:

2. Dalili na biyu shi ne shishshiginsu cikin binciken tushen ayyuka. Da farko, na nemi sanin gaskiyar al'amarin waɗancan mutane sai na kasance tare da su na lokaci mai tsawo amma ban iya gane komai game da su ba. Har ma na zo na tafi ƙasar Indiya na tuntuɓi malaman can, duk da haka babu abin da na samu game da su. Sai da Allah Ya nufi zuwana ƙasa mai tsarki, inda na shagaltu da ilimin Hadisi na tsawon shekara goma, na kuma tuntuɓi manyan malaman can, sa'annan Allah Ya sa na dace da samun dalilai masu tabbatar da ƙaryar waɗancan mutane na ƙungiyar nan ta Indiya masu da'awar Mahdi ga Muhammadu ɗan Khal Al-Jonagwari. Godiya ta tabbata ga Allah, Wanda Shi ne Mafi sanin shiryayye.

Kuma ya isa dalilin ƙaryata da'awar waɗancan mutane (saboda) kashe Malamai da suka dinga yi da kuma rashin ƙwararan hujjoji na kare da'awarsu.

Idan kuma an koma ga Alƙur'ani da Sunnah, ƙaryarsu ta gama bayyana. Muna neman tsarin Allah daga ɓata."

Ɗan Hishamuddeen ya kuma faɗi a can ƙarshen babi na goma sha uku, inda ya kawo fatawar malaman Makkah mai alfarma game da batun Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanar shi a ƙarshen zamani da kuma hukuncin wancan ƙungiya ta Indiya wacce bayaninta ya gabata. Fatawar kuma ta biyo bayan wata tambaya ce da aka yi kamar haka: "Allah Ka nuna mana gaskiya gaskiya ce, ka ba mu ikon bin ta, kuma ka nuna mana ƙarya, ƙarya ce ka ba mu ikon nisantar ta.

Masu girma, Malamai kuma jagororin addini masu shiryar da Musulmi, Allah Ya taimake ku, me za ku ce game da waɗansu mutane masu da'awar wani mutum daga ƙasar Indiya wanda ya mutu a shekara ta ɗari tara da goma (910 AH) a gari mai suna Faratta, cewa shi ne Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa a ƙarshen zamani, har da kuma cewa wanda ya yi inkarin wannan ya kafirta. Sa'annan kuma mene ne hukuncin wanda ya yi inkarin Mahdi. Muna buƙatar ku yi mana fatawa, Allah kuma Ya ƙara maku yardarSa."

An nemi wannan fatawa ce a zamanin shi, Ɗan Hishamuddeen. Amsar kuma ta kasance kamar haka:

Godiya ta tabbata ga Allah Maɗaukakin Sarki. Allah Ya daɗa tsira da aminci ga ManzonSa, shugabanmu, Muhammadu da iyalansa da Sahabbansa. Allah Ka ba mu dacewa na sanin gaskiya cikin abin da aka samu saɓani a kansa.

Gaskiyar magana ita ce da'awar waɗancan ƙungiya ƙarya ce mummuna kuma jahilci ne ƙarara, sa'annan bidi'a ce mummuna, kuma ɓata ce babba.

Da farko dai da'awarsu ƙarya ce saboda ta saɓa wa HADISAI masu yawan gaske da ke tabbatar da cewa, shi, Mahdi, zai kasance ne daga cikin Ahlul Baiti (sharifai), kuma zai mallake duniya, gabashinta da kudancinta. Zai kuma bayyana tare da Annabi Isa, amincin Allah ya tabbata a gare shi, ya kuma kasance cikin rundunarsa ta yaƙar Dujjal a ƙasar Falasɗinu kusa da Baitl Miƙdis, kuma shi, Mahdi, zai jagoranci al;ummar nan a salla, har Annabi Isa ma zai yi salla a bayansa. Zai yanka Assufyan, ya kuma fatattaki rundunar shi, Assufyan, wanda zai afka wa Mahdi a tsakanin Makkah da Madinah, har babu wanda zai tsira daga cikinsu sai mutane biyu kawai.

Kuma daga cikin alamomin Mahdi da ake sauraron bayyanarsa, akwai alamomi fiye da ɗari biyu da ake iya tantance Mahdi da waninshi. An kuma same su ne daga Annabi (saw) da Sahabbai da Tabi'ai a cikin littafan Hadisai sanannu. Dukkansu kuma suna tabbatar da ɓatar waɗancan mutane masu da'awar wancan mataccen mutumi shi ne Mahdi wanda aka ce zai bayyana a ƙarshen zamani. Daga cikin abin da ke tabbatar da jahilcisu ga Sunnah shi ne taurin kansu da inkarinsu ga abin da Sunnah ta ƙunsa.

Sa'annan dalili na biyu shi ne kasancewar suna kafirta Malamai waɗanda suke inkarin da'awarsu a cikin littattafansu. Haka kuma suna zartar da hukuncin kisa a kan duk wanda ya yi inkarin da'awarsu, sai dai idan ya tuba ya jaddada Musuluncinsa, inji su. Alhali su ne kafirai, mulhidai, ɓatattu waɗanda suka yi ridda, saboda sun kafirta Sahabbai da Malamai shugabanni.

Ya shugaba, Allah Ya ƙara ɗaukaka addini da kai, ya kyautu ka yi wa waɗannan mutane maɓarnata hukuncin da ya dace da su, har sai sun dawo sun rungumi gaskiya.

Abu na uku shi ne idan har ya tabbata cewa, suna inkarin Sunnah kai tsaye, sai a yi musu hukuncin kafirci da ridda, sai a kashe su. Idan kuma inkarinsu ya kasance don taurin kai ne ga malaman Musulunci, sai a yi masu horo da ya dace da mummunan laifinsu da aƙidarsu, sai a tsare su a yi masu duka sa'annan a yafe musu, da makamantan waɗannan da za su iya hana su daga bin waccan mummunar hanya, ya kuma dawo da su kan hanyar gaskiya.

Allah Wanda dukkan tsari ya tabbata a gare Shi, Mai shiryarwa, Mai karɓar tuba, Ya sa mu dage cikin masu gaskiya, domin Shi Mai yawan baiwa ne da jin-ƙai. Wanda ya rubuta shi ne bawan Allah kuma mabuƙaci zuwa ga baiwarsa, mai begen ziyarar ɗakinSa, Ahmadu ɗan Hajar As-Shafi'i. Allah Ya yafe masa tare da malamansa da iyayensa. Ina kuma cikawa da godiya ga Allah da salati ga AnnabinSa Muhammad (saw) da iyalan gidansa da Sahabbansa, kuma mai zikirin Hasbunallahu da La haula wa la ƙuwwata illa billahi da wa ufawwidhu amri ilallahi....). Alhamdu lillah.

Al-Hanafi ya bayar da fatawa, ya ce: "Ya Allah Ka yi mana rahama, Ka ba mu dacewa a cikin al'amurranmu. Aƙidar waɗancan mutane da aka ambata, tare da duk munanan ababe da aka faɗa game da su lallai ɓatattu ne. Saboda ba su da tushe. Ya kuma wajaba a kwaɓe su kuma a tsawata masu tare da tsanantawa. Domin saɓawar aƙidarsu ga ingantattun nassoshi na Hadisai da labaru masu yawan gaske waɗanda suke tabbatar da cewa, Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa zai bayyana ne tare da Annabi Isa, (tsira da amincin

Allah su tabbata a gare shi). Har ma Annabi Isa zai taimake shi wajen yaƙar Dujjal.

Kuma akwai alamomin da za su gabaci zuwansa, daga ciki akwai bayyanar As-Sufyani, da ɓacewar wata a cikin watan Ramadan. A wata riwayar ma an ce wata zai ɓace sau biyu cikin watan Ramadan, kuma a samu ɓacewar rana a tsakiyar watan. Faruwar haka kuma za ta zama saɓanin al'ada a wurin masana lissafin taurari. Waɗannan abubuwa kuma duka babu wanda ya faru. Ko shi ya sa na ce, hakan kuma ya nuna cewa aƙidarsu ɓatacciya ce, kuma buƙatarsu ba ta biya ba.

Amma kuma bai halatta ba a kafirta su. Idan kuma su suka kafirta wanda ya saɓa wa aƙidarsu ɓatacciya, to, su ne suka zama kafirai. Saboda wanda ya kafirta Musulmi shi ne kafiri. Sai a neme shi da ya tuba ko a kashe shi. Allah Yana tare da duk mai taimakon gaskiya. Wanda ya faɗi wannan bayani ya kuma rubuta shi (shi ne) bawan Allah, Ahmadu Abussururi ɗan Ɗiya'i Al-hanafi, (Allah Ya ƙara masa luɗufi). Yana mai ƙarasawa da godiya ga Allah da roƙon tsira da aminci ga ManzonSa tare da zikirin (wa ufawwidhu amri ilallahi) da kuma Hasbunallahu)."

Wani malami mai bin mazhabar Malikiyya shi ma ya bayar da fatawa ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah Shi kaɗai, komai sai da nufin Allah da Shi kuma na dogara. Bayan haka, Aƙidar waɗancan mutane dangane da cewa, wancan mutumin wanda ya riga ya mutu shi ne Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa a ƙarshen zamani, aƙida ce ɓatacciya. Saboda Hadisai ingantattu da suka yi bayanin Mahdi.

A cikin bayanin bayyanarsa an ambaci waɗansu fitintunu da za su faru gabanin bayyanarsa. Daga ciki kawai bayyanar Assufyani da kifar da sojojin da za su yi yaƙi da shi a Baida'a da ɓacewar rana a tsakiyar watan Ramadan da ɓacewar wata a farkon watan Ramadan da waɗansu alamomi kuma ban da waɗannan.

Haka kuma Hadisai sun nuna Dujjal zai bayyana ne a zamaninsa. Waɗannan duk ba su faru ga wancan mutumin da aka ambata ba. Saboda haka ne da'awarsu ta cewa, shi ne Mahdi ta zama a zahiri ƙarya ce marar tushe. Dangane kuma da aƙidarsu ta cewa duk wanda bai yarda da su ba ya kafirta, idan har suka bayyana kafirta dukkan Musulmi wanda ya saɓa masu, to, fa su sun fita daga Musulunci, sun zama su ne kafirai. Sai a neme su da su tuba ko kuma a kashe su. Allah Ya kiyaye mu daga ɓata, Ya tabbatar da mu a cikin Musulunci a kullum albarkacin shugaban manzanni. Wanda ya rubuta shi ne

Muhammadu ɗan Muhammad Al-Khaɗɗab Al-Maliki (Allah Ya gafarta masa) tare da iyayensa da malamansa da Musulmi baki ɗaya.

Wani malamin kuma mai bin mazhabar Hambaliyya ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah. Ya Allah Ka nuna mana gaskiya a cikin duk abin da aka samu saɓani a cikinsa. Bayan haka, babu shakka cikin kasancewar aƙidar waɗancan muatne ɓatacciya ce. Domin amintattu daga cikin masu ruwaya sun ruwaito daga Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya bayar da labarin bayyanar Mahdi a ƙarshen zamani. Kuma ya ambaci abubuwan da za su gabaci zuwansa da siffofinsa da abubuwan da za su faru a zamaninsa. Daga ciki akwai saukowar Annabi Isa (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) da Annabinmu. Zai kuma sauko ne a zamanin shi (Mahdi), kuma za su haɗu da shi, har ma ya yi salla a bayansa. Haka kuma bayyanar Dujjal da yaƙinsa.

Waɗannan abubuwa dole sai sun faru, ga shi kuma wannan mutumin (mai da'awa) ya riga ya mutu tun gabanin faruwarsu. Allah Ya kiyaye mu daga taɓewa da bin Shaiɗan.

Su kuwa masu wannan aƙidar sun saɓa wa gaskiya da Musulmi suke tsaye a kai, saboda haka sun fita daga Musulunci, sun yi ridda. Allah Shi kiyaye. Duk wanda kuma ya ƙaryata bayyannar Mahdi wanda Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya bayar da labarinsa, to, ya kafirta. Kuma ya fita daga addini. Ya kamata shugabanni, masu tafiyar da al'amurran Musulmi (Allah Ya taimake su), su zartar da hukunci a kan waɗannan masu ridda, a neme su da tuba kwana uku. Idan sun ƙi a kashe su da takobi. Ta wannan hanyar za a tsayar da yaɗuwar 'yan-bidi'a. Kuma Musulmi su huta daga sharrinsu. Allah Shi ne Mafi sanin daidai, kuma a gare Shi ne makoma take.

Wanda ya rubuta shi ne bawan Allah, Yahya ɗan Muhammadu Alhambali, Allah Ya kare shi da luɗifinSa. Yana mai ƙarasawa da godiya ga Allah da neman tsira da aminci ga ManzsonSa, da zikirin (la haula wa la ƙuwwata illa billah da Hasbunallahu) da istigfari da tawakkali ga Allah."

Al-Muttaƙi ya faɗi a cikin **Alburhan**:

Ya ku 'yan'uwana kada ku rafkana ga barin ma'aunin da muka faɗa muku wanda da shi za ku mayar da martani ga duk wani mai da'awar shi ne Mahdi tun gabanin bayyanar ainihin wanda aka yi nuni da shi.

Domin wannan ƙage Allah Ya kiyaye shi kamar yadda aka kiyaye Alƙur'ani.

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا الذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُ لَحَافِظُونَ ﴾ الحجر: ٩

*"Mu Muka saukar da Alƙur'ani Mu kuma Muke kiyaye shi."*
**Alƙur'ani 15:9**

Duk wanda ya zo da wani abu da ya saɓa wa wannan addini, yana kuma zaton a kan gaskiya yake, take Allah sai Ya kawo masana Alƙur'ani da Sunnah da za su ƙaryata shi cikin yardar Allah."

Al-Sharfi Al-Samhudi ya faɗi a cikin **Jawahirul Aƙadaini Fi Fadhlil Sharifaini:**

"Sananne ne hadisin da Manzon Allah ke faɗi a cikinsa cewa, Adilai za su ɗauki wannan ilimi a kowane lokaci, waɗanda ba za su sassauta wa gurɓatawar masu shishshigi da tawilin jahilai ba. Ibn AbdulBarri da Al-khaɗibul Bagdadi sun zo da wannan Hadisin a cikin Al-Jami'u, da ruwayar Isa ɗan Munabbahi, kuma ya ce ingantacce ne daga Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Alhafiz Alkhaɗib Albagdadi ya ce:

Wannan shaida ce ke nan daga Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) cewa, Malamai (masu irin wannan siffofi da suka gabata) su ne jagororin Musulmi. Saboda dagewarsu a kan tsare shari'a daga juyewa da shishshigi. Kuma shi (Manzon Allah) ya fi son a koma gare su dangane da duk al'amurran addini."

Bayan maganar da'awar Mahdi, akwai kuma wani bala'i da ya game ko'ina, shi ne na da'awar Kuɗubanci da walittaka daga waɗansu waɗanda ba su cancanta ba. Ahmadu Zarruƙ ya zo da wannan batu a cikin **Umdatul Muridil Sadiq** tare da bayanai masu gamsarwa a kan ƙaryata masu irin wannan da'awar.

Kuma ku sani ya ku 'yan'uwana cewa, ni fa ban yi da'awar ni Kuɗubi ne ko waliyyi ba. Ana dai jin haka ne daga bakunan mutane kamar yadda suke cewa, ina tashi sama kuma ina tafiya a kan ruwa kuma ana naɗe mini ƙasa ina tafiya zuwa Makkah da Madina; kuma an hore mini teku kamar yadda aka hore shi ga waliyyai kamilallu. Da kuma cewa, na wuce babin tarbiyyantar da mutane a kan tsoron Allah da bin dokokinsa sau da ƙafa, zuwa babin tarbiyyantar da su a kan Kusaira (wannan lafazi da harshen gida ne).

Na faɗi waɗansu baitoci da harshenmu na gida dangane da waɗancan abubuwa da ake danganawa a gare ni. Zan kawo bayanin baitocin a nan saboda a tabbatar da gaskiya kuma a kore ƙarya insha Allah.

Dangane da faɗi da ake cewa, ana naɗe mini ƙasa har in je Makka da Madinah da cewa ina tafiya a kan ruwa, kuma ina tashi a cikin sararin samaniya ko kuma cewa, na kai ga matsayin Kuɗubi, wannan duka ƙarya ce yanke. Amma dangane da walittaka, to, iyakar abin da na sani game da kaina shi ne cewa, Allah Ya tsayar da ni a wani matsayi bayan na bi ta kan waɗansu haloli tun daga ƙuruciya har na kai shekara talatin da ɗaya, sai wani haske na musamman daga Manzon Allah, (Allah Ya yi daɗin tsira da aminci a gare shi) ya fisge ni. Kafin in sami wannan rabo na abu mai daɗi tamkar aljanna, na kasance mai tsananin bege ga Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) har ta kai ga ina kuka ina maimaita waƙar Kukan Rashin Manzon Allah, wacce Abu Sufyan ɗan Haris, (Allah Ya ƙara masa yarda) ya tsara. Na kasance ina karanta ta ga Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

**Waƙar ita ce:**

Na yi kwanan rashin barci, dare kuma ya tsawaita*
Daren wanda masifa ta same shi ai matsawaiciyar masifar da ta Same mu ta girmama

A yammacin da aka amshi ran Manzon Allah*
Kasarmu ta wayi gari saboda abin da ya same ta

Kamar sassanta za su dare*
An girgiza zukata, wannan kuma

Ko kaɗan bai yi girman abin da ya faru ga Musulmi*
Wanda ya san ya zukata suka zubar da hawaye

Har ka ce za su fita daga jikkuna*
Wahayi kam ya yanke daga sauka

Alhali Jibrilu ya kasance yana kai wa da komowa*
Manzo ya kasance mai kore mana shakka

Da wahayi a kan yi masa ya gaya mana*
Yana shiryar da mu, ba tsoron ɓata

Alhalin Manzo yana jagorarmu*
Faɗima ki nuna baƙin ciki yau ba laifi ba ne

Ko da ba ki nuna ba ba ki da abin yi*
Kabarin mahaifinki fiyayyen ƙabari ne
Kabarin da shugaban mutane ke cikinshi

Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce da ni tsaya a nan. Sai na tsaya, take ya yi mani bishara da cewa, "ni ne zan nuna maka hanyar addini, saboda haka ba za ka ɓata ta."

Wannan busharar ta fi mani alheri a kan duniya da abin da ke a cikinta. Wannan yana tabbatar da faɗin da na yi cewa, ni matsayina, matsayin (Arbabul-ahwal) ne, wanda shi kuma yana bayan matsayin (Arbabul Maƙamat), wanda shi kuma bai kai na (Muƙamul Kammal) ba. Saboda haka ba gaskiya ba ne cewa, ni ina daga cikin Kamilallun waliyyai waɗanda suka riƙa a cikin halara ta Ubangiji.

Dangane kuma da zancen aljannu, na dai san cewa, sun taɓa bayyana gare ni, ina cikin ƙuruciya, ɗan shekara goma sha uku, sai suka ɓace mani. Ba su sake bayyana gare ni ba sai can da na zama saurayi ɗan shekara ashirin da biyar. Daga wannan lokaci kuma ba su gushe ba suna zuwa wurina har yau ɗin nan, amma fa duk wannan a ganin damarsu ne kawai. Amma cewa an hore mani aljannu kamar yadda aka hore wa kamilallun waliyyai, wannan ba gaskiya ba ce yanke.

Dangane kuma da tarbiyya, iyakar abin da na sani shi ne, ina tarbiyyantar da mutane a kan tsoron Allah, wanda shi ne aikata umarninSa da nisantar abubuwan da Ya hana; haka kuma ina yi masu tarbiyyar (Istiƙama), wadda ita ce koyi da ɗabi'un Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Amma ba gaskiya ba ne cewa, ina tarbiyyar mutane a kan (kashafi) kamar yadda kamilallun waliyyai suke yi. Malamai sun kasa shehunnai zuwa kashi uku: Shehun ilimi; da shehun tarbiyya; da kuma shehun tarƙiya. Kuma na yi faɗakarwa a kan matsayinsu cikin wata waƙa da na yi da harhsenmu na gida.

Waɗannan shehunnai duka ba za a daina samun su ba matuƙar duniya ba ta gushe ba. Amma malamai sun ce za su dinga raguwa kamar yadda komai na al'amurran addini da duniya ke raguwa.

Sidi Al-Hasan Al-Yusi ya faɗi a cikin laccarsa cewa: "Taƙaituwar zamani da masu rayuwa cikinsa ba dole ba ne su jawo yankewar addini cikin hankula da yankewar shugabanni (babba da ƙarami). Haka kuma nasiha ba za ta yanke ba da makamantansu. Hukuncin Allah ne wanda kuma ManzonSa, mai gaskiya, (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya bayar da labarinsa."

Da wannan ne kuma muka zo ƙarshen wannan littafi namu mai suna "Gargaɗi ga 'yan'uwa game da da'awar Mahdi wanda aka yi alƙawarin bayyanarsa a ƙarshen zamani." Littafin ya samu ne da taimakon Allah, bayan sallar Azuhur, a ranar Litinin cikin watan Zul-Hajji mai alfamar a shekara ta SIRDAKI Bayan Hijirar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

Godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya shiryar da mu, da ba mu shiryu ba, ba don Ya shiryar da mu ba. Fiyayyen tsira tare da cikakken aminci su tabbata ga shugabanmu, Muhammad da iyalansa da Sahabbansa gaba ɗaya. Allah Ya ƙara yarda da shugabannin Tabi'ai da Malamai, da kuma shugabannin nan Mujtahidai guda huɗu da duk masu koyi da su har zuwa ranar Kiyama.

Allah Ka yi Rahama ga al'ummar (Annabi ) Muhammadu (saw), ƙarin godiya ga Allah da kyakkyawan taimakonSa kuma Tsira da amincin su tabbata ga wanda babu wani Annabi  bayansa, amin.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai.

# وثيقة أهل السودان

## وإلى من شاء الله من الإخوان في البلدان

# WASIKAR MUTANEN HAUSA

Na

## Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo

**Mai Fassara**

**Mallam Muhammad**

**Edita**

**Dr. Hamza A. Ainu**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ........ 327
Yin Umurni Da Kyakkyawan Aiki ........ 327
Wajibi Ne Yaƙar Masu Sakaci Da Ayyukan Musulunci ........ 328
Yaƙar Kafiran Amana Haramun Ne ........ 328
Yaƙar Kafirai Abokan Gaba ........ 329

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Allah Ya yi salati ga shugabanmu, Annabi Muhammadu da mutanen gidansa da Sahabbansa, Ya yi tsira da aminci mai yawa.

Duk godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya yi ni'imamu da ni'imar imani da Musulunci kuma Ya shiryar da mu da shugabanmu majiɓincinmu, Muhammad. Mafificin salati da mafi tsarkin aminci daga Allah su tabbata a gare shi.

Bayan haka, wannan wasiƙa ce daga Ɗan Fodiyo, Sarkin muminai Usman zuwa ga dukkan mutanen Hausa, kuma zuwa ga wanda Allah Ya so daga 'yan'uwa a cikin garuruwa. Ita, wasiƙa, ce mai amfani a cikin waɗannan zamuna. Ina cewa dacewa daga Allah take.

### Yin Umurni Da Kyakkyawan Aiki

Ku sani ya ku 'yan'uwana, lallai yin umurni da kyakkyawan aiki wajibi ne bisa haɗuwar malamai kuma hani da mummuna wajibi ne bi sa haɗuwar malamai. Kuma lallai yin gudun hijira daga garuruwan kafirai wajibi ne bisa haɗuwar malamai.

Kuma jiɓintar muminai wajibi ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai sarautar da sarkin muminai wajibi ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yi masa ɗa'a da dukkan na'ibansa wajibi ne bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai jihadi wajibi ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai naɗa sarkin muminai a cikin garuruwa wajibi ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma naɗa Alƙalai wajibi ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai zartar da hukunce–hukuncen shari'a wajibi ne gare su bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai hukuncin gari, hukuncin sarkinsa a bisa haɗuwar malamai, shi ne in ya kasance Musulmi, to, garin ma ya zama Musulmi. In ya zama kafiri, to, garin ma ya zama garin kafirci. Ya wajaba a yi hijira daga gare shi. kuma lallai yaƙar sarki kafiri wanda ba ya cewa **"La'ilaha illallahu"** a asali wajibi ne a bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai karɓar sarauta daga gare shi wajibi ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yaƙar sarki wanda ba ya faɗin **"Lailaha illallahu"** saboda al'adar gari, kuma ba ya da'awar Musulunci wajibi ne bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai karɓar sarauta daga gare shi wajibi ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yaƙar sarkin da ya yi ridda, ya fita daga addinin Musulunci zuwa addinin kafirci wajibi ne bisa haɗuwar malamai, kuma lallai karɓe sarauta daga gare shi wajibi ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yaƙar sarkin da ya yi ridda amma bai fita daga addinin Musulunci ba saboda kasancewarsa yana da'awar Musulunci kuma yana cuɗanya ayyukan Musulunci da ayyukan kafirci kamar sarakunan Hausa wajibi ne bisa haɗuwar malamai.

**<u>Wajibi Ne Yaƙar Masu Sakaci Da Ayyukan Musulunci</u>**

Kuma lallai yaƙar masu yin sakaci da ayyukan Musulunci daga Musulmi waɗanda ba su kasance ƙarƙashin wani sarki daga sarakunan muminai ba wajibi ne bisa haɗuwar malamai. Idan aka kira su zuwa cikin mubaya'a suka ƙi, har sai sun shiga cikin mubaya'ar. Kuma lallai kafirta Musulmi da ayyukan Bidi'a haramun ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai kafirta Musulmi da saɓo haramun ne a bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai zama a garuruwan kafirai haramun ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai rashin shiga ƙarƙashin mubaya'ar sarkin muminai ko na'ibansa haramun ne a bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yaƙar Musulmi waɗanda suka kasance a garuruwan Musulmi haramun ne bisa haɗuwar malamai.

Kuma lallai cin dukiyarsu da zalunci haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai bautar da 'ya'ya na Musulmi haramun ne a bisa haɗuwar malamai. Duk ɗaya ne sun kasance a garuruwan Musulunci suke ko a garuruwan abokan yaƙi.

**<u>Yaƙar Kafiran Amana Haramun Ne</u>**

Kuma lallai yaƙar kafiran amana haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai cin dukiyoyinsu da zalunci haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai bautar da 'ya'yansu haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma lallai yaƙar jama'ar riddaddu wajibi ne bisa haɗuwar malamai, kuma dukiyarsu za a kai Baitil-mali sai dai akwai saɓanin malamai game da bautar da su. Amma abin da ya fi shahara rashin bautarwar. Kuma wanda ya bautar bai da laifi idan ya yi aiki da magana ta wani malami shi, ganima, ce. Kuma a cikin bautar da su akwai maganganu biyu, shahararriya an hana, wanda ya aikata shi bai yi saɓo ba in ya yi koyi da wanda ya ce halal ne.

## Yaƙar Kafirai Abokan Gaba

Kuma lallai yaƙar kafirai abokan yaƙi wajibi ne bisa haɗuwar malamai. Kuma dukiyoyinsu ganima ce kuma bautar da su haramun ne. Kuma lallai yaƙar azzalumai wajibi ne bisa haɗuwar malamai, kuma cin dukiyoyinsu da zalunci haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma bautar da su haramun ne bisa haɗuwar malamai. Kuma ana iya taimakawa da makamansu a kansu sannan a mayar musu. Kuma a cikin dukiyoyin Musulmi waɗanda suke zaune a garuruwan abokan yaƙi akwai maganganu biyu, ingantattun halacci.

A nan ne **Wasiƙar Mutanen Hausa** ta ƙare da ma wanda Allah Ya so daga 'yan'uwa da godiyar Allah Mataimaki Mai baiwa. Ina mai yin salati da sallama ga Mustafa, zaɓaɓɓe daga zuri'ar Adnan tare da mutanen gidansa da Sahabbansa da dukkan ma'abota Imani, Amin.

# عمدة المتعبدين والمحترفين

# MADOGARAR MASU IBADA DA MASU SANA’A

Na


**Shehu Usumanu Ɗan Fodiyo**

**Mai Fassara**

**Mallam Ɗalhatu Ahmad Zaria**

**Edita**

**Prof. Suleiman Musa**

## ABUBUWAN DAKE CIKI

Gabatarwar Mawallafi ........ 335
Ilmin Furu'a (Fiƙihu) Na Bayyane. ........ 343
Alma'u Ɗahiru (Ruwa Mai Tsaki). ........ 343
Wankan Janaba. ........ 343
Alwudu. ........ 343
Attayammumi (Taimama). ........ 344
Alhaidu Wal Istihada (Jinin Haila Da Na Istihada). ........ 345
Auƙatus Salati (Lokutan Sallah). ........ 346
Shuruɗus Salati (Sharuɗɗan Sallah). ........ 347
Assalatu (Sallah). ........ 348
Kaɗa'il Fawa'iti (Rama Sallar Da Ta Kuɓuce). ........ 348
Assahawu (Sujadar Rafkanuwa). ........ 349
Aljum'a (Sallar Jumma'a). ........ 349
Azzakatu (Zakka). ........ 350
Zakatul Fitiri (Zakkar Fidda Kai). ........ 351
Assaum (Azumi). ........ 351
hajj (Aikin Hajji). ........ 352
Ilmul Furu'ul ɓadinati (Ilmin Furu'a Na Ɓoye.) ........ 352

## GABATARWAR MAWALLAFI

### Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-Kai

Allah Ya yi daɗin tsira da aminci ga shugabanmu, Annabi Muhammadu da iyalan gidansa da sahabbansa da aminci mai yawa.

Bawa mabuƙaci ga rahamar Ubangijinsa, Usmanu Ɗan Muhammad Ɗan Usmanu wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo, Allah Ya lulluɓe shi da rahamarsa, amin.

Godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya ɗaga ginshiƙin sunna kuma Ya ɗaukaka hasumiyarta, kuma Ya ƙasƙantar da samuwar bidi'a, sannan Ya yaye haskenta Ya bayyana alamomin haƙiƙaninta, Ya bayanna asiranta, Ya yaye hanyoyin ɓarna kuma Ya shafe gurabunta. Tsira da aminci su tabbata ga Annabi Muhammad wanda ya bayyana hanyoyi na haƙiƙa; ya ƙarfafa bangarenta kuma ya yi umarni da bin sunnah, kuma ya lizimta fifita ta. To, aminci ya tabbata ga alayensa da sahabbansa gaba ɗaya da shugabannin tabi'ai da malamai masu aiki.

Bayan haka, wannan littafi shi ne **Umdatul Muta'abbidina Wal Muhtarifi** Na (Madogarar Masu Ibada Da Masu Sana'a).

Na rubuta shi ne domin yin bayani a kan abin da Allah Maɗaukaki Ya faɗa a cikin littafinSa da abin da ManzonSa ya faɗa a cikin sunnarsa a cikin sanin asalin addini da kuma ilmin furu'a (Fiƙihu) bayyananniya da ɓoyayyiya, ba zan kawo istinbaɗin malamai a cikinsa ba.

AbdulWahab Ash'sha'arawi ya ce a cikin littafin **Dururul Manshura Fi Bayani Zubudil Ulumu Mashahurati** a game da duk abin da Allah Ya ɗora wa bayinSa, game da abin da shari'a ta bayyana shi kawai, yana nufin Alƙur'ani da kuma Sunnar Manzon Allah (saw) a bayyane; ba Istinbaɗi ba.

Abin da ake nema shi ne ya san ilmi, domin Allah Maɗaukaki Ya sharɗanta a bayyana, domin shi ne iliminsa da ake tambayar bawa game da shi a Lahira. Duk waɗannan neman sanin sa babu laifi a game da shi kuma babu laifi a game da shi, kuma babu wahala a kan wani game da samun sa. Ba dole ba ne ya juyar da rayuwarsa ga baki ɗaya a game da neman sanin sa da kuma neman hanyoyi wajen tabbatar da shi, domin abin da yake ƙunshe da shi, shi ne aikata kaza, ku bar kaza.

Ba a samun tsaiko game da fahimtar da wanda bai yi karatu ba, saɓanin abin da masu Ijtihadi suka sharɗanta a zamanin shugabanni, domin ba a tambayar wani mutum game da shi a lahira, kuma neman sanin sa akwai ƙunci

akwai wahala, kuma yana buƙatar sarayar da rayuwa, rashin samun tabbatar da shi kamar yadda ake gani a cikin illimin asalin Addini.

Ina faɗi da Allah nake neman dacewa: Lallai Allah Maɗaukaki Ya tabbatar da dukkan asalin addini a cikin Alƙur'ani mai girma, wanda Ya keɓance kaɗai ta Shi kaɗai ta bauta da abin da Ya keɓance Annabawa da siffofi na ji da gani domin Shi, Allah Maɗaukaki, Ya tabbatar da samuwar halitta da faɗarSa:

﴿ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ﴾ الحج: ٦،

*"Abin da ya sa haka domin Allah Shi Ne gaskiya."* Alƙur'ani 15:6

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ﴾ الروم: ٢٧

*"Kuma Shi Ne Wanda Ya fari halitta, sa'annan kuma Zai mayar da ita."*
Alƙur'ani 30:27

Sannan kuma Ya tabbatar da kasancewarSa samamme ne.

﴿ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ﴾ الحج: ٦،

*"Abin da ya sa haka domin Allah Shi Ne gaskiya"* Alƙur'ani 15:6

Da kuma tabbatar da cewa Shi dawwamamme Ne.

Da faɗarSa:

٣ ﴿هُوَ ٱلْأَوَّلُ﴾ الحديد:

*"Allah Shi Ne farko."* Alƙur'ani 57:3

Kuma Ya tabbatar da kasancewarSa Shi wanzajje ne da faɗarSa:

﴿وَتَوَكَّلْ عَلَى ٱلْحَىِّ ٱلَّذِى لَا يَمُوتُ﴾ الفرقان: ٥٨،

*"Kuma ka dogara ga Rayayye Wanda Yake Ba Ya mutuwa."*
Alƙur'ani 25:58

﴿وَٱللَّهُ هُوَ ٱلْغَنِىُّ﴾ فاطر: ١٥

*"Kuma Allah Shi Ne Mawadaci."* Alƙur'ani 35:15

Kuma Ya tabbatar da kasancewarSa Shi Mai Irada (nufi) ne da faɗarSa:

﴿ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴾ هود: ١٠٧

***"Shi Mai aikata abin da Ya yi nufi ne."*** **Alƙur'ani 11:107**

Kuma Ya tabbatar da ƙaddara da faɗarSa:

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيْءٍ خَلَقْنَٰهُ بِقَدَرٍ ﴾ القمر: ٤٩

***"Lallai Mun halicci dukkan komai da ƙaddara."***
**Alƙur'ani 54:49**

Kuma Ya tabbatar da kasancewa Shi Masani Ne da faɗarSa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴾ الأنفال: ٧٥

***"Lallai Allah Masani Ne ga dukkan komai."*** **Alƙur'ani 8:75**

Kuma Ya tabbatar da kasancewarSa Shi rayayye Ne, da fadarSa:

﴿ هُوَ ٱلْحَيُّ ﴾ البقرة: ٢٥٥،

***"Yana ji."*** **Alƙur'ani 2:255**

Kuma;

﴿ أَسْمَعُ وَأَرَىٰ ﴾ طه: ٤٦

***"Yana gani."*** **Alƙur'ani 20:46**

Kuma Ya tabbatar da kasancewarSa Shi Mai Magana Ne da faɗarSa:

﴿ وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ تَكْلِيمًا ﴾ النساء: ١٦٤

***"Allah Ya yi magana da Annabi Musa magana."*** **Alƙur'ani 4:164**

Kuma Ya tabbatar da kasancewarSa Shi Mai zaɓi Ne a cikin aiki da kuma bari da faɗarSa:

﴿ وَرَبُّكَ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخْتَارُ ﴾ القصص: ٦٨

***"Ubangijinka Shi ne Yake halitta abin da Ya so kuma Yake zaɓa."***
**Alƙur'ani 28:68**

Kuma Ya tabbatar da aiko Manzanni da faɗarSa:

﴿ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِىٓ إِلَيْهِم ﴾ يوسف: ١٠٩

*"Ba Mu aiko da wani a gabaninka ba sai mazaje waɗanda Muke yin wahayi zuwa garesu"* Alƙur'ani 12:109

Kuma Ya tabbatar da aiko da Muhammadu (tsira da aminci su tabbata a gareshi) ga baki ɗayanta. Da faɗarSa:

﴿ مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ﴾ الفتح: ٢٩

*"Muhammadu Manzon Allah ne."* Alƙur'ani 48:29

Kuma Ya tabbatar da kasancewarsa shi ne ƙarshen Annabawa da faɗarSa Maɗaukaki kuma

﴿ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ﴾ الأحزاب: ٤٠

*"Cikamakon Annabawa."* Alƙur'ani 33:40

Kuma Ya tabbatar da gaskiyar Muhammadu da dukkan Manzanni da faɗarSa:

﴿ وَصَدَقَ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴾ يس: ٥٢

*"Kuma Manzanni sun yi gaskiya."* Alƙur'ani 36:52

Kuma Ya tabbatar da amanarsu da faɗarSa a cikin hikayar maganarSa

﴿ إِنِّى لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴾ الدخان: ١٨

*"Ni Manzo ne a gareku kuma amintacce."* Alƙur'ani 44:18

Kuma Ya tabbatar da isar da saƙonsu, da faɗarSa

﴿ ٱلَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَٰلَٰتِ ٱللَّهِ ﴾ الأحزاب: ٣٩

*"Su ne waɗanda suke isar da saƙon Allah."* Alƙur'ani 33:39

Kuma ya tabbatar da kasancewarsa suna yin aure, da faɗarSa:

﴿ وَجَعَلْنَا لَهُمْ أَزْوَٰجًا وَذُرِّيَّةً ﴾ الرعد: ٣٨

*"Muka sanya musu mata da zuriyya."* Alƙur'ani 13:38

Kuma Ya tabbatar da kasancewarsu suna cin abinci kuma suna zuwa kasuwanni. Da fadarSa:

﴿ لَيَأْكُلُونَ ٱلطَّعَامَ وَيَمْشُونَ فِى ٱلْأَسْوَاقِ ﴾ الفرقان: ٢٠

*"Suna cin abinci kuma suna kasuwanci."* Alƙur'ani 25:20

Sannan Ya tabbatar da kasancewarsu Mala'iku da faɗinSa:

﴿ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ جَاعِلِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُو۟لِىٓ أَجْنِحَةٍ ﴾ فاطر: ١

*"Godiya ta tabbata ga Wanda Ya ƙagi sammai da ƙassai, Wanda Ya sanya Mala'iku Manzanni ma'abota fuffuke."*
Alƙur'ani 35:1

Kuma Ya tabbatar da kasancewar mutuwa da ajali da faɗarSa:

﴿ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَـْٔخِرُونَ سَاعَةً ۖ وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴾ الأعراف: ٣٤

*"Idan ajalinsu ya yi ba a jinkirta masu daidai da sa'a, kuma ba a gaggauta musu."* Alƙur'ani 7:34

Kuma Ya tabbatar da muminai a lokacin tambayar Kabari da faɗarSa:

﴿ يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ﴾ إبراهيم: ٢٧

*"Allah Yakan tabbatar wa muminai da suka yi imani da zance matabbaci a duniya da lahira."* Alƙur'ani 14:27

Kuma Ya tabbatar da azabar kabari da faɗinSa:

﴿ أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ۖ ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ ٱلْهُونِ ﴾ الأنعام: ٩٣

*"Ku fito da rayukanku a yau, za a saka muku da azabar wulaƙanci."*
*Alƙur'ani 6:93*

Kuma Ya tabbatar da Ni'imar Kabari,

﴿ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴾ الواقعة: ٨٨،

*"Amma mai mutuwar idan ya kasance daga makusanta ne,* Alƙur'ani 56:88

﴿ فَرَوْحٌ وَرَيْحَانٌ وَجَنَّتُ نَعِيمٍ ﴾ الواقعة: ٨٩،

*"Sai hutu da kyakkyawan abinci da kuma Aljannah ta ni'ima."* Alƙur'ani 56:89

﴿وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٩٠ فَسَلَٰمٞ لَّكَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٩١﴾ الواقعة: ٩٠ – ٩١

*"Amma kuma idan ya kasance ma'abota dama ne aminci ya tabbata daga cikin ma'abota dama."* Alƙur'ani 56:90-91

Kuma Ya tabbatar da tayar da mutane da faɗarSa:

﴿وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٞ لَّا رَيۡبَ فِيهَا وَأَنَّ ٱللَّهَ يَبۡعَثُ مَن فِي ٱلۡقُبُورِ﴾ الحج: ٧

*"Lallai tashin Kiyama mai tahowa ne babu kokwanto a cikinsa. Kuma lallai Allah Zai tayar da duk wanda ke cikin Kabari."* Alƙur'ani 22:7

Kuma Ya tabbatar da tara jikkuna da faɗarSa:

﴿وَحَشَرۡنَٰهُمۡ فَلَمۡ نُغَادِرۡ مِنۡهُمۡ أَحَدٗا﴾ الكهف: ٤٧

*"Muka tara su ba Mu manta da wani ɗaya daga cikinsu ba."* Alƙur'ani 18:47

Kuma Ya tabbatar da bada littafi da faɗarSa:

﴿فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ﴾ الحاقة: ١٩

*"Duk wanda aka ba shi littafinsa da hannun damarsa."* Alƙur'ani 69:19

A cikin haƙƙin muminai da kuma faɗarSa, to, amma

﴿وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ﴾ الحاقة: ٢٥،

*"Wanda aka ba shi littafinsa a hannun hagunsa a cikin haƙƙin kafirci….."* Alƙur'ani 69:25

Kuma Ya tabbatar da auna ayyuka da faɗarSa:

﴿وَنَضَعُ ٱلۡمَوَٰزِينَ ٱلۡقِسۡطَ لِيَوۡمِ﴾ الأنبياء: ٤٧،

*"Za Mu sanya ma'auni na adalci ranar Alƙiyama."* Alƙur'ani 21:47

Kuma Ya tabbatar da azaba da faɗarSa:

﴿فَٱهۡدُوهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡجَحِيمِ﴾ الصافات: ٢٣

*"Ku shigar da su zuwa ga hanyar jahiim."* Alƙur'ani 37:23

Kuma Ya tabbatar da akwai wuta da faɗarSa:

﴿ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا ﴾ الكهف: ٢٩

*"Lallai Mu Mun yi tanadin wuta ga azzalumai."* **Alƙur'ani 18:29**

Kuma Ya tabbatar da Alkausara da faɗarSa:

﴿ إِنَّآ أَعۡطَيۡنَٰكَ ٱلۡكَوۡثَرَ ﴾ الكوثر: ١

*"Lallai Mu Mun ba ka Alkausara."* **Alƙur'ani 108:1**

Kuma Ya tabbatar da akwai Aljannah da fadarSa:

﴿ وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُواْ جَنَّةٗ وَحَرِيرٗا ﴾ الإنسان: ١٢

*"Mun ka saka masu da aljanna da kayayyakin alharini."*
**Alƙur'ani 76:12**

Kuma Ya tabbatar da gani da muminai za su yi maSa a lahira da faɗarSa:

﴿ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ نَّاضِرَةٌ ٢٢ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٞ ٢٣ ﴾ القيامة: ٢٢ – ٢٣

*"Wasu fuskoki a ranar masu ni'ima ne masu dubi ne zuwa ga Ubangijinsu."*
**Alƙur'ani 75:22-23**

Waɗannan su ne asali (tushen) adalci, wanda ya keɓance kaɗaita Allah Shi kaɗai da bauta da wanda Ya keɓanci Annabawa da abin da Ya keɓanta da shi na siffofin ji da gani. Haƙiƙa, dukkaninsu Allah Maɗaukai Ya tabbatar da su a cikin Al-Kur'ani Mai girma. Kuma dukkanin abin da ba mu ambata ba a cikinsu, to, an shigar da su a cikinsu.

Yana wajaba ga kowanne baligi da ya ƙudura ta kamar yadda suka zo (gabata). Abdul Wahab Ash-Sha'arani ya ce a cikin littafin **Durul Manshura Fi Bayani zabadil Mashahura.** Waɗannan Usl dukkaninsu sanannu ne kuma abin tabbatarwa a wurin kowane Musulmi. Ma'abota Musulunci yana kawar da kai a game da lura da shi a kan hanyar masu ilimin magana. Ya faɗa a cikin littafin **Kawa'idul Kashfiyya almudhati Li Ma'ani Siffati Uluhiyya.** Shin zai nemi abin da ya wajaba a dalili na hankali daga wurin muminai? A kan ingancin waɗannan ma'anoni na hankali. Bayan tabbatar da dalili na yanke? Lallai yin haka jahilci ne. kaicon wanda ya ɗauki tsawon zamani yana kafirta duk wanda ba ya dubi da dalili. To, ya halinsa ya kasance kafin nazari da kuma yayin nazarin shi, Musulmi, ne ko a'a? Shin ya kasance yana yin sallah yana yin azumi ko a'a? Shin ya kasance ya tabbata a wurinsa lallai Allah

Maɗaukaki Shi ne kaɗai ne a cikin mulkinSa, kuma lallai Muhammadu Manzon Allah ne? ko ko a'a?

To, idan ya kasance yana ƙudurta waɗannan dukkaninsu. Wannan shi ne na halin marasa ilimi. Ya bar shi a kan abin da suke na imani, a kan abin da yake kansu na sanin Allah.

In ya kasance ba ya ƙulla waɗannan al'amurra sai bayan ya yi nazari a cikin maganganun masu magana. Muna masu neman tsari daga wannan Mazhaba, inda ta kai shi zuwa ga mummunan nazari, wanda yake kai shi zuwa ga rasa imani.

Kuma ya faɗa a cikin littafin **Kawa'idul Kashfiyya:** Ina nufi ne ya kai ɗan'uwa cewa lallai Musulumai ba su rubuta littafin ilimin magana ba domin su tabbatar wa kansu da waninsu ilimin sanin Allah Maɗaukaki. Su sun rubuta su ne domin tunkuɗe (kawar) da husuma ga waɗanda suke da ilimin falsafa da kuma Mu'utazilawa suka nemi Allah Ya yarda da su, suka nemi tsayar da dalilai yankakku a kansu, domin su dawo zuwa ga aƙida ta wajabcin imani da abin da Manzanni suka zo da shi daga wurin Ubangijinsu ba waninSa ba.

Sannan ya ce ka sani, lallai manufarsu kare aƙida daga karkata da ɓarna da ɗimaucewa a cikin ɓata, saboda haka ya riƙi dalilansa daga Alƙur'ani mai girma domin dukkaninsa mutawattiri ne Kaɗa'iyyin (Ya biyo ta hanyar da babu ƙarya) sannan kuma tsararriya.

## ILMIN FURU'A (FIƘIHU) NA BAYYANE

### Alma'u Ɗahiru (Ruwa Mai Tsaki)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأَنزَلْنَا مِنَ السَّمَآءِ مَآءً طَهُورًا﴾ الفرقان: ٤٨

***"Mun saukar daga mai tsarkakewa."*** **Alƙur'ani 25:48**

Mai tsira da aminci ya ce:

(وخلق الله الماء طهورا، لا ينجسه شيء، إلا ما غير لونه، أو طعمه، أو ريحه)

***"Ya halicci ruwa mai tsarki mai tsarkakewa, babu abin da yake sa masa najasa sai dai abin da ya canza launinsa ko ɗanɗanonsa ko warinsa."***

Ibn maja ya ruwaito shi.

<u>Wankan Janaba</u>

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَإِن كُنتُمْ جُنُبًا فَاطَّهَّرُوا﴾ المائدة: ٦

***"In kun kasance kuna masu janaba, ku yi tsarki"*** **Alƙur'ani 5:6**

Ya zo cikin **Sahihil Bukhari** daga Aisha Allah Ya yarda da ita,

إذا اغتسل من الجنابة بدأ بغسل يديه، ثم يتوضأ كما يتوضؤ للصلاة، ثم يدخل أصابعه فى الماء، فيخلل بها أصول شعره، ثم يصب على رأسه ثلاث غرفات بيديه، ثم يفيض الماء على جسده كله."

***"Lallai Manzon Allah (saw) ya kasance in zai yi wankan janaba, yakan fara da wanke hannayensa sai kuma ya yi alwala kamar yadda yake yi alwala domin yin sallah. Sa'annan sai ya shigar da hannayensa a cikin ruwan sai ya tsettsefe gashinsa da su. Sa'annan ya zuba a dukkanin jikinsa gaba ɗaya."***

Haka kuma a cikin **Sahihil Bukhari** daga Aisha (Allah Ya yarda da ita) ta ce:

"كنا إذا أصابت أحدنا جنابة أخذت بيديها ثلاثا فوق رأسها، ثم تأخذ بيديها على شقها الأيمن، وبيدها الأخرى على شقها الأيسر.

***"Mun kasance idan janaba ya samu ɗaya daga cikinmu, takan ɗebi ruwa sau uku ta zuba a kanta, sannan ta ɗebi ruwa da hannunta, ta zuba a tsagin jikinta na dama da kuma tsagin jiknta na hagu."***

## Alwudu (Alwala)

Maɗaukaki ya ce:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا قُمْتُمْ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ فَٱغْسِلُوا۟ وُجُوهَكُمْ وَأَيْدِيَكُمْ إِلَى ٱلْمَرَافِقِ وَٱمْسَحُوا۟ بِرُءُوسِكُمْ وَأَرْجُلَكُمْ إِلَى ٱلْكَعْبَيْنِ ﴾ المائدة: ٦

***"Ya ku waɗanda ku kayi imani, idan kun tashi zuwa yin sallah, to, ku wanke fuskokinku da hannayenku da ƙafafunku zuwa idon sawu."***
**Alƙur'ani 5:6**

Kuma Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** daga Amru Ɗan Abi Hassan ya ce, "Lallai ya tambayi Abdullahi Ɗan zaid a game da alwalar Manzon Allah (saw), sai yace

**فأكفأ على بيده التور، فغسل يديه ثلاثا، ثم أدخل يده فى التور، فمضمض واستنشق واستنثر ثلاث غرفات، ثم أدخل يده، فغسل وجهه ثلاثا، ثم غسل يديه مرتين، إلى المرفقين، ثم أدخل يده، فمسح رأسه فأقبل بهما وأدبر مرة واحدة، ثم غسل رجليه إلى الكعبين.**

***"A kawo masa salkar ruwa, sai ya yi musu alwala irin alwalar Manzon Allah (saw), ya zubo ruwan salkar nan da hannunsa ya wanke hannunsa sau uku, sannan ya shigar da hannayensa a cikin salkar, sai ya kuskure baki ya shaƙa ruwa, kuma ya fyace da kamfata sau uku, sa'annan ya shigar da hannunsa a cikin salkar ya wanke fuskarsa sau uku, sa'annan ya shigar da hannunsa a cikin salkar ya wanke hannunwansa sau biyu zuwa gwiwar hannu, sannan ya shigar da hannunsa cikin salkar ya shafa kansa ya yi gaba da su ya yi baya dasu sau ɗaya, sannan ya wanke ƙafafuwansa guda biyu zuwa idon sawu."***

## Attayammumi (Taimama)

Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَإِن كُنتُمْ جُنُبًا فَٱطَّهَّرُوا۟ ۚ وَإِن كُنتُم مَّرْضَىٰٓ أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوْ جَآءَ أَحَدٌ مِّنكُم مِّنَ ٱلْغَآئِطِ أَوْ لَـٰمَسْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمْ تَجِدُوا۟ مَآءً فَتَيَمَّمُوا۟ صَعِيدًا طَيِّبًا فَٱمْسَحُوا۟ بِوُجُوهِكُمْ وَأَيْدِيكُم مِّنْهُ ﴾ المائدة: ٦

***"In kun kasance ba ku da lafiya, ko ɗayanku na kan tafiya ko ɗayanku ya dawo bayan gida, ko kuma kun shafi matayenku, kuma ba ku samu ruwa ba***

***sai ku nufi ƙasa wuri mai tsarki. Sai ku tafi fuskokinku daga ƙasar.”***
**Alƙur’ani 5:6**

Kuma ya zo daga cikin **Sahihil Bukhari**.

A game da ƙissar Ammar da Umar, Ammar ya ce:

"فضرب النبي صلى الله عليه وسلم يديه الأرض، ومسح وجهه وكفيه".”

***“Sai na je wurin Manzon Allah (saw), sai ya ce sai Manzon Allah (saw) ya buga hannayensa guda biyu a ƙasa, ya shafi fuskarsa da tafin hannuwansa guda biyu.”***

**Alhaidu Wal Istihada (Jinin Haila Da Na Istihada)**

Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْمَحِيضِ ۖ قُلْ هُوَ أَذًى فَٱعْتَزِلُوا۟ ٱلنِّسَآءَ فِى ٱلْمَحِيضِ ﴾البقرة: ٢٢٢

***“Suna tambaya game da haila, ka ce ita ƙazanta ce, ku nisanci mata a lokacin da suke yin haila.”*** **Alƙur’ani 2:222**

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** daga Abi Sa'idul Khudri, Mai tsira da aminci ya ce lokacin da ya wuce taron mata a ranar idin layya ko idil fitir ya ce:

(ما رأيت من ناقصات عقل ودين أذهب للب الرجل الحازم من إحداكن)

***“Ban ga mai tauyayyen hankali da Addini ba wadda take fizgar hankalin namiji (tafiyar da hankalin namiji) fiye da ɗaya daga cikinku.”***

Sai suka ce:

"وما نقصان عقلنا وديننا يا رسول الله؟"

***“Mene ne tawayarmu ta Addini ya Manzon Allah (saw)?”***

Sai ya ce:

(أليس شهادة المرأة مثل نصف شهادة الرجل؟)

***“Ashe shaidar mace bai kasance yana matsayin rabin shaidar namiji ne ba?”***

Sai suka ce:

"بلى."

***"Haka ne."***

Sai ya ce:

(فذلك من نقصان عقلها. أليس إذا حاضت لم تصل؟)

***"Wannan shi ne tawayar hankali (raunin hankali). Kuma ashe in tana haila ba ta kan bar sallah ba?"***

Ya ce:

(فذلك من نقصان دينها).

***"Wannan shi ne tawayar addininta (Raunin Addini)."***

Kuma ya zo cikin **Sahihil Bukhari** daga Aisha Allah Ya ƙara mata yarda ta ce: Faɗimatu Bintu Abi Ubaishin ta ce wa Manzon Allah (saw):

"إنى لا أطهر، أفأدع الصلاة؟"

***"Ni na kasance ba na tsarki (watau jinin Istihadha na zubo mata) ba haila ba ne, idan hailarki ta zo maki, sai ki bar sallah?"***

Sai Manzon Allah (saw) ya ce:

(لا، إنما ذلك عرق، وليس بالحيضة. فإذا أقبلت الحيضة فاتركي الصلاة، فإذا ذهب قدرها فاغسلي عنك وصلّي).

***"A'a wannan jijiya ce (watau ma'ana Shaiɗan ne yake jan mata jijiyarta jini ne ke zubar mata) ba haila ba ne. Idan hailarki ta zo maki sai kibar sallah, idan gwargwadon lokacinta ta tafi sai ki yi wanka ki yi sallah."***

## <u>Auƙatus Salati (Lokutan Sallah)</u>

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ فَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ حِينَ تُمْسُونَ وَحِينَ تُصْبِحُونَ ﴾ الروم: ١٧،

***"Saboda haka tsarkakewa ta tabbata ga Allah a lokacin da suke maraice da kuma lokacin da suke shiga safiya."*** Alƙur'ani 30:17

﴿ وَلَهُ ٱلْحَمْدُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَعَشِيًّا وَحِينَ تُظْهِرُونَ ﴾ الروم: ١٨

***"Godiya ta kasance a cikin sammai da ƙasa da kuma lokacin maraice da lokacin zawali."*** Alƙur'ani 30:18

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** daga Jabir Ɗan Abdullahi ya ce:

جابر بن عبد الله: "وكان النبي صلى الله عليه وسلم يصلي الظهر بالهاجرة، والعصر والشمس نقية، والمغرب إذا وجبت، والعشاء أحيانا، وأحيانا إذا رءاهم اجتمعوا عجل، وإذا رآوهم أبطئوا أخر، والصبح كانوا أو كان النبي صلى الله عليه وسلم يصليها بغلس."

***"Manzon Allah (saw) ya kasance yana sallar azahar a lokacin garjen rana(zafin rana) sallar la'asar, kuma rana tana nan da haskenta. Magariba kuma idan ta wajaba, Isha'i kuma wani lokaci da wani lokaci, idan ya gan su sun taru yakan gaggauta ta, idan ya ga sun yi jinkiri yakan jinkirta ta. Asubahi ko sun kasance ko kuma Manzon Allah (saw) ya kasance yakan sallace ta ne da jijjifi (da duku-duku)."***

**Shuruɗus Salati (Sharuɗɗan Sallah)**

Maɗaukaki Ya faɗa a game da sha'anin tsarki:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ وَيُحِبُّ ٱلْمُتَطَهِّرِينَ﴾ البقرة: ٢٢٢

***"Yana son masu tuba, kuma Yana son tsarkaka."*** **Alƙur'ani 2:222**

Sannan kuma Ya faɗa a cikin sha'anin kallon Kibla

﴿فَوَلِّ وَجْهَكَ شَطْرَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِۚ وَحَيْثُ مَا كُنتُمْ فَوَلُّوا۟ وُجُوهَكُمْ شَطْرَهُۥ﴾البقرة: ١٤٤

***"Suna masu fuskantar da fuskokinku gefenSa."*** **Alƙur'ani 2:144**

Kuma Ya faɗa wajen sha'anin rufe al'amurra:

﴿خُذُوا۟ زِينَتَكُمْ عِندَ كُلِّ مَسْجِدٍ﴾ الأعراف: ٣١

***"Ku riƙi adonku wajen kowane masallaci."*** **Alƙur'ani 7:31**

Kuma Ya faɗa a cikin sha'anin barin magana:

﴿وَقُومُوا۟ لِلَّهِ قَٰنِتِينَ﴾ البقرة: ٢٣٨

***"Ku tsayu domin Allah kuma masu ƙasƙantar da kai (ai kuna masu yin shiru)."*** **Alƙur'ani 2:238**

Kamar yadda ya zo a hadisin Zaidu Ɗan Arƙam. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

## Assalatu (Sallah)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَۚ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ كَانَتۡ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ كِتَٰبٗا مَّوۡقُوتٗا﴾ النساء: ١٠٣

***"Ku tsayar da sallah, lallai ta kasance a kan muminai littafi ne wanda aka sanya masa lokaci."*** **Alƙur'ani 4:103**

Ya zo a cikin Sahihil Bukhari daga Abu Hurairah (Allah Ya ƙara masa yarda) a cikin ƙissar Balaraben ƙauye;

**إذا قمت إلى الصلاة فكبر، ثم اقرأ ما تيسر معك من القرآن، ثم اركع حتى تطمئن راكعا، ثم ارفع حتى تعتدل قائما، ثم اسجد حتى تطمئن ساجدا، ثم ارفع حتى تطمئن جالسا، ثم اسجد حتى تطمئن ساجدا، ثم ارفع حتى تطمئن جالسا، ثم اسجد حتى تطمئن ساجدا، ثم افعل ذلك في صلاتك كلها).**

***"Idan ka tashi zuwa yin sallah, ka yi kabbara, sannan ka karanta abin da ya sauwaƙa na daga Kur'ani, sa'annan ka yi ruku'I har sai ka natsu kana mai yin ruku'i, sa'annan ka ɗago har sai ka daidaita kana mai natsuwa, sannan ka yi sujada har sai ka natsu kana mai yin zama. Sa'annan ka yi sujada har sai ka natsu kana mai yin sujada, sa'annan ka ɗago har sai ka nastu kana mai yin zama. Sa'annan ka aikata haka a dukkanin sallarka.***"

**Kaɗa'il Fawa'iti (Rama Sallar Da Ta Kuɓuce).**

Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ﴾ طه: ١٤

***"Ka tsayar da sallah domin tunawa da Ni."*** **Alƙur'ani 20:14**

Ya zo cikin Sahihil Bukhari daga Anas Ɗan Malik daga Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya ce:

(من نسي صلاتا فليصلها إذا ذكرها، لا كفارة لها إلا ذاك ﴿وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ﴾.

***"Duk wanda ya mance da wata sallah, to ya sallace ta a lokacin da ya tuna da ita. Ba wata kaffara a game da ita, sai dai hakan ka tsayar da sallah domin tunawa da Ni."***

## Assahawu (Sujadar Rafkanuwa)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ لَّقَدْ كَانَ لَكُمْ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ ﴾ الأحزاب: ٢١

***"Hakika, abin da ka yi mai kyau ya tabbata a gareku a wurin Manzon Allah (saw)"*** **Alƙur'ani 33:21**

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** a cikin Babis Sahawu, daga Abdullahi Ɗan Bahaira lallai shi ya ce:

"صلى لنا رسول الله صلى الله عليه وسلم ركعتين في بعض الصلوات، ثم قام فلم يجلس، فقام الناس معه، فلما قضى من صلاته ونظرنا تسليمه كبر قبل التسليم، فسجد سجدتين وهو جالس ثم سلم.

***"Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya yi sallah raka'a biyu a cikin sashin salloli, sannan ya miƙe bai zauna ba, sai mutane suka miƙe tare da shi, a lokacin da ya gama sallarsa, sai muka yi sauraren sallamewarsa, sai ya yi kabbara kafin ya yi sallama, sai ya yi sujada guda biyu alhali yana zaune, sa'annan ya yi sallama."***

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** a cikin wata ruwaya ta daban daga Abu Hurairah ya ce:

"صلى النبي صلى الله عليه وسلم ركعتين، فقيل: "قد صليت ركعتين." ثم سلم، ثم سجد سجدتين.

***"Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya yi mana sallah raka'a biyu, sai aka ce masa ka yi mana sallah raka'a biyu, sa'annan sai ya yi sallama, sa'annan ya yi sujada guda biyu."***

## Aljum'a (Sallar Jumma'a)

Ya zo cikin **Sahihil Bukhari**, Allah Madaukaki Ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نُودِىَ لِلصَّلَوٰةِ مِن يَوْمِ ٱلْجُمُعَةِ فَٱسْعَوْاْ إِلَىٰ ذِكْرِ ٱللَّهِ ﴾ الجمعة: ٩

***"Ya ku waɗanda suka yi imani idan an yi kiran salla ran Juma'a, ku tafi zuwa ga sallah."***

Daga Abu Hurairah lallai shi ya ji;

رسول الله صلى الله عليه وسلم يقول: (نحن الآخرون السابقون يوم القيامة، بيد إنهم أوتوا الكتاب من قبلنا، ثم هذا يومهم الذي فرض الله عليهم فاختلفوا فيه، فهدانا الله له، فالناس لنا فيه تبع، فاليهود غداً والنصارى بعد غد).

***"Manzon Allah (saw) yana cewa mu ne na ƙarshe mu ne na farko a ranar Alƙiyama, bayan cewar su an ba su littafi a gabaninmu, sa'annan wannan ranarsu ce wadda Allah Ya farlanta ta a garesu, sai suka yi saɓani a cikinsu, sai Allah Ya shiryar da mu da wannan ranar, mutane masu bin bayanmu a cikinsa Yahudu suka zaɓi ranar Asabar, Nasara suka zaɓi ranar lahadi."***

## Azzakatu (Zakka)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ﴾ المزمل: ٢٠

***"Ku bayar da zakka."*** **Alƙur'ani 73:20**

Ya zo cikin **Sahihil Bukhari** daga Abu Hurairah ya ce: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya ce:

(من آتاه الله مالا فلم يئد زكاته، مثل له يوم القيامة شجاعا أقرع، له زبيبتان، يطوقه يوم القيامة، ثم يأخذ بلهزمتيه – يعنى شدقيه – يطوقه يوم القيامة، يقول "أنا ما لك، أنا كنزك") ثم تلى

***"Duk wanda ya ba shi dukiya bai bayar da zakkarta ba, za a canza dukiyar ranar ƙiyama ta zama (Shajja'aƙra) maciji mai girma yana da harshe guda biyu za a yi masa sakandami da shi ranar Alƙiyama zai rinƙa cizon su Bilahazamataihi (Da ɗaburinsa guda biyu), za a yi masa sakandami da shi ranar ƙiyama zai riƙa cewa ni ne dukiyarka taskarka."***

Sai Manzon Allah (saw) ya karanta wannan ayar:

﴿ وَلَا يَحْسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَبْخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ هُوَ خَيْرًا لَّهُم ۖ بَلْ هُوَ شَرٌّ لَّهُمْ ۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُوا۟ بِهِۦ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴾ آل عمران: ١٨٠

***"Waɗanda suke yin rowa da abin da Allah Ya ba su daga cikin falalarsa, kada su yi tsammanin yin rowar nan alheri ne a garesu a'a sharri ne a garesu, da sannu za a sa musu sakandami da abin da suke yin rowar ranar Kiyama." Alƙur'ani 3:180***

Haka kuma ya zo a cikin **Sahihil Bukhari**, daga Abi Sa'idul Khudri: Lallai Manzon Allah (saw) ya ce:

(ليس فيما دون خمسة أوسق من التمر صدقة، وليس فيما دون خمس أواق صدقة، وليس فيما دون خمس ذود من الإبل صدقة).

***"Babu zakka daga cikin abin da bai kai ausaki biyar ba na dabino, babu zakka daga cikin abin da bai kai Uƙiya biyar ba, babu zakka daga cikin abin da bai kai Raƙuma biyar ba."***

## Zakatul Fitiri (Zakkar Fidda Kai)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ قَدْ أَفْلَحَ مَن تَزَكَّىٰ (١٤) وَذَكَرَ اسْمَ رَبِّهِ فَصَلَّىٰ (١٥) ﴾ الأعلى: ١٤ – ١٥

***"Haƙiƙa, ya samu babban rabo wanda ya tsarkaka (14) kuma ya ambaci sunan Ubangjinsa sannan ya yi sallah."*** **Alƙur'ani 87:14-15**

"فرض رسول الله صلى الله عليه وسلم زكاة الفطر: صاعا من تمر، أو صاعا من شعير، على العبد، والحر، والذكر، والأنثى، والصغير، والكبير، من المسلمين، وأمر بها أن تؤدى قبل خروج الناس إلى الصلاة."

***Ya zo cikin Sahihil Bukhari daga Ɗan Umar ya ce, "Manzon Allah Ya farlanta zakkar fidda kai sa'i na dabino, a kan bawan da ɗa, da namiji da mace da ƙarami da babba, daga cikinsu Musulmai, kuma ya yi umarni a bayar da ita mutane su fita zuwa Masallaci."***

## Assaum (Azumi)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا كُتِبَ عَلَيْكُمُ الصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى الَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴾ البقرة: ١٨٣

***"Ya ku waɗanda suka yi imani, an farlanta yin azumi a kanku kamar yadda aka farlanta shi a kan waɗanda suka gabace ku, ko kwa ji tsoron Allah."*** **Alƙur'ani 2:183**

Ya zo cikin **Sahihil Bukhari** daga Abu Hurairah ya ce:

"قال أبو القاسم: (صوموا لرؤيته، وأفطروا والرؤيته. فإن غم عليكم فاكملوا عدة شعبان ثلاثين).

***"Ku yi azumi domin ganin sa, idan aka rufe shi daga gareku, ku cike ƙirgar ku ta Sha'aban kwanaki talatin."***

## Hajj (Aikin Hajji)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلْبَيْتِ مَنِ ٱسْتَطَاعَ إِلَيْهِ سَبِيلًا ﴾ آل عمران: ٩٧

*"Akwai ziyartar ɗaki a kan mutane domin Allah ga wanda ya samu ikon zuwa."* **Alƙur'ani 3:97**

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** daga Abu Hurairah (Allah Ya yarda da shi) ya ce; na ji Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya ce:

(من حج لله، فلم يرفث، ولم يفسق، رجع كيوم ولدته أمه).

***"Duk wanda ya yi aikin hajji don Allah bai yi kwarkwasa ba, kuma bai yi fasiƙanci ba, ya dawo kamar yadda uwarsa ta haife shi."***

Ya zo cikin **Sahihil Bukhari**, kuma daga Ɗan Abbas;

أن النبي صلى الله عليه وسلم وقت لأهل المدينة ذا الحليفة، ولأهل الشام الجحفة، ولأهل اليمن يلملم، ولأهل النجد قرن المنازل، فهن لهن، ولمن أتى عليهن من غير أهلهن ممن كان يريد الحج، والعمرة، فمن كان دونهن فمن أهله، حتى أن أهل مكة يهللون منها

***"Lallai Manzon Allah (saw) ya sanya miƙati ga mutanen Madina shi ne zulhulaifa, kuma miƙatin mutanen Sana'a shi ne Juhufa, su kuma mutanen Yemen Yalamlam, su kuma Najad shi ne Karni Manazil. To waɗannan miƙati na waɗannan garuruwa ne, duk wanda ya zo gare su wanda yake ba yana cikinsu ba ne, ga wanda yake yin nufin yin aikin hajji ko Umra, duk wanda ya kasance ko ma bayansu , to yana cikinsu har mutanen Makka za su yi tahalili gare shi (Miƙati)."***

## Ilmul Furu'ul ɓadinati (Ilmin Furu'a Na Ɓoye.)

Maɗaukaki Ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوْبَةً نَّصُوحًا ﴾ التحريم: ٨

*"Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku tuba zuwa ga Allah tuba na gaskiya."* **Alƙur'ani 66:8**

Maɗaukaki Ya ƙara da cewa:

﴿وَذَرُوا۟ ظَـٰهِرَ ٱلْإِثْمِ وَبَاطِنَهُۥٓ﴾ الأنعام: ١٢٠

*"Ku bar aikata laifi na sarari da na ɓoye."* **Alƙur'ani 6:120**

Ya zo a cikin **Sahihil Bukhari** daga Abu Hurairah ya ce: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya ce:

(والله إنى أستغفر الله واتوب إليه فى يوم أكثر من سبعين مرة).

***"Wallahi lallai nakan nemi gafarar Allah, kuma ina zuwa gareShi a kowace rana fiye da sau saba'in."***

Ku tuba ya ku 'yan'uwana daga dukkan zunubbai na sarari da na ɓoye. Su tsarkake zukatanku daga siffofi masu halakarwa daga cikinsu akwai jiji-da-kai." Maɗaukaki Ya ce:

﴿سَأَصْرِفُ عَنْ ءَايَـٰتِيَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ﴾ الأعراف: ١٤٦

***"Da sannu zan juyar da ayoyiNa ga waɗanda suke yin girman kai a cikin ƙasa ba tare da haƙƙi ba."*** Alƙur'ani 7:146

Yana daga cikin siffofi masu halakarwa, shi ne yin fushi ta hanyar ɓarna, mai tasowa daga ƙiyayya ta ƙabilanci. Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِذْ جَعَلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْحَمِيَّةَ حَمِيَّةَ ٱلْجَـٰهِلِيَّةِ﴾ الفتح: ٢٦

***"Lokacin da waɗanda suka kafirta suka sanya ƙiyayya ta ƙabilanci a cikin zukatansu, ƙabilanci irin na jahiliyya."*** **Alƙur'ani 48:26**

Yana daga siffofi masu halakarwa, ita ce hassada. Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلَا تَتَمَنَّوْا۟ مَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بِهِۦ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ﴾ النساء: ٣٢

***"Kada ku yi burin abin da Allah Ya fifita sashenku a kan sashe da shi."***
**Alƙur'ani 4:32**

Yana daga cikin siffofi masu halakarwa, ita ce riya. Maɗaukaki Ya ce:

﴿فَوَيْلٌ لِّلْمُصَلِّينَ ۝٤ ٱلَّذِينَ هُمْ عَن صَلَاتِهِمْ سَاهُونَ ۝٥ ٱلَّذِينَ هُمْ يُرَآءُونَ﴾ الماعون: ٤ – ٦

***"Bone ya tabbata ga masu sallah (4) Su ne waɗanda suke rafkana a game da sallarsu (5) Su ne waɗanda suke yin riya."*** **Alƙur'ani 107:4-6**

Yana daga cikin siffofim masu halakarwa, rowa. Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَمَن يَبۡخَلۡ فَإِنَّمَا يَبۡخَلُ عَن نَّفۡسِهِۦ﴾ محمد: ٣٨

***"Duk wanda yake yin rowa, to, yana yi ga kansa."*** **Alƙur'ani 47:38**

Yana daga cikin siffofi masu halakarwa, shi ne son girma. Maɗaukaki Ya ce:

﴿تِلۡكَ ٱلدَّارُ ٱلۡأٓخِرَةُ نَجۡعَلُهَا لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوّٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فَسَادٗاۚ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلۡمُتَّقِينَ﴾ القصص: ٨٣

***"Wannan gidan lahira Muna sanya shi ga waɗanda ba su neman ɗaukaka a cikin ƙasa ko ɓarna, kuma ƙarshe mai kyau yana ga masu tsoron Allah."*** **Alƙur'ani 28:83**

Yana daga cikin siffofi masu halakarwa, son yawaita dukiya saboda alfahari. Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَتُحِبُّونَ ٱلۡمَالَ حُبّٗا جَمّٗا﴾ الفجر: ٢٠

***"Kuna son dukiya so irin na tarawa."*** Alƙur'ani 89

Maɗaukaki Ya ce:

﴿أَلۡهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ١ حَتَّىٰ زُرۡتُمُ ٱلۡمَقَابِرَ﴾ التكاثر: ١ – ٢

***"Alfahari da yawan dukiya da dangi ya shagaltar da ku daga ibada mai amfanin ku har sai da kuka kasance cikin ƙaburbura."*** Alƙur'ani 102:1-2

Yana daga cikin siffofi masu halakarwa shi ne mummunan zato ga Musulmai. Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱجۡتَنِبُواْ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعۡضَ ٱلظَّنِّ إِثۡمٞ﴾ الحجرات: ١٢

***"Ya ku waɗanda kuka yi imani, nisanci mafi yawa na daga zato domin sashin zato zunubi ne."*** Alƙur'ani 49:12

Ina gargaɗi a gareku ya ku 'yan'uwana da siffantuwa da siffofi masu sawa a tsira. Na farkonsu shi ne tuba, Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ﴾ النور: ٣١

***"Ku tuba zuwa ga Allah ga baki ɗayanku muminai, ko kwa samu babban rabo."*** Alƙur'ani 24:31

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne tsoron Allah Mai girma. Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخۡشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقۡهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ﴾ النور: ٥٢

*"Duk wanda ya bi Allah da ManzonSa biyayya, kuma ya ji tsoron Allah, kuma ya yi maSa ɗa'a, waɗannan su ne masu samun babban rabo."* Alƙur'ani 24:52

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne gudun duniya. Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَلَا تَمُدَّنَّ عَيۡنَيۡكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّنۡهُمۡ زَهۡرَةَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا ﴾ طه: ١٣١

*"Kada ku miƙar da idanuwanku zuwa ga abin da muka jiyar da su daɗi da shi, nau'o'i daga garesu, kamar fure na rayuwar duniya."*
**Alƙur'ani 20:131**

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne gudun duniya. Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَمَن يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسۡبُهُۥٓ ﴾ الطلاق: ٣

*"Duk wanda ya dogara ga Allah, to, lallai Shi Mai isar masa ne."*
**Alƙur'ani 65:3**

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, miƙa al'amari zuwa ga Allah. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَأُفَوِّضُ أَمۡرِيٓ إِلَى ٱللَّهِ ﴾ غافر: ٤٤

"*A cikin hikayar maganar mumini da yake cikin mutanen Fir'auna. Ina miƙa al'amarina zuwa ga Allah."* **Alƙur'ani 40:44**

Yana daga cikin sifffofi masu sawa a tsira, shi ne yarda da hukuncin Allah. Maɗaukaki Ya ce:

﴿ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ يَهۡدِ قَلۡبَهُۥ ﴾ التغابن: ١١

*"Wata musiba ba za ta samu ba sai da izinin Allah. Duk wanda ya yi imani da Allah, Allah Zai shiryar masa da zuriyyarsa."*
**Alƙur'ani 64:11**

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne tsoro. Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ﴾ آل عمران: ١٧٥

*"Ku ji tsoro Na (Ni Allah) in kun kasance muminai ne."* Alƙur'ani 3:175

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne samun rahamar Allah. Maɗaukaki Ya ce:

﴿لَا تَقْنَطُوا مِن رَّحْمَةِ اللَّهِ ۚ إِنَّ اللَّهَ يَغْفِرُ الذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُ هُوَ الْغَفُورُ الرَّحِيمُ﴾ الزمر: ٥٣

*"Kar ku yanke ƙauna ga rahamar Allah domin Allah Yana gafarta zunubai ga baki ɗayansu domin Shi Mai gafara ne kuma Mai jin-ƙai."*
Alƙur'ani 39:53

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne girmama Manzon Allah (saw). Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تَرْفَعُوا أَصْوَاتَكُمْ فَوْقَ صَوْتِ النَّبِيِّ وَلَا تَجْهَرُوا لَهُ بِالْقَوْلِ كَجَهْرِ بَعْضِكُمْ لِبَعْضٍ﴾
الحجرات: ٢

*"Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɗaukaka saututtukanku bisa sautin Annabi. Kuma kada ku bayyana sauti gare shi a magana, kamar yadda kuke bayyana magana a tsakaninku."* Alƙur'ani 49:2

Maɗaukaki Ya ce:

﴿النَّبِيُّ أَوْلَىٰ بِالْمُؤْمِنِينَ مِنْ أَنفُسِهِمْ ۖ وَأَزْوَاجُهُ أُمَّهَاتُهُمْ﴾ الأحزاب: ٦

*"Annabi shi ya fi cancanta ga muminai fiye da kawunansu, kuma matansa iyaye ne a wajensu."* Alƙur'ani 33:6

Yana daga cikin siffofi masu sawa a tsira, shi ne tausaya wa al'ummar Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi). Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَتَوَاصَوْا بِالصَّبْرِ وَتَوَاصَوْا بِالْمَرْحَمَةِ ﴿١٧﴾ أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ الْمَيْمَنَةِ ﴿١٨﴾﴾ البلد: ١٧ – ١٨

*"Suka yi wa juna wasiyya da yin haƙuri, kuma suka yi wa juna wasiyya da tausayawa(17) Waɗannan su ne ma'abota albarka."*
Alƙur'ani 90:17-18

Ya Mai gafara, Ya Mai jin-ƙai, Ka gafarta mana dukkan zunubanmu, kuma Ka yi mana rahama domin darajar Annabin rahama, ka sanya mu daga cikin mutanen albarka. A nan ne littafin **Umadatul Muta'abbidina Wal Mutaharrifina** ya zo ƙarshe.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangiji Talikai. Mafificin salati ga shugabanmu, Muhammad da alayensa da sahabbansa ga baki ɗaya. Kuma yardar Allah ta tabbata ga shugabannin tabi'ai da malamai masu yin aiki da shugabannin nan guda huɗu masu yin Ijtihadi da waɗanda suka rataye da su har zuwa ranar sakamako.

Allah Ka yi wa al'ummar Annabi Muhammadu Salati ga baki ɗayansu. Amin.